A MAFARKI NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah almustapha

Daga alkalamin✍✍Fa'eeh Bungudu

BISIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

Wannan shine littafina nafarko Dana fara wallafawa Allah Ina rukonka daka bani damar kamalashi lafiya kamar yanda nafarashi lafiya

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of Perfect Writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S *

Pen is mightier than the sword*

Dedicated to my lovely sis Laila Almustapha Murai

Yaa Allah ina rokon ka kabani damar rubuta abunda Al umma zasu yi aiki dashi kuma su Amfana, kabani ikon rubuta shi cikin koshin lafiya na kammala shi lafiya

Warning!!!Banyarda wani ko wata su juyamin labarina ba ta kowace siga batare batare da an nemi izini na ba wannan dokace kuma duk wanda yayi ban yafe ba wannan labari kirkira ne bada gaske bane duk wanda yayi dai dai da labarinsa to yayi hakuri akasine. Daga cikin abund littafi na ya kunsa

Tausayi
zumunci *zazzafar soyayya*
sarauta *cin amana*
ta,addanci

DA SUNAN ALLAH MAI RAHMA MAIJINKAI

EPISODE 1

FREE PAGE1

Natsatssiyar budurwa ce ke tafiya anatse bata kallon komai face inda take sanya kafafunta, tayi nisa acikin tafiyarta kenan ta tsinkayi muryar wata budurwa na kwala kiran Halee! Halee! da jin wannan murya ta budurwar dake kwala kiran Sunan halee ko ba,a fada mata ba tasan khady ce tsayuwar ta da minti biyu sai ga khady ta iso inda take atsaye.

Isowar khady keda wuya ta furta haba Halee kinsan bakya da issashiyar lafiya ya za,ayi kije Aiken baba ta ta maimakon ki fada mata gaskiyar cewa baki da lafiya nasan zata k'yaleki ni sai intafi kinga ko yanzu gudo wa nayi bayan bayan tashiga bandaki,nasan da kin sanar mata da ni sai intafi koh haka ke da dadi ga uwar rana gashi bakya da lafiya,har taga ma mitar ta kyakkyawar budurwar nan da aka kira da halee bata tanka mata ba.. Daga ni dai yarinyar miskila ce😄 chan bayan kamar minti biyu haka ta cigaba da tafiyar ta kamar bataji abunda khady ke fada ba duk da kuwa tana jinta rass kuma tasan tabbas ko ba,a fada ba khady gudowa tayi tabiyo ta.

Da khady taga alamar ba tsayawa zatayi tabata kudin aikar ba na baaba tsaibe,kuma taga alamar yan miskillancin sun motsa dole haka tabita suka cigaba da tafiya atare har suka iso kantin da zasu yi siyayyar ta kayan miya

Sallama sukayi atare amsa musu sallamar tsohon dake tsaye akan tebir na kayan miyan yayi cikin sakin fuska Dan dama baba tsohon yasan su musamman halee ya saba da ita sosai tunda kusan kullum sai an aike ta yin cefane da sauran aikace aikacen akasuwa.

Washe baki tsohon yayi yana furta a,ah Haleematu sadiya ce kayataccen murmushinta tasaki jin ya ambaci cikakken sunanta Wanda mutun daya ne ke kiranta da wannan Sunan sai kuma mutun daya Wanda bata San ko wanene shi agareta ba Amma tabbas aka ambaci cikakken sunanta tana jin wani iri ajikinta

Muryar baba tsohon ce tadawo da hankalinta agaresa yana furta na nawa za,a bada cikin Dan murmushi ta furta baba tsohon ina wuni lafiya,ita ma halee haka amsa musu yayi duka yana dariyar halee aransa najin ga tambayar da yayi mata ga abunda ta furta masa shiyasa yarinyar tashiga ransa Dan akwai tarbiya gata kamila anatse kara mai maitawa yayi" na nawa za,a bada"cikin Dan yin kasa da kai ta furta acikin zazzakar muryar kamar ana busa sarewa ko algaitu gata da sanyi Wanda intana magana zakaji har tsikar jikin ka natashi na Dari uku da ta furta ne yasanya ni dawo wa daga sumar tsayen danayi tun lokacin da ta buda baki ta gaisar da tsohon.

Toh baba tsohon ya furta aleda ya saka musu baka ya mika musu sallama sukayi masa sukayi wucewar su, suna tafiya khady na zuba uban surutu alokacin da ita kuma Halee take ta zullumin komawar ta gida Dan tasan gamuwar su da Babah Asabe bamai kyau bace dan tasan sai ta mata fadan dadewar ta duk da dama ta saba,Amma yau da yakasance batajin dadin jikinta tana fama da matsanancin ciwon kai sai take jin shakkun yadda zata iske gidan,tana cikin wannan tunani sai ga hawaye shar😢 a idanunta gwanin tausayi Khady data lura da yanayin da take ciki ne duk da ba bakonta ganinta hakan Dan danan hankalinta yatashi Dan tana mugun son halee kamar jinin jikinta,da tausayinta cikin tausayinta ta furta haba Halee meyafu kuma, dan Allah kitsaida hawayen nan suna Sosa mun rai kuma kinga kan hanya muke kiyi hakuri nasan damuwar da kike ciki bata wuce sanin ko ke wacece bah da damuwar baabah ta 'baaba Asabe' kiyi hakuri in sha Allah komai zai zamo tarihi Halee nah hawayenta ta share mata wayenda ke tsiyaya a I danunta tana girgiza mata kai alamar ta tsayar dasu da kyar ta tsayar da hawayen ta ganin damuwa kwance akan fuskar Yar uwarta!tafiya suka cigaba da yi kowa da abun da yake sakawa aransa,babu Wanda yakara furta uffan har suka iso gidan,

Dan madaidaicin gidane suka tsaya kafin su shiga cikin dar dar musamman Halee gidane dai dai na talaka mai rufin asiri ginin bulo da filista zauren gidan suka tsaya suna shawarar Wanda zai fara shiga domin gudun abunda zasu tarar dakyar dai dukansu sukayi shahadar shiga da sallama abakunan su

Sallamar su ta ta katse ganin Baba Asabe na mitar rashin dawowar Halee akan lokaci da kuma fitar Khady bada saninta ba,

A hankali halee take ta durkusa gurin Yar matashiyar matar da bazata wuce shekara talatin da uku ba a duniya!Baba Asabe kenan wadda Sunan ta yake Lauratu amma mafi yawan mutane suna kiranta da Asabe saboda masifarta da ankira Baba Asabe za,a San itace Dan Sunan ta kaf ya bace.

Cikin sanyin muryarta da yazame mata jiki tace baaba ga kayan miyar kinga na dad'e koh wallahi Baba tsohon ne mun tarar da layi agurin sh...uwar hararar da baba Asabe ke sakar mata ce tasan ya ta yin shiru badan ta shiryawa hakan ba,dama kanta adone yake dan bata son kallon cikin idanun manyanta musamman ma na Baba Asabe ....taci karo da hararar da take sakar mata,bata ida ganin tsawon hararar ba ta kara done kanta kasa cikin tsoron abun da zai biyo baya..

Kiran Sunan Allah take yi a zuciyarta Dan tasan yau tata takare sai ta sha rankwashi akai da gori kala kala da zagin da bata so zuciyarta ce taji tsinke tausayin kanta da kanta yakamata.

Bata ida gama tunaninta ba ta tsinkayi muryar Baba Asabe nama khady fadan binta da takeyi abaya inta aiketa duk da kullum haka suke muddin Baba asabe ta aiki Halee to tabbas in Khady tadawo sai ta bita sundawo tare koda kuwa dawowar su daga makaranta ne aka tura Haleen sai ta yi sand'a ta bita...

Baba asabe ce take furta wallahi Hadiza ki shiga taitayinki Dan ubanki na fahimci bakya game zancen da nake maki ace ke kullin sai kinsaka ni yakar baki ehh~bakinta har kunfa yakeyi saboda masifar da ke cinta dama Baba Aabe masifaffiya ce ta bugawa ajarida.

Wai nikam nace dama haka masu suna Lauratu suke ne??😂

Hankalin khady (Hadiza) yayi dubun tashi bata kanta takeyi ba Dan tasan karshen masifar kan halee zai kare. Ahankali ta furta innata kiyi hakuri ke dallah rufe mun baki sha shar banza kawai ana miki gata kina botsarewa,inji cewar Baba Asabe , aikullun haka kike cewa ayi hakuri tau Dan ubanki ki kara kiga yadda yadda zanyi da suyar namanki agidan nan takai karshen maganar tana ban kamata harara

Kiwuce ki cire uniform dinki kizo ki Debi ruwan zafi gasu chan nadora miki amadafa.

Toh Khady ta furta cikin tutse bakinta mai makon ta wuce sai ta tsaya taga yadda za,a kwashe da Halee tana jin tsoron tashin ciwon Yar uwarta Wanda take ganin hard a damuwa kesanya tashin sa,tana mugun son ta da tausayinta, gashi yanzu haka tana fama da kan daya zame mata al ada dan duk yatashi tana wahala sosai wasu lokuttan har suma takeyi inyatashi saboda yadda take samun high temperature.

Bayan Baba Asabe tajuyo kan Halee wadda ke durkushe har yanzu bata daga duk da yadda rana ke gasata ga sumintin yadau zafi hawaye take zubarwa na tsoron masifar ta Baba Asabe Dan tasan kanta abun zai dawo ya kare ga ciwon kanta da ke

ta kara hawa jikinta sai kara dumewa yake yi da zafi..hawayene shar suka zubo a I don ta suna sauka abisa kyakkyawar fuskarta.

Mu hadu a next page domin jinya zata kaya tsakanin Halee da Baba Asabe

Me kuke tunani akan Halee??

Kucigaba da bibiyata domin warware muku duk wani tunanin ku.✌✌

Yawan like dinku da comment shi zai tabbatar mun da kuna bibiyata,in har naga comments da like da yawa zan kara muku yawan pages.

Nasan zaku ga chanji na sunan Baba tsaibe da yakoma Asabe ga wadanda suka fara karantawa babu editing

□A MAFARKI NASANTA□

in my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga alkalamin✍✍fa'eeh Bungudu

*PERFECT ESSENTIAL

WRITER'S ASSOCIATION

□P.E.W.A□

home of perfect writer's together we stand □

ESSENTIAL WRITER'S *

Penis mightier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE2&3

Typing□□□

Gefen hijab dinta tasanya ta share hawayenta muryar Baba Asabe ce tadawo da ita daga maganar zucin da takeyi

Da masifa take furta munafuka algunguma wallahi bari kiji duk ranar da kika kara bari Hadiza tabiki in na aike ki wallahi ko na lahira sai yafi ki jin dadi sha sha marar asali kawai tsintacciya yar gaba da fatiha wadannan kalmomi da Baba Asabe take yawan furta mata suna daga mata hankali sosai fiye da zaton mai tunani duk ranar da Baba Asabe ta furta su agareta sai tasha kukan ta ita kadai alokacin kuwa Khady ce kawai ke iya lallashinta.

Har tunani take yi anya kuwa ita badaga sama tafado ba,wasu lokuttan kuma takanyi tunani kodai ita din yar gaba da fatiha ce kamar yadda Baba Asabe ke yawan furta mata,tunani barkatai dai ke shiga akanta aduk lokacin da ta tunano da kalmomin masu muni agareta sai dai kawai takori shaidan da Addu,ar neman tsari daga sharrin zuciya.

Dan tun Tashinta gidan wayennan kalmomin su suka bayyanar mata da ita din wacece agidan Baba Adee tun alokacin da ta fara mallakar hankalinta ta fahimci cewa ita din ba jinin Baba Adee bace da Baba Asabe sai dai duk da cewa ta fahimci komai akai bata taba gigin tambayar dayan su asalinta ba dan gudun maganar da zataji wadda zata iya saka ta rasa rayuwar ta wadda ayanzu take maleji da ita,Barema koda zata tambayi Baba Asabe baza ta iya sanar mata da komai ba domin koda Baba Adee ya kawo Halee gidan bai sanar da ita komai akanta ba,yadai sanar mata ya tsinceta ne akan hanyar shi takomawa gida tsakin gusau da furfuri dake jihar zamfara wannan kenan.

Cigaba....

Maganar da Baba Asabe ce keyi tadawo da ita daga dogon tunanin da tashiga na munanan kalmomin da Baba Asabe ta furta agareta Baba Asabe ce ke furta sakarya munafuka ana magana kina sunne kai kamar takwarai sha sha sha ballagaza kuma wallahi kinji narantse na kara aikarki kika dade sai kinci ubanki, mtssw taja uban tsaki tawuce warta fuuuu.

Kamar ance tajuya tahango Khady tsaye itama tana tsiya yar da hawaye kamar yadda itama Halee take zubar da nata hawayen

Yau nina naga ikon Allah inji cewar Baba Asabe wai ke Hadiza Uban me kika hada da yarinyar nan ne ehhh sha sha wuce kiban guri ko in tattakaki anan mtsww tana sanya hannu ta warci ledan kayan miyar ta shigewar ta madafa tana mitar ita kadai,Ta dora sanwar rana dan dama duka aikin gidan Halee ce keyi toh yau ma anyi lattin dora girkin ne kuma tasan Baba Adee yana nan dawowa bada jimawa ba shiyasanya ta kyaleta bata tilas ta mata yin girkin ba.

Alkalamin✍✍

□□fa'eeh bungudu□

A MAFARKI NASANTA

Bayan shigewar Baba Asabe a kitchen Khady tayi sauri ta matso inda Halee ke durkushe tayi zukunnin rakumi cikin uwar ranar da ta bude tana ta faman zubda hawaye ga hannunta dafe da kanta dan tun lokacinda Baba Asabe ta zage ta da kalmar dan ubanta kanta yakara sarawa bayan jin wadanchan kalmomin na farkon Baba Asabe take yawan furta mata na marar asali tsintacciya bayansu babu abunda ke kona mata rai kamar azagi mahaifinta da mahaifiyar wanda ko da za,a yankata bazata iya cewa ga yadda kamanninsu yake ba ko tana da iyayen oho?Amma duk aka zagesu tana jin bakin ciki marar misaltuwa wanda bazai fadu ba,tana sonsu duk da bata taba ganinsu ba ko jin labarinsu.

Dafa kafadanta da Khady tayi ne yadawo da ita daga dogon tunaninta dakuma kara gudun ruwan hawayenta wanda zuwa yanzu kukanta yafara karfi har da shessheka dago lulu eyes din ta tayi wayenda suke dauke da zara zaran eyelashes masu tsarin kyau masu dauke da kwarjini farare tass dasu kwayar idonta har wani walkiya take yi na farin cikin idanun nata,A yanzu kuwa sunkoma jajaye saboda damuwa da ciwon kan datakefama dashi ga kuma kukan da tafara yi.

Zararan eye lashes nata sunkara curewa guri daya saboda ruwan hawen da suka jika su,Khady kuwa tunda suka hada idanu da Halee taji guiwoyin ta sun sage dan kuzarin datake dashi taji ya gushe,tausayi Babbar kawar tata kuma wadda tazame mata yar uwa wadda takejinta kamar tsoka da jininta.

Ahankali ta furta Halee! kanta ta kara dagowa akaro na biyu bayan mayar dashi kasa da tayi tana tsiyayar hawaye da idanu Khady tama alamar ta tashi suje daki tunda tasan yanzu bata bukatar wani dogon zance saboda ciwon kanta gashi taji jikinta yakara daukar zafi sannan in Baba Asabe ta iskosu wata masifar ce sabuwa wadda kuma take tunani ayanzu kwakwalwar Halee bazata iya dauka ba,Hannunta ta mikamata Halee bata ce komai ba takama hannun Khady ga gamn ta rike.

Ahankalin suke takawa kowa da tunanin da yake yi azuciyarsa harsuka isa dakin da yake chan gefe mallakinsu su biyu

Baba Asabe da duk taga komai .....✍✍✍

A MAFARKI NASANTA

daga Alkalamin✍✍

fa'eeh bungudu

please like share & comment

A MAFARKI NASANTA

in my dream i know her

By

Pha'eezah almustapha

Daga Alkalamin ✍✍

fa'eeh bungudu

Dedicated to my lovely sis laila Almustapha murai

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of perfect Writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S *

pen is migthier than the sword*

EPISODE 1

FREE PAGE4

Typing

Bata ce musu kala ba har suka shige dakin tsaki taja mtssw tana furta yarinya sai kace mayya da shegen taurin ran tsiya ace duk wahalar da nake gana mata bata sanya ta guduwa daga gidan nan ba mtssw takara jan wani tsakin tana furta mayya kawai tun randa tazo gidan nan Baban Hadiza samun shi ya ragu gashi komai shi shalelensa dan naman miyar ma da muke samu da yawa ya ragu ada daga ni sai hadizata yanzu kuwa takai karshen maganar cikin jan dogon tsaki wanda Yafi nadazu tayi shigewar ta daki tana cigaba da masifarta ita kadai

Nikam nace Baba Asabe shi naman miyar halan dai bakisan sauyin ubangiji ba 😇

fa'eeh bungudu

Halee da Khady shigar su daki keda wuya dukkaninsu suka samu guri suka zauna kowa rai ba dadi musamman khady wadda take jin haushin abun da mahaifiyarta keyiwa Haleen.

Matsowa Khady tayi inda Halee ke shingide gefen katifarsu data sha gyara kamar gadon Amare

Zama kusa da ita tayi tare da kamo Hannunta daya ta furta cikin tausayin Haleen kiyi hakuri kibarwa Allah komai ninasan Babata bata taba kin kiba har cikin ranta kawai dai shaidan ne ke zugata da kuma sharrin wani yanki na zuciyarta dan yin shiru tayi kafin tacigaba da magana Halee! dago kyakkyawar fuskarta tayi ta kalli Khady ....banason Son ina ganin damuwa abisa kyakkaywar fuskar nan taki,Mai sanya samarin zamfara hadarin titi☺

Tunda Khady tafara magana bata tanka mata ba amma maganar ta takarshe sai da tasaka ta yin wani kayataccen murmushi wanda har sai da two side dimple dinta dana kasan gemun ta suka lob'a gwanin burgewa.

Itama Khady Murmushinta tasaki mai kyau wanda har cikin ranta yake nuna tsantsar farin cikinta naganin murmushin yar uwar tata Halee wanda yake ba kullum take yinsa ba duk da fuskarta irin ma,abociyar yalwar murmushi ce kamar ta junaid Abban sojoji😄Amma damuwa ta hana ta bayyanar da asalin annurin Fuskarta.

Fa'eeh Bungudu

Dama Khady tasan tabbas ta furta mata irin wannan kalmar sai ta yi murmushi,ita abunda ke sakata yin murmushin gani take bawani kyau ne da ita ba kamar yadda Khady ke yawan fada mata da kuma classmate nasu,saboda ba kullum take samun damar duba fuskar ta ta ba Amadubi dan cewa take bashine agabanta ba,ita gani take kyawon da duk ake fada tana dashi nabanza ne saboda kyawu ba asali baida amafani acewarta,ita yanzu sanin asalinta ya fiye mata kyawun komai agareta a cikin duniyar nan.

So dayawa in Khady ta matsamata da cewar tana da kyau na fitar hankali takan cemata "kyawu ba asali babu amfani" kuma da ta fadi wannan kalmar sai ta fashe da kuka Khady tayi ta aikin lallashinta Yanzu ma khady bata matsa mata da wata maganar ba dan gudun karamata damuwa.....

Wash hannu nah wallahi typing wahala

kuyi manage da wannan ba yawa

Mu hadu a next page domin kara warware muku matsayin Halee agidan Baba Adee

Kuyi hakuri da sauyin dakuka gani

Masu comment da like ina godiya□□

khadseen□

Halimatu B Auki□

□fa'eeh bungudu□

Pls like share & comment

□A MAFARKI NASANTA□

in my dream i know her

By

Pha'eezah almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□fa'eeh bungudu□

Dedicated to my lovely sis laila Almustapha murai□

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

□P.E.W.A□

Home of perfect Writer's together we stand □

ESSENTIAL WRITER'S

*

Penis mightier than the sword *

Proud of my first my novel□

JIN JINA TA□□ MUSAMMAN ZUWA GA BABBAR KUNGIYAR MU

□P.E.W.A□

Ina alfahari daku musamman uwayen gidana□

MHIZ BAREEMAH (marubuciyar yan biyu macizai ne) the twins snake□□

OUM AMJAD (marubuciyar yan biyu)the twins□

EPISODE1

FREE PAGE5

TYPING□□□

Kawar da shirun nasu tayi ta hangar ta hanyar furtawa Halee kitashi ki watsa ruwa bari indebo muna ruwan zafi tana gama fadar haka ta cire hijabin uniform dinta tayi waje.

Bayan fitar ta daga dakin Halee ta tashi daga kishingid'en datake tacire hijabinta ta nad'esa Sa tasanya acikin acikin sip dinsu wadda Khady bata ya mutsa ba,sannan ta jawo zanen da take wanka dashi tayi tadaura bayan ta cire kayan jikinta tasanya acikin basket na Tara datti Dan karamin hijabinta Wanda take wanka dashi tasanya ta cigaba da gyara kayan da duk suke ahargitse acikin sip dintasu Wanda Khady ce ta ya mutsa su dazu da zataje makaranta..

Tana cikin gyaran sip d'in ne sai ga khady tadawo da ruwan acikin small bucket bayan ta amsa mata sallama ne

Ta Tsinkayi Muryar Khady Tana Furta nidai Halee kibar gyara kayan nan kinga baki da lafiya duk da naga yau jikin naki da sauk'i nazata sai munje asibiti ~takai karshen maganar fuskarta da alamar damuwa

Hararar wasa wasa Halee tasakar mata tana idasa lankafe hijab daya daya rage saura ta gama,Ahankali ta juyo ta dauki ruwan zafin da Khady ta ajiye mata tare da furtawa Khady karki damu Sisi nah nafara zama strong women tayi maganar ne cikin sanyin muryarta da yazame mata jiki takai karshen maganar tana sakar mata kayataccen murmushinta mai Sa maza□ had'ari atiti😎

---------- □fa'eeh bungudu□

Itama Khady murmushin ta mayar mata dashi bata k'ara cewa komai ba ta kama hangar da zata sadata da d'an madaidaicin toilet dinsu dake cikin dakin har ta kusa isa ta tsinkayi muryar Khady na furta "Halee kibari inzo in had'a miki ruwan tunda naga baki da karfin jiki tafiyar taki takara. Zama slowly"

Ko ayanzun ma murmushin Halee tasakar mata Wanda har kyawawan hakora ranta farare Tass suka bayyana gwanin burgewa,itama Khady Murmushin tayi tana furta ohh! Yau su Anty Halee yan sarautar sun motsa kenan girgiza kanta tayi tana kara sakin murmushi na mamakin halin Yar uwarta na rashin son yin magana.

Itama cire uniform din nata tayi tadaura zanen da wankanta tayafa katon mayafi tana ficewa daga dakin

---

Tun akofar dakin nasu tafara magana cikin farin ciki take furtawa Baba Adee sannu da zuwa saboda tajiyo muryar shi lokacin suna magana da Khady.

A bangaren Halee kuwa tana shiga toilet din ta fara gudanar da wankanta cikin natsuwarta da tazame mata jiki duk da yadda ranta yake ba dadi....

"Dady sannu da zuwa" ya hanya?Muryar Khady ce ta ratsa tsakar gidan nasu har zuwa barandar da wannan dattijo yake azaune.

Murmushi wannan dattijon yi har takara so inda yake dattijon kirki Wanda sunan shi yake Abdul rashid Amma anfi saninsa da Baba Adee Wanda akalla zai kai shekara hamsin aduniya.

(wannan suna Khady ce tafara sanya masa shi alokacin tana karama bata iya fadin Dady kamar yadda Halee ke fadi sai ta mayar dashi Adee Wanda ganin haka yasa itama Halee ta mayar dashi Adee jin Yar uwar ta na kiransa haka)

Sai kuma sunan yabisa har na waje suka kara masa da Baba wannan kenan..

Har ta durkusa agabansa Murmushi ne kwance akan fuskar Sa ganin yadda ta turo baki gaba nak'in amsa mata sannu da zuwan da ta masa,Baba Asabe ce dake tahowa da amadaidaicin kofin silver domin kawo masa yasha ta furta kekam dai Hadiza meyake damunki ehhh!daga dawowar Sa sai fara turar masa baki kamar wadda aka daka tana magana tana tsiyaya masa ruwa akaramin cup shima na silver mai kyau

Kurb'a ruwan da Baba Asabe ta mikamasa kurba guda yace rabu da ita kinji dije,aiko ida rufe bakinsa baiyi ba Khady takara turekke bakin nan gaba....

Dariya yayi wadda take fitar da suffar shi ta magidantan kirki yace ke koh:khadija Dan Ankiraki da dije ai bawani abu bane suna ne mai dadi koh! yakai karshen maganar yana Dan yin murmushi,ganin tayi shiru batace komai ba,yace nasan fushin da like yi nafarko ban karba miki sannu da zuwan ki ba na biyu na kiraki da sunan tsofaffi yakai karshen maganar yasa cikin yin Yar karamar dariya wadda har far in hakorinsa na Makkah ya bayyana sannan yacigaba da magana kin san Khadija nace kibar yimin sannu da zuwa tundaga nesa shiyasa na kyaleki na biyu kuma ayi hakuri laifi nane shalelen Laure....yana murmushi

Baba Asabe dake gefe itama murmushinta yi,Itama Khady murmushin ta saki jin ankira ta da shalelen Babarta cikin dariya ta furta hard a ta dadynta dukan su dariya suka sanya.

Maganar Baba Adee ce ta dakatar da da riyar su Wanda maganar bata yima Baba Asabe dadi har fuskanta ya nuna,inda yake furta "yake cewa ina Shalele ".....

Yawan likes dinku da comment shahizai Sa Ku samu page biyu arana

*A mafarki nasanta *

Daga Alkalamin

fa'eeh bungudu

Mu hadu next page✌✌

Dan jin cigaban maganar ta Baba Adee

Dakuma jin Amsar da Khady zata bashi, nasan kun matsu kuji asalin Halee

---

Kucigaba da bibiyata ahankali zan warware muku duk wani sashe na littafina....

WASAN YANZU AKA FARA

Kuyi hakuri ba editing domin dazu sai da nagama wahalar typing gaba daya ya goge.

Pls like share and comment.

A MAFARKI

NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh Bg

Dedicated to my lovely sis Laila Almustapha

Murai

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S*

Pen is mightier than the sword*

EPISODE1

FREE PAGE6

dama na fada muku page dinku na friday sai yau to ga alkawarinku nan na cika

TYPING

Khady cikin murmushi ta furta tana daki na barota ta shiga wanka kai yad'a ga mata alamar gamsuwa,firarsa ya cigaba da yi da yarsa cikin lumana yana tambayar ta ya karatunsu na islamiyya da na boko tana bashi amsa da alhamdullillah, masha Allah sai akara dagewa kinji Ya furta cikin jin dadi,kai Khady ta d'aga masa tana furta in sha Allah Anan take sanar masa da Halee bata je ba yau,Assha!Assha! meya hanata zuwa injin dai ba ciwon kanne nata yatashi ba...Yakai karshen maganar cikin nuna tausayinta kara furta wa Khady yayi tun yaushe yatashi ?tun dazu da asuba,tashi ki kira mun ita in ta fito tau tace sannan ta tashi ta wuce dakin nasu domin kiran Halee.

Fa'eeh Bg

Kanshi ya juyo dashi gefen da Baba Asabe take Yana furta Laure shine baki gayamun ba tunda nashigo,Baba Asabe da tun da tun dazu take cike da jin haushin shi nakiran Halee da yayi da shalelensa duk da bayanzu ne tafara jin yana kiranta haka ba tun tana karama,Dan bata son yana nuna wa Halee soyayya fiye da Khady duk da yana kamantawa Acewar ta yar tsintuwa ba "ya bace,dakyar ta bud'a bakinta tabashi amsa saboda haushi ga tsoron ta nuna mishi taji zafin maganar da yayi mata

dakuma Kiran Halee Shalelensa,Haba Baban Hadiza yanzu fa ka dawo,ruwa kadai kasha ni dama yanzu nake niyyar sanar maka takai karshen maganar cikin danne wani kololon bakin ciki da yataso mata,niyya ya maimata abayyane yana gyad'a kansa cikin alhini ya nagayamiki duk randa ciwon shalelena yatashi ki rika kirana awaya in ba nanan sai inturo nurse kamal ya duba ta Amma da yake ita ba Khadija bace sai kike yin biriss da lafiyarta,ace kullum sai na maimaita miki maganar cewa ita din amana ce ta Allah agare mu,Amma na fahimci bakya ganewa kuma na fahimci har yanzu na baki dauke ta amatsayin yarki ba dan ina da tabbacin da Khadija ce keda wannan lalura haka da kin kasance mai kulawa nasan da gudu zaki sanar mini in ya tashi amma dan rashin Amma ni kike shaida ma wai yanzu kike da niyyar sanar mini,nasan kuma da khadijan ce da tun da asuban nan kinkira kinsanar mini,nasan kin sani keda kanki kika karbi amanar yainyar nan ba wani ba dan haka kiji tsoron Allah ki kara riketa da Amana.

Duk wannan maganar dayake kanta nakasa dan tasan yau ta dan ballo wani yanki na fad'ansa,ita inbanda tasan duk randa Halee bataje makaranta ba ciwon ta yatashi da bazata san bata da lafiya ba,tunda kosu yaran sun sani ko sungayamata babu abunda take iya yi face ma tabi Haleen da zagi ko gwacine,batun yau ba Halee na rashin lafiya Amma Baba Asabe bata kiransa tasanar masa in baya gida da yake ba,a garin yake aiki ba in yatafi yana kwana biyar ko sati kafin yadawo shiyasa wasu lokuttan har ta gama jinyarta bai sani ba.

Maganar shi tadawo da ita daga maganar zucin da takeyi....Yana furta wallahi Laure ki guji b'acin raina izuwa wannan lokaci ransa yakara baci ya hasala jin saoboda shirun da tamasa,Cikin danyin kasa da kai Baba Asabe ta furta Baban Hadiza Allah yabaka Hakuri,bai tanka mata ba sai ma cigaba da maganar sa da yayi yana furta baki san girman Amana ba Laure ba shiyasa Amma zanyi maganinkin dan bana son kikawo mini shirme cikin gidana dan haka kikiyayi b'acin raina karki kai ni baango .....

Sallamar su Halee ce ta dakarar shi daga sake yin magana,Assalamu alaikun dady nah

Halee ce ke ke maganar da murmushi kwance abisa kyakkyawar fuskarta kyau da annuri wanda ke nuna farin cikinta na dawowarsa gidan,cikin shigarta ta wata doguwar riga yadi pink mai taushi da d'an madaidaicin hijab dinta fari wanda yakara haska farar fatar ta wanda har kashe ido take yi kamar zinari acikin azurfa,inka kalle ta kyakkyawar fuskarnan sai sheki take yi kamar wankakken gold gwanin burgewa kai bazaka ce tana da daamuwa....

Fa'eeh Bg

Wslm Halimatu Sadiya mai tagwayen suna kuma shalelena inji cewar Baba Adee cikin farincikin ganin ta yake furucin murmushi kwance afuskar shi shima.

"sannu da dawowa ya hanya" ? inji Halee tana kara sakin kayataccen murmushinta jin yakira cikakken sunanta wanda kamar ga bakinsa aka rada sa,kuma tana jin dadi yakira ta da hakan,Alhmdllh lafiya qlau hanya yakarfin jikin ki ance baki ji dad'i ba, cewar Baba Adee,ehhh naji sauki alhmdllh ai har nasha magani na yanzu kafin in fito,d'anyin shiru tayi tuna yadda tasha maganin wanda sai da Khady tace zata hada ta da dady ne sannan tasha shi dakyar kamar tayi kuka dan ta tsani magani ko allura,Dan kallon khady tayi wadda itama ita take kallo jin yadda take bayani kamar

ba sai da ta tilasta mata ba,kawar dakanta tayi daga kallon Khady tana maida hankalinta ga Baba Adee wanda ke furta masha Allah haka ake so ai har ina maganar akira likita ko muje asibiti

Murmushi tayi tana yin kasa da kanta wanda har kyawawan hakoranta farare tass suka bayyana gwanin burgewa tace Naji sauki dady kuma sosai,murmushi ya karayi yana furta to madalla Allah yakara Afuwa,Ameen Halee da Khady suka amsa, yakaratun su da makaranta ya tambayeta kaamar yadda yatambayi Khady,Alhmdllh ta furta,kara furta mata yayi ya gidan kuma dan shiru tayi sai kuma cikin yanayin sanyinta ta furta lafiya lau kai yajinjina kawai batare da yakara furta komai,Baba Asabe ce da tagama girkinta na jallof din taliya da taji alayyahu,Ahankali tasauke wanda ta zubowa Baba Adee agaban sa cikin wani filet na tangaram irin na da mai kyau tana furta Baba Hadiza ga abincinka nan tayi maganar fuskar ta sai sa sai sa ba fushi ba murmushi dan bataso tana wani abu yakara hawa,wadda tun lokacin da ta samu su Khady sukazo gurin ta bar wurin tare da kayansa ta kai masa daki sannan ta wuce kitchen.

Bayan ta aje abincin ne ta koma ta debo masa ruwa na randa masu sanyi acikin jug mai kyau na kofin silver sannann tazauna,bai cemata komai ba yajawo filet din da ta aje agabansa yadora gabansu Halee yana furta kuje ku wanko hannayenku kuyi bisimllah muci abinci koh cikin farin ciki suka amsa masa da tau,Baba Asabe ce tayi karaf tana da niyar da katar dasu tana furta gana su chan akitchen na zuba musu suje su dauka,hannu kawai yadaga mata yana kara mata maimaita musu da suje su wanke hannayensu,wanke hannayen su keda wuya suka fara cin abincin tare dashi bayan duk sunyi bisimillah abayyane yaji su suna ci da hannu shi da spoon,cikin natsuwa suke cin abincin su tare dashi gwanin burgewa wanda dagani sun saba ne,Baba Asabe bata kara furta komai ba harsuka gama cin abincin su suka sha ruwan randa masu sanyi wayenda takawo masa,bayan sun wanke hannayensu suka furta alhmdllh atare wanda dama dab'i ar da ya sabar musu da itace,zasu yi basmala atare hamdala atare komai suna yinsa atare ne sun tashi da soyayyar junansu tun suna kana na.

Fa'eeh Bg

Masha Allah ya furta to tunda duk kun koshi sai aje afara shirin zuwa makarantar islamiyya koh,ehh suka amsa suna mikewa suka wuce dakin su cikin natsuwa ..

Shima tashi yayi ya wucewarsa nasa dakin domin watsa ruwa,Baba Asabe bata iya cemasa komai ba har ya yi shigewar sa dan tasan ta ba'llo ruwa,tasan bazai jirata ta hada masa ruwan wankan ba duk da shi ba mutum ne mai riko ba.

Abunda yafaru kafin fitar Khady gidan shine bayan tadawo makaanta

Cikin sallama ta shiga madai daicin gidan dai dai rufin asiri gida ne mai dauke da daki uku biyu suna kallon juna sai daya achan gefe wanda yake shine nasu halee biyun kuma nasu Baba Adee da Baba Asabe,sai toilet daya natsakar gida, da kichen shima chan gefe farkon shigowa gidan ga tsakar gidan ma da wali gidan masha Allah ko ina ka duba kwal kwal yaji suminti,inda ta iske Baba Asabe tsakar gidan tana fifita da yake lokacin zafi ne,Sallamar ta Baba Asabe ta amsa mata da murmushi ta na furta tagaban goshina kindawo itama khady cikin mayar mata da murmushin ta furta ehh Babata nasame ki lafiya,lfyalau Hadizata

Babata yau Dady zai dawo koh!inji Khady,ashe kina lissafi yar nan yaufa ne zai dawo murmushi mai hade da murna khady tayi tana furta yo ba dole ba Babata,

Munyi missing nasa ne tana maganar tana dosar dakinsu da gudu tana kwalawa Halee kira,Halee! Halee!

Tana yaye labulen taga wayam katifarsu bakowa adakin, katifarsu kadai ce da tasha lailaya sai kayan sip dinsu wanda Khadyn ta ya mutsa kafin taje makaranta,wanda Halee ce take aikin bayan tadan ji dama damar jikinta,tana cikin aikin ne Baba Asabe ta kirata ta Aiketa kasuwa kutsa kanta tayi cikin tare da kara lelleka ko ina dan tabbatar wa indagaske Haleen bata ciki ne har toilet dinsu ta leka bayan ta kwankwasa taji shiru tambayar kanta tayi toh ina Halee taje ita da bata lafiya kuma?ganin bata da mai bata amsa yasanyata fita daga dakin bayan ta sargafe jakkarta ama 'ajiyarsu,fitowar ta keda wuya ta yo tsinke gurin Baba Asabe tana mai furta Babata ina Halee taje ne,fuska adaure Baba Asabe ta furta na aiketa kasuwa,tun yaushe Khady ta kara furtawa cikin jin haushin Babar ta ta,shiru Baba Asabe tamata wanda dama tasan tunda taji tana kwala kiran sunan Halee tasan cewa sai tazo ta tsureta da tambayoyi kamar yar jarida ,kuma ta san tana iya bin bayanta yanzu dan haka kuwa bazata bartata fita ba komai kafuwarta

Khady ganin bata bata amsa ba yasa ta furta babata kinfa san bata da lafiya kika aike cikin wannan uwar ranar tana maganar kamar zatayi kuka shine kuma kika ta har kasuwa duk wayennan kantin basu isaba sai kasuwa.....

Baba Asabe ce ta furta an aiketa din wani ta fadawa bata lafiya ne eh dazaki zo ki tsare ni da surutun banza....

Nikam nace Baba Asabe adaiji tsoron Allah.

ALLAH YASA MU DACE

muhadu daku anext page

Zuwa monday in sha Allah lahadi babu update.

jiya kunjini shiru nayi typing sai da nagama na danna wani gun by mistake duka ya goge ga dan ciwon kai danake fama dashi,kusakani a addu'o'in ku

A MAFARKI NASANTA FANS

INAYINKU OVER MUSAMMAN MASU BIBIYATA FACE BOOK INA GANIN COMMENT DINKU INA GODIYA KUMA NA WHATSAPP INA GODIYA SOSAI MASU COMMENT DA WAYENDA BASA YI

ku cigaba da bibiyar alkalamin

Fa'eeh Bg

in sha Allah daga gobe zamu bar kasar nan domin dauko muku rahoto sai kuma mundawo,in akwai masu zuwa su fito mutafi jirgi kyautane

Wayenda badasu za,a sai gyara zama tsaf dan jin rahotannin mu.....

* Allah yasa mudace*

Pls like share and comment

A MAFARKI

NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh Bg

Dedicated to my lovely sis Laila Almustapha

Murai

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S*

Pen is mightier than the sword*

Ban amince a had'a mini document ba ko achanza mini wani sashe na littafi na inkuma kikayi nabarki da rabba

EPISODE1

FREE PAGE7

TYPING□□□

Wuce kibani guri ko in tattaka ki gurin nan,jiki ba k'wari ta wuce d'akin su tana zagayen neman yadda zatabi bayan Halee kasuwa,tabar Baba Asabe na masifarta ita kad'ai,Chan kamar minti uku haka taji tsif dama tana tsaye ne bakin k'ofa,koda ta lek'a ta tabbatar da Baba Asabe tabar tsakar gidan aiko da sauri da sand'a ta fice gidan gudu gudu sauri sauri ta fice daga gidan har ta cimmata Dan dama tasan hanyar da Haleen ke bi har ta isketa.

□Fa'eeh Bg□

Itakuwa Baba Asabe data shiga toilet din tsakar gida Dan tayi fitsari,tana fitowa tafara kwala Kiran sunan Khady,Hadiza!Hadiza! Domin tagaya mata ta d'ora mata ruwan zafi,Tsif taji ba,a amsa mata ba k'ara Kiran sunan tayi sai dai shiru aiko da sassarfa ta lek'a d'akin nasu Dan tabbatar da zargin ta,aiko tana yaye labulan taga wayam babu Khady babu ba alamarta Jakarta kadai ta hango sargafe, Nan ta rike k'ugu bayan tasaki labulen d'akin tana cigaba mitar ta na rashin dawowar Halee da wuri da kuma fitar Khady gidan,ita kuwa Halee ta fiyarce tata gata ga kamar ta dama,dama bata da saurin tafiya ne,wannan kenan ....

□Fa'eehBg□

Mukoma cikin labari .....

Jirgin✈ mu yayi landing lafiya😊

* INDIA,MUMBAI*

Babban Birnin India-mumbai garine Wanda yatara kowace irin al umma daga k'asashe daban daban,Wanda yakasance kowa da abunda yakawo shi garin inka cire yan asalin India din mazauna garin na Mumbai,wasu karatu wasu kasuwanci,wasu kuwa neman lafiya,wasu yawon shakatawa,wasu kuma aiki ne yakawo su.

Nasan wasu zasu ce Babban Birnin India ai new Delhi ne karku damu😊 wannan shine kawai abunda nayi ra,ayin sakawa□

Gujarat 105 unguwa ce Babba ta masu idon nera shiyasa zakaji ko ina tsif kamar ba bil adama acikin manyan ginukan na alfarma, inda na kutsa kaina acikin cikin wani katafaren gida Wanda yakasance upstair ne, kuma ya amsa sunansa house,Wanda yaji farin fenti da ash colour mai haske da daukar ido,gida ne Wanda yaji kawa ta ko

ina tunda compond din gidan zaka shaidar da hakan,k'aton parking space ne achan gefen dama dauke da manya manyan motoci wad'anda ake Kira car wayenda akalla zasu Kai goma,daganin motocin dai bugun America ne new design yan 2022 sai 2023 wayenda bakowa ke taka su anigeria ba sai Wanda yaji gishiri da sugar,sai wani k'aton swimming fool dake Chan ta gefen hagu Wanda yakara kawata gidan,ruwan cikin sa har wani sky blue sukeyi gwanin burgewa, swimming pool din yadan shiga lungu da alama akwai kofar sa achan ta baya, bayan ta gaban gidan,ko ina tsaf ga iska tana kad'awa shuke shuken gidan sai kad'awa suke yi suna bada wani k'amshi mai dad'i ko ina sai walkiya yake yi part biyu ne acikin gidan iri daya gidan ya hadu iya had'uwa rabinsa duk gilas ne tundaga bakin kofar shiga ciki zaka gane hakan.

Muryar wani guy naji

Daga ciki yana kwala Kiran Ammar!cigaba da kiran sunan yayi kamar ransa abace,Ammar yakara furtawa! wai uban me kake jira haryanzu baka fitoba har na fita compound nadawo,shiru danaji ne yabani damar shiga cikin falon bayan wannan guy din yacire code din kofar,nikuma na antaya daga ciki wani had'adden falo na fad'a Wanda yaji kayan more rayuwa ta ko ina gashi yasha had'addun cusions masu taushi farare kar dasu,ga katuwar Tv Nan manne abango,ga k'aton dinning table anan shima gwanin burgewa,Wanda yake kusa da wata kofa Wanda nafi tunanin kofar kitchen ne mai had'e da store, falo ne na kasa Wanda yake dauke da d'akuna uku agefe suna Dan nesa da juna agefen hagu,sai wani ahannun dama inda nake tunanin toilet, bayan nagama karema dakin kallo,kuma ina da tabbacin nan ne naji muryar wannan guy d'in,juyawar dazanyi kenan dan hawa kan upstair din da ya raba tsakanin hagu da dama,idanuna ne suka tsaya chak sanadiyyar kicibus da sukayi da wani had'adden guy a hoto yasaka kanana kaya ya daura labcoat akai irin dai shigar likitota wadda takara kawata shigar tasa,sai wani k'aton hoton Wanda yakara Jan hankali na yana sanye da kayan tiyata ajikinsa blue colour tare da abun awon Bp waton stethoscope ya rungume hannayensa akirji yana sakin wani had'adden murmushi chocolate colour skin dinsa sai sheki take yi,ga Zara zaran eyelashes dinsa cike wayenda suka Kara kawata manyan idanunsa wayenda ke kwance akarkashin cikakkiyar gashin gyarar sa,sumar kansa kuwa daganin ta kasan tana Shan gyara na musamman tare da sajen sa,pink colour din labbansa sai sheki sukeyi gwanin burgewa hancin Nan kuwa zungur kamar biro Masha Allah.

Sai wani hoton shima na wani farin guy shima dai kyakkyawane saye da irin shigar ta wancahna guy din na farko.

Maganar da naji daga saman ce ana furta Ammar Amma dai Kai Dan iska ne ace har yanzu baka shirya ba tun d'azu nabarka kashiga wanka fa Amma Dan wulakanci har yanzu baka gama shafe shafenka ba,shiyasa nayi maza nafada ciikn d'ai daga cikin dakunan wanda naji sautin maganar na fitowa,Muryar wannan guy dince tadawo Dani dai dai daganin zubin halittar Wanda ke zaune akan mirror da towel daure akugunsa daya kuma agefen kafadarsa, kwantaccen gashi ne abisa kansa Wanda dagani ya hada da jinin larabawa ko fulani daga bayan sa zaka fahimci yana da faffadan kirji tare da kwantaccen gashi Wanda yake luff gwanin burgewa jikinsa ko ina lui lui dashi daganin sa kaga Dan hutu kafafuwansa da tafin hannun sa wayenda yake ta faman murtsuka mai dasu gwanin burgewa Wanda dagani zasu yi kamar na sabon jariri,chocolate colour fatarsa sai sheki takeyi.inda wannan guy din yake furta ai narantse bazan jiraka ba tafiyata zanyi yana maganar ne kamar ransa abace kasan yau muna da meeting ga tarin patients na jiranmu Amma shine kak'i saurin shiryawa,wadannan maganganun dayake yi su suka dawo Dani daga sumar tsayen Dana yi, inda nakai duba na ga saurayin dake maganar,shima dai hadadden ne kamar Wanda naji ankira Ammar, ashe ma shine wannan fari tass din guy Wanda nagani afalo, yasha

Kyau cikin kananan kaya yadora labcoat akan kayan sa inda naga an rubuta Dr .Al Amin jabir Muhammad soja Wanda mafi yawan colleagues da abokansu suna kiransa da Dr AJ...

Dacin Raine bayyane akan fuskar Dr AJ bayan yagama mganar

Yana batun fita ne yaji anriko hannun sa,yana kucce kuccen ya kwace hannunsa kenan yaji an rungume shi dasauri ya turesa yana furta ji iskanci Kai fa Ammar Dan iska ne mtsww yaja dogon tsaki,jiyayi Ankara riko hannunsa wannan karon .....

Mu hadu next page

Gobe in Allah yakaimu

Comment din ku kadai nake bukata...

Fa'eeh Bg

A MAFARKI NASANTA FANS

INAYINKU OVER MUSAMMAN MASU BIBIYATA FACE BOOK INA GANIN COMMENT DINKU INA GODIYA SOSAIKUMA NA WHATSAPP INA GODYA MASU COMMENT DA WAYEN DA BASAYI

Pls like share and comment...

https://chat.whatsapp.com/HO4hVB1luhXGyRzaOdWy68

A MAFARKI

NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh Bg

Dedicated to my lovely sis Laila Almustapha
Murai

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S*

Pen is mightier than the sword*

Dan Allah duk wanda yakaranta wannan page yayi mini Addu,A

Allah yabiya mini da dukkanin bukatu na tare da dukkan kulluhin musulmi

EPISODE1

FREE PAGE8

TYPING

++++++++++++++++++++++++++++++++++++

wannan karon daya fisge hannunsa baiji an rungume sa ba sai dai yaji anja hannunsa,anzaunar gefen gado,baice kara cewa uffan ba har ya zauna.

Had'a idon da sukayi daDr. Ammar ne yana sakar masa wani shu'umin murmushi ne yasan ya sa galla masa wata katuwar harara yana mai jan tsaki,shiko Wanda naji ankira Ammar A hankali cikin wata kasalalliyar murya ya furta just give me three minute ohk! yakai karshen maganar yana mai k'ara sakin yalwataccen murmushi a fuskarsa, wanda maganar da yayi iya kar labbansa ta tsaya,maganar da yayi ce bayan barowar sa kan madubin,tasanya ni kara cikin natsuwa ta daga sumar tsayen da na kara yi ganin hadadden guy din da na gani ahoto falo Amma tabbas afili yafi kyau daganinsa kaga ingarman namiji mai ji da kudi,mulki da izzah ga fatar nan tasa sai sheki take yi kamar an mata wankan madara sai narasa tantance shin chocolate colour ne skin nasa ko fari ne mai dan duhu,wanda fuskar sa takara nuna hutun da yake samu....

Zazzak'ar muryar sa kuwa kamar ana kad'a sarewa inyana magana kmar kayi bacci saboda dadin ta,saboda zakin ta da taushinta in yayi magana kamar ba,a bakinsa tafito ba,daga yanayin Kallon da masa na fahimci akwai jan aji da izzah da yanga kamar mace kuma baida son magana,Ammar dai daga ni miskili ne na karshe...

Bayan ya gama maganar da iyakar labbansa ta fito inba ka kalli bakinsa ba ba zaka san dakai yakeyin maganar ba,juyawa yayi ahankali yataka kamar yana tsoron carpet din dake kwance male2 ad'akin ta huda masa k'afa,har ya isa inda doguwar sip dinsa take wadda ake bud'ewa da thumbprint inda yasanya dai daga cikin zara zaran yatsun sa na hannu take hadadden sip din tashiga budewa da kanta har ta kai karshe wow! bansan lokacin da baki na ya furta hakan ba,Allah yasa ba wanda yajini...

Kayane birjik kamar botique wasu asama wasu ak'asa,sashen ko wanne daban su trouser,men panties,t shirt ,necktie suma gasu nan atsare ta ko ina sip din kayane atsare chan daga karshe suit ne jere kala kala sai walkiya sukeyi,sai sashen shaddodi,yadukka da huluna irinsu mu hadu banki ,su ku'be, har da irin su tadara mai irin na gidan sarauta kamar yanayin na(raba gardama) labarina...sai dai na wannan likitan sunfi na (raba gardama) kyau kuma design dinsu ba,a irin na nigeria bane daga ganin su kaga bugu turai sun sha kari har sun gaji,sai daga chan sama wata hanger ce rataye da wasu fararen riguna masu kama da labcoat,dasu long sleeve,under wears,short nikers da vest,handkerchief, kowanne da gefensa akan hanger din.

.....

Hannunsa ne yana jawo d'aya daya daga cikin fararen rigunan labcaot,

Shi kam Dr.Alamin Aj murmushin bakin ciki kad'ai yake yi yana jan tsaki yana mai duba hadadden agogon da ke hannunsa kamfanin apple,dogon yakara ganin har minti uku ya wuce har yakara biyar akai,Dr.Ammar kuwa duk da yaji jerin tsakin dayake ta faman saki kuma yana ganin hararar da yake ta sakar masa bai tanka saba

.....Komawa yayi yadauko wani had'dden wandon jeans bak'i,bayan ya aje labcoat din,ya juyo kenan Dan ya ajesa kan gado yaji Dr Aj yakara jan wani mugun tsaki wanda sai da Dr. Ammar ya rufe kunnuwansa yana mai yamutsar beautiful face dinsa D'an kallon Dr.Aj yayi wanda yayi tik'in tik'in da fuska,Dauke kansa yayi,A hankali yajuya gurin sip din yana sakin kayataccen murmushi a fuskarsa wanda ya bayyanar da dimple dinsa na gefe daya yatsan sa yasanya cikin kwarewa kamar wani jarumin ya lalaci tsinin hancinsa,wannan dabi'ar sa ce ta lakarta tsinin hanci in yana cikin yanayi mai dadi dakuma yan maganar sa nakai.

Dama haka yake Idan yana jin shirmen sa haka yakeyi da d'ai dai yake zabo kayan da zai saka acewar sa suna masa nauyi ne ahannu,wani lokacin ma in Dr Aj ya ga zai tsayar dasu shike zab'o masa kayan kamar wani karamin yaro

Abun da yasa yajuya ya fahimci Dr Aj yakai kololuwar b'acin rai yanajin uwar hararar da yake sakar masa,ga tsukkin da yake ta faman ja suna neman jaza masa light headache,shiyasa kawai ya juya batare da ya aje trouser dinba yakoma domin ya hado kayan baki d'aya,da isarshi bakin sip din yasanya kyakkyawan hannunsa yazaro farar vest da long sleeve fara kar mai dogon hannu,da handkerchief fari, yana gama zab'ar kayan yadanna wani madanni kamar na ura daga kasan inda ake thumprint,A hankali katuwar sip din tarufe ruff kamar dai yadda take farko.

Fa'eeh Bg

A hankali yataka zuwa bakin gadon ya aje su anan gefen labcoat din a kusa da Dr.AJ din

Wanda kallo daya yayiwa Al amin Aj ya dauke kansa, yana cigaba shirinsa cikin natsuwa wandon yafara jawowa zai sanya wanda yayi dai dai da d'ago idon Dr Aj,ganin abunda Dr yake kokarin yi ne na sakin towel d'insa kasa yasanya sa dasauri yadauke kansa yana fadin marar kunya kawai yana jan karamin tsaki,bai san cewa Dr motsinsa Dr.Ammar na ankare dashi ba har dauke kan da yayi,shi atunaninsa babu short ajikin sa shiyasa yayi saurin dauke kan nasa duk da yasan ba halin shi bane sakin tsaraici tun suna yara shi ba ya yadda wani ya gane masa jiki in za,a musu wanka dakyar yake yadda wata rana sai dai akai shi gurin Aunty....

Murmushi kawai Dr Ammar yayi yana cigaba da sanya wandon sa acikin dan short din da ya chanza tun atoilet cikin wayen da ke a lakkame a hanger,vest dinsa yasanya da long sleeve dinsa masha Allah na iya furtawa takawaa yayi zuwa kan madubi yana kara gyara lallausan gashin sa da sajensa tare da kara taje sa da murtsuka masa kalolin mayukka bayan wanda yashafa acikin toilet,sannan ya fefesa turare kusan kala biyar oud masu bala'in kamshi,man bakin sa ya shafa :lips balm: wanda yakara kawata kyakkayawar fuskar sa da aina hin kyawonsa da shekin fatar sa,dama bakin sa bai rabo da maskin lips balm domin wannan dabi'ar yasaba da ita tasha man baki kamar mace,shidai Dr Aj kallon ikon Allah kadai yakeyi yabuga tagumi yana yi yakai duban sa ga agogo,ace katon saurayi yazauna ya dinga shafe shafe kamar mace, azuciyarsa yayi furucin.

Dan yin murmushi DR .AMMAR yayi jin maganar da Dr. AJ yafurta wadda yayi kasa kasa,tsinkayar muryarsa Dr Aj yayi yana furta nagode ma Allah da ba maccen nake ba kamace kagani yakai karshen maganar cikin yin dan karamin murmushi Dr aj da yaji abunda ya furta duk da baiyi tsammani yajisa ba dan ciki ciki yayi maganar,sai bai yi mamaki ba dan yasan yadda dan uwan nasa yake da mugun ji kamar kunnen maciji..

sai bai bai basa amsa ba yashare sa .

~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~

©Fa'eeh Bg

~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~

cikin dan kan kanin lokaci dakin yakara gauraye da kamshin turarrukkansa

A Hankali yajawo labcoat dinsa irinta ta Dr. Aj samfurin ta likitota fara tass sai shekin sabon taka takeyi kamar ma sabuwa ce akan kayan sa yadaura irin da yadda kuka san likitota nayi masha kawai zamu ce domin tsaya wa rubuta kyawon da yayi page din bazai dauka ba,stethoscope dinsa dake akan hadadden gadon sa ya sargafa abisa wuyan rigar sa dan danan yakara fitowa likitan sa sak,ga sunan shi nan ya bayyana radam agefen rigar tasa cikin tsari mai kyau inda aka rubuta DR. ABDUL RASHID A ALIYU da manyan baki Amma colleques nasu nasu da childhood friends na kiransa da DR.AA

 wasun ma cikin colleques nasu suna kiransa Dr. Ammar a gida kuwa suna kiransa Ammar Saboda sunan kanen mahaifinshi da yaci shiyasa aka masa lakani da Ammar.

A hankali ya juyo inda Dr aj yake sannan ya kalli hadadden agogon zinarin dake daure a tsintsiyar hannunsa kirar kamfanin rolex wanda yadaura bayan tsayuwar sa kan madubin wanda yakara kawata shigar tasa skin din sa sai sheki takeyi.

A hankali bayan yataka ya zabi dai daga cikin shoerock din dake dauke da takalma iri iri masu kyau wanda sai da yafara saka sock baka aciki sannna yasanya takalman nasa masu kyau bakake rufaffi sai walkiya sukai gwanin burgewa

A gogon nasa yakara dan kallo ganin lokacin da yadiba har ya wuce wani ya zo wani yakaru, sannan cikin izza ya furta man katashi mutafi karmuyi late...

wani ...

Kallo da Dr aj yamasa ne yasa sakin wani killer smile wanda ya tsaya iya labban sa,dama da gayya yayi maganar dan yasan mutumen nasa acike yake kamar ya fashe wanda kuma yasan fushin nadan lokaci ne zai sauko .....

Shiko Dr aj dayake kan pressing phone dinsa baice masa komaiba yadauki nashi stethoscope din ya sargafa,wanda dama sargafe yake awuyansa ne,gajiyar jiran Dr Ammar ce tasa ya cire ya ajiye shi gefe,duba kansa yafara yi agaban madubin dan tabbatar da komai normal sannan ya fice daga dakin shima uban gayyar dake tsaye yana kallon sa A hankali ya matsa gefen gadon yadauki wayar sa dake chaji abisa bed side drower sannan ya fice daga cikin dakin cikin tafiyar takama da izzah yana ta faman zuba uban kamshi kamar sabon ango.....

Fitar su dakin ce tabani damar

Karewa da Katon bedroom din kallo fari ne tass mai kyau wanda yake katone ne nagaske ashe ma Ciki da falo ne ban lura ba wurin uban sauri,bedroom din tana da fadi sosai gadon ya hadu iya haduwa,da sip din sa wadda take lafe abango kamar babu ta sai gefen hagu ga katon mirror mai dauke da kayan gyaran jiki irinsu mayukka masu tsada manyan manyan turarukka da man gyaran gashi da sauran kayan amfani,sai wata kofa dake gefe wadda nafi tunanin toilet ne inda na lek'a sa ya hadu iya had'uwa dukkaninsa glass ne aciki ga katon bahon wanka nan irin na turawa mai kyau da katon madubi da yaji kayan amfani irins sabulu shower gel da turarukkan wanka,toothpaste, brush komai akwai ga tsakiyar toilet din gudan fankacece komai akwai aciki na bukata ya tsaru iya tsaruwa,curtain din kuma milk ne masu kyau.

Falo na dawo bayan na fito daga toilet din inda falon ya hadu shima ya hadu komai na cikin sa yakasance lite blue and white har cusions da labulayye komai agyare gwanin burgewa kamar ba dakin men ba.

Sawun tafiyarda naji ne yasani waigawa dan ganin wanda ke tafowar

Dr Ammar ne yana shigowa direct bedroom nasa ya yi tsinke

Cikin sanda nima nabi bayansa

Gurin aje takalmi yanufa shoe rock wadda ke cike da takalma na alfarma masu kyau,wadda ke akusa da sip dinsa takalmin dake kafarsa yacire ahankali tare da ciro wasu masu masu kyau sai walkiya suke yi suma cover shoes ne kamar na farkon sai dai kalace ta banbanta wadanchan baki ne a kala su kuma waddan nan fari,bayan yachanza su ne ya dauki yar madaidaiciyar bag tasa kamar ta school mai kyau yasar gafa agefen kafadarsa yana ficewa.

Ahankali yake takonsa har ya fito falo sannan ya isa inda wata dankararriyar mota take fake kirar benz a tsakiyar compound din gidan ,dama Dr aj yayi ya kunnata har sun yi reverse, Ammar yace yayi mantuwa cikin jin haushi Aj ya tsayar da motar anan tsakar gidan.

A hankali yasanya zara zaran yatsunsa yabude front sit yazauna Dr .Aj bai cemasa uffanba duk da yaga chanjin takalmin da yayi cikin ranshi kuwa kuwa fadi yake mutun sai shegen kichifi kamar mace,kai kam Ammar matar ka tabani mtssw yana jan tsaki abayyane, Dr Ammar kuwa bayan ya gyara zaman sa har ya maida karamar jakarshi sit din baya yana jiran Dr aj yatada motar shiru sai dai yaji tsakin da yayi,murmushin mai kyau kawai yayi yana furta man gulma ta kakeyi azuciya koh yakai karshen maganar yana kafesa da manya idanunsa .....Shiko Dr.Aj harar wasa yasakar masa yana furta abunda ma yafi gulmar ka za,ayi,yafigi motarsuka fice daga gidan bayan sun sanya belt mai gadi na wangale musu katon gate din.....

□Fa'eeh Bg□

next page tommorrow in sha Allah

Comment dinku kadai nake bukata FANS □□□ domin shine kwarin gwiwata □□

godiya agare ku ta musamman

.....

fiddausi dan galadima

siddiqerh muhammad

halima bashar bello

ukuteey

anty zee

oum amjad

sha'awa hamis

Oum sudais

Umma

Da ma wayenda ban ambata ba

wannan page naku ne

□□□□□□

Allah yabar kauna□□

ina ganiin comment dinku ina jin dadi sosai□□□

Allah yakai haske acikin kabarin ka

Baba Bello ya yalwanta kabarin ka dana dukkan kulluhin musulmi,□□

Mukuma kasa mucika da imani ya Allah □□pls say amin !

* Allah yasa mudace*□□

Pls like share and comment

□A MAFARKI NASANTA□

in my dream i know her

By

Pha'eezah Almstapha

Daga Alkalamin ✍✍

□Fa'eeh Bg□

Dedicated to my lovely sis laila Almustapha Murai□

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand □

ESSENTIAL WRITER'S*

pen is mightier than the sword*

Group na whatsapp ina mai kara baku hakuri akan abunda ya faru

`^^^^^^^^^^^^^^^^^^

EPISODE1

FREE PAGE9

TYPING

Tafiya suke yi ahankali kan katon titin dayake da abun burgewa ta yadda aka tsara shi,ba,abun da ke tashi a cikin motar face sautin sanyayyiyar wakar rihana mai taken my umbrella

Uban gayyar yayi shiru ya jingina da sit din sa yana sauraren wakar idanunsa alumshe fuskar nan sai sa,sai sa ba murmushi ba dariya,karar wayar sane da aka kirane dake ringing waka mai sanyi ta mahaifiya ne yasanya sa bude manyan idanunsa a hankali tare da daura su akan screen din wayar wanda sunan nurul hayat ya bayyana b'aro b'aro b'aro akan wayar da numban nigeria + 234.....A hankali bayan ya gama karewa wayar kallo wanda har kira na biyu ya shigo yasanya kyakkyawan hannnunsa ya dauki wayar tasa dake gefensa aje kirar iphone latest one 15 pro max picking din call din yayi yana mai kara wayar akunnen sa akunnensa tare da sakin kayataccen murmushi yana furta Assalamu alaiki nurul hayat,daga chan dayan bangaren,murmushi aka saki wanda yakara sanya masa natsuwa,wslm kyakkyawan likita na takai karshen maganar cikin nuna farincikinta,murmushi ya mayar mata dashi tare da furta fatan kina lafiya nurul hayat? daga chan bangaren ta amsa da lafiya lau ya aiki?Alhamdulillah,ya furta mata cikin kulawa kamar yadda tayi masa tambayar,A hankali yakara furta inasu maheer da nisa,maheer na school kasan suna shirye shiryen graduation ne oh hakane fa jiya ma munyi magana dashi yasanar mun,Nisa fa?ya kara tambayawa cikin kulawa da ladabi amsa tabashi da dama ai nida maher kadai ne agidan sai sarki,yuhanis tana gurin sister Husaina tatare gurin sumy,A hankali bayan gama saurarenta ya furta meyasa kika barta kinsan bata son karatu ga sumayya ma duka daya suke,yakai karshen maganar kamar yana jin tsoron yin maganar yana kokarin danne wani abunda ke shirin taso masa na jin sunan sarki da ta ambata,murmushinta ne yaji tana furta nur yanzu fa ba yarda bace sun girma kowa censu tayi hankali 18+ suke fa kaga kuwa sunyi hankali da channe dai basa son zuwa makarantar kuma lokacin babu Wayo ne gashi ma yanzu suna gab da yin ss.c e.graduation Uhmm kawai yace,bawai dan ya yadda da karatun nasu ba shi atunanin sa mahaifiyar tasu tana kokarin kare su ne kawai dan yasan yadda yake fama dasu in sunje nigeria dakyar da lallashi suke samu suje school...Kuma ehh dagaskiyar ta yanzu sun girma da daine yake tilasta musu zuwa makarantar itada sumy amma ayanzu su da kansu suke zuwa dan sun mahimmancin karatun,wannan kenan.....

Fa'eeh Bg

Shirun da taji yamata ne yasanyata ta A hankali furta YARIMA, gaban sa ne yayi muguwar fad'uwa jin furucin nata yanzun ma shiru yamata dama tasan abunda zai

faru kenan, dama irin hakan tana yawan faruwa duk ta kirasa da sunan bakin sa yana masa nauyin amsa sunan, dalili kuwa shine takirasa da sunan ne ko zai nuna alamar cewa yasauko daga fushin da yake ne da mahaifinsa,da kuma jin in yanzu ko yana son sarautar da yake gudu wadda mahaifinsa yake son lakaba masa shima yasamu ya huta wanda kuma shine yasanya sabani atsakaninsu domin kowa kafaffe ne like father like son ,da dai taga alamun bazai ce komai ba,ta furta cikin sanyin murya ABDUL RASHID har yanzu kana nan kan bakan ka ?takai karshen maganar cikin yanayin da bazai iya juraba,wannna karon faduwar da gabansa yayi sai da yadafe kirjinsa wanda ko Dr aj dake tuk'i a hankali sai da yajuyo ya kallesa dan ganin alamar razana atattare dashi ga kuma hannunsa dafe da kirjin sa,A hankali yaji shima jikin nasa yayi sanyi ganin d'an uwan nasa cikin wannan yanayi,Dayan Hannunsa kawai ya riko da hannun da baya driving dashi ya damk'e acikin nasa, yasan cewa tabbas ko ba,a fada ba maganar sarauta ce, akayi masa,wanda ya rasa wace irin kiyayya ce tsakanin Ammar da sarauta da har baison mulkin wanda kuma yake tunanin shine abunda yasanya sa rashin son komawa kasarsu,idanu suka had'a dashi ya girgiza masa kai da alamar be strong man shikuwa Dr.Ammar dauke kansa kawai yayi batare da ya nuna wani abu afuskarsa ba .

Achan bangaren mahaifiyarsa dataji shiru ne yasanyata duba wayar dan tabbatar wa inyana online,,,,,,,,,,,,,,,,,kuma dama akan sarautar ne yakarbi aikin da kasar india tabasu bayan kammala karatunsu,wanda shikuma Dr Aj yana da burin dawowa k'asar sa ta haihuwa domin yin aiki acikinta dan su taimaki kasarmu ta nijeriya,Amma saboda Dr. Ammar yasadaukar da nashi burin suka fara aikin tare anan kasarta india wanda izuwa wannan lokaci sunansu yayi shura a india dama fadin duniya baki daya,kowa yasan Dr.Abdul rashid Aliyu Ahmad da Dr.Al Amin Muhammad soja,inda kowace k'asa masu dauke da manyan asibitoci suke son su samu damar gayyatar su sumusu aiki koda na dan lokaci ne amma basu samun wannan damar saboda shidai Dr.Ammar kaifi daya ne acewar sa kasar india su suka fara daukarsu aiki har suka yi suna a ko ina to ayanzu bazai iya barin kasar ba dan yaje wata kasar da sunan aiki ba,haka shima Dr. aj duk da yana da burirrika,inda kawai zai iya yin aiki yabar india shine kasarsa ta nigeria ko shi dan saboda nan ne cibiyarsa take,kuma yana son taci amfanin ilimin suwannan kenann.....

mukoma inda muke .....

A hankali ta furta karka damu kaji tana mai sakin murmushi,Ina d'ana yake takara furtawa,cikin sauke wata nannauyiyar ajiyar zuciya wadda har sai da taji sautin ta,Wanda shi yakara tabbatar mata da Dr ammar har yanzu yana nan kan bakansa nak'in son sarautar, da wata murya mai sanyi ya furtama ta gashi nan,to basa wayar ta furta masa,Dr aj dake driving yakarbi wayar bayan ya saki hannun na dr ammar a hankali yakara ta akunnen sa yana furta momy yakike cikin murmushi ?lafiya lau my son ta furta kuntashi lafiya,lafiya lau yabata amsa kara furta masa tayi ya aiki Alhmdllh yakara bata amsa toh masha Allah!A hankali takara furta naji kamar a hanya kuke koh?ehh momy,sai ina halan ? dan naga kunfita da wuri yau,ehh momy muna da meeting ne kuma kinga yau monday akwai tarin patients, eh hakane fa toh Allah ya kaiku lafiya akula da titi,in sha Allah yafurta mata,sannan takara furta in kun gama abunda kukeyi anjima inkana freee ka kirani akwai maganar da nake so inyi dakai,cikin girmamawa yace in sha Allah momy i will contact you A hankali takara furta asauka lafiya,Allah yasa ya furta sannan sukayi sallama tare da yanke kiran.....

Kuyi manage da wannan ba yawa...Naso inbaku page biyu but abunda yafaru dazu yadan taba ni,kaina ke ciwo ko typing din nadan yishi sai ahankali.

Allah yasa mudace,Abunda ya tsanan ta agaremu Allah ya yayemuna

pls like share and comment

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/HO4hVB1luhXGyRzaOdWy68

A MAFARKI NASANTA

in my dream i know her

By

Pha'eezah Almstapha

Daga Alkalamin ✍✍

Fa'eeh Bg

Dedicated to my lovely sis laila Almustapha Murai

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S*

pen is mightier than the sword*

EPISODE1

FREE PAGE

TYPING

Dora wayar,yayi abisa laps din Dr Ammar a hankali Wanda ke jingine da sit dinsa ya lumshe da idanunsa yayi tsif kamar Wanda ruwa yaci ko kwakkwaran motsi,ba abunda yake tunani face maganar da mahaifiyarsa tamasa wadda kusan bayan dan lokaci takan yimasa maganar taji ta bakinsa ko yajanye nasa Ra,ayin bisa ga na mahaifinsa,fatan Sa kawai A wannan karon Allah yasa batayi fushi dashi ba,dan bazai iya jure fushinta ko na second ne abun yawa zai masa azuciya

Wayar Sa da Dr Aj ya aje masa ce tadawo dashi daga tunanin zucin da yaje a hankali yasa hannu yadauki wayar ya tsura mata lumsasaun idanunta kamar mahaifiyar tasa ce agaban sa,Ajiyar zuciya yasauke mai nauyi,yana kara lumshe idanunsa tare da budesu

Maganar da Dr Aj yayi ce tasa yadago idonsa daga kallon da yake yi ma wayar tasa,inda yake furta masa kar ka sanya damuwa aranka nasan awannnan karon batayi fushi mai zaifi ba kai inaji bazata tayi fushi dakaiba saboda daga yanayin yadda muka yi magana da ita na tabbatar da hakan,Wata katuwar ajiyar zuciya Dr .ammar yakara saukewa,baice furtawa Dr. Aj komai ba,Dai dai sun kawo katafaren asibitin da take Babba afadin India wadda mutane da dama ke yowar tattaki India domin samun ingantacciyar lafiya,Asibiti ce da tayi shura a fadin duniya,Babbar asibiti ce da ta Tara many an likitota ta sassa da ban da ban kama daga likitan kwakwalwa,na zuciya,likitan mata kai ko wanne fanni akwai

Su Dr Ammar da Aj suna dai daga cikin manyan likitotan dake taka rawa ta kowanne fanni acikin asibitin shiyasa sunan su yayi fice musamman Dr.Ammar.

 A mafarki nasanta

Daga Alkalamin

Fa'eeh Bg

MAHARASTRA 24 HOURS HOSPITAL MUMBAI INDIA

..... Asibiti ce Babba wadda ta tsaru iya tsaruwa taji kayan aiki a ko ina,da kayan more rayuwam,musamman ita wannan asibiti su suke jinyar marar lafiyar da kansu,kudi kawai zaka zube kagama naka aikin....

Bayan wangale musu gate da mai gadi yayi tare da nuna farin cikinsa na zuwan su,duk da yadda yake cike da mamaki naganin wadannan manyan likitota sukadai batare da masu tsaron su...Kunsan indiawa akwai bada kariya ga wayenda suke musu hidima dan ko kare ne tsaf za,a sanya mashi bodyguard bare manyan likitota wayenda india take ji dasu dama kasa baki daya.

Haka dai ya rufe gate yana mai tambayar kansa lafiya ?suka zo sukadai ganin kamar suna risking rayuwarsu ne tafiya su kadai, abunka da turawa..nima dai ohon nace dan bangansu tun chan gidan ba,ashe dama suna sa body guard to amma lafiya?na tambayi kaina,bani da mai bani amsata haka nayi shiru abuna.

Wurin da yaksance na musamman dansu wato parking lot nasu wanda suke motocinbsu suda sauran colleques nasu,gashi nan kowa anyi tagging din sunansa akan board din mai kya.

Inda naga an rubuta Dr.Al amin dr aj yanufa dan nan ne nafarko kafin na Dr ammar Wanda shima sunan sa arubuce yake cikin tsarin burgewa,Bayan sun parker motar tasu kowa yacire sit belt dinshi Dr.Ammar dayajawo karamar bag din shimai kama da school ba,wayarsa dake ajiye atsakanin lap dinsa yadauka,A hankali yadora kafarsa ta dama wadda take sanye hadaddun takalmansa yana mai kara gyara zaman stethoscope dinshi da labcoat dinshi yana ida fitowa da gangar jikinsa baki daya,futowar sa keda wuya yaci karo da wasu garadan maza kirar america atsaye agefenn motar tasu kowannensu fuskarsa ba Annuri,Shima Dr aj haka ce takasance dashi bayan yafito yaci karo da irin garadan mazan da Dr Ammar ya ci karo dasu ,Murmushj kawai Dr.Aj yayi,nasan arina ya furta domin dama ya hango motocinsu pake agefen titi kirar hilux da wasu daga cikin motocin da gwamnatin ta bada masu kyau,Amma baiyi tunanin zasu cikin hospital din ba,ashe dama suna ciki.

Abangaren Dr ammar kuwa bayan cin karo da yayi dasu take yakara murtuke kyakkkyawar fuskar sa kamar bai taba koda murmushi ba.

Daya daga cikinsu ne ya furta sorry sir! duk sauran suka hada baki suna maimaita abun da ya furta,wannan umurnin gwamnati ne mutumen yaci gaba da magana,mukare ku tako wani hali yanzu idan yanzu idan akaji ka koremu zamu iya rasa hanyar samun cin abinmu,wannan aikin shimuka dogara dashi kayi hakuri bazamu kara ba,ko wacchan ma matsala akasamu we are sorry sir haukat suka kara hada baki atare suna maimaitawa,yana maganar ne cikin harshen indianci

Sassauta fuskar sa yayi tun bayan jin bayanin d'aya daga cikin su wanda yake shine tsoho acikinsu.

Dalili kuwa shine bazaiso ace ta sanadinshi baa sun rasa hanyar samun abincinsu,danshi yakasance mai tausayi ne ga nakasa garesa,ma'ana talakawa wayenda yafi su arziki,A hankali yak'are musu kallo sannan yadauke kansa,su kam daganin yanayin fuskar ta boss dinsu sai suka yi calming na zukatan su ,maganar da yayi ce tasaka su furta thank you sir ,duk sai suka juya gefen da Dr aj yake,bayan ya d'aga musu hannu kawai,alamar ya isa, Cikin hada baki suka furta ma Dr. aj Goodmrnng Sir! mrnng fn ya furta cikin sakin fuska ya cigaba da magana dama yaji maganar da Dr.Ammar yayi nacewa suje wurin sa inyace su dawo kan aiki shikenan,shine Dalilin godiyar da suka ma Dr. AA din Dan sun riga sunsan inta tashine bama zai koresu ba kan dan karamin laifi,Murmushi yasaki Bayan tunawa da duka wannan case din akanshi ne, A hankali ya furta dasu karku k'ara irin haka kunji,cikin yaren na indianci domin acikin su akwai wayenda basa jin turancin, Amsa masa sukayi da yes sir atare duk da yasan komai tsarinsa ne,tunanin da yafaru ne yadawo masa masa arai.....

Fitarsa ce keda wuya a cikin gari sai motar sa ta tsaya,inda tayar motar tayi faci gashi kuma babu spare tyre a cikin motar wanda basu san da hakan ba sai da ta tsaya musu kuma adai dai inda ba Al umma,tafiya ce zaiyi domin wakiltar su taro shida Dr.Ammar,A wani taro da zasu gudanar na likitota,dole haka samu gefen titi shida bodyguard dinsa suka parker motar,anbuda booth ko za,a samu spare amma

babu,domin motar tamusu bazata ne,sai an duba lafiyar mota ake fita da ita,yau saboda urgently meeting ne sai basu tsaya dubawa ba ashe tayar motar na bukatar iska.

Agogon hannun sa ya duba yaga lokacin su yana yana ta yin gaba kawai sai ya yanke shawarar kiran Dr.Ammar.....

Kwance yake a cikin k'aton swimming pool din ya nutse aciki kamar ba mutum aciki ko ina tsit sai kamshin flowers da kukan tsuntsaye ke tashi, ko ina yanata walkiya sama tayi sky blue ga ruwan dake cikin swimming full din gwanin burgewa....

Fa'eeh Bg

Tunani yake yi akan maganar da duk mahaifiyarshi ta kira sa,sai ta tunatar dash,kuma aduk lokacin da yanuna kamar bai fahimci maganar ta ba sai tayi fushi dashi,wanda damuwar ce ta zame masa biyu gata mahaifinsa wanda duk akanta ne mahaifiyar tasa take yin fushi dashi,ga kuma mafarkin sa dayazame masa jiki,wanda duk wani shaki ki nasa yasan da wannan mafarkin nasa saboda tun yana D'an shekara bakwai yafara yinsa,ko mafarkin mene ne ?oho!

K'arar kiran da yasanyawa Dr. Aj ne a waya ke amsa kuwwa akunnensa cikin sauti mai dad'i,A hankali ya katse tunanin da yake Bayan D'agowa daga Nutsen da yayi..

A hankali ya fara takowa har yafito cikin ruwan lemar ruwan ta kwanta ajikinsa cikin burgewa,kyakyawan gashin kirjinsa yakwanta luff,da sumar kansa,k'aramin short ne ajikinsa,wanda yadaura towel akai da wani karamin towel ahannun sa yana goge kansa da shi,wanda wani d'ai daga cikin yaran sa suka miko masa,wayarsace bai bada damar tab'awa ba.

A hankali yasanya zarazaran ya tsunsa yadauki hadaddiyar wayar tasa wanda zuwa wannnan lokacin har kiran yakatse,wani yasake shigowa a wayartasa picking call din yayi.

A bangaren Dr .aj kuwa tsaki yake ta faman bugawa har sai da bodyguard nasa suka furta yallabai ko d'ayan mu yakoma yadauko wata motar tunda bakayi reaching nasa ba,Domin suma bodyguard nasa mota biyu suka je da fito da ita kuma duk irin budaddun nan masu kama da hilux,tasa ce kawai Audi,cigaba da magana bodyguard din yayi yana furta tunda naga ka kira sa har sau uku bai daga ba,ko baya kusane

Shiru Dr aj yayi yana sauraren maganar ta yaron nasa dan yasan halin kayan sa yanzu haka yana chan yana laziness dinsa gurin daukar kiran yana dialing numban again.... picking din call din yaji anyi shi yasanya shi kara wayar akunnen sa kirar i phone 15 pro max irinta da Dr aj,yana mai jan dogon tsaki

Abangaren Dr ammar kuwa A lokacin da yaji saukar tsukin acikin kunnensa sai da yajanye wayar akunnen nasa sannan yakara mayarwa tare da d'an kallon wayar tasa inda naga an rubuta blood line b'aro b'aro ajikin wayar tasa,tab'e dan karamin bakin sa yayi bayan ya ya dan kalli wayar sai kuma yasa ki kayataccen murmushinsa mai kara wa fuskar sa annuri,dan yafahimci mutumin nasa har yanzu akai yake dama koda yafita fushi yakeyi dashi,Dan yace bazai je taron ba sai dai shi ya wakilcesu,tunawa da yadda yafita ne yakara saka shi sakin murmushinsa wanda ke kara bayyanar da kwarjininsa,

A hankali yafurta man lafiya ?kai da ke cikin meeting ya akayi kuma kake kokarin damu na da kira,haushine yakara turneke Dr aj Bayan gama sauraraen furucin nasa,cikin jin haushin sa ya furtama Dr aj ka turo mun dai daga cikin body dinka da wata motar,motar da nashigo tasamu matsala tayan yayi faci ne kuma babu spare yana gama maganar ya katse kiran ....

Page guda kuka samu maitsawo..

mu hadu next page monday in sha Allah

Ina godiya amafarki nasanta fans

Allah yasa mudace

Ya Allah ka kara kawo muna zaman lafiya acikin wannan kasatamu

Like share and comment pls .

A MAFARKI NASANTA

in my dream i know her

By

Pha'eezah Almstapha

Daga Alkalamin ✍✍

Fa'eeh Bg

Dedicated to my lovely sis laila Almustapha Murai

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S*

pen is mightier than the sword*

EPISODE1

FREE PAGE11

TYPING □□□

MUYI SALATI GOMA GA ANNABI....

Allahumma salli ala muhammad wa ala ali muhammad kama sallaita ala ibrahim wa ala ali ibrahim innnaka hamidun majid,Allahumma barik ala muhammad wa ala ali muhammad kama barakta ala ibrahim wa ala ali ibrahim fil alamina innaka hamidun majid□

ya Allah kasanya mu acikin wayenda zasuyi makwabtaka da Annabi Muhammad s a w□ agidan Aljannah□

A b'angaren Dr.Ammar kuwa bayan Dr.Aj yakatse kiran sai yaji duk baiji dad'i ba,bai kyautama sa ba,kuma yasan haryanzu fushi yake yi dashi....

Ahankali yakira d'aya daga cikin yaran nasa ya basa izinin daukar daya daga cikin motocin dank'ara dank'ara din motocin nasu dake parkey a parking lot,sannan yayi Amfani da Gps tracking yanemi inda su Dr.Aj suke,da numban aj din,sannan yakaimusu spare tyre yadawo da wacchan yakai karshen maganar cikin bada umurni...

Ohk sir! sannan yabasa umurnin yaje yakarbi car keys din,gurin ma,ajinsu,bayan yakarbo d'ai daga cikinsu ya fice daga gidan cikin wata arniyar mota,

Bayan fitar sa shiko Dr.Ammar falo yadosa yana tafiya d'ai d'ai kamar mai tsoron taka k'asa,code din kofar yasanya wanda yasanya kofar ta glass bud'ewa ahankali,shigewar sa yayi abunsa bai zarce ko ina ba sai upstairs inda bedroom nasa yake da shigarsa direct toilet yafada.

Bayan kamar awa d'aya haka ya fito daga wanka yana kimtsa kansa....Yana tsaye agaban fankacecen mirrorn nasa yana taje lallausar suman kansa,wayar sa tayi karar shigowar message har yaso yashare saboda a tunaninsa Dr. Malini ce wadda ta addabi rayuwar sa yayi blocking numbannta yafi akirga da sababbin layi amma abanza kullum cikin turo masa sako take yi....

DR.MALINI

dai wata had'addiyar budurwace jinin indiyawa jinin larabawa,domin ita din ruwa biyu ce mahaifiyarta balarabiya mahaifinta ba indiye,shiyasanya ta ko ina malini ta had'u iya had'uwa bata da makusa,gata yar gawu,son kowa kin wanda ya rasa.

Class mate dinsu ce alokacin suna medical schl, sunyi karatu tare,dan alokacin ma team dinsu daya da ita,kuma suna abota da ita duk da dai shi Dr ammar bai cika magana ba da ita ba saboda tun farko ya fahimci inda ta dosa sai dai bata bayyanar ba....

Sai bayan sungama karatu ne ta fito mishi da abunda ke zuciyarta,kuma tun anan yagaya mata shi baida ra,ayinta Dama yasan abunda ke ranta,wanda shiyasanya har tayi yadda zatayi tashigo rayuwarsu.....

Batayi mamaki ba tunda tasan shi mutunne mai sanya ido akan abunda yake ganin kamar zaizamo cutarwa agaresa tasan cewa sai da yayi bincike kanta kafin ya yadda ta shigo rayuwar su...

wanda A yanzu ma a hospital daya suke aiki,anan ma tabiyo su,tanemi aiki anan saboda shi

duk da yafito fili Yagayamata baida ra'ayinta hakan baisa ta saduda ba saima kara kutsa kanta da takeyi agareshi wannaan kenan....

Bayan kamar minti goma haka,bayan ya idasa kimtsawa cikin shigarsa ta gajeran wando milk da riga ligt purple,yatako ahankali inda wayar tasa take yashe akan gadon zara zaran yatsunsa ya sanya yadauki phone din,danna power yayi wanda take wayar takawo haske,inda yafara kallon notification,inda yaci karo da message from blood line yadanyi mamaki kad'an na meyasa bai kirasa ba,har yaso yashare mxg din kamar farko da yake tunani Dr.malini ce ....

A hankali ya bude mxg din inda naga anyi rubutun da yaren india kamar haka "Dude Naga car din nagode"abunda kawai sakon ya kunsa,yakaranta sa yafi akirga,he ask him self morethan three times why Aj thanks him like that?daga karshe dai ya yanke shawarar kiran layin nasa....

Kiran wayar Ammar ne yashigo a wayan Dr aj inda naga an rubuta bloody yanaganin kiran yadakale,wani kiran ne yasake shigowa awayantasa,yayi kwafa yana picking call din cikin jin haushinsa,wayan yasanya akunnensa yayi shiru,A bangaren Dr ammar shima shirun ce tabiyo baya,A hankali ya furta kai ka turo mun sako dan yakara tabbawatarwa duk da yaga numban sa ce..

shiru dr.aj yayi masa yak'i kara cewa duk sa yaji yamaimata masa tambayar,shiru ne yabiyo baya Dr ammar yagama tambayar shi....

.....Allah sarki Dr.AJ Bawan Allah Kana hak'uri.

Dr.Aj ne ya katse shirun nasu YAna watsar da tambayar da ammar yake masa,dacewa banga motar ba ni yanzu ma ina nan gefen titi inda motar ta tsaya nida bodyguard dina,shiru Dr.ammar yayi yana sauraren Aj yana k'ara tunano da sak'on da ya rubuto masa na godiya...

No wonder shiyasa ashe yayi masa godiya ashe yaron da ya tura bai kaimasa motar ba,to meya faru?ya tambayi kansa,iee zuwa wannan lokacin da yake maganr zuci har ya fara hasala zuciyar ta maza ta motsa,katse kiran yayi,yazari car key dasauri da wayar sa a hannu yafito bai zarce ko ina ba sai inda had'addun motocinsu suke parkey gwanin burgewa, kamar motocin DLD😁.....

Bodyguard dinsa naganinsa suka taso da sauri dakatar da su yayi ta hanyar d'aga musu hannu,cikin katsa musu tsawa ya furta musu cikin harshen turanci "what d hell are you fucking to do guys? Duk sukayi shiru suna zare ido cikin yanayin tsoro sudai asanin su basu masa komai ba kuma ba halinsa bane.....

To meya hasala haka?d'ai daga cikin sune yafurta sorrry sir may be he does'nt have charge and he don't want to tell you directly sir,dan yafahimci inda bacin ran na ogansu yasamo asali tunda yaga haryanzu enuuch bai dawo ba wanda ya bawa Car key...

Dr.Ammar komai bai cemasa ba yadanna makullin haddadiyar motar dake hannunsa dan danan had'addiyar motar farar motar kirar lemozing ta bude kanta gwanin burgewa murfin yanayin sama,shigewa sa yayi ahankali yadannan wani abu acikin motar ta rufe da kanta kamar ba,a budeta ba,mai gadinsu wanda yake d'ai daga cikin yarannasu ne ya wangale katon gate din gidan ganin ogan nasu ya doso wurin gate tafiyar minti uku ta kawo sa bakin gate din gidan wanda yake wangale,yana isowa yataka wani burki yana zuge glass din motar,yana furta kabawa sauran yan uwanku sako kar wanda yabiyoni in nafita i want be alone,yakai karshen maganar cikin bada umurni,dan ya hango su sun shisshiga motocinsu ,cikin rusunar da kai ya furta yes sir dan shi bai san abinda ke faruwa ba saboda shi nashi aikin tsaron gate ne.....

Fa'eeh Bg

ba yawa kuyi manage dashi

Banda lafiya ne,Ina barar addu,arku

To be continue tomorrow in sha Allah

Pls Dan Allah kurika comment domin shine kwarin gwaiwarmu

like share nd comment pls

□A MAFARKI NASANTA□

in my dream i know her

By

Pha'eezah Almstapha

Daga Alkalamin ✍✍

□Fa'eeh Bg□

Dedicated to my lovely sis laila Almustapha Murai□

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand □

ESSENTIAL WRITER'S*

pen is mightier than the sword*

EPISODE1

FREE PAGE12

TYPING □□□

Announcement

Ina tunatar daku A mafarki nasanta ba free book bane,yanzu muna kan free pages ne da mungama free pages za,a fara payment.....gamasu bukata□

~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~

Yana gama maganar sa ya figi motar da karfi jikake tana wani k'uuw,suma yaran sa dake bayan sa ahankali suka tada nasu motocin bayan fitar sa gate suka duk da sun hango gate man yana kokarin rufe k'ofa.....
~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~

Suna isowa bakin d'in suka dakata,d'aya daga cikin su ne ya furta sir bude muna gate d'in ,saboda dukansu ya girme su,shiyasa aka bashi tsaron gate...

A hankali wannan tsohon gate man din ya mayar musu da amsa cikin yaren india domin shi baya jin turanci,ya furta Dr.yace kar wanda yabisa,jin wannnan magana tasa ta tayar musu da Hankali,shi bai ma san yadda abun yake ba sai da suka sanar dashi,an aiki enuch da mota yakaiwa Dr.Aj amma har yanzu bai je ba,kuma meeting din na gaggawa zaije....

Dan danan hankalin sa yatashi,dan dukkansu sun san muhimmancin wannan meeting da uwayen gidansu zasuje,saboda meeting ne daya tara manyan likitoci na kasashe daban daban,gashi d'ayansu bai je ba tun da in d'aya yaje a wani lokacin ya isar sai d'aya yayi attending a system live ta hanyar comference call da ake hadawa ga wayenda basu samu damar halarta ba..

Jimami suke atsakaninsu,d'aya daga cikin sune yayi k'arfin halin furta guys muna cikin matsala idan wani yasamu Dr.bazamuji dad'i ba domin munyi ma gwamnati rantsuwar karemata su,kuma munyi rantsuwa ga abun bauta shiva,dan haka dole mu daure hakan nan mubisa duk da yayi warning namu ......Ga ra nasa fushin da wanda lord shiva zai yi damu

.....Kunsan indiyawa da rikon Addini.....

Allah yakyauta,yakara tsare muna imanin mu

Bayan sunyi na,am da maganar ta dan uwansu sai suka nemi gate man da ya bud'e musu gate din wanda shima yayi na,am da shawarar tasu duk da shi musulmi ne,duk da kuma ta wani gefen yana jin shakku,wanda suma sauran duk hakance azukatansu.....

.....nima dai anan alkalamina yakara k'aimi wajen dauko muku rahoto.....Ku cigaba da bibiyata.....

Fa'eeh Bg

Ficewa sukayi atsare cikin gidan a cikin manyan2 motocinsu kirar hillux da wasu daga cikin normal car nasu bakake wulik,bayan wangale musu gate d'in da yayi..

****

Suna fita ya rufe gate din yana jimamin Abinda zai biyo baya.

A bangaren Dr.Ammar kuwa bayan fitar sa bai zarce ko ina ba sai inda Dr aj sukayi parking na motocinsu,Domin gudu ne yayi ba d'an kad'an ba, ta hanyar amfani da Gps tracking ya isa inda suke, A hankali ya tunkari motar da Aj yake ciki duk da yaji gaisuwar da yaran suke masa amma ba wanda ya tankama,Dr aj dake cikin mota har sakon zuwan Dr.Ammar ya iso masa ta hanyar Babban yaronsa dake gefen motar atsaye....

A hankali yaron Dr aj dake atsaye kusada murfi motar ya bu'de masa murfin bayan motar ,mai makon ya shiga sai yayi tsaye yana k'arewa cikin motar kallo,Bayan kamar minti biyu yasanya yasanya k'afarsa d'aya a hankali ya zauna yana mai k'ara tamke kyakkyawar fuskarsa,A hankali itama dayar leg dinshi ya janyeta zuwa cikin motar kamar wanda ankayiwa dole shiga,shiko Dr.Aj duk da yasan da zuwansa kuma yaga shigowarsa bai nuna masa ba yamai da hankalinsa kan meeting d'in da yake kallo live a yar madaidaiciyar tvn dake makale akujerar driver,wanda ake gudanarwa ahadadden hall na garin mumbai mai suna.....

(MUMBAI EXPENSIVE HALL)

wanda shine Babban hall wanda gwamnatin india ta zube mak'uddan kudade gurin ginshi,wanda yaji kayan more rayuwa ta ko ina....

Shima Dr.Ammar baice masa uffan ba kawai yayi joining meeting din ta hanyar kunna tvn dake bayan kujerar dake gabansa tare da makala bluthood a kunnen sa kamar yadda aj din yayi,cigaba da kallon yadda meeting d'in ke gudana sukayi,Bayan yayi joining duk wanda ke gurin yaga Dr ammar A hankali sukayi ta daga masa hannu alamar gaisuwa shima yana d'aga musu .....Bayan sungama gaisawa suka ci gaba da gudanar da meeting din su kamar yadda suka fara banbancin kawai dr.Ammar ayanzu yana musu yan gyare gyare ne,ko yayi solving wani issue tunda duk suna ganinsa ..

Dr.Aj ba abunda yake face murmushi da alhinin halayen dan uwan nasa baiyi zaton zaiyi joining meeting ba haka,ganin rigimar da suka sha tashi bazai je ba sai dai shi yaje ya wakilcesu,haka dai suka gama gudanar da meeting din atsanake har suka kai matsaya sukayi conclusion suka watse,sukuma suka kashe tvn....

Enucch ne yak'araso jiki asanyaye bayan ganin motar ta uban gidan nasa,Parkeyn yayi agefe,ya gaiggaisa da "yan uwansa,tsaye yayi gefen da ogan nasa yake,Bayan tsayuwar da minti biyar sai ga sauran bodyguard din sun iso gurin ta yin amfani da location,duk suka firfito daga cikin motocin su a hargitse.....

A bangaren su Dr aj kuwa bayan gama meeting din su,shiru ne yabiyo baya,Dr aj yakatse shirun nasu ta hanyar furtawa Dr ammar wanda ke jingine da sit dinsa idanunsa alumshe,cikin murmushi "meya ka woka nan"shiru yayi masa duk da yana jin sa,"fitar mun amota"

wannan furuci na Dr aj ne yasanya sa a hankali ware manyan idanunsa masu cike da kwarjini da haske ga kwayar idonsa maroon mai shining,Kafe aj yayi dasu wanda har sai da Dr aj yakara ja baya yana furta lafiya?

Shiko uban gayyar murmushi ne ya wanzu akan kyakkyawr fuskar sa,yana ficewa daga cikin motar koda yafito enucch ya fara cin karo bawan Allah yana ta kame kame am yallab'ai sir kayi hakuri wallahi namanta wayana a gida kuma ina tsoron komawa gida bayan nayi nisa karkaga kamar namaka rainin wayau ko yanzu ma su joshu ne nakira da karamin wayana suka min kwatancen gurin (dai daga cikin yaran aj).....

~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~

Duk wannnan maganar yanayinta da indiancine saboda shina bai jin turanci,kuma duk abunda yake fadi dr ammar najinsa sai dai bai ce masa komaiba har ya isa inda ya parka motarsa yaren sa dake gurin duk suka taso da hannu ya dakatar dasu yana shigewar sa motarsa .....

Reverse yayi yabata wuta sai kan titi tare da shara raara gudunsa,shima dr aj umurnin ya bawa yaransa wanda cikin minti daya suka bar wurin har yaran dr ammar din....

~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~~

Alkalamin Fa'eeh Bg mai kaifi ne kamar wuk'a,kucigaba da bibiyata dan jin karshen wannan labari mai cike da abun tausayi,soyayya,cin amana,ta,addanci duk acikin littafin amafarki nasanta....Nasan wasu zasuce ai haryanzu ba,a fara nuna mafarkin ba😂to karku damu kudai sanya hakuri duk zamu kai chan .....

Dan Allah kurka comment domin shine kwarin gwiwarmu akoda yaushe

A MAFARKI NASANTA

in my dream i know her

By

Pha'eezah Almstapha

Daga Alkalamin ✍✍

Fa'eeh Bg

Dedicated to my lovely sis laila Almustapha Murai

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S*

pen is mightier than the sword*

EPISODE1

FREE PAGE13&14

TYPING □□□

Lokacin da Dr.ammar yatashi motar Sa har ya hau kan titi duk akan idon Dr aj murmushi kad'ai yayi yana girgiza kansa....

A b'angaren Dr .ammar kuwa yana kawowa bakin gate d'in gidan ya dannan horn sai ga k'aton gate din yana wangalewa,Wanda dama gate man din yana kusa da controller din gate din ya bude masa.

Yasanya hancin motar cikin katafaren gidan nasu yana dosar parking space,bayan yayi parking dinta a inda yadace

Ya fito da had'addiyar kafar sa mai sanye da wasu rufaffun takalma boot masu kyau milk colour sannan a ahankali yasanyo dayar waje tare da gangar jikinsa,mik'a yayi sai kuma a hankali yafara takawa bayan rufe motar tahanyar danna key din dake hannunsa,katon falon nasu ya nufa zama yayi daya daga cikin cusion dake d'akin yana sauke nannauyiyar ajiyar zuciya,sai kuma ahankali ya lumshe idanunsa....

Motocin su Dr.Aj ne suka shararo harabar gidan bayan bude musu gate da akayi,A hankali suke diddirowa daga motocinsu,wanda shima dr aj yafito daga motar tasa bayan bude mishi kofar da bodyguard dinsa yayi.

Kofar shiga falon yadosa,sukuma sauran yaran suka gyara parking nasu...Sallamar da yayi ce tadawo dr ammar tunanin zucin daya kasance masa dole akullum inyayi mafarkin nan nasa to duk yinin ranar zai kasance acikin tunanin sa ne,badai natsuwar zuciya,

A hankali ya bud'e manyan idanunsa da suka dan fara sauyawa na damuwa,ya dora su akan,Dr al amin aj,dake gefen sa wanda har yazauna ma,A hankali kuma yadauke idanunsa kan aj din wanda shima kallonsa nasa yake yi dan ya fahimci kamar akwai damuwa a fuskar dan uwan nasa.....

A hankali dr.Aj yafurta masa meye matsalar dude,shirun daya masa shi yakara tabbatar masa da zarginsa na cewa tunanin dake kezo masa arai bazasu wuce

mafarkinsa ba da kuma mahaifinsa, sai mahaifiyar wadda ke yawan yin fushi dashi akan sarautar da baida ra,ayi kanta...

Bayan ya k'ara k'are masa kallo sai kuma yadafashi ahankali yana furta calm down man anything will be fine ohk!yakai karshen maganar cikin tausayin dan uwan nasa....

A hankali kuwa Dr.Ammar yaware manyan idanunsa kan dr aj sannan yacire hannunsa da ke kan kafadarsa ya mik'e a hankali ya doshi upstair har yafara taka step na daya na biyu sai ya juyo a hankali yadan kalli aj dake zaune kan rugs yana kallonsa,A hankali kamar bai son yin maganar irin an masa dole cikin zazzakar muryar sa mai yanayin natsuwa ya furta wa dr aj thanks,wanda koshi dan saboda hankalin sa nagaresa ne da bazai ji abunda ya furta ba da iya labbansa ....

Yana gama maganar ya cigaba da tafiyarsa,shiko dr aj murmushi kad'ai yayi yana girgiza kansa,dan hangosa da yayi ya lakaci tsinin hancin wanda alamace dake nuna yana cikin yanayi mai dad'i,Shigar sa haddadden falon nasa wanda yake ko ina tsaf ank'ara gyarashi bayan fitarshi,takalmin sa ya fara cire da safarsa bayan yazauna akan rugs dake dakin masu taushi bayan kamar minti biyar ya bude idanunsa dake alumshe bayansa najingine da kujerar ya mike ahankali ya wuce yashige had'adden bedroom nasa,yana maida takalimin a inda suke,Kayan jikin sa ya fara cirewa a hankali komai yana yinsa atsare kamar wata mace yana gamawa yajawo d'ai daga cikin towel nashi dake cikin sip sabbin kal yad'aura nan take hadaddiyar surar shi takara bayyanar da kanta ga lallausar cholcolate skin din sa sai kyalli takeyi....

Toilet yayi shigewar sa cikin takun kasaita,kansa yasakarwa shower ruwan masu dan dimi suna dukan sa atsaye idanunsa alumshe,bayan ruwan sun duke sa sosai sai yadannan wani abu take shower din yatsaya,kan hadadden katon bahon wankansa na kwalba wanda kana iya hango na waje daga ciki amma shi bazai iya ganin ka ba,yashige bayan ya cire towel nasa yajefa shi a cikin haddaden washing machine na cikin toilet din..

ya dade acikin bahon wanka inda yayi nutse,sannna ya dauro wanka sa da turarrukansa da shower gel mai kamshi,a natse yafito yana takawa in da jerin towel din sa suke da bathrobe,wata farar batherobe yajawo fara kar gwanin burgewa domin shi Allah yamishi son farar kala shiyasa zaka mafi yawan komai nasa farine,bayan yasanya ta ne yajawo dai daga cikin kananan towel dake wurin ya daura akansa bayan yagoge kansa dashi,kansa yake karewa kallo amadubi dake cikin toilet din....

Ficewa yayi ahankali cikin toilet din bayan yagama tsayuwar sa abakin mirror din yana karema kansa kallo...

Stool din dake gaban kamfacecen madubinsa dake shake da kayan gyara jere gwanin burgewa...

Cigaba da goge gashin kansa yayi mai taushi da walkiya,bayan yazauna,bayan kamar minti uku ya goge gashin kan nasa da sauran danshin ruwan dake jikinsa,yafara murza mansa na fata mai sanyayyen kamshi kamar turare lungu da sako haka yake murza man nasa akan fatar sa,bayan yagama neyajawo hair cream nasa mai kyau mai kara ma gashin sa sheki ya murzasa tare da taje sa,dan danan kyawon sa yakara bayyana sumar kansa sai sheki takeyi,lipsbalm din sa yashafa akan

kyakkyawan labban sa pink colour masu laushi,turarukkansa ya fesa tunda kan body spray oud masu kamshi,kala kala wanada akalla zasu kai guda biyar,kan sipdinsa yakoma inda yadan thumprint take kuwa sipdin ya shiga bude kansa,sashen da yake na under wears da short trouser yamatsa,jawo dai daga cikin short trousers din yayi sky blue color da short fari da kuma best fara sai yakoma sashen armless yazaro mai layin blue ajikin yana gamawa yadanna abun rufewa take ta rufe ruf,cikin natsuwa yafara shirinsa.

Fa'eeh Bg

A b'angaren dr. aj shima bayan wucewar dr ammar ya wuce shi dake kusa da na Ammar din daga gefen damar shi dakin yaji komai na more rayuwa,banbancin dakin shine cusion shi nashi maroon color ne dan shi kalar na matukar burgesa da fari kamar dr ammar din.....

---

* Nikam ban ga laifin ku ba domin farar kala tayi,ko mala'ku kagani masu farin kaya tokai kawuce wurin,a kabarin mu ma sune suturar mu domin sune suturar mu takarshe a duniya,Annabi muhammad s a w farin kaya yake sakawa duk ranar idi,haka ma ranar juma,a wannan yana dai daga cikin sunnoninsa...Allah yasa mudace yasa muyi kyakkyawan karshe,Yasa da mu da mala'kun rahama*

---

shima dai yashityawr sa tsaf cikin irin kayan dr ammar.

A hankali yake taka step step din da wayar sa a hannusa dayan hannun kuma acikin aljihun wandonsa yana tafiya dai dai cikin izza daga yanayin tafiyar kasan ta zaratan maza ce wadanda suka da mulki iko...

Kamshin turarensa ne yasanya dr aj dagowa daga kan wayar sa dayake kan preesing,wanda ke zaune akan dining table wanda shima bai dade da fitowa ba....

A hankali yatako izuwa kan dining har ya iso inda aj yake,cikin sanyin murya ta gwarazan maza ya furtawa aj lafiya?yana mai jan kujerar dake facing dr aj,ganin ya tsare sa da idanu,zama yayi yana ajiye wayar tasa agefensa.

Murmushi kawai dr aj yayi yana furta dude dole dr malini ta zauce wannan madarar kyau haka,ya k'une kyakkyawar fuskar sa yayi jin furucin dr aj din yana sakin karamar tsuka wadda aj kadai yajita shida yake kusa dashi " mts",murmushi kawai aj yayi yana aje wayar tasa agefe...

kukunsu ne sajid khan yakaraso yana fadin afternoon sir yana mai kokarin yin serve na dr ammar,dakatar dashi yayi,da hannu,sai kuma ahankali yajawo dai daga cikin haddadun filet din dake kan dining din yafara saving kanshi,farar shimkafa da miyar da taji na man sa yadiba sannan yajawo wani filet din ya debi hadadden farfesun kaji wanda yaji hadi sai tashin kamshi yake yi.

A hankali cin abincinsa dan shi kam ingurin ci ne bai wasa da cikin...

Aj dayake ganin duk abunda ke faruwa murmusawa kadai yayi dan dama yasan abunda zai faru kenan,kusan kullum haka suke shida sajidkhan indai yazo zai zuba

masa abinci cewa yakeyi baiso duk da zaman kukun nasu musulmi,dan shi mutun ne mai bakar tsandar tsiya,ansha chanja musu masu dafa abinci saboda shi,sai akan wannan ne haryanzu baiyi complain ba,shi abun ma dariya yake basa da haushi mutun ya girka abinci amma kace baka son yayi serve naka saboda bak'ar rigima,kara girgiza kansa yayi yana cigaba da cin abincinsa da sajidkhan ya zuba masa....

Motsin chokulla kadai ke tashi a falon sai karar ac,dr aj ne yayi ma kukun alama da ya wuce kawai,a hankali ya dago kansa ya kallesu duk su biyun cikin second guda yamayar da kansa kasa yacigaba da cin abincinsa.....

Bayan wucewar sajidkhan kitchen suka cigaba da cin abincinsu hankali kwance.

Karar shigowar sako ne a wayan dr ammar yasaka dr aj dago kansa yakallesa,a lokacin shima yadagi nasa,ido daya dr aj yakashe masa yana sakin kayataccen murmushi dan tabbas yasan sak'on wayene yashigo wayar ammar din,shikam dr ammar duk da yaga abunda Aj din yamasa bai nuna ba sai ma cigaba da cin abincinsa da yayi hankali kwance yana mai kara tamke fuskar sa.

Aj yana gama cin abincinsa ya mike tare da daukar wayar yana barin kan dining table din .....

A hankli dr ammar shima ya mike yabar kan dining a hankali fuskar nan a tamke,a falo shima yazauna kan 3 sitter wanda shikuma aj yana kan 2sitter yana pressing phonedinsa.

kyawawan kafafunsa ya mike yana mai daura hadadden throwpillow akan dan shafafen cikin sa,har yakwanta kuma meya tuna sai ya mike zaune yana jawo wayarsa dake gefen kafens,thumprint yadanna wanda take takawo haske har yayi niyyar ya wuce sakon da yaga anturo da private number ,sai kuma yaji yana kwad'ayin bud'esa,abunda yaci karo dashi ne ybasa mamaki dan shi baiji alamar shigowar sakon ba dan yaga sako biyu ne suka bayyana na biyunne wanda yaji shigowar sa shine na dr malini nafarkon baiji shigowar sa ba,ya karanta sakon ya fi akirga har private number din yake karantawa,inda na leka kan wayar dan ganin abunda aka basa mamaki dan shi baiji alamar shigowar sakon ba dan yaga sako biyu ne suka bayyana na biyun ne wanda yaji shigowar sa shine na dr. malini na farkon baiji shigowar sa ba,ya karanta sakon ya fi akirga har private number din Da yabayyana yake karantawa,inda na lek'a kan wayar dan ganin abunda sakon ya k'unsa nan naci karo da rubutu kamar haka da manyan haruffa da yaren mu na hausa "¿KA NEMI YAR UWARKA TANA RAYE¿?"

.....Tambayar kansa yake yi waya turo sak'on ?...ba amsa ¿

Nima dai kaina yad'aure kowa cece wannan yar uwartasa oho?kuma a waya turo sak'on ????????nima dai ana n alkalamina ya fadi.....,kucigaba da bibiyar akalamin✍ ✍ Fa'eeh Bg domin warware muku duk wani abun da yashige muku duhu acikin littafin a mafarki nasanta..... Kuyi hakuri da

 rashin samun update jiya hakan yazo sanadiyyar rashin chaji da banida.....

Shiyasa ma na had'a muku page biyu..

Comment kadai nake bukata ko like

Sannan plskutayani sharing

inayin ku percent a mafarki nasanta fans over Allah yabark kauna

A MAFARKI

NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh Bg

Dedicated to my lovely sis Laila Almustapha

Murai

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S*

Pen is mightier than the sword

EPISODE1

FREE PAGE15

TYPING

****

****

****

****

***

**

*

Ina mai kara baku hakuri akan abunda yafaru in sha Allah hakan bazata sake faruwa ba domin mun dau kwakkwaran mataki na farko link dinmu na wannan sabon group bazai fita ko ina ba,sai wanda muka ga dama muka saka..

....Rasa mai basa amsa ne,da kuma wanda zai warware masa sakon ne yasanya shi goge sa gaba d'aya.

Sai sak'o na biyu wanda atak'aice yabud'esa ya karanta inda sak'on yak'unshi kalaman soyayya masu zafi da tsayawa arai da yanayin tausayi acikin kalmomin,ko k'ir baiji ba alokacin da yake karan ta wannan sak'on na Dr.Malini yana gama karanta wannan sak'o na dr.Malini ya gogeshi yana jan k'aramaar tsuka...

Tare da jawo tv control yana kara volume da bayan chanza tasha izuwa ta labarai,cigaba da kallon labaran sa yayi hankali kwance duk da tunanin wannan sak'o da yad'an tsaya masa arai,shidai aj duk da yaga yadda dr ammar yake ta kallon screen d'in wayar sa da alamun mamaki da rud'u bai bai matsa wa kansa da son tambayar sa ba,dan ya fahimci akwai abunda dr AA yake b'oye masa ayanzu k'ila sak'on sirrine duk da baisan ta ina sak'on zai fitoba,to wane kalan sirri ne wanda Dr.Ammar zai b'oye masa oho?ba amsa yakice tunanin da yake aran sa yayi jin sallamar d'ai daga cikin yaran nasu yana neman izinin shigowa.....

Gate man ne yashigo dama shi musulmi ne daga cikinsu kuma yagirme musu...

Hannu dr.ammar yad'aga masa yana basa izinin shigowa bayan amsa sallamar sa dasuka yi, A bangaren dr aj tunani yake aransa meya tado da gate man yanzu...

Bai gama tunanin sa ba yaji gate man din wanda yake da kagansa kaga tsufa atattare dashi yana furta sir gani naga kiran dakamun,aj ya furta wa kansa ohh ashe ammar ne yakirasa ko saboda me,?rasa mai basa amsa yasanya shi zubamusu idanu su biyun....

A hankali Dr.Ammar yad'ago kansa suka had'a ido da dr.aj saurin d'auke kansa yayi tare da lumshe idanunsa,yana mai bud'e bakinsa a hankali ya ce da wannnan tsohon

mai gadi "hv a seat father"murmushi kawai tsohon yayi mai suna sabirkhan cikakken ba indiye,yana furta aa'ah sir nagode,aj dai kallon su kawai yake suka gaisa da tsohon baik'ara cemasa komai ba.....

A hankali dr Ammar yak'ara maida kansa k'asa bayan jin amsar da tsohon ya basa ya yi rejecting request nasa,bayan ya bud'e idanunsa dake lumshe,sai yaji duk baiji dad'i ba danshi kam yana darajja tsofaffi kuma yana tausayinsu,har yanajin hukuncin da yake son ya yanke kamar yafasa na korarsu gaba d'ayansu da nufin akawo musu wasu sabbi tunda wad'annan basa aikin su yadda yadace danshi baisan kuskure ba,cewa yake gangancine,duk da baiso aka basu suba tun farko.....

Bayan gama zancen zucinsa ne ya bud'e dan k'aramin bakin dan karamin bakin sa mai dauke da pink lips da suka sha lipsbalm sai glowing suke,father

Could I ask you to move a little?you and your colleques sannan ya cigaba da maganar sa da yaren india ga tsohon tunawa da yayi baijin english cikin kwarewa da yaren ,har yagama maganar sa sabirkhan bai ce komai ba face murmushin da yake ta saki,sai da yagama ya furta masa sorry sir,ya juya yayi wucewarsa .....

Bayan fitar sa shikam aj da yacika da mamaki dan wannan ne karo na farko da yaji aj ya yanke game dasu batare da shawararshi ba,cikin kafe ammar da idanu ya furta saboda me ?zaka nemi su matsa daga nan gidan kuma har da suspension na wata daya eh?

yana mai cigaba da tuhumarsa da idanu,Cikin halin ko inkula kamar bazai amsa ba sai kuma ya furtamasa ra,ayi yana gama fad'in maganar sa yatashi da wayar sa ahannu yayi wucewrsa upstair zuwa bedroom nasa,da ido kad'ai aj yabisa yana girgiza kansa,shima yana mik'ewa ya fice compound din su domin dakatar dasu,bayan yafito ne yatarar dasu cirko cirko atsakiyar compound d'in atsaye suna jimamin umurnin ogan nasu,bayan ya gama kallon gaba daya tare da karantar yanayinsu,yayi gyaran murya,duk suka hankalta dashi suka fara mik'a masa gaisuwa yana amsawa musu cikin sakin fuska....

a hankali ya furta musu kar wanda yaje ko ina nasan ko mene zuwa anjima zai bar maganar zan shawo kansa..

Duk sai sukayi na,am da maganarsa,yacigaba da magana nasan abunda kuke tsoro kar gwamnati taji abunda yafaru na suspension din da yabaku,namuku alkawaro bawanda zaiji,nasan cewa incident din da yafaru d'azu da safe ne yasanya sa baku wnnnan hukuncin duk da banga alamar fushi afuskarsa ba,dan shi mutun mutune wanda baicika bayyyanar da fushinsa ba...

Godiya duk suka masu nuna jin dad'i har ya juya sai sabirkhan ya tsaidashi ta hanyar fad'in sir,juyowa yayi dan ga tsoho sabirkhan yace da aj yallab'ai ban tari numafashinka ba,amma inaga da kabar hukuncin yadda yake saboda ina da tabbacin duk wannnan abun akan ka yayasa saboda fahimtaar da yayi ranka ya sosu alokacin da aya aika akaima maka mota,kuma ba,aje da wuri ba,shiyasa,dan nima na fahimci bada son ransa ya furta musu maganar suspension ba ,shiyasa tunda yafara

maganar sa ban nuna alamun b'acin rai afuskata ba sai dai murmushi da ya wanzu akanta,inda ka lura ko d'ago kansa baison yi gudun had'a ido dani,kabarshi kawai dan inyaga katsaidamu zaiga kamar ka kwatse sane.....

Murmushi kawai aj keyi har zuwa lokacin da tsohon nan yagama maganar sa,yak'ara da cewa kuma inada tabbacin ransa ya b'aci matuk'a dan naga alamar hakan alokacin da zai fita suka biyosa ya furta bai bukatar kowa ya bisa acikinsu....Kuma kasan halinsa baison ya sanya doka atake,nasan wani laifin ne kuma binsa da sukayi,mukuma yallabai kasan munyi rantsuwa akan zamu kare ku ta ko wanne yanayi kuma nasan kasan mahimmancin rantsuwa.

Uhmm aj ya furta yana mai girgiza kansa tare da sakin murmushi a fuskarsa,toh shikenan father dan haka suke kiran tsoho sabirkhan,kuje amma nan da kwana uku ku dawo nasan zuwa lokacin ya sauka ya furta musu,touh suka amsa masa dashi.Suka fara watseqa suna shisshiga motocinsu domin zuwa quaters nasu dake chan gaba da gidan su aj,bayan sun mimmika car keys ga aj dakuma gate controller...

Dr.Ammmar dake chan tsaye kan windown din dakinsa ne ya furzar da iska mai zafi abakinsa yana mai jin ba dad'i aransa duk da yasan yayi ne dan ya farantaran dan uwansa,A hankali yabar bakin window din yana komawa kan hadadden gadonsa ya kwanta flat yana kallon ceilling daga shi sai towel dama fitowar sa daga wanka kenan....

Aj nashiga shima ya wuce nasa dakin wanda izuwa lokacin har ankara gyara falon sai tashin kamshi yakeyi ankwshe food flask din dasuka ci abinci angyara lungu da sako sai sanyin ac daya kara ma falon natsuwa ko ina masha Allah.

□□Fa'eeh BG□□

Aj ne bayan shigarsa nasa dakin ya aje car keys din da gate controller din ya jawo wayar sa yana dialing numban sabirkhan gate man....

Bayan yad'aga kiran sun gaisa cikin mutunci,tambayar sa yayi daya turo mai dai daga cikin yaransu wanda zai kula da gate din kafin su dawo aiki to kawai yace sannan sukayi sallama...

A b'angaren dr.Ammar nan bacci yakwasheshi bai farka ba sai dayaji ana kiraye kirayen sallar la,asar,A hankali kiran sallar ke shiga kunnuwansa mikewa yayi a hankali yana addu,ar tashi daga bacci tare da ambaton kalmatu shahada.....fuskarsa yake yamutsa wa bayan duba hadadden agogon dake kan bedsite drowernsa hud'u dai dai ya gani ta buga shi yasanya sa tashi da hanzari dan yaga lokacin yayi kusa,ankusa tada sallah,shaf shaf yashiga wanka bayan yayi brush yayi wankansa tare da dauro alwallah,bayan yafito tsane jikinsa dayayi turare kadai ya fesa sannnan ya bude sip din sa yazaro dai daga cikin jallabiyoyinsa da short,da vest baka dasauri yazura jallabiyar bayan sanya underwears din yasauka kasa yana ta sakin kamshi,koda yasauko kasa yatarar da aj tsaye yana jiransa,shima cikin shirin jallabiya irinta dr ammar sai dai banbancin colour shi aj tashi fara shikuma ammar dark maroon wadda ta karbi fatarsa,ba wanda yaceda dan uwansa kala har suka fita falon suka shigamota aj yajasu zuwa masallaci....Dama mai gadin ya iso yakarb'i gate

controller din suna zuwa ya wanagale musu gate din ta hanyar danna remote din,yau da mota suka fita ganin sun makara ,duk da masallacin basu da nisa dashi cikin unguwar tasu ta manyan masu naira maisuna gujarat 105 estate.....

Next page monday in sha Allah

Like pls...Nd comment

* Allah yasa mudace*□□

Pls like share and comment

□ A MAFARKI NASANTA□

In my dream i know her

By

pha,eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

□ P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S

Pen*is mightier than the sword*

EPISODE1

FREE PAGE16

TYPING □□□

----------*DRUG ABUSE

□□□□

SHAYE SHAYE ILLANE GA RAYUWARMU,INA SAMARI, INA YAN MATA KU GUJI TA AMMALI DA MIYAGUN K'WAYOYI DOMIN SUNE ABU MAFI SAURIN HALLAKAR DA RAYUWAR MU....MUNA□□□ KIRA DA BABBAR MURYA,DAKUMA BADA SHAWARA A GUJEWA DUK WANI KAYAN MAYE DAN SAMUN INGANTACCIYAR RAYUWA MAI AMFANI*

HANYOYIN DA ZAKA KARE KANKA□ DAGA AIKATA WANNAN DABI'A SUNE

*KAUCEWA ABOKAN BANZA

*ZAMA DA MUTANE NA GARI

*SANYA TSORON ALLAH AZUCIYAH

*BADA SHAWARA TA KWARAI GAMASU AIKATAWA

*CIRE KWOKWANTO GA AL AMURRANKA

*KAUCEWA MASU AIKATAWA

*YADDA DA KADDARA KO WACE IRI CE ILLA MAI KYAU CE KO MARA KYAU CE.

□□MU KIYAYE DOMIN RAYUWAR MU ABA CE MAI AMFANI ATATTATARE DAMU,DOMIN AMANA CE UBANGIJI YA BAMU....ALLAH KAYIMUNA MUWAFAK'A□□

****

*****

***

**

*Bayan sun dawo daga masallaci suka cigaba da kallonsu afalo a tashar da ake hasko wasan ball, har magriba ta gabato suka dunguma akafa sukaje a wannnan karon domin sauke farali...

"kowannen su dakin sa yawuce direct bayan bayan dawowar daga sallar dan fresh up,AA ne fara fitowa Dan bakar yunwar dayake ji shiyasa bai tsaya shiriritar sa ta shiryawa ba,dama yunwa ce kadai kesanta sa yayi gaggawar yin abu sa dasauri sai

kuma in yasan suna da tarin patient da zasu gani ko kuma akwai emergency case a hospital din....

A hankali ya doshi kan dinning din nasu yana baza kamshi cikin shigar short trouser fari da kuma vest blue wadda takara haska fatar sa ...

''zaman shi keda wuya sai ga sajidkhan dan dama yaga fitowar ogannasa daga tagar kitchen ta chan mai kallon dining,

"barka da dare yamasa sannnan yajawo pilet yana mai bud'e manyan food flask dake kan dining din masu kyau,duk da yaji bai amsa masa maganar sa sai ya furta sir mai za,a zuba maka,"Anything" ya furta atakaice

Tuwon semo ya zuba masa da miyar egusi da taji busasshen kifi,ya dora masa agabansa tare sa sanya masa spoon a ciki da zuba masa ruwa a karamin cup na glass da lemu,A hankali ya fara cin abincinsa,Aj da tun d'azu ya iso wurin yaga abunda yafaru yau Dr AA ne ya bari kuku ya zubamasa abunci...Yasan cewa bak'ar yinwa ce nanake da cikin sa shiyasa ya yadda amma da ba haka ba da kai tsaye zai dakatar dashi....

"Kansa kawai ya girgiza yana mamakin halin dan uwan nasa

"shima dai tuwon shinkafa da miyar wadda taji naman sa rago ya zaba,bismillah yayi cin abincinsa hankali kwance kamar ammar din,Muryar Dr ammar ce ta karad'e gurin yana mai furtawa sajidkhan "have me some water in a rubber"cikin calmly voice dinsa,ohk sir!ya furta, ruwan ya kawo masa aroba mai dan fadi

"hannunsa yacire dake kan spoon ya kada sa acikin robar ya ya wanke hannunsa sannna yasanya acikin filet din tuwonsa,Yunwar da yake ji bazata bar sa cin abin da spoon gani yake kamar yana bata masa time,domin shi mutunne da baya wasa da cikin sa,shiyasa ya cire spoon din yasanya tattausan hannunsa,mai da robar sajidkhan yayi kitchen ya maida robar ma,ajinta bayan yayi discard din ruwan..

Abincinsu suke ci hankali kwance,musamman dr.Ammar wanda kaikayi zaton manyan lomomi zaiyi daya sanya hannu sai dai ahanklai yake saka abincin adan karamin bakinsa cikin natsuwa kamar ma bai tauna tuwon..Yana gama cin semo dinsa yayima sajidkhan alamar akara masa,Sai yanuna masa na shinkafa,a wani sabon filet din ya cigaba da cin abincinsa hankali kwance..

Shikam Aj tuni yabar kan dining din yana waya wanda daga ji macece ta hanyar yadda yake mayar mata martani.....

Shima dr ammar nagama cin abincinsa ya mik'e ahankali ya wanke hannunsa a sink din dake gefen dining din,lura da akwai aikin da mai aikin nasu yake yi akitchen din....

Wayar sa yadauka kawai yawuce warsa falo cikin tafiyar kasaita wadda sarauta tagama ratsa jikinsa,da zuwan sa yazube akan 2 sitter yana lumshe idanunsa jinsa yafara dawowa nrml da yunwar da ta dibesa, bayan kamar minti biyu ya lura da wayar sa aj din keyi,wanda koba,a fad'a ba yasan sumayya ce yake waya da ita wadda ke bima aj din,Amma anfi kiranta da sumy ....

 Fa'eeh BG

Jin tambayar da yayima nacewa ina Auta husna ne yasanya sa kara tabbatarwa.

Ahankali ya kunna piano game yana bugawa cikin kwarewa da natsuwa,Maganar da aj yayi ce tasanyasa dakatar da game din,inda aj din ke furta wa sumy din kin raina ni ko sumayya tun yaushe nace kibar min wannna maganar amma bakya ji koh,yakai karshen maganar da yanayin hasala,cigaba da maganar yayi yana furta ki sani matsayi daya na dauke ku da ita,nace kibar mun maganar NISA domin kuwa itama kanwa ce agurina bayan wannnan babu komai,daga chan dayan bangaren naji ana furta sorry yaya aj,shiru yayi bai tankamata ba jin wata murya mai sanyi nakwala kiran sumy!sumy!wanda har sautin yake ratso kunnuwansa daga cikin wayar ..

Chanza firar da dayan bangaren akayi shi ya tabbatar yakara tabbatar masa da muryar da yaji,Ajiyar zuciya yasauke ab'oye ya makarnata ya furtamata kamar basu yi wannan gaisuwar ba inda take furtamasa ya aiki,lfylau ya furta itama tana furta karatu alhmdllh,Bayan jin ta amsa ma wadda ke kiran sunan nata,ta hanyar furta na,am nisa lafiya wannnan kira haka da murmushi a fuskarta ta furta kizo anfara shirin" imlie " dan suna matukar son shirin wanda starlife suke haskawa akullum mai dogon zango ,musamman nisa wadda sunan ta yake (yuhanisa)tana mugun son shirin dan ita takoyawa sumy sonsa,a cewar ta jarumin mijin imlie na farko yana kama da yaya aj dinta dan tana mugun son aj kamar ranta,sumy kadai tasan da maganar sai kuma wasu daga cikin kawayensu.....

Fahimtar da nisa tayi sumy waya take kuma da yayansu ganin yadda ta natsu,yasanya A hankali ta karaso kan gadon tana mai fadin allah yasa baiji ni ba tana rufe dan karamain bakinta,Murmushi ne ya subucewa dr.aj jin radar da tayuwa sumy,sannnan ya furtawa sumy bata wayar,A hankali sumee take mikamata wayar itama tana murmushi da addu,ar Allah yabawa kawartata ya yannasu ta yi wucewar ta falo...

A bangaren dr AA najinsan kuma yaciga da buga game dinsa,dan tun dazu Aj yamayar da wayar handsfree sanadiyyar rashin network na kirki da babu baiji sosai..

.....Shiru ne ya biyo baya bayan ta amshi wayar,A hankali tace yaya ina wuni murmushi yasaki yana furta kinmanta mu yanzu dare ne,laah ta furta tana rufe

bakinta mai kama dana yayanta,tamboyi yamata game da kart tana amsa masa da alhmdllh cikin dan rashin sakewa dashi

Shiru ne yabiyo baya sai kuma ta katse shirun nasu,ta hanyar furta masa ina yaya Ammar ?

yana jin sautin Muryar kanwartasa sai dai yayi kamar baiji ba,duk da kallon da aj ke masa domin sarai yasan yanajinsu ...

Jin tana magiyar abatashi inyana kusa yasanya a hanklai yabaro kan kujera din sa yake yadaw kan hannun kujerar da aj kezaune,dan jin raunanniyar muryar kanwartasa tana rkon akan kawai taji muryarsa yasan duk laifinsa ne da baya cewa abasu waya inyakira,tunda basu da waya har yanzu basu bada izinin abasu ba wayan saboda kallon kananan yara da suke musu,ganin haryanzu basu gama secondry ba,a yanzu suna ss 3ne akarshen shekara zasu gama..

Hello!"yaya A ta furta tana sakin kayataccen murmushinta da hr aj dake kusa dashi yaji sautinsa dan yacire handsfree din bayan amsar wayar daga hannun aj..

Shima murmushin yasaki yasaki har saida dimple dinsa suka loba gwanin burgewa dama ayanzu duk kaga murmushinsa irin haka mahaifiyar sa ce ko kanwarsa wadda takasance ita ce autar su,suna mugun son juna datausayin junansu musamman Babban yayannasu da ayanzu yake abun tausayi...

hw are u ?fn ta furtamasa,ya schl da krt yakara tambayar ta ta furta masa Alhmdllh,Anbar doja koh tace ce eh cikin murmushi toh acigaba da kokari duk da bai yadda da maganar taba yasan su da rashin son zuwa makaranta tun suna kananan .

A hankali ya tsinkayi muryar ta tana tamabayar sa,yaya A yaushe zaku zo kugammu? murmushi yasaki yana fadin ashe kina gidan maaminah yayi hakan ne dan kawar da tambayar tata,ehh ta furta yau sati na daya,ohk!ya furta tare da tambayar ta inasu husnat da sumayya,"duk suna falo ta furta to ki gaidasu,toh ta furta cikin sanyin jiki jin yakawar da tambayar da tamasa don dama ta harbo jiginsa....

Yanzu dai je ki bawa maaminah wayan dan haka yake kiran kanwar ta mahaifiyarsa,mahaifiyar Aj,Hajiya husaina,kai yaya batasan andauko wayanta ba nima na isko sumy da itane,kuma yanzu intaga mundauko fada zatayi,murmushi yayi dan yasan halin mamin da bata daukar wargi duk da zaman ta nason barkwanc,kuma dama yasan basu fada mata zasu dauka ba,tunda yasan basuda waya,murmushi yakara saki yana mai fadin "to kudaina daukar mata bada izininta ba,babu kyau hakan,kurika tambayarta indai kungayamata ta "ya 'yanku zaku kira zata baku kunji koh"tau yaya in sha Allah ta furta.....

"in sha Allah inkuka samu result mai kyau a qualified exams naku zan siya muku waya mai kyau,murmushi tasaki mai hade da dariy tana fadin dagaske yayah ,kansa yadaga kamar yana gabanta yana furta eh,i love you so much yayah,proud of you the best brother in the world takai karshen maganar cikin farin ciki marar misltuwa domin dama sun matsu asiya musu wayoyi saboda mafi yawancin kawayen su na da ita,"me

too ya furta cikin farincikin dayasamu kansa aciki Bye ki je ki aje waya yanzu kar taganku koh,toh yya tafurta tana masa godiya da sallama suna yanke kiran.....

Kowa ransa fess,cikin murmushin sa mai kara kawata fuskarsa ya juya ya dubi aj yana furta masa take your phone yana kara furta bari inje in dauro alwallah naga isha'i tagabato,da ohk kawai Aj ya bisa,shima yana mikewa yarage voluke din tv yana chanza tasha izuwa inda ake kira,ar qur'ani,ya wuce upstair shima tare da wayansa shaf shaf dukkaninsu suka dauro alwallah suka wuce masallaci don gabatar da sallar isha'i acikin jam'i....

Bayan dawowarsu aj kashe wutar falon da tvn kowa ya wuce nasa bedroom din dan yin bacci bayan sunyi sallama wannan kenan.....

BACK TO THE PRESENT .....

Murmushi kawai Dr aj yakara saki bayan gama tunano abunda yafaru kwana biyar da suka wuce yana mamakin hali irin na abokin nasa kuma dan uwansa.

Godiya bodyguard din nasu suka k'ara masa kafin suka koma gurin da dr .Ammar d'in yake tsaye shima suka kara masa godiya da basa hakuri,karbar jakar hannun sa daynsu yayi domin kaima sa office nasa.

Wanda shima bangaren dr aj hakance ta kasance agurinsa..

A hankali suka doshi hadadden hall din da yake cikin wannan katafaariyar asibitin ta mumbai wadda take da dubbanin tarihi na cigaban da ake samu ta hanyar kula da marassa lafiya shigarsu katafaren hall din daya tara dubbanin likitotah masu ji da kud'i da wanka,kowa yana zaune akan kujerar da take mallakinsa wadda ke dauke da sunansa.

A Hankali suka fara gudanar da taron cikin kwanciyar hankali,dama suna meeting din ne kan cases da ake yawan samu ne akan yawan mutuwar mata awajen haihuwa,suna son gano dalilin da silar faruwr hakan cikin alumma.....

.....

Kudai kucigaba da bibiyar alkalamina.....A sannu zan warware muku wannan labari maicike sa tausayi,nishadi ilman tawarwa,soyayya,sarauta,cin amana,ga xumuncibugu da kari kuma ta,addanci wanda yakasance abunda yake ciwa alummar mu tuwo akwarya ganin yadda shuwagabbani suka zuba ido aalamarin da har yanxu ankasa samun mai yin katutu da al amarin,ganin kamar sunfi karfinsu wanda kuma ba haka bane,mu munsan addua bata bar komai insunfikarfinsu ai basu fi karfin ubangiji ba....sannnu bata hana zuwa sai dai adade ba,aje inji hausawa,dan haka karku sanya kucigaba bibiyar labarin....

NEXT PAGE TOMORROW IN SHA ALLAH

KUTAYANI SHARING BOOK DIN NAN PLS DOMIN AKWAI DARASI MAI YAWA ACIKI .....

□ A MAFARKI NASANTA□

In my dream i know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

□P.E.W.A□

Home of perfect writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S

pen *Is mightier than the sword*

TYPING□□□

EPISODE1

FREE PAGE17

WANENE DR.AMMAR(AA)

cikakken sunansa Abdulrashid Aliyu Ahmad,haifaffen garin Gusau,jihar Zamfara,Dane Ga sarki Aliyu Murai,sunan mahaifiyarsa hassana hamza wadda suke kira da unni,mama kenan ayaren (korea) mahaifinsa da mahaifiyarsa Auren soyayya sukayi,kuma auren zumunta,Mahaifinsa sarki Aliyu murai rikakken Dan kasuwa ne,wanda yake da kaloli kuma manyan kamfanona akasashen daban daban a

duniya,A yanzu haka shine yake rike da sarautar ta zamfara A babbar masarautar murai ta Gusau'Ammar shine d'aa na farko ga iyayensa,sai mai bimasa hamza wanda yaci sunan kakansa na uwa,ana masa lakani da mahir,sai Auta yuhanisa inda taci sunan yayar kakarta ta uwa,suna kiranta da nisa,Ammar yana da shekara ishirin da takwas aduniya,mahir kuma yanada shekara goma sha biyar,sai nisa tana da shekara goma sha takwas aduniya,Mahaifiyar sa gimbiya hassana "yace ga wan mahaifin su sarki Ali Sarki,Hamza murai kenan,takasance yan biyu ita da mahaifiyar aj,sai autar su laila,sunan mahaifiyar su fateema suna kiranta Ammie,Ammar yaci sunan k'anin mahaifinsa Abdul rashid wanda shine autan su sarki Ali su uku ne maza,suna da mace daya mai suna khadija,suna kiranta mama dije wadda ke aure agarin kano tana auren wani custom,tana ya guda sunanta umaimah,wadda ita kadaice rabonta,tun rasuwar yan biyun ta na fari,sai kuma umar shine ke bima sarki Ali murai,Sai Abdul rashid ,sannan khadija,sunan mahaifiyar su sadiya suna kiranta hajiyar safkare,a takaice hajia,dukkanin su sunyi aure,.....Dr.Ammar yayi karatunsa tundaga secondry har tertiary a kasar india inda kuma kuma yasamu aiki achan shida aj,Dr ammar mutun ne mai tsantseni ga tsandar tsiya duk da yana da laziness bai yadda yasaka ma kansa kanzanta ba,baida daukar raini,dan gayu ne na asali,baida daukar raini,kuma bai da wulakanta talaka hasalima shi mai tausayinsune,mutun daya ne yake iya wa da halinsa shine dr aj kuma shine babban abokin sa,domin sun kasan ce kamar yan biyu kamar yadda iyayensu suke,dr ammar dai kyakkyawa ne na karshe,har yanzu bai da budurwa duk da harin da yan mata suke kawo masa,natayin soyayyarsu,mutun daya ce tazame masa kamar cingum itace dr malini,domin Allah yasanya mata wani sonshi duk d yana kokarin nuna mata bata cikin tsarinsa hakan baisa tayi sanya ba wannnan kenan...

SAI DR.AJ

Cikakken sunansa dr Al amin jabir muhammad soja,dane ga leutenant jabir muhammad wanda yakasance army ne na nigeria,shine shugaban sojojin arewa,sunan mahaifiyarsa husaina inda suke kiranta ummi,Aj yanada kanne uku inda namijin dake bimasa yarasu tun yana karami mai sunan mahaifinsu jabir ,sai mai bima margayi jabir sunanta sumayya,sai Auta Asma'u suna husnat,wadda taci sunan kakarta su ta wurin uba,Aj sa,a ne da dr. ammar kwana arba'in ne tsakaninsu,Sai sumee wadda take da shekaru sha tara sai auta husna nada shekara goma sha uku,aj da sun taso komai sunayinsa atare,Aj shima baida wata tsayayyar budurwa har yanzu Wannnan kenan...

MUDAWO LABARI

~~NIGERIA ZAMFARA~~

~~ BUG~~

~~UNGUWAR SABON GARI~~~

.....Bayan fitowar Baba Adee daga wanka Ya shiryawar sa cikin shiga ta kamala dai dai rufin asiri cikin yadinsa mai kyau black,bayan fitowar sa wanka wanda da taimakon Bba Asabe ya shirya wanda kuma shine dalilin saukarsa da wuri dama shi ba mutun bane mai riko..

" A bangaren su Halee kuwa bayan kammala shirin su na zuwa islamiyyya suka dauki jakun kunansu,sunfito rass dasu cikin uniform ash colour hijab har kasa masu kyau sai sheki sukeyi,dukannin su sun amshe su musamman ma Halee wadda farar fatar ta tak'ara haskawa, kyakkayawar fuskar ta ta fito rass doguwar fuskar ta kara yin wani shaf mai kyau cikin dogon hijab dinta gwanin burgewa,sunata zuba kamshi mai dadi,wanda sai ka matso su zakaji shi,ba mai cutarwa ba kamar dai yadda aka annabi ya siffanta turaren mata,

'Dan Baba Adee akwai son kamshi domin mafi yawancin tsarabarsu ta turare ce,shiyasa koda yaushe zakaji su cikin kamshi....

Sallama sukayiwa Baba Adee da Baba Asabe Dake zaune a barandar gidan suna dan taba fira jefi jefi...

Miji da mata sai Allah..

ficewa Gidan sukayi bayan amsa addu,o'in da yasaba yimusu inyana gida...

Bayan wucewar su Halee islamiyya,shima Baba Adee yaficewar sa zuwa masallacin unguwartasu dan gabatar da la,asar kan lokaci.....

~~GUSAU,ZAMAFARA~~

Gusau ta sambo mai dimbin al umma noma shine abun alfaharinku,Gusau Babban birni ne na jahar Zamfara wanda yatara dubbanin Al umma ta kowane sashenn yarukka da yan kasuwa,musamman manoma,da ma aikatan gwamnati da manyan yan siyasa,Babban Abunda yake abun burgewa agaresu shine yadda sukayi riko da aladunsu,da addini da kuma sarautunsu,sai kuma abun da yake mai mahimmanci da suka rike shine Bin shari'ar musulunci,gari ne daza kasamu suna bin dokar musulunci wanda ko gidan karuwai zai yi wuyar samu a jihar...

MASARAUTAR MURAI

Babbar masarauta ce dake cikin jihar zamfara gusau wadda gaba daya nigeria suna alfahari da ita domin kafaffiyar masarauta ce tun zamanin Sarki Ali murai wanda shine sarki nafarko wanda yafara yin sarauta ajihar tun zamaninsu shehu usman dan fodiyo Na sokoto,shiyasa takasance mai mai dimbin tarihi...

'kuma shine yayi ruwa yayi tsaki gurin kafa wannan masarauta mai tarin Al ummah ,wadda tazamo abar alfahari a idon al ummar nigeria jin irin kokarin da sarki Ali murai yayi gurin kafa masarautar..

Mutane daban daban daga cikin ya yan Ali murai sun rike sarautar wannann masarauta har izuwa yanzu da ake k'ara samun cigaba...

Tattab'a kunnen Ali murai a yanzu shiyake mulkar masarautar,inda take samun kulaawa dakuma Al.ummar dake karkashin ta,Ahannun d'an d'an sarki Ahmad..

WASH TYPING AKWAI WAHALA...KUYI MANAGE DA WANNAN....BANJIN DADIN JIKI NANE.....

GOBE IN SHA ALLAH ZAKU SAMUN KARIN PAGE

Kuyi sharing,

Sannan ku danna min like akasan page din....

Ina godiya sosai masoyan amafarki

Halee tace agaishe ku...

□FA'EEH BG□

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream i know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

□P.E.W.A.□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S

Pen*is migthier than the sword*

EPISODE 1

FREE PAGE18↔

TYPING□□□

TUSHEN MASARAUTA

"Ali murai shine Asalin wanda yarik'a masarautar yana da mata kwaya d'aya tal,sunan ta Hajiya lubah (iyami) da "ya "ya maza biyar,d'an sa nafarko sunan sa bello,sai nabiyu sunan sa Haruna,na ukun Abdul aziz,sai na hud'unsu Isma'il,sai Autansu yahaya..

Bayan rasuwar sarki Ali murai sai aka nad'a d'ansa na farko Bello wanda shi yacigaba da kula da masarautar yana da mata d'aya da y'a y'a hud'u namiji biyu mace biyu,Bayan wasu shekaru shima Bello yakwanta dama,wanda mutuwartashi ta kowa ya jita A Masarautar saboda sak halinsa irin na mahaifinsa sarki Ali murai,Mahaifiyarsa takoka da rashinsa da y"an uwansa da ma Alummar Masarautar.

Bayan gama zaman makoki Aka nad'a d'an uwansa Haruna,Haruna yak'arb'i mulki cikin salama ,Sai bayan shekaru sittin sannan Allah yakarbi ransa..

..Abdul Aziz Yakarb'a shi kwata kwata ma bai ka shekara hamsin ba akan karagar mulkin saboda ciwon daya ci k'arfin sa na k'oda,sai aka nad'a Isma'il,Bayan Nad'in Ism'el,Sarki Abdul aziz yakwanta dama....

Isma'el ya cigaba da mulkin masarautar Bayan shekara saba'in bisa karagar mulki yakwanta dama,wanda bayan rasuwar sa,Anyi rigima sosai da Yahaya danshi kwata kwata bayason sarautar,acewar sa kayan wahala ce da takura,bai karb'a har sai da mahaifiyar su iyami ta kwanta ciwo akan hakan,ciwon zuciyaar ta yatashi wanda yasameta tun bayan rasuwar mijinta sarki Ali murai,sanadin bak'in cikin

Yahaya da yakafe bazai k'arb'i masarautar ba,masarautar da mijinta sarki Ali murai yasga gwagwarmaya wurin ginata,daga k'arshe dai yakarb'a ganin yadda ran mahaifiyar sa ya b'aci gashi harda kwantawa ciwo....

'Anyi bikin nad'in sarauta da ba'a tab'a yin irinsa ba alokacin kowa kaga fuskar sa da annashuwa da farinciki kamar sauran lokutta domin sun san cewa ba su shiga mugun hannu ba dan duk cikin ya"yan sarki Ali murai babu wanda yamusu mugun riko,Yahaya yakarbi mulki cikin aminci tare da alkawalin kula da Alummar masarautar,yana da shekara talatin akaragar mulki matar shi tahaifi namiji wanda

shikad'ai ne rabonta har tabar duniya,yaron yaci sunan margayi tsohon sarki Bello,bayan wasu yan shekaru,Kwatsam ranar aka wayi gari da mutuwar sarki Yahaya murai,wanda mutuwar sa ta girgiza kowa musamman yaronsa sa Bello,Bayan rasuwar sa da kwanakki itama tsohuwa Iyami mai ran k'arfe ta kwanta dama,tana da shekaru D'ari da hud'u a Duniya.

Wanda kowa yaji mutuwar wayen nan bayin Allah Acikin Masarautar da ma wajen Masarautar..

Bayan rasuwar yahya Anyi rigima sosai A fada akan wayenda za,a dora akwai d'an wajen margayi bello da yace yanaso sai kuma d'an wajen magaji wanda yaya ne ga Sarki Ali murai,daga k'arshe dai Muhammadu bello D'an wajen sarki Yahaya shi aka bawa bisa ga chanchantarsa duk da akwai k'aranta atare dashi dan duk sun girme masa.

Anyi nad'in sarauta tareda Daurin Auren Sarki Bello Alokacin yana da shekara ishirin da hud'u A duniya,Bayan hawansa akaragar mulkin yana d'a yan uwansa manyan muk'a man masarauta,domin cigaban Alumma .

Ya Auri yar wajen sarkin zazzau na hud'u alokacin mai suna Gimbiya Ruk'ayya bayan shekara gimbiya Rukayya ta haihu ta samu yan Biyu maza,Alokacin ne kuma matar tsohon sarki margayi yahaya uwar muhammadu bello tabar duniya,Anyi taron suna cikin alhinin wannan rashi,tacigaba rainon yan biyu dinta,Bayan wasu shekaru tasamu wani cikin inda tahaifi Namiji yaci suna Aliyu,sunan tsohon sarki...

'A Daren sunan Aliyu ne wani Babban tashin hankali yafaru inda wuta ta kama ad'akin su hassan da husaini duk suka k'one k'urmus sanadiyyar wutar lantarki suda mahaifiyar su gimbiya Ruk'ayya wadda taje dubasu daga nan ta musu Addu,ar kwanciya bacci duk da tasan cewa bazasu kwanta hakan nan domin takoyar dasu,alokacin suna shekara shidda A duniya,Mutuwar data girgiza Sarki Bello da kuma masarautar wanda sai da sarki Bello yasuma alokacin da aka sanar dashi,Bayan jimamin rashin Sarki Bello yaci gaba da rainon D'an sa Ali....

**Bayan shekara guda sarki Bello yayi Aure ya Auri wadda take baiwa ce Amasarautar, ya Aureta ne saboda ganin irin kulawar da take bawa Aliyu wanda kuma ita kad'ai yake yadda da ita,Sai ya " yenta ta kuma ya Aureta domin samun farin cikin D'an sa tilo daya.

Lafiya lau masarauta take tafiya tareda cigaba mai yawa,Bayan wasu shekaru Sarki Bello na Biyu yabar Duniya yana da shekaru hamsin akan karagar mulki,inda yabar Aliyu cikin maraici mai yawa duk da wannan yentacciyar Baiwa mai suna Nana Asma'u tana sonshi tana bashi kulawa mai kyau saboda yadda take jinsa kamar d'anta na cikinta..

BAyan gama jimamin mutuwar sarki Bello na || biyu aka nad'a d'ansa Aliyu alokacin yanaa da shekaru ishirin da hud'u a duniya.

Bayan na d'insa da shekara guda yayi Aure ya Auri yar masarautar sokoto jikar yar sarkin musulmi na ||| na uku;mai suna ummulkhairi ana kiranta gimbiya (umma),Bikin yatar dubbanin Al umma takowace masarautun nigeria da manyan yan siyasa,masu kudi..Ankawo Amarya lafiya cikin fada acikin sashen ta mai kyau,suna cin Amarcin su lafiya lau tare da zaman Amana....

Komai yana tafiya dai dai ta b'angaren mulki yadda yakamata.

Bayan shekara d'aya gimbiya umma tahaifi santalelen d'anta namiji ranar suna yaro yaci sunan sa HAMZA ALIYU MURAI,Anyi taron biki lafiya,inda tacigaba da rainon yaronta,Bayan haihuwar Hamza da wata takwas tasake samun wani cikin alokacin gimbiya ummulkhairi taso zubarda cikin ganin Hamza ko shekara bai had'a kar yasha ciki,sai dai mai martaba sarki Aliyu yahana zubar da cikin sai dai yasa aka cire Hamza daga nono...

Taraini cikinta lafiya lau batare da tasha wuya ba,watannin haihuwar cikin nayi nak'uda ta motsa amma yaro yaki fitowa ak'arshe dai CS akayi mata aka ciro santalelen d'anta mai kama da uban sa sak,yaron yaci suna Ahmad...

.....Bayan wasu "yan shekaru sarki Aliyu D'an Bello jikan Yahaya D'an Sarki Ali Murai yabar Duniya alokacin,yabar Duniya da shekaru arba'in akaragar mulki,Mutuwar sa tagirgiza y"a yansa guda biyu a duniya da matar sa ummulkhairi,inda tacigaba da kula da yayanta cikin kulawa,Bayan Rasuwarsa da yan watanni Nana Asma'u matar margayi sarki Bello na || tabar duniya...

Sarautar dole aka bawa magajin gari rik'on kwarya kafin ya'yan sarki Ali su kai lokacin iya rike sarautar,domin dukkaninsu bazasu wuce shekara goma sha biyar Alokacin ba.

Bayan wasu shekaru Ahmad yayi aure ya auri matarsa Bafullatanar Adamawa itama yar gidan sarautace sunanta Haleematu sadiya suna kiranta hajiyar safkare wanda sunan da kakarta ta lakamatane,ya Aureta yana da sheakara ishirin da shidda aduniya sunyi Auren soyayya da gimbiya halimatu,kuma aloakacin ne aka damk'a sarauta hannun Ahmad duk da sai da akayi rigima dashi dan yace bazai karb'a ba sai dai abawa y"a yanshi tunda shine Babba,Dakyar aka samu yakarba bayan ya yan nasa ya sanya da mahaifiyarsu gimbiya ummulkhairi suka tasoshi gaba....

Anyi bikin nad'in sarauta lafiya cikin annashuwa da salama,ta fannin zaman takewarsa da matar sa masha Allah za,ace gwanin burgewa.

****Bayan shekara daya gimbiya halimatu sadiya ta haifi santalelen d'anta mai kama da ubansa sak jinin fulani,farin cikin wannan masarauta bazai boyu ba musamman sarki Ahmad da D'an uwansa hamza,wanda ke ji kamar shi akayiwa haihuwar...

*Ranar suna yaro yaci sunan kakan sa sarki Aliyu Bello jikan yahaya d'an Ali murai*yaro yasamu gata ta kowanne fanni,Alokacin shima Hamza yayi Aure ya Auri Gimbiya Hauwa'u yar masarautar Fulanin Bungud'u ana mata lak'ani da fulani,fulani macece mai fadin rai da rashin son talaka,da mugun son kanta,ba kamar gimbiya halimatu ba mutuniyar kirki mai mutunci,BAyan Aurensu da Hamza sai tafara nuna

mishi ai sarautar dashi ta dace domin shine Babba yace abashi sarautar,ai shine dana farko ga sarki Ali Bello,sai ya rik'a nuna mata baida buk'ata,kullum haka suke rigima da ita,har zuwa lokacin da tasamu cikin Mustapha A lokacin kuwa matar sarki Ahmad Halimatu tasamu ciki na biyu ta haifi umar,sunan mahaifinta kenan,tana kiransa da emir,Bayan kamar wata takwas sai ga wani cikin na ukku inda ta tahaife sa lafiya,tasamu Abdul rashid,tacigaba da rainon ya yanta cikin kwanciyar hankali.

Daga cikin abin bak'in cikin da yafaru Akwai rasuwar gimbiya ummulkhairi matar tsohon sarki Ali,Mahaifiyar sarki Ahmad da Hamza,sunyi rashin mahaifiyarsu abar kaunar...sai dai muce Allah yajikanta da al ummar musulmi baki daya.....

Yaa Allah Duk wata mahaifiya □□dake kwance akarkashin k'asa,Allah kajik'anta da rahaama,da musulmi baki daya,Yaaa Allah wayenda suke raye kuma ka k'ara musu lafiya mai amfani tare da tsawon rai mai albarka□

Rashin uwa rashine 😭Babba Arayuwa

Allah yabar mu dasu □

Matar Hamza Fulani tak'ara samun wani cikin nabiyu ta haifi d'anta namiji mai suna Muhammad ana masa lak'ani da Malan,tana da ya"ya biyu kenan.

Itama sarauniya halimatu taka'ara samun wani cikin bayan shekara uku inda ta haifi yarta mace mai suna khadija inda daga gareta haihuwar ta tsaya mata chak.....

Sarauniya Halimatu yaranta sun taso cikin soyayyar junansu Da yan uwansu yan gurin magaji hamza,domin shi d'an uwansa ya nada magaji bayan rasuwar wanchan magajin.....

Duk da tsangwamar da Fulani take nuna musu amma hakan bai hanasu jan yan uwansu ajiki bah.

Ta b'angaren magaji Hamza kuwa yana shan matsin lamba gurin Hauwa'u (fulani)kan karbar mulki alokacin takara samun ciki tahaifi ya mace mai suna ummulkhairi suna kiranta (khairiyya) dan taci sunan kakar ta ne wanda daga gareta haihuwar ta tsaya ma fulani chak..

A lokacin Duk fulani tana masa matsin lamba wanda har tafara cin galaba akan sa,dan bata tsaya haka nan ba,sai da talek'a gurin malammaan tsibbo (bokaye) Wal iyazubillah....

bokaye mana domin tahakan ne wasu suke amfani dashi sai suce ai malami ne shi bokan,ana amfani da sunan malamman ana shirka ana cutar Al umma..ALLAH YAYI MUNA TSARI DASU...Masu zuwa gurin bokaye Allah yashiye su□

MU HADU GOBE IN ALLAH YAKAIMU

YAU KAM KUNSAMU LONG PAGE,DAN KONI NAJI AJIKI NA,KUNGA NA GOGE LAIFINA NA JIYA,DUK DA BANI DA LAFIYA NE

NAGODE SOSAI ALLAH YABAR KAUNA

KUFARA SHIRI ANKUSA GAMA FREE PAGES,DAN BATUN SAMBAD'O KUD'INKU.....

Kucigaba da bibiyar Alkalamina

Yau duk sai A hankali typing din domn page d in yatado mini da rashin da mukayi...Allah yajik'anku da rahama Baba Bello,kakana Baba Yahaya,Alhajin Auki,Mariya,gwaggo yar sarki, Allah yasa Aljannna takasance makomarku da dukkan musulmi baki daya..AMEEEN...

A MAFARKI NASANTA

In my dream i know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one,Episode one kenan za,a fara payment,Na episode two!!!✌✌

TALLAH!!! TALLAH!!! TALLAH

Ina yan kasuwa masu son tallata hajarsu,ga dama tasamu domin Muna tallata kowace irin hajace daga jihohi daban daban harda ma k'asashe,akan farashe mai sauk'i,zaku iya tuntubarmu ta lambobin waya kamar haka.....

+ 2348069059746

+ 2349078741775

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

□P.E.W.A.□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S

Pen*is migthier than the sword*

EPISODE 1

FREE PAGE19

TYPING□□□

" Rana ta farko daya isko sarki Ahmad da maganar yana son sarautar ta dawo hannunsa,Sarki Ahmad bai nuna komai ba akan fuskar sa,sai dai murmushi da ya wanzar akanta tare da furta masa zaiyi magana da manyan masarauta,duk da yasan lallai su amince ba,saboda tun farko da yardarsa aka d'orasa,kuma ba,a chanza sarki kai tsaye ba da kwakkwaran dalili ba a wanchan lokacin..

Koda sarki Ahmad yagana da manyan masarauta sun nuna k'in Amincewarsu kaitsaye.

'kiran d'an uwan nasa yasanar dashi domin badashi anakayi zaman ba,kamar ganawar sirri ce,daga su sai maimartaba sarki sarki Ahmad sukayi ta,yana yin yadda yaga D'an uwansa yana kuka kasharb'an hankalinsa yatashi sosai,dole yasanya taron gaggawa yace yayi murabus kan kujerar tare da katse duk wasu tambayoyin da aka so tsiyesa dasu inji manyan masarautar..

'Farin cikin da yagani kwance akan fuskar d'an uwan nasa Hamza shine Abunda yatsaya masa arai,Bayan komawar sa gida bai b'oyewa gimbiya Halimatu sadiya komai ba,Tayu mamaki sosai duk da tasan akwai wata a k'asa sun san halin matar sa sarauniya Hauwa'u zata iya yin komai sun yarda cewa bayin kansa bane..

:::::::Rayuwa tana tafiya yadda yakamata,sarauniya Hauwa,u (fulani) mulki ya shigo hannu sai taka talakawa take yi son ranta duka bayi alokacin sun san halinta tsoronta sukeyi sosai domin wulakanta su bakomai ne awajenta ba,musamman na sashenta,Yadda take da mugun hali haka tab'ata D'anta Muhammad,shi mustapha ba

haka yake ba halin babansu suka biyo shida macen da takara haifawa mai suna ummulkhairi,wadda taci sunan kakarsu Ta wajen uba,suna kiranta khairiyyah..

A lokacin da akayi juyin mulkin duka ya yan sarki Ahmad maza basa nigeria suna wajen karatu,Aliyu yana china yana karantar Business Administration,sai umar yana Kasar Uk yana karatu fannin bincike da tsaro,sai Autan maza Abdul rashid yana kasar sudan yana karantar MBBS karatun likitanci kenan,Duk da alokacin sunji mulkin yabar hannun mahaifinsu ba wanda yadamu dan dama basu wani dauki mulkin wata tsiya bah.

Bayan kamar shekara bakwai lokacin umar yagama nasa karatun har masters ya had'o,yadawo gida alokacin ne kuma mahaifinsu sarki Ahmad yakwanta dama,😭 mutuwar data girgiza kowa dole dukkaninsu suka dawo nigeria dan ganin gawar mahaifinsu,wanda kafin suzo ma an binne ta,ganin basu iso da wuri ba,khadija kadai tasamu damar isowa da wuri ita dake Adamawa gurin kakaninta tana karatun a wata private school ta Nursing wanda tashiga a wannan year din,koda suka iso rashin ganin gawar ta mahaifin nasu sai takara rikita su,in kagansu alaokacin sai ka sun baka tausayi,wannan mutuwa basu kad'ai ta girgiza ba harda Alummar zamfara baki d'aya domin sanin halayen sa na kirki da kyautatawa al umma da yake yi...

'Matuk'ar girgiza sarki Hamza ya girgiza ba kad'an ba Alokacin da aka sanar dashi yana tsaye,shine ma dalilin dawowarsa hayyacinsa,kuka yakeyi wiwi,yana furta kaichona,na k'untatawa D'an uwa nah,da k'yar fadawa da manyan masarauta suka lallashesa .....

"Gimbiya Halimatu sai da tayi kwana biyu bata farfad'o ba daga suman datayi bah...

Bayan kwanakki da rasuwar sarki Ahmad, Sarki Hamza yatara taron gaggawa na manyan masarauta,take yasanar musu da kudurinsa na son yin murabus,maganar takawo cece kuce a fada lokaci da sarauniya Hauwa,u taji wannnan zance tayi farinciki sosai jin cewar sarauta zata dawo hannun ya yanta,ita a tunaninta Muhammad ko Mustapha za,a bawa tunda mahaifinsu ne yasauka,wanda dama shine burinta tun farko shiyasa ta yishigenta da fice har sarautar ta dawo hannun sa..

Sai kuma 'wani Babban labari na tashin Hankali daya sanya Gimbiya Fulani suma.....

'Jin sarki Hamza yagabatar da 'matar sa ta biyu waddaya aura shekaru sha bakwai da suka wuce,tare da ya yanta mata uku,duka kyawawa,na farkon sune yan biyu hassana da husaina sai ta karshen su Auta mai suna lailat,yagabatar dasu ne A masarautar dan yana so sudawo dazama ciki tare da sauran dangi...

Sunyi Aure da matar sa Fateema yar k'asar makkah,ana kiranta Ammie,Fateema dai balarabiya ce sak gaba da baya,sunyi Auren soyayya da sarki Hamza A lokacin da yaje k'asar ta makkah yin wani taro na sarakuna,Tanuna tana sonsa Alokacin shima kuma yaji yana sonta Duk da lokacin akwai sihiri mai K'arfi ajikinsa wanda ba kowa ke iya ganewa bah...

Ya Aureta ne Achan k'asar jidda inda Asalin iyayenta suke,tana zama wurin ya yan tane sarkin makkah alokacin.

Mutane da dama sun shaida d'aurin Auren fateema hakim da kuma sarki Hamza Aliu murai ...

Bayan D'aurin Aure yad'aukota suka dawo nigeria wanda dik cikin masarautar sarki Ahmad kad'ai yasan da Auren sai kuma wasu daga cikin manyan masarauta,saboda ya nemi Alfarmar yazamo sirri bayaso maganar takai ga sarauniya hauwa,u domin Alokacin harda d'an tsoronta aka saka masa azuciya..

Sarki Ahmad har ziyara yana kaiwa fateema (Ammie) a gidan da sarki yakaita a d'ai daga cikin manyan unguwanne da suka Amsa sunansu na masu naira ...

kuma tun lokacin da Ammie ta haifi twins dinta sarki Ahmad mai mutuwa yabar wasiyyar ko bayan ranshi yana son cikin zaratan mazan ya yansa koda d'aya ne ya Auri cikin wayen nan twins d'in,Bayan twins tak'ara samun mace aka lailat.....

SU FULANI ANGA TASHIN HANKALI WANNAN KAM SHI AKE KIRA TA LEK'O TA KOMA....Zafi bibbiyu...

□FA'EEH BG□

Wannan labari yazamo farinciki ga wasu wasu kuwa bak'in ciki,domin itakam gimbiya Halimatu sadiya tayi farin ciki dan dama mijinta yasanar mata da Ammie din wanda sak'o tana basa inzaije,yakaiwa hassana da husaina da lailat,kuma suna musayar gaisuwa wa junansu,har numban wayar juna suna da ita,Murmushi kad'ai tayi dajin wannann labari dama kuma tana dakon zuwansu,suma su umar (emir) da su Aliyu sunyi matuk'ar farinciki musamman Mustapha da khairiyyah sunyi murna sosai ganin sun kara samun yan uwa....

Bayan gabatar dasu ga fada aka damk'a su gurin gimbiya halimatu domin tama rakkiya sashen ta domin itaace Babba Amasarautar,dama tasanya ma,aikata sun gyara sashen da yake Mallakin Ammie ne ita da " ya "yanta...

Bayan gama gaisawa da juna tagabatar da ga dukkanin bayi ma,aikata dake aiki asashen ta da kuma wayenda zasu yi aiki asashen Ammie din..

Sannna suka d'unguma zuwa katafaren sashenta wanda yaji kayan more rayuwa ta ko ina..

"A fada kuwa suna tattaunawa kan maganar murabus na sarki Hamza,ya kuma sanar musu cewà shi ya nemi d'an uwansa sarki Ahmad yasauka yabasa mulki kuma bay in

kansa bane shidai yasan ko mene umurni aka basa,Amma bai sanar musu wanda yayi mishi hakan ba domiin kariyar mutuncin ya yanshi..

Kuma yace yana son yamika'a sarautar ka yayen d'an uwansa sarki Ahmad da sarautar tunda dama dukkaninsu sunkai mizanin hankali,sunyi na,am da zancen sa kuma sunga dacewar hukuncin sarki Hamzan,zancen yama wasu dadd'i wasu kuwa bai musu ba,A lokacin inkaga fuskar Muhamad

(Malan)zakaga tsantsar bak'inciki da b'acin rai tattare dashi daga farkon maganar yazata shi za,a bawa baiyi duba da shine k'arami ba ma...Fuskar nan tasa tayi jawur cikin abunka ga farar fata har kwanci jini tayi,ga bak'in cikin bayyanar wasu ahalin nasu inda ma yayi farinciki ba maza bane...

'Baiko bari akagama magana ba yabar fada rai b'ace yayi sashen mahaifiyarsa,wanda achan ma yatarar da wani tashin hankalin sarauniya hauwa,u kamar tayi hauka duk ta rud'a sashenta,ga Ammie da gimbiya Halimatu sunzo sashenta dan agana da juna amatsayinta na uwar gidan Ammie din,dakuma zaman ta na sarauniya matar sarki, su laila dasu hassana da husaina, sai kuka sukeyi khadija nataya su,wadda takejin kaunar yan uwan nata, domin basu tab'a ganin tashin irin wannan tashin hankali ba.

Mustapha ne ke jan ta tana kucce kucce dan shima dama zuwansa sashen kenan ya isko wannan kayan haushi kayan kunya gaban bayi take zage zage zuwa ga maimartaba sarki Hamza da kuma Ammie harda ma gimbiya Halimatu,Bayan mustapha yasamu nasarar janyeta daga falon izuwa uwar d'akinta,shima Muhammad yabi bayanta da fuskarnan tashi kamar tayu aman wuta,itadai khairiyyah sai aikin lallashin yan uwan nata take yi dan itama tunda tagansu taji sun kwanta mata arai tanajin soyayyarsu har cikin zuciyarta...

Gimbiya Haleematu da Ammie A hankali suka bar sashen nata tareda su hassana harda khairiyyah ma zuwa sashen na Ammie kowa zuciya ba dad'i.

A b'angaren sarauniya Hauwa,u fulani kuwa kuka take wiwi kamar wadda akayiwa mutuwa,sunyi lallashinta harsun gaji sai da mustapha yayi dubarar kiran mahaifinta sarkin Fulani sannan suka samu kanta.

"Mustapha gaba d'aya sai da yaje sashen su Ammie da gimbiya Halimatu yabasu hakuri kan abunda yafaru sannan yak'ara lallashin yan biyu da su khadija.....

A bangaren fada kuwa bayan fitar Muhammad maimartaba sarki Hamza yanemi jin ta bakin ya yen sarki Ahmad,Bayan sanar musu da bukatar

sa,Kamar yadda yasanarwa sauran mutanen acikin fadar,bayan gama jin zancensa duk sukayi shiru,dan dukkanin su babu wanda sarautar ke kod'awa ak'asa kanwarsu ce khadija ke d'anjan sarautar,ko yadda suke gudanar da rayuwarsu inka kalla zaka san akwai jinin sarauta ajikinsu mai karfi...

Maganar sarki Hamza ceta katse shirun inda yake cewa yana jiran Amsar su,suka ce abasu nan da,gobe in sunyi shawara da mahaifiyarsu,da haka zaman nasu ya watse anbarshi akan gobe za'ayi hukuncin dasuka yanke.....

Nima anan na dakatar da alkalamina

Bayan ya subuce daga hannu na😂

Sai monday in Allah yakaimu da rai da lafiya

Zaku samu cigaba

Like pls share nd comment

Like pls nd comment kuma atayani sharing Dan Allah...

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one□,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!✌✌□□

TALLA!!! TALLAH!!! TALLAH

ina yan kasuwa masu son tallata hajarsu,toh ga dama tasamu domin muna tallata kowace irin hajace daga jihohi daban daban harma da k'asashe,akan farashe mai sauk'i,zaku iya tuntub'armu ta lambobin waya kamar haka.....

+2348069059746

+2349087741775

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream i know her 2023 novel *is the story of an* *innocent girl call Halee yarinyar da* *tataso cikin rashin iyaye sannan ta* *had'u da kalubalin rayuwa mai matukar* *girgizawa inda bayan haduwar ta da* *iyayenta,wayenda suke nesa da* *rayuwarta tasamu loosing memory,sai* *kuma takara samun "psycho" tab'n* *hankali kenan shin ko meye silar* *faruwar hakan?SHIN WAD'ANNAN* *YAN BINDIGA DA NA HANGO KODAI SUNE SILAR RABA* *HALEE DA IYAYEN TA,?ME KUMA IYAYEN NATA SUKA MUSU INHAKA* *NE?KAI WANNNA ALAMARI AKWAI* *RIKITARWA,SOYAYYA KAM ZAKU* *SHATA,SANNAN YAR UWA ZUCIYARKI* *ZATA TABU*.....*SHIN KO WAD'ANNAN YAN TA'DDA* *ALKALAMINA ZAIYI AIKI KANSU?SU WANENE ABAYANSU ? SHINSUMA ZASU IYA KARBAR HUKUNCI ?DUK DA KASANSEWARSU MANYAN KASA*

DUK AMSOSHINKU ZAKUJI SU ACIKI WANNAN BOOK KUCIGABA DA BIBIYATA.

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCIATION

P.E.W.A.

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER

pen*is mightier than the sword*

EPISODE1

FREE PAGE20

TYPING...

Bayan barin sarki Hamza fadar bai zame ko ina bah,sai sashen sarauniya hauwa'u dan yasan tabbas akwai matsala yasan bai kyau tamata ba duk da ya fahimci alokacin akwai sa hannunta cikin macin da yasamu na karb'ar sarauta,kuma a lokacin da yayi auren b'oyen duk laifintane shi baisan abunda yashiga kanshi ba na tsoronta ba alokacin,Auren ma nasu da Ammie Allah ne yak'addara shine..

Shigar sa sashen nata ma,aikata nata russunawa tare da fadawan dake abayan sa,kai kadai yake iya d'aga musu har yakai ga shiga Babbar uwar d'akanta wadda take taji komai har kujeru akwai ciki da tv,duk haka d'akunan suke na masarautar kowanne sashen haka yake,gimbiyah halimatu ce kadai tasa aka cire mata ta ta tvn ta uwar

dakanta,saboda ita macece mai natsuwa hayaniyar tvn na takura mata acewar ta,tafison taji ta shiru ita kad'ai tana jan charbi tana azkar dinta domin macece mai son ibada kullum bata rabo da charbi a hannunta ko tana karatun alqur'ani.....

Bayan sarki Hamza yayi sallama,acikin uwar d'akanta yashiga bayan yaji shiru,ba,a amsa masa sallama ba...

Nikam nace dama ya,za,ayi a amsa maka sallmah yallabai kishiya ai ba wasa bace bare ta auren boye,abun akwai ciwo,sai dai dan Allah yan uwa mata mudaina kishin hauka,arika kai zuciya nesa....Akamanta kuma arik'a daukar k'addara Duk yadda tazo,Domin Allah yariga yarubuta cewa matar sace itama,sai dai abi da addu,ar zama lfy da haduwar hankali..

Jingane take kan gado takura wa tv ido kamar akwai abunda take fahimta hankalin ta baima jikinta..Gimbiya fulani kenan,Fulani! sunan ta da yakira ne yasanyata d'an kallon inda yake tsaye hawaye ne suka cigaba da tsiyaya a idonta ganin ga dukkan Alamu ya nuna maganin yasaki jikin sarki Hamza,.....

nikam nace dama boka ko malan sun isa su juya mutun ne har karshen rayuwarsa ai abun hajiya nadan lokacine ,ke kuma mai kwasar kafafu kije dan neman agaji gurinsu saboda rashin hankali ,wai harda kayan dakin ki kika siyar dan ki samu wani abun ga wanda shima ubangijin ne ya samar dashi to bari kiji kyi hattara,domin kuwa bokaye kudin ki kadai suke ci babu mai yima bawa face Allah,dan haka kimayar da yar tabarmar ki dakike shirin siyarwa dan kaima kunkurmin kato,wanda zai mutu acikin azabar Allah,inva tuba yayi ba,domin Allah mai jinkan bawansane,Allah yatsare muna imanin mu□□,masu niyar zuwa Allah kaga nar dasu,domin ko sau daya kika taka gurin malaman tsibbo ko bokaye Allah zai yi fushi dake za,a jingine komai naki na ibada,Har sai kinyi kwana arba'in,kinga idan kika mutu awanna lokaci kin mutu kafira,anyi zuwan zomo duniya,Allah ykara ganar da mu,ya kuma k'ara muna karfin imani domin mai k'aramin imani shiyake kai kansa ga wadannan kafiran musulman

*-------- *----------*----------*---------*---------*----------*

'Da dadane jikinsa narawa zaizo yadurkusa mata yana tambayar ta meya faru,Amma yau gashi yanzu harda kiran sunanta babu alamar tsoronta a idonsa,zafi bibbiyu gana zuwan Ammie da iyalanta gana murabus din zaiyi yamayar da mulkin hannun ya yan gimbiya Halimatu...

Hakuri yabata akan Auren da yayi batare da yanuna mata komai ba,ganin tadan saki yasanya sa fita yakoma sashen sarauniya Ammie baiwar Allah,domin ganawa dasu dakuma jin in sashen yamusu,su hassana sunyi farincikin ganin mahaifin nasu dan sun saba dashi sosai

Hakuri yabata da abunda yaji yafaru lokacin da suka je sashen na fulani domin mustapha yasanar dashi komai bayan barowarsa sashen na fulani.

BAiwar Allah tanuna masa bakomai dan dama Ammie akwai saukin kai,kamar yadda nafada muku chan baya lak'aninta ne har ya yanta ma haka suke kiranta dashi..

A bangaren yaran gimbiya halimatu kuwa sun sanar da ita komai tanuna farincikinta afili dama burin margayi sarki Ahmad ne cikin ya yansa wani ya gaje sa,sun yanke hukuncin abawa umar tunda shi yagama karatunsa kuma har yasamu aiki ma,federal government sun masa appointment na minister of security and investigation crime (S.I.C),ganin yadda takardunsa sukayi kyau da kuma kwazonsa awurin bikin yaye dalibbai,umar yaso yayi ja inja da yan uwan nasa musamman yayansa Aliyu sai da mahaifiyar su tasanya baki aciki ya amince ya karb'a,

"Anan yakawo maganar Aure duk da yanajin nauyin,amma baijin zai iya bari yayi sake ba,yasanar musu da kudurinsa na cewa shikam yayi mata domin yaga laila yana so yar wurin Ammie,tun lokacin yayi arba da ita yaji yakamu da tsananin sonta,sunyi farinciki sosai dajin wannan labari musamman ma gimbiya halimatu,duk da laila tana da shekaru sha biyar ne lokacin dan secondry ma tagama alokacin,su hassana da husaina ne su sunwuce tertiary institution daya tana karantar fasion and designer daya kuma masscom a skyline university a branch dinsu dake gusau.....

Sunyi na,am da zancen sa kwarai dagaske Alokacin da zancen yaje kunnen sarki HAmza yayi farinciki sosai zai cika burin dan uwansa na had'a auratayyar ya yansu...

Itama Ammie tayi farinciki sosai ta bangaren lailat tunda aka sanar mata da maganar sai ta tsinci kanta soyayyar emir,kowa yayi farinciki banda mutun daya itace sarauniya hauwa'u taso hana haduwar auren Allah yahana,tunda taji wanda za,a bawa sarautar shine laila zata Aura,sai taji ina ma khairiyyah yazab'a....kaaji soin kai

Niko nace tun ran gini tun ranzab'e fulani, matar mutun k'abarinsa

''Anyi nadin sarauta tare da daurin Aurensu cikin lumana,inda aka k'ara gyarawa da k'awata manyan ginukkan na zamani na masarautar,inda aka ware musu ,bayan angyara dai daga cikin bangarorin masarautar wayenda suke atsare ginukkan gwanin burgewa irin ginin sarauta na asali,anyi taron biki lfya an watse tareda Addu,ain samun zaman lfya ga amarya da angon ta sabon sarki....

Bayan gama bukukuwan kowa yakoma kan harkokin gavansa,Aliyu da Abdulrashid kowa yakoma kasar karatunsa harda khadija dasu khairiyyah da mustapha,dake karatu a suma acikin gari a noun university dake kano ,muhammad(malan) kad'ai akabari domin yace yafison karatu agida shiyasa aka yake karatu a FUG,yana karantar politial science...

''''''''''''''Bayan wasu shekaru shima Aliyu yazama cikakken dan kasuwa dan yasamu damar da kowace zai iya kafa kasuwancinsa batare da wata wahala ba,yayi Aure ya auri Hassana,inda har ta haifi santalelen yaron ta namiji kyakkyawa jinin larabawa da fulani,inda yaro yaci suna Abdul rashid ana masa lak'ani da Ammar Anyi shagali sosai wanda ba,atab'a yiba,inda itama Husaina ta yi Aure ta Auri wani Babban Abokin sarki umar mijin laila,Wanda yaganta A auren su laila din har ya nemi Aurenta,leutenant

jabir muhammad soja Abokinsa ne nak'udda tare su sukayi karatu a uk,bayan dawowarsu najeriya ne shima jabir yasamu matsayin leutenant....

Inda itama ta haifi d'anta sak kamar ta jikinne na babansa bayan tayi arba'in ne,itama Hassana ta haife nata cikin...

Yaron husaina yaci suna Al- amin sunreni ya yansu cikin Aminci da kwanciyar hankali

....A bangaren sarauniya lailat da umar tsif kake ji har yanzu tun abun bai damun laila har yafara damunta,A wasu lokuttan zata zauna tayi ta kuka ganin yan uwanta wayenda ma tariga aure sun haifu ita kuma shiru,sarki Umar shike lallashinta da kuma gimbiya halimatu,kaji*surukar arziki**Allah ya had'a mu da irinsu*

Da kuma Ammie ,daga cikin abun bakincikin da yafaru akwai rasuwar tsohon sarki Hamza,inda mutuwar ta gigita Ammie saboda bata wasu dangi sai shi akasar nigeria shine gatanta sai ya yanta,shine take samun sanyi agaresa saboda gimbiya Hauwa'u kullum cikin musguna mata takeyi aboye tun kafin su hassana suyi Aure take wahalar dasu tahanyar furta musu bak'ken maganganu ko sanya su aiki wanda basu saba da yinsa ba,Amma ammie bata taba fadawa mai martaba ba,zagi kala kala tana sha har cewa da ita takeyi wayasani ma ko sarki takari yakwaso ita ba balarabiyar kwarai bace,*nace su larabawan dama akwai na k'arya*..Duk da taga dukkanin tsarin halitta ta larabawa atare da ammie din..

Sunyi kukan rashin mahaifinsu,khairiyyah

harda suma itada lailat shiko malan ko ajikinshi dan yana ganin kamar mahaifin nasa yatare masa gaban hantsine gurin kwatar sarautar...

Hassana da Husaina laila sunji sosai mutuwar,bayan gama zaman makoki suka cigaba da rainon y yansu.....

""""""

kyakkyawan yaron sakinta a k'asa saboda yadda kukan yashiga kunnensa Yana yamutsar kyakkyawar fuskar sa Kamar yasaki kukan shima.....

Aiko da gudu d'ayan yaron ya koma cikin gida yana kwala kiran Aunty! Aunty ! wata farar kyakkyawar matashiyar matace wadda bazata shekara ishirin da hud'u ba ta b'ullo daga k'ofar kitchen tasha kaya na alfarma,tana furta lafiya Yarona,cikin shesshekar gudun da yayi yake fad'in Aunty Ammar ne yasaki norah k'asa,bai rufe bakinsa ba sai ga nanny din dake kula da norah tare da yaron danaji ankira Ammar d'auke a hannunsa tana tsala kuka,harda shid'ewa shima kuma Ammar d'in hawaye ne ke tsiyayar masa a ido..

Muryar nanny d'ince take fadin Allah yataimaki gimbiya sarauniya ya matsamun sai nabasa itane,gashi ba wani iya daukar ta yayi ba,shine nabasa nadan zagaya ne sai chan nji kukanta,ki gafarceni,yanzu haka ma nayi nayi dashi yabani ita inlallasheta yak'i gashi shima kukan yake yi,murmushi kawai tayi bayan gama sauraren bayanin baiwar,

Jawo hannun wanda aka kira ammar tayi sannnan ta karb'i yarinyar da naji ankira norah a kafad'ar ta tadaura ta tashiga girgiza ta,shikuma Ammar tazaunar dashi akan kujera tana share masa hawayen sa da suka kasa tsayuwa....Nora da zuwa wannnan lokaci tayi shiru jinta abisa kafad'ar mahaifiyarta sai shesshekarta kad'ai kake ji,tak'ara tsala kuka wanda yafi na farko tanayi tana shidewa fararen manyan idanunta sunyi jawur dasu na azabar datake ji, wanda take jikin ta yagashe,cikin shesshekar kuka Ammar yake furta Aunty kibawa nora hak'uri tadaina kukah yana cigaba da kukan shima,d'ayan yaron ne ya matso kusa gareshi yana fadin Ammar kayi shiru kaji yakai karshen maganar cikin tausayin sa,daga yanayin yadda suke kasan cewa suna mugun son junansu,hawayen sa yashare masa yana k'ara furta norah tayi hakuri Ammar bakaji tay shiyu ba.....

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one□,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!✌✌□□

TALLA!!! TALLAH!!! TALLAH

ina yan kasuwa masu son tallata hajarsu,toh ga dama tasamu domin muna tallata kowace irin hajace daga jihohi daban daban harma da k'asashe,akan farashe mai sauk'i,zaku iya tuntub'armu ta lambobin waya kamar haka.....

+2348069059746

+2348087504734

A MAFARKI NASANTA

*In my dream i know her*2023 novel *is the story of an* *innocent girl call Halee yarinyar da* *tataso cikin rashin iyaye sannan ta* *had'u da kalubalin rayuwa mai matukar* *girgizawa inda bayan haduwar ta da* *iyayenta,wayenda suke nesa da* *rayuwarta tasamu loosing memory,sai* *kuma takara samun "psycho" tab'n* *hankali kenan shin ko meye silar* *faruwar hakan?SHIN WAD'ANNAN* *YAN BINDIGA DA NA HANGO KODAI SUNE SILAR RABA* *HALEE DA IYAYEN TA,?ME KUMA IYAYEN NATA SUKA MUSU INHAKA* *NE?KAI WANNNA ALAMARI AKWAI* *RIKITARWA,SOYAYYA KAM ZAKU* *SHATA,SANNAN YAR UWA ZUCIYARKI* *ZATA TABU*.....*SHIN KO WAD'ANNAN YAN TA'DDA* *ALKALAMINA ZAIYI AIKI KANSU?SU WANENE ABAYANSU ? SHINSUMA ZASU IYA KARBAR HUKUNCI ?DUK DA KASANSEWARSU MANYAN KASA*

DUK AMSOSHINKU ZAKUJI SU ACIKI WANNAN BOOK KUCIGABA DA BIBIYATA.

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

pen*is mightier than the sword*

EPISODE 1

FREE PAGE 21

TYPING□□□

...'Sallamar wani matashin mutun ne cikin shiga ta alfarma ta kayan sarauta alkyabba da rawani masu kyau tare da wani bafade guda amma shi yana bakin bakin kofa ne,Muryar shi ce ta katse da yazo dashi yakin furta meyasamu mamanah labari ya isar mun fada gata chan tana kuka,Murmushi matar da aka kita tana fad'n haba Babban sarki Norah ai ta dena kukan ma ka kwantar da hankalinka baka ji tayi shiru ba,cikin ya nayinsa da sanyin hali ya furta layla miko mun ita inganta,yana zama akan hadaddun rugs d'in dake falon na alfarma,tab'a jikinta yayi bayan tamika masa ita,ajiyar zuciya yasauke,jin jikin nata zau da zafi,lokacin baiwar Allah har ta fara baccin wahala,Murya asanyaye yace meyasameta ne.?..

A hankali gimbiya laila tafurta tafad'i ahannun mutumin tane,kaganshi chan gefe ma shima yana nashi kukan,duban sa yakai inda Ammar suke,Bayan yagama k'are musu kallo tsaf su duka,sai kuma Ahankali ya k'yafato su ,alamar su zo,a hankli suka taso hannyensu rik'e dna juna,Ammar ne ya duk'a k'asa yayi kneeldown tare da kama kunnuwansa yana tsiyayar da hawaye yana kallon norah dake baccin wahala beauty face dinta tak'ara fitowa fess, cikin wani yanayi ya furta kace norah tayi hakri itace fa tasa na sake ta ba da ganganba,dodon kunne na naji zai fashe yakai karshen maganar kamar ya yayi ihu yake ji na jin zafin halin da norah din take ciki.....

Murmushi wanda aka kira da uncle yayi yana share ma Ammar hawayen sa dasuka kasa tsayawa,jawoshi yayi yazaunar agefensa inda D'an uwansa yazauna,A hankali yafurta mai sunan Autan maza yana jin wani abu na taso masa bayan kiran sunan Autan mazan,kayi shiru kadaina kukan nan kaji Halimatu sadiya tayi bacci ma kaga tadaina kukan yakai karshen maganae yana shafa beauty face dinta,

Ajiyar zuciya ammar yasauke mai nauyi kamar wanda waci bakar wahala yasamu hutu,Jin cewa ta hakura, wanda har uncle din saida yaji fitar ta,har Aunty da yanzu tazauna bayan gama bawa ma'aikatan dake cikin kitchen umurnin abunda zasu aiwatar yau domin bazata samu damar shiga kitchen dinba norah ba lafiya...

murmushi mai taushi gimbiya laylat ta sauke tana mai shafa lallausar sumar dake shimfid'e abisa kansa,domin kuwa tana mugun son Ammar musamman yadda yake nuna kulawar ga norah dinta,wadda tun ranar da fad'o duniya yake kokarin daukar dawainiyarta duk da karancin shekarunsa,wannna soyayya dayake ma nora har maamaki take bata ba ita kadai gaba daya a halin ma sun san yadda norah take agurin Ammar ,shiyasa take jin wani kud'uri yana shigarta ahankali .....

Bayan kwana biyu tun faduwar da norah tayi kullum cikin kuka take ga rashin bacci har saida aka kira family doctor nasu ya duba ta sannaan yatabbatar musu da ciwon kaine ke damunta mai tsanani,tun lokacin tasamu sauki bayan an rubuta mata magungunna,daga baya sai abun yadawo wanda duk bayan kamar watanni sai tayi ciwon kai da zazzabi mai zafi,Ammmar shine mai jinyarta lokacin duk da yarintarsa dan Alokacin yana da shekara shidda itakuma shekara daya da rabi Aduniya, kuma tun alokacin yadau alkawarin zama likita saboda norah ganin yadda take wahala,Domin yakula da ita ita kadai...Wannnan kenan.....

MUKOMA CIKIN LABARI

Bayine ta ko ina suna gabatar da dukkanin ayyukan dasuka zame musu Al adah wato kai kawo domin gudanar da aikin su,kowa da kalan uniform na sashen da yakewa hidima da masu kula da kofa fada, masu kula duk wani motsi na fadar,masu kula da dawakai,abun gwanin burgewa sai wanda yagani...

Tangamemiyar masarauta ce mai tsaunukkan gine gine masu kyau irin dai yadda kuka san ginin gidajen sarauta suke,tako wanne gefe haskene tar kamar rana na ban mamaki ko lif lif da shuke shuke,ga gurin aje dawakai da motoci na alfarma.

Wata faffadiyar koface wadda zata sadaka da fadar sarki nan na kutsa kaina domin dauko muku rahoto duk da manyan dakarun dake tsaronnata ..

Had'addiyar fada ce mai abun burgewa tako ina fadawa ne atsaitasye ga wata kujera ta alfarma wadda tasha adon gold sai shining take yi ga fadawan dake gefen kujear baibaye da ita sai fifita sukeyi ma wanda ke kan kujerar ta alfarma Ahankali duk da AC din dake huro iska mai dadi wanda yahadu dawani kamshi...

A hankali fadawan suke furta gyara dai sarki Mai dubbanin alkhairai,Allah yakara lafiya,jin tarin dayake yi wanda ke nuna alamar mura ke damun mai yin tarin,Hannunsa yad'aga cikin nuna mulki da Izzah,Alamar ya isa A hankali naji kyakkyawan dattijon da bai haura shekara sittin ba yayi magana da muryarsa mai nuna dattako da manyan taka,yana mai furata "har yanzu yarima baice komai ba ne galadima"?

Mutumin da naji ankira da galadima ne naga yaduk'ar dakansa yana furta Allah yataimaki sarki,ehh haryanzu bai nuna yaga sak'on mubah,yau wata takwas kenan,ni anawa ganin Allah yataimaka sarki kawai akyale sa sannan Ku gyara tsakaninku....

Wani murmushi mutumin yasaki Wanda yatsaya iyakar labbansa,zaka gane hakan inka kura mai ido duk da yana cikin rawani ,shiru baiba galadima amsa ba,saima mikewa da yayi,Dan danan fadawa suka fara karesa suna furta gyara dai sarki mai dubbanin alkhairi,gyara dai sarki mai masarautar gado mai garin na sambo,,,

Mai garin na sambo zai fito,wata murya CE ke d'aga wannnaa sauti a waje,kirari suka cigaba da yimasa tare da kara gyara masa alkyabbar sa ta alfarma sai walkiya take na duwatsun gold,A hankali yake takawa harsuka fito daga babbar fadar tasa sai dai yau baibi ta kofar dazata sadashi da sashen UNNI ba

Yafito ne ta kofar dazaka iya ganin komai dake gudana atsakiyar masarautar,tafiya yake yi Ahankali inda duk inda sukabi ma'aikata bayi sai sun masa irin gaisuwar nan da yan Korea suke yi a series dinsu na sarauta ga shuwagabannisu gamasu kallon su zaku gane yadda nake nufi Niko vow suke cemishi....

(Adan sunkuyar dakai kadan sai alankwasa hannu biyu ahade su guri daya kamar mai daidaton sallah,sai a saita shi akan tsakiyar goshi)Allah yasa kunhgane😉

Kansa kawai yake d'agawa alamar karba gaisuwar tasu acikin lemar da suka ware masa ta alfarma, har ya isa inda manyan motocin suke aparkey na alfarma,Isar sa wurin d'ai daga cikin fadawan da ke lullube dashi ya bude masa wata arniyyar parado new design bak'a wulik mai tinted glass irin yan 57billion dake parkey agefe cikin wata had'addiyar rumfa inda dagani nan ne mazaunin aje wasu motocin na musamman😳 kai FA'EEH wannan karya...koda yake abunda nagani ne ai😇

Ahankali yashiga cikin motar dai dai Wanda ke rike da dai Wanda ke rik'e da had'addiyar umbrellan da suka kara masa tun lokacinda aka shimfida masa bugaggiyar carpet ta alfarma an rubuta MURAI'S PALACE akanta cikin tsari mai kyau....

Bayan shigarsa motar tafiya kad'an sukayi da direban da yatuk'osa da sauran fadawan sa dasuka k'asa da algaitu da busa suna masa kirari,motar drivern yafaka A wani tangamemen gida dake d'ai daga cikin gidajen masarautar na alfarma,take fadawa suka zagaye motar suna masu kakkaresa bayan yafito a lokacin har an kara shimfida masa carpet tare da bud'e masa umbrella ta alfarma abun gwanin burgewa sai Wanda yagani wollah in maku hausar mu ta sakkwato😀.

Tafiya kad'an yayi ya Iso kofar shiga mai rike da had'addiyar kofar ce wadda zata sadaka da falo, ya wangale masa bayan ya rusuna masa alamar gaisuwa

Shigarsa had'adden falon na alfarma yabani damar debe keyar ido nah masha Allah nake furtawa tsayawa kwatantamuku tsaruwarsa bata lokacin ne,falon yaji komai na more rayuwa....

A hankli dukkanin bayin dake kai kawo suna hidima asashen suke rusunawa suna gaidashi hannu kadai yake iya d'aga musu har ya isa wata kofar inda naga wata dattijiwa mai uniform wasu colour masu kyau tafito,Ashe Babbar Amintacciyar masarauta ce tun lokacinsu Ammi take hidima dasu,

Inda yanzu ma ita keyiwa sarauniya hassaana da sarki duk da bawata hidimar bace kawai dan duba sauran ma,aikata ne sai yin iso ga sarauniya,

Iso tayi ma sarki ga sarauniya bayan tagama yimasa kirari nuna gasuwarta bayan ya karba tawucewar Alokacin duka ma,aikatan kowa yacigaba da aaikinsa....

Sallamar ce acikin uwar dakin tasanya kyakkyawar matar dabazata wuce shekara Arba'in wadda daka ganta kaga zubin larabawa, in kallo daya zaka mata kagane wacece ita idan har kasan gwarzon d'anta,Amsa sallamr tayi atsanake cikin murya mai nuna farinciki,furtamasa tayi "marhaba biki shugaba adili ya zaujaty ,Abul mahir Abul yuhanis,Abul Abdul rashid " takai karshen maganar ciki. Kara kawata fuskarta da murmushi,Murmushi yake ta saki Wanda yake kara kawata fuskarsa dan yana mugun son wannan kirarin Nata murmushinsa ne yafara gushewa jin furucinta nakarshe

Wanda dama tasan hakan zata faru shiyasa bakasafai take yimasa shiba,Wanda aduk lokacin da tamasa kirarin ta ambaci sunan Abdul rashid,Abu uku ne ayanzu ke zomasa arai damuwar d'an yarima,dakuma k'anensa daya b'ata shekara talatin da suka wuce dakuma dakuma babban rashi dasuka yi na dan uwansa da iyalansa a shekarun baya,b'at murmushin dake kan fuskarsa yakyau zuwa hawaye bayan jin komaai yadawo masa sabo arai.....

Chakwakiya to ko meyasamu dan uwan nasa da iyalansa?wane kalar rashine ne wannan

Shin wanene kuna d'ayan d'an uwansa daya b'ata kuma ashekarun baya?

Ko suwaye wayen yan uwan NASA?

Gaskiya yabani TAUSAYI dattijon nan ☹nima kamar inzubda masa da hawaye

Shin ko kungane wane yarima ake

magana ?

Duka zaku samu cikon amsoshinku anan gaba kadan

Kucigaba da bibiyata duk zan warwaremuku in sha Allah In Allah yamauna aron rai

A MAFARKI NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!✌✌

TALLA!!! TALLAH!!! TALLAH

ina yan kasuwa masu son tallata hajarsu,toh ga dama tasamu domin muna tallata kowace irin hajace daga jihohi daban daban harma da k'asashe,akan farashe mai sauk'i,zaku iya tuntub'armu ta lambobin waya kamar haka.....

+2348069059746

+2348084504630

A MAFARKI NASANTA

2023 novel is the story of an innocent girl call Halee yarinyar da *tataso cikin rashin iyaye sannan ta* *had'u da kalubalin rayuwa mai matukar* *girgizawa inda bayan haduwar ta da* *iyayenta,wayenda suke nesa da* *rayuwarta tasamu loosing memory,sai* *kuma takara samun "psycho" tab'n* *hankali kenan shin ko meye silar* *faruwar hakan?ya ALAMARI AKWAI* *RIKITARWA,SOYAYYA KAM ZAKU* *SHATA,SANNAN YAR UWA ZUCIYARKI* *ZATA TABU*.....*SHIN KO WAD'ANNAN YAN TA'DDA* *ALKALAMINA ZAIYI AIKI KANSU?SU WANENE ABAYANSU ?SHINSUMA ZASU IYA KARBAR HUKUNCI ?DUK DA KASANSEWARSU MANYAN KASA*KO MASU MUKAMIN *MENE DASU DA HAR ALKALAMINA YA KIRA SU MANYA KASA*....

DUK AMSOSHINKU ZAKUJI SU ACIKI WANNAN BOOK KUCIGABA DA BIBIYATA

---

https://chat.whatsapp.com/GNSky8tcQT72iE1IVm7Vpt

A MAFARKI NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!

TALLA!!! TALLAH!!! TALLAH

ina yan kasuwa masu son tallata hajarsu,toh ga dama tasamu domin muna tallata kowace irin hajace daga jihohi daban daban harma da k'asashe,akan farashe mai sauk'i,zaku iya tuntub'armu ta lambobin waya kamar haka.....

+2348069059746

+2348084504630

A MAFARKI NASANTA

In my dream i know her

2023 novel is the story of aninnocent girl call Halee yarinyar da *tataso cikin rashin iyaye sannan ta* *had'u da kalubalin rayuwa mai matukar* *girgizawa inda bayan haduwar ta da* *iyayenta,wayenda suke nesa da* *rayuwarta tasamu loosing memory,sai* *kuma takara samun "psycho" tab'n* *hankali kenan shin ko meye silar* *faruwar hakan?ya ALAMARI AKWAI* *RIKITARWA,SOYAYYA KAM ZAKU* *SHATA,SANNAN YAR UWA ZUCIYARKI* *ZATA TABU*.....*SHIN KO WAD'ANNAN YAN TA'DDA* *ALKALAMINA ZAIYI AIKI KANSU?SU WANENE ABAYANSU ?SHINSUMA ZASU IYA KARBAR HUKUNCI ?DUK DA KASANSEWARSU MANYAN KASA KO MASU MUKAMIN MENE DASU DA HAR ALKALAMINA YA KIRA SU MANYA KASA*....

DUK AMSOSHINKU ZAKUJI SU ACIKI WANNAN BOOK KUCIGABA DA BIBIYATA

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE22

TYPING

A hankali tataso daga kishingid'en da take zuwa wurin mijinta cikin had'addiyar alkyabbarta

Hannunsa talakamo acikin nata sannan ta zaunar dashi akan hadaddun rugs din dake cikin bedroom din nata mai had'e da tafkekiyar tv da wankacecen gado na alfarma da tintimi irin na gidan sarauta mai taushi akan tattausar turkish carpet dake malale adakin

.....Hawayen sa share masa tana mai kwance masa rawanin da yarufe rabi da kwatar fuskarsa,nan da nan fuskar Ammar ta bayyana agaresa hatta yanayin chocolate colour skin dinsu iri daya ne,duk da yafi kama da mahaifiyarsa ta idanunta da lips dinta ammar hatta girarsa irin ta mahaifinsa ce da tsawon,inbaku manta ba mahaifiyarsa da mahaifinsa tsatso daya ne Diyan wa da k'ane ne shiyasa zaka ga kamar dukkansu kamar su d'aya iayayen nasu da.....

Bayan ta cire masa rawanin ta taimaka masa yacire alkyabbarsa tare da taimakon sa,A hankali ta bd'a fridge din dake chan gefen wata kofa da nafi tunanin store ne da karamin kichenn,dauko filet da glss cup mai kyau tayi na alfarma tadauro ruwan da juice masu sanyi

Tsiyaya masa tayi tana mai kara masa abakinsa kurb'a guda yayi yajanye bakinsa yana mai sauke ajiyar zuciyah,A hankali ta bud'a bakinta ta ambaci sunansa "Ya Aliyu"haka take cemasa idan suna keb'ance ko zaujy , agaban al umma kuwa tana kiransa da maimartaba wannnan kenan.

jin Bai amsa mata ba, sai tayi Murmushi tana furtawa aranta yau kenan sarautar takaara motsawa,murmushi takara saki tunowa da duka rabin halayen Ammar shiya kwaso komai nasu duka d'aya tafannin halayya...

Magana ta cigaba da yi cikin natsuwa "kayi hakuri yaa Aliyu nasan dukkanin damuwar ka,In sha Allah Hamma Abdul zai bayyanah"

' sai ga hawaye shar a idanunta gefen hannunta tasanya tashafe cikin jin wani zafi yana taso mata acikin ranta,

"Tabbas ina ji ajiki nah laila da hamma umar suna acikin ni'imar Allah,kabar sanyawa kanka damuwa kuma in sha Allah ko wanene sila asirinsa zai tonu duk da bamu da wata shaidar cewa ga yadda abun yafaru Amma inaji ajiki nah komai yafaru ne akarkashin sharrin wasu kuka ne ya kubce mata mai karfi,bai hana ta ba,sai da tayi mai isarta sannnan ta tsagaita dan shima kanshi hakuri kadai yake yi yana ji kamar ya fasa nasa kukan ne...

Jawota jikinsa yayi ya rungume ta yana cigaba da lallashinta,A hankali sarki Ai ya furtawa gimbiya hassana "bansan abunda yasanya zuciyatah takasa gasgata cewa emir da layla sun mutu ba

Ako dayaushe inaji kamar zasu dawo garemu ne,inaji ajikina dukkaninsu har Autan maza zasu dawo garemu nan bada jimawa ba,Bayan sauraren maganar mijin nata sai tayi murmushi wanda yafi kuka ciwo.....

 ta furta" yayah Aliyu sai dai mujira dawowar hamma Abdul...shida kawai mun wayi gari babu sa,kamanta Cewa Ansamu gawawwakinsu bbu kyan gani norah ce kadai ba,asamu koda kashinta ba,sai hawaye shar aidonta cigaba da maganar ta tayi

kagakuwa Kuwa babu yadda za,ayi su dawo garemu.....Ta idar da maganar cikin wani yanayi mai radadi da ciwo..

Murmushi yak'e yayi bayan jin zancenta,danshi sai yanzu ma yake kara tuna wasu abubuwan a lkacin da yarasa d'an uwan nasa da iyalansa,

Tambayar kansa yayi tabbas akwai zoben azurfa wanda mahaifinsu yasamusu duk su duka kuma alokacin da yasanya musu shi yasanar musu da cewa azurfar zinari ce mai kyau wadda ko wuta baza ta iya k'onata ba,ko da ace wutar ta tab'a ta zaiyi wuya ta fita hannun mai ita inbashi yacire ba,

K'ara tuno lokacin da za,a wuce da gawawakin su kushewa bayan yimusu yar dubar domin ruwa bazai sanyu ajikinsu saboda yadda suka chanza kamanni,sai dai gwargwado abunda gawar zata iya dauka,riko hannun d'an uwan nasa yayi mai kama da kwarangwal yana hawaye yana tofa masa Addu,a,A lokacin baiga zoben a hannun sa ba,sai maganar mahaifinsu tafad'o mai arai.....Zoben baijin wuta...

Tou Amma ina zoben yashiga da suka k'one k'ila yafita tare da naman jikinsa,touh ina zoben yashiga acikin gidan?sai maganar mahaifin su ta fado masa arai inda yace "koda wuta ta tab'a zoben zai zauna hannun maishi ne,sai idan ancire sa da dubara",Alokacin tunani barkatai ne sukayi ta zomasa arai,duk sai ya watsar dasu saboda tashin hankalin da suke ciki alokacin.....

Abu daya ne yatsaya masa arai maganar rashin samun gawar norah ko wata alama ta nuna akwai ta awurin....

Maganar gimbiya hassanat ce tadawo dashi daga firar zuci ko ince tunanin dayake "Cin abinci ko wanka zaka fara ?sannan insa Akawo ma nan?ganin yafada duniyar tunani....

Murmushi ya dajin jerun tambayoyin da ta jero masa,Cikin kara yin murmushi " har yanzu yarinya kike komawa,hassnat duk wayenn nan tambayoyi yanzu amsa suke nema,murmushi tasaki tana mai d'aga masa kai tare da gyara daya,murmushin yakara saki mai hade da dariya ganin yau rigima take ji,itama karamar dariyar tayi,furta mata ya afara hada mun ruwan wanka,nabiyu abinci da adining zanci tareda "ya "yana...

Murmushi tayi tana furta kamanta yau akwai school mahir yatafi itakuma yuhanis taana gurin husaina,murmushi yasaki yana shafa gemunsa wanda yafara tara yar furfura ooh hakane fa kinga na manta da auta na kusa yau da anga rigima cewa zatayi namanta ta ta baki daya tunda har namanta cewa tana gidan husaina...

Murmushi unni tayi tana furta aiko dai sarkin rigimar ka sai kai

Murmushi yakaryi yana furta toh akawo mun nan gimbiyata,murmushi tasaki jin furicinsa,har tajuya ta tsinkayi muryar sa yana furta shin kunyi waya da mai sunan Autan maza?

Chak ta tsaya domin abazata taji domin anyi shekara bai mata magaanarsaba saboda fushin da yake yi dashi,Akan kafewar sa,wanda har ita sai da abun yashafa sarki yashareta nawata daya kanta saka bakinta ya bar mganar tunda baiso wanda kuma kullum cikin bincikar yaron nata take koza'a dace tunda shima kaifi daya ne kamar mahaifinsa....

Idan bazata manta ba yau shekara da wata takwas ko ma tara za,ace da sarki Ali baiyi maganar Ammar din agabanta ba duk da abaynta yana bibiyarsa,ta email wanda kosun tura sakon baya dubawa,yana boye mata ne gudun kar ta ga kamar ya karaya shiyasa bai bata damar yimasa maganar sa agabansa ba...

Murmushi ne yasubuce mata.....

Nima anan zan dakata sai gobe in Allah yakaimu

Inkunyi comment da yawa zaku samu long page gobe ,zanbiyaku bashi ne kawai na jiya alhamis da bakusamu ba

Kunsan weekend bana typing ranar hutu ce

Like pls comment share

DAGA ALKALAMIN ✍

□FA'EEH BG□

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE23

TYPING□□□

Juyo wa tayi a hankali tataka inda yake zaune ta kafesa da idanunta,jin idanunta akansa yasanya sa kawar da kansa Yana mai lakace tsinin hancinsa,irin yadda Ammar yakeyi inyana cikin yanayi mai kyau

Hannayensa ta rik'o tana furta Alhamdulillah aranta,A hankali ta bud'a bakinta tafurta nayi magana dashi shekaranjiya,yana lafiya shida d'an uwansa,tambayar ta yak'ara yi har yanzu yana kanbakansa duk da yana da labarinsa,Amsa tabashi cikin d'ar d'ar "eh amma ina nan ina kokarin janyo tunaninsa izuwa garemu da fushina...

" Dan duk lokacin da mukayi waya dashi ina nuna masa fushi na inbarsa cikin zullumi nasan cewa baison damuwar d'ai daga Cikin mu,ko sharekan da yayi nasan kai kafara nuna masa taurin kai irinka naka,Allah kad'ai yasan yanayin dayake ciki ayanzu,zuciyarsa akar ye take,ni nasan waye Ammar cikin sa da bayansa,kuma nasan waye mahaifinsa...takai karshen maganar cikin jin tausayin yaron nata wasu hawaye ne suka zubo a idonta..

Murmushi sarki Ali yasaki jin kalamin ta na k'arshe..

"A hankali ya furta na janye maganar bashi sarautar,ayanzu inaso su dawo kusadamu gaba d'aya

Ayanzu haka nakusa kammalla Gina masu babbar asibitinsa domin sudawo su rik'e ta shida d'an uwansa su kula da ita....

Farinciki ne mai yawa ya bayyana A fuskar gimbiya hassana,rungume sa tayi tana zubarda hawayen farin ciki da godiya ga Allah,daya nuna mata wannnan rana data dad'e tana mafarki

Shima rungume ta yayi cikin farin cikin dayasamu kansa a cikin cigaba da maganar sa yayi " nasan cewa Ammar yana da kud'in da zai Gina wannan Asibitin,Amma na zab'i inginata masa ita dakaina saboda inason yarike ta da mahimmanci idan yatuna wannann kyautar mahaifinsa ce a garesa,kuma A duk lokacin da akayi ceton rai

acikin Asibitin nasan cewa ladar zata je garemu kobama Raye muda sauran iyayenmu...

In sha Allah wannnan Asibiti zata zamo Abin Alfahari acikin wannna kasar mu tana Nigeria dama sauran kasashen...

'Murmushi da dariya ne yake fita akan fuskar gimbiya hassana a lokaci d'aya k'ara rungume sa tayi acikin jikinta,

Murmushin ne shima yake yi na farincikin ganin yalwataccen farinciki a akan fuskar matar tasa,Wanda tada d'e batayi ba, Wanda tun bayan da yafara maganar murabus,juya mulki ga Ammar d'in,Wanda alokacin anti tak'addama sosai dan yakafe yace baiso mulkin shiyasa mai bai cika kawo musu ziyara tun da yaji anfara maganar,sai dai tawaya su gaisa shida mahaifiyarshi da "yan uwansa,Dan har wayar sarki yabar kira tun lokacin da akayi rigimar yakira mahaifin nasa yafi missed call ishirin bai d'aga ba,domin alokacin yana fushi dashi mai tsanani,saboda maganar da sukayi inda yake sanar masa kar yak'ara kiransa da mahaifinsa indai bazai karb'a ba,shiyasa daya kirasa bai d'aga ba domin yasan ba maganar da yakeson ji d'aga bakin sa bace zai furta masa...shiyasa shima sai yasharesa bai k'ara Neman saba tun lokacin duk da dukkansu suna azabtuwa,Amma zuciyar d'ayace,kowa kafiya da taurin rai..

Sarki Ali yatsinci kansa sosai cikin farinciki sanin da yayi Ammar d'nsa zaiyi farinciki fiye da nasa jin wannan labari....

Wayarta tadauko dasauri bayan mik'ewarta d'aga jikinsa,muryarsa ta tsinkaya yana furta karki sanar masa sai ankammala komai har janye maganar basa mulkin,b'ata fuska tayi,tana furta "saboda me adili"? "

Murmushi yayi ganin yadda tayi kamar wata k'aramar yarinyar,yana furta inaso ne kawai yazame masa Abun kamar A MAFARKI ne murmushi tasaki,tana furta hakan yayi, Amma dai bari insanar wa sister wannan abun farincikin sai muyi farincikin tareπ

"Murmushi yayi yana furta to ki kwatse ta koh kar ta kirasu ta sanar da Al Amin,Amsawa tayi cikin k'aramar dariya ai ko haka za,ayi.....

Ruwan wanka ta had'a masa a cikin k'aton bahon wankan na silver mai kyau,dake a cikin had'ad'den k'aton toilet din dak'in nata Wanda yaji kayan k'yalk'yali ta ko ina.....

Bayan yashiga yayi wanka tafito masa ta da kayan da zai sanya,sannan ta fita domin Bada umurnin akawowa abinci a turakarta,A falon da na biyu kamin kashiga uwar dakin nata,Abincin suka jera cikin tsari mai kyau akan wata had'addiyar carpet din dake malale afalon,Alokacin duka ma'aikata sun gama ayyukansu na rana...

Kuyi hakuri da wannan ba nida isashen chaji ne

Shinko kuna ganin Dr.Ammar zaiyi farinciki?

Kuma zai baro k'asar India?

Shin ko akwai sanadin da yakai sa k'asar India karatu,ko ko dai Ra,ayin kansa ne?.....

Jama'a ina labarin Halee nasan wasu harsun manta da ita .....

A gobe in sha Allah zamu lek'a rayuwar Halee baiwar Muji a wani hali take sannan wace irin rayuwa take fuskanta ne ayanzu shinko Baba Asabe ta shafa mata lafiya ganin idanun Baba Asabe ko kodai tacigaba da muzguna mata.....

Wacece ita?

Mekuke tunani game da rayuwar Halee?

Mu had'u a comment section dan jin hasashen kowannenku.....✍✍

Shin tsintacciyar ce dagaske kamar yadda Baba Asabe ke yawan furtama taa?

Shin waya bada Amanar Halee da har Baba Adee yakirata da Amana?

Sannan waya bada Amanar ?

Waih.....

Nima fa kaina ya kulle

Kudai kawai kucigaba da bibiyar Alkalamina✍✍domin Warware muku wannan labari mai cike da darussa...

Kuyi sharing kuyi comment

 FA'EEH BG

A MAFARKI NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!

TALLA!!! TALLAH!!! TALLAH

ina yan kasuwa masu son tallata hajarsu,toh ga dama tasamu domin muna tallata kowace irin hajace daga jihohi daban daban harma da k'asashe,akan farashe mai sauk'i,zaku iya tuntub'armu ta lambobin waya kamar haka.....

+2348069059746

+2348084504630

A MAFARKI NASANTA

2023 novel is the story of an innocent girl call Halee yarinyar da *tataso cikin rashin iyaye sannan ta* *had'u da kalubalin rayuwa mai matukar* *girgizawa inda bayan haduwar ta da* *iyayenta,wayenda suke nesa da* *rayuwarta tasamu loosing memory,sai* *kuma takara samun "psycho" tab'n* *hankali kenan shin ko meye silar* *faruwar hakan?ya ALAMARI AKWAI* *RIKITARWA,SOYAYYA KAM ZAKU* *SHATA,SANNAN YAR UWA ZUCIYARKI* *ZATA TABU*.....*SHIN KO WAD'ANNAN YAN TA'DDA* *ALKALAMINA ZAIYI AIKI KANSU?SU WANENE ABAYANSU ?SHINSUMA ZASU IYA KARBAR HUKUNCI ?DUK DA KASANSEWARSU MANYAN KASA KO MASU MUKAMIN *MENE DASU DA HAR ALKALAMINA YA KIRA SU MANYA KASA*....

DUK AMSOSHINKU ZAKUJI SU ACIKI WANNAN BOOK KUCIGABA DA BIBIYATA

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S□□

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE24

TYPING□□□

INDIA.....

wata kyakkyawar yarinya ce mai zubin asalin larabawa fara tass da ita ta isko sa zaune abakin ruwa,itama sai ta zauna akusa dashi,ba yanzu ne yafara ganinta ba bare ya damu Akullum tana zuwa wurinsa suyi fira wata rana ma fad'a,ta bud'a bakin ta kenan Tana furta D'an uwanah sai ga wasu mutane masu bak'ak'en kaya sunzo wurin da zuwansu suka yi kan wannan yarinya suka daddafeta tana kuka tana rok'on karsu cutar dashi,wanda shima wasu sun rirrik'esa kasancewar su majiya karfi sai yaakasa kwatar kansa agaresu bare itama yataimaketa,haka suka sanya bindiga suka harbeta yana kallo ga kukanta da yake ji har tsakiyar kansa zuciyarsa har wani b'al b'al take na tashin hankali,suna gamawa da ita duk sai suka gudu har wayenda suka rik'esa suna masu furta masa kaima zamu dawo kanka,baibi takansu ba sai yadda zai ceto ranta yakeyi, sai ma Rungume wannan yarinya da yayi wadda har yanzu baian sunantaba Amma yasaba da ita sosai har sonta yashigesa baisani ba duk da yana kokarin b'oyewavzuciyarsa hakan

Kuka yake kamar wani k'aramin yaro yana jijjigata wanda take mayafin dake kanta yazame wanda yabbayanar da lallausar doguwar sumar ta har yarufe mata rabin fuskarta saboda yadda yabarbazu,ganin ta fara nisa ne Alamar mutuwa zatayi yayi ga jininta yana ta zuba,yasanya vail dinta yad'aure mata inda suka harbetan aciki ganin jinin yak'i tsayawa ne kuma yasanya sa cikin rud'u yak'ara sanya handkerchief d'insa yana k'ara danne wurin harbin,kuka yake cigaba da yi yana girgiza kansa alamar no cikin rud'u lallausan gashin kansa duk ya hargitse,sungumar ta yayi kamar wata jaririya yana yi yana kallon kyakkwar fuskarta ganin yadda take fitar da numfashi na wahala,

Takawa yafara yi daniyar bata agajin gaggawa acikin gidan nasa sai yaga hannayenta sun saki yaraf Alamar ta mutu kenan,wata uwar k'ara yasaki yana girgizata a matuk'ar rud'e yana furta "nooo karki tafi kibarni",ganin bata motsaba yakara furtawa cikin fitar hayyaci "karki tafi ki barni" Yana kuka kamar karamin yaro .....

Misalin karfe 3 :00 na dare

Kwance yake akan had'adden gadonsa juye juye yakeyi akan gadon kamar wanda ke cikin wani yanayi na damuwa,ya had'a zufa duk da karfin a.c dake a bedroom din nasa da sanyin da gari yake dashi na watswar hadari Dr.Ammar kenan.....

Bayan kamar minti hud'u ya farka agigice cikin fitar hayyaci yana furta "karki ki tafi ki barni",A hankali yafara yadawo wa cikin natsuwarsa Addu'o'i yayi na neman tsari Akan mafarkin dayayi,take mafarkin da yagama yi yafara dawo masa akai kamar ayanzu abun ke faruwa duk da yasaba yin mafarkin sa da wannan yarinya,Ammana ya yau yabashi tsoro..

Tagumi Ya rafka bayan gama tunano da mafarkinsa wanda yasha banban da sauran mafarkan nasa da yarinyar,Dan shin ruwa da yaji akwar min idonsa ne yasanya shafo kyakkyawar fuskarsa da lallausan hannunsa guntun hawaye ne yaji sun gangaro suka zubo acikin idanun nasa bisa beauty face dinsa big sparkling eyes nasa sai suka kara haske da shining na ruwan hawayen da ke cikinsu curly eyelashes nasa suka k'ara cure wa waje d'aya...

Tambayar kansa yayi shin yanzu dagaske sun kashe masa ita?kuma suwane ne wad'an nan mutane da har suka yi masa barazana?,me ta musu?meye had'inta dasu,?yana jin badadi aransa zuciyarsa tayi d'aci mafarkin nasa na yau abun yatab'a shi duk da yasan mafarki ba gaskiya bane,Amma yasaba da yarinyar tana tayashi fira abakin swimming fool nasu shiyasa akodayaushe yake yawan zuwa bakin ruwan ko zai ga koda fatalwartace ....

Tambayar kansa yak'ara yi wacece ita da har ta iya kiransa da D'an uwanta? duka wayen nan tambayoyi suna tayawo ne acikin kwakwalwarsa,rasa mai basa Amsoshin tambayar sa ne yasanya shi tashi yayo alwallah,ya zura jallabiya fara mai taushi,akan short d'insa,ya shimfid'a sallaya ya raya darensa sannan yayi karatun alqur'ani mai girma acikin zazzakar muryar sa domin kuwa Dr ammar akwai kira'a yana da hizif talatin akansa ne,

Addu'o'i yayi na Allah yasa mafarkinsa ba gaskiaya bane,sannan yanemawa kansa kariya da wannan baiwar Allah da haryanzu ko sunanta baisani ba,sannan yayi Addu'a ga k'anen mahaifinsa da nora da na Allah yajik'ansu da rahama,yakuma bayyanar da takwaransa lafiya,sannann kuma yana Addu,a da fatar Allah mahaifinsa yasauko daga fushinsa,sannan yayiwa Al ummar musulmi addu,ar zama lfya, ire iren wayen nan Addu'o'in sune yayi sannnan yacigaba da kira'ar sa har yaji ankusa tada sallar asuba,fitowa nasa d'akin yayi yana k'wankwasa ma Aj kofa A lokacin shima Aj ya shirya suka d'unguma sai masallacin unguwar su....

NIGERIA

BUNGUD'U ZAMFARA

Halee ce ta mik'e zaune daga barcin da take yi tana furta innalillahi wa inna ilaihi raji'un,khady ce itama ta mik'e zaune tana tambayarta lfya?,

A hankali ta bud'a bakin ta cikin rashin kuzari da tsoro ta furtawa khady cewa "mafarki nayi",dafa ta khady tayi tana tana furta kamar wane kalar mafarki kenan..Shiru tayi mata tana jin zuciyar ta ba dadi,sai kuma ta fara bata labarin mafarkin nata 'wasu mutane ne suka zo kasheta sai ga wani mutun mai kayan sarauta ajikinsa yazo yataimake ni sai dai banga fuskar sa ba saboda rawanin dayarufe fuskartasa,ahaka yayi iya kokarin yakare ni sai dai Allah bai nufa ba sai suka kasheni,sannann kuma kafin in mutu naji suna furtamasa saura shi shima zasu dawo kansa,dukkaninsu jikinsu yayi sanyi musamman Halee dake bada labarin tanaji kamar abun zai faru dagaske ne,kasheta d'in da maganar da suka furtama wannan bawan Allah,Khady ce cikin kwantar ma Halee da hankali ta furta karki saka damuwa Halee mafarki ba gaskiya bane,ni wai ma kinyi Addu,ar kwanciya kuwa?ta tambayeta ne duk da tasan Halee bata wasa da Ibada,tasan awasu lokuttan ma ita ke shafeta da Addu, a in bacci yadauke ta batayi ba,ta tambaye ta ne kawai domin kawar mata da tunanin da ke shirun addabar ta,d'an kallonta Halee tayi cikin damuwa tana langab'e wuyanta kyakkaywar fuskarta takara kyau,kara furta mata khady tayi ganin bata bata amsa ba,aikin shed'an ne kawai may be kinyi kuskure awurin yin Addu,ar ne musakeyin Addu'ar ta furtama Halee da ke ta Kallonta,murmushi tayi tana furta mukawana lafiya bayan gama Addu,ar tasu suka gyara kwanciyar su,Amma ita kam Halee har Asuba tayi bata runtsa ba,tunani ne barkatai ke zomata...

A hankali ta mik'e daga kan katifarsu zuwa toilet nasu ta dauro alwallah,raka'atanil fajr ta gabatar sannan tayi Asuba tagabatar da Addu'o'in ga wannan bawan Allah,wanda ko da ace tagansa afili bazata iya ganesa saboda rawanin da yayi k'awanya wa fuskarsa,sannan tayi Addu'ar Allah ya had'a ta da iyayen a Aljanna idan har sun mutu..

Inkuma suna raye Allah yabayyanar mata dasu,Byan tayi karatun alqur'ani acikin zazzak'ar muryar,dogon hijab dinta na sallah ta cire ta lunke,sannan tasanya d'an k'araminta na tsakar gida komawa tayi kan katifar su d'an runtsawa kafin gari ya waye taje yin ayyukkanta basai Baba Asabe tazo tashinta ba,saboda weekend ce babu makarantan boko sai ta islamiyya,gashi Baba Adee ya koma mafara gurin aikinsa tun satin da ya wuce.....

Bayan ta kwanta baccin yagagareta tunanin mafarkin da tayi take

Hawaye ne ke silala a idonta wanda bata san dalilin su ba,ko na tausayin wannan bawan Allah ne ko na tausayin rayuwarta ne,shesshekar kukanta ne yasanya khady bud'e idanunta tar akan Halee bayan jin shesshekar kukan nata,wadda tunda takoma barcin bata tashi ba saboda tana fashin sallah...

Leka kyakkyawar fuskar Halee tayi dan ta tabbatar indagaske ne kukan takeyi duk da tasan kuka bai wa Halee wahalar yi,sharkaf taga kyakkaywar fuskar Halee da hawaye batace mata komai ba tabarta tacigaba da shesshekar kukan ta sai da tayi mai isarta ko zuciyarta zata samu salama,domin yin kukan ma wata rahama ce ga d'an Adam...

Bayan ta tsagaita da yin kukan sai kuma bacci yakwasheta daga nan kishingiden da take.....

Halee baiwar Allah

Koda ta farka har khady tayi wanka tahad'a mata musu abun da zasu karya dashi sannan ta gyara ko ina na gidan har jidan ruwa ma tagama A murtsatse.

Kallonta kawai Halee keyi wadda tafarka cikin zullumi tuna wa dayau batayi aikintaba,kafe khady tayi dake zaune akan d'an madaidaicin mirron d'akin nasu ta shiryawarta cikin doguwar riga ta atamfa, da manyan idanunta da tambayoyi barkatai aranta, khady lura da kallon datake mata ne yasanyata yin murmushi tana furta madam ki tashi kiyi wanka mu karya sai kiji komai,Murmushi itama Halee tayi har sai da fararen hak'oranta suka Bayyana tana mai mik'ewa tazuro fararen kafafun ta sannan takama hanyar toilet,tareda daukar flask na ruwan zafi ahannunta,har takusa kai bakin kofar toilet din ta tsinkayi muryar khady na furta Aunty na had'a miki ruwan wankan ki maido da flask din murmushi Halee tayi,tana juyowa Ahankali tasakarma khady yar karamar harara tana furtawa cikin sanyin murya "nikam banace kibar cemun Aunty ba?,harda wani rik'e habarta irin ba wasan nan,khady kuwa mezatayi in ba dariya ba ganin yadda halee tayi,"watan ma dariya nabaki tak'ara furtawa cikin d'an murmushinta mai narkar da zuciyar yan maza,har sai da dimples dinta suka bayyana,take kuma tak'ara turneke fuska irin ba wasan nan,Khady ce cikin dariyarda ke cinta gani fuskar da Halee tasha,kama kunnuwanta tayi tana kokarin hadiye dariyarta tana furta sorry shalelen dady,Itama Halee dariyar ce ta kubcemata,jinta ambaci shalelen da Baba Adee ke kiranta dashi wanda take mugun so arayuwarta tun bayan iyayenta wayendabata ko san suwaye ba.....

Wassh hannu na ai namuku kokari

Kuyi hakuri ban samu namuku editing ba.

next page tomorrow in sha Allah

Me kuke tunani game da wannan mafarki na Dr ammar?

Shin wace yarinya ce wannan?

Kucigaba da bibiyar alkalamina duk zan warware muku kowanne babi na book d'ina

Comment,like,share pls

https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!✌✌

MASU SON

TALLA!!!SHOULD *CONTACT ME VIA*

+2348069059746

+2348084504630

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE25

TYPING

Dasauri ta juya zuwa toilet din tana furta mama dije ruwan wanka na zasu huce tana dariya,tare da turo kofar toilet d'in,Dan tasan khady batason sunann nan na mama dijen da take kira mata ita kuma batason auntyn datake kira mata duk cikin su babu wanda yasan wanda yagirmewa wani acikinsu..

Khady da aka kira da mama dije har ta kumbura koda halee ta fito daga tolet daure da towel mai dan girma da hijab dinta d'an karami wanda tashiga dashi toilet din da zanen da tashiga dashi a hannunta,tunda ta fito take k'unshe dariyarta ganin yadda khady tayi kichin kichin da fuskaWadda har tabar kan madubin nasu..

d'an madaidaicin madubin nasu da yaji kayan gyara gwarwado na talaka,musamman turarukka sunfi yawa saboda Bba Adee akwai son kamshi,har sun saba da sanya sa ako da yaushe sai dai yana gargadin su kar su rika sanya mai tashi sosai inzasu fita ,sai dai su rika sanya wanda kamshinsa bai tashi kamar yadda annabi saw yasiffanta turaren mata,da na maza..Mai kala shine na mata amma kamshinsa bai tashi kamshi na jan hankali bare yazamacutarwa ga wani,wanda inkika shafa sai anmatso kusa dake za,aji kamshinsa,na maza kuwa marar kala ne sai dai mai karfi ne wanda duk inda suka giffta sai anji sa...

Bayan ta zauna akan kujerar madubin tafara yin "yan shafe shafen mu na mata akan lallausar fatar ta wadda kullum kamar ana mata wankan madara duk da bata da wata natsuwar zuciyah da kwanciyar hankali,turaruka ta fesa sunyi biyar nan da nan d'akin nasu yarikice da kamshi dan itama Halee nmba Banza ba wurin son k'amshi kajol tashafa da man baki lip glow take kyawonta yakara bayyana irin zubin larabawan qatar da fulanin eqypt..

A hankali tajanye hijab d'in dake kanta take yalwataccen gashinta mai laushi da santsi yabayyana wanda yake adunkule saboda kwana biyu baisamu gyara ba,warwareshi tayi masha Allah na iya furtawa, tajeshi tayi yasauka har kan gadon bayanta tasanya man gyaran gashi har wajen kala uku wanda take kannata yad'auki walkiya gwanin burgewa,Daure gashin take kokarin yi sai dai yana kuncewa sai danbe takeyi dashi gajiyar datayi ne yasanya ta fara alamar sakin kuka tana kallan khady ta madubi wadda ke zaune akan gabar katifar su,Khady dake ta k'unshe dariyar ta ce ta fito fili har tasauko daga fushin nata na wasa,'tana furta Allah yak'ara bake bace kinsan yadda gashin nan naki yake da santsi haka kika yi ta labta masa mai nikam ba abunda zan iya miki ta iyar da maganar ta na k'ara kwashewa da dariya har da rik'e ciki ganin yadda kyakkaywar fuskar Haleen ke nuna Alamar takai k'arshe kiriss take jira ta fasa kuka,kukan tafara kuwa dagaske harda buga kafafu ak'asa,fararen kafafunn ta kawai kake hangowa tana tsitsillasu akan tiles d'in d'akin kanta akan desk na madubi tana furta "nikam aske gashin zanyi na huta kawai, khady kuwa na kwasar dariya...

Rezor blade ta zago daga chan sakud'an madubi,harta d'aura akan jelar dogon gashin ta dake chan kan gadon bayanta tajawoshi gaba,zata yanke khady ta rik'e hannunta tana furta hurul aini meya yayi zafi haka yanzu dai bani rezor d'in mik'amata tayi tana cunno bakinta gaba,mik'ar da ita tayi tana daga kan madubin tana "furta mata Aunty yanzu idan kika aske gashinfa kuma kikayi Aure mijin ki naso yaza'ayi ....takai kqrshen maganar tana boye dariyarta ....

A hankali Halee ta furta sai insauka na kanti man irin na yan Nigerian film..

"Khady CE ta furta to inyace baya son sa fa ya zakiyi?,hararar khady tayi domin ta fara isarta da surutu Ga kanta yafara ciwo..

"A hankali ta furta Ke ni bazanyi Auren

Ba ma tana mai takawa izuwa sip dinsu sashen da kayanta suke ajiyeta bud'a dan kowa Dana sa gefe domin dinsu daban daban ne saboda Khady tad'ara Halee jiki,wata doguwar Riga roba ta fiddo da hijab karami,bayan ta sanya hijab har k'asa dama d'abi'ar tace sanya kaya acikin hijabi saboda kunyarta...

Ko khady dasuka tashi tare bazata iya kawo yadda take da kyan sura ba tunda suka fara girma ko bacci in zatayi sai ta sanya hijab,khady tayi tayi tabari Amma ina yazame mata jiki....

Tana cikin sanya rigar ne Tatsinkayi muryar khady na furta matar liman kiyi sauri kar Abincinmu ya huce gashi na zuba toh,tace mata tana furta,"Aa ah ba matar liman ba matar Malan cikin sakarma khady harara,dukan su dariya suka sanya na furucinta,tsaf ta shiya acikin doguwar Rigar ta wadda ta bayyanar da duka dirinta acikin hijab din kasancewar sa na roba ne kuma bakin kunkurunta ya tsaya ga tsayayyun breast din ta nan cikin rigar sun bayyanar da girman su saboda bata saka bra,acewar tana takura ta,turare ta fesa akan kayanta ta taka ahankali kan carpet din da Khady ta ke zaune wadda ta shimfid'a itama ta zauna,khady da ta fara cin abincinta CE ta furta zuba naki ga filet nan dan nikam naga alamar shirin naki bazai kare ba,filet ta dauka tazuba jalof din macaroni dan kad'an Khady CE tagaza yin hakurin maganar dake cinta ta furta " kin san wani abu?" Kai Halee ta girgiza mata, "wallahi Halee mijin ki zaiyi fama.....

GUSAU

Abangaren su sarki Ali da unni bayan ya fito wanka ya kimtsa da taimakon ta...

 manya manyan food flask ne farare kar tafara kwasowa daga falon nata zuwa uwar d'akin nata dakanta domin haka take bata yadda wasu suyi wata hidima ga mijin ta indai wurin cimakarsa ce dakanta takeyin komai,Kuma bata bari bayi su shiga har uwar dakin NATA inba Aminttacciyar masarauta ba wadda takasance tun ta kakanni ita take masa komai koda asashen sa ne.

Bayan tagama jera kulolin atsakiyar katuwar carpet din dake malale sai tayi masa I so yazauna kafafunsa ya tankwashe bayan zamansa,favourite food dinsa tazuba masa tuwon shinkafa da miyar kuka da taji busashen kifi zai tashin kamshi takeyi spoon tasanya masa aciki,d'ayan filet d'in tasanya masa farfeson kayan ciki dayaji gyara sai tashin kamshi yakeyi...

Abincinsa yake ci ahankali shayi ta had'a ma kanta itama tana kurb'a a hankali....

Muryar dan matashin saurayine dabazai wuce shekara ishirin da biyar ba ko da hud'u take yin sallama A cikin falon dukkaninsu Amsa sallamr sukayi suna masu kallon kofar shigowa,wani kyakkyawan saurayi ne Wanda daka gansa kaga gimbiyat hassana(unni)

Hatta farin fatar sa natane tsawonsa zai ne na mahaifinsa,kumbure fuska yayi ganin yadda duk suka tsira masa idanu kowa da kallon tuhumar da yakeyi masa....

Takowa yakeyi cikin tafiyar takama irinta tafiyar sa sak irinta Ammar zama yayi Ahankali kusa ga mahaifiyarsa yajingina da jikinta,sarki Ali dake kallonsa ne yagirgiza kai yana sakin murmushi yacigaba da cin abincinsa,kwantacciyar sumar kansa take shafawa da hannunta d'aya tana cigaba da kurbar shayinta....

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one□,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!✌✌□□

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE26

TYPING□□□

Gyaran murya sarki Ali yayi Wanda yasanya mahir d'ago manyan idanunsa yakallesa,muryar sarki Ali ke furta wai kai Baba yaushe zaka girma ne eh kullum Kullum haka kake komawa d'an jiya Yanzu idan ka karya mun kad'ar mata fa ya ida maganar Yana sakin murmushi,Dukkaninsu ma murmushin sukayi, cigaba da magana yayi wai ko kamanta akwai yuhanis A bayanka ne Yana rike hab'arsa irin mamaki...

Dariya mahir yasanya ganin yadda mahaifinsa yayi,A hankali ya furta Ayyah Abbanmu ni Dama nine Autan ba wacchan sakaryar ba,...

"Ai inson jiki ne da shagwab'a sai naga kamar ka fita ma inji" cewar sarki Ali

Murmushi kawai gimbiya hassana take ta saki jin rigimar tasu,bata cika sanya baki ba saboda Karrama sunan sunan mahaifinsu dake gareshi,shiyasa take d'an basarwa saboda Alkunyar jinin larabawa da Fulani dake yawo ajikinta..

A hankali ta furta Baba na meya dawo dakai gida irin wannan lokaci kai da kace kuna da lectures har har uku ko ma hudu ne,Agogon hannunsa ya duba karfe biyu 2:00 pm na rana ya mutsa fuskar sa yayi yana furta" unni kinga sai karfe hudu bayan la'asar zamu koma hall kuma kinga lecturen da zai muna lecturen karfe hud'un akayiwa mutuwa mahaifiyarsa ta rasu sanadiyyar gobara sanadiyyar wutar lantarki datakama gidan tsohuwar shine dukan mu duka yan hall din mu har lecturen da yake lecture awannan lokaci duk muka tafi gidan mutuwar muyi gaisuwa,shine daga chan nacewa su Abdallah na wuce saboda kaina dake ciwo",Addu,a suka yi ga mamaciyar cikin jimamin domin kowa yasan kunar wuta yadda take da azaba bare ma Ace duka jikinka ta cinye,ALLAH YAKARE MU DA SHIGA WUTAR JAHANNAMA□

Wanda Alokacin dukkansu sai da suka ji wani kololon aransu,ganin yanayin da mahaifannasa suka shiga yasanyasa jin ba dadi yanaji dama bai sanar dasu batun mutuwar ba domin yasan dama dole zasu badadi,tun da irin haka ta yataba faruwa ga uncle dinsu lokacin bashida wani wayo kuma Ammie tana yawan yin maganar agaban su cewa sun tab'a rasa family d'aya acikin zuri'ar su,ta sanadiyyar gobara,domin tana cewa dasu su rika sanya su a Addu'a,duk dashi yasan su harda yar tasu Sai dai bazai iya tuna yadda fuskokinsu suke ba duk da ance suna kama sosai ne da su,Ayanzu yana son yaji yadda labarin abun yafaru duk da yasan wani abu daga ciki...

Muryar mahaifinsa ce tadawo dashi daga tunanin zucinda yashiga"maheer kaci abinci sai kasha magani ko kaje ka d'an huta"?murshin yake yasaki jin maganar da mahaifinsa ya furta,gashi shikuma yana da tambaya agaresu,Amsawa yayi da touh! sai kuma ya bud'a bakinsa da murya mai rauni yace "Abba da Unni please ku k'ara sanar dani labarin su uncle dasuka k'one achan baya Domin Ammie tana yawan furta mu musu Addu'a inason insan silar wutar tasu...

Murmushin karfin hali irin na mahir sukayi sai kuma Ahankali sarki yafurta kanason kasan yadda labarin yake duk da nasan kasan su alokacin baya wanda bawani wayo ne dakai ba...

kai mahir yad'aga.

LABARI.....

A wata safiyar laraba da bazamu tab'a mantawa da ita ba A cikin masarauta muka wayi gari cikin tashin hankali bayan samun labarin gidan D'an uwa na Sarki Umar Yakama da wuta.....

A lokacin da labarin ya riski sarki Ali dasauran mutane masarautar sun kid'eme sosai fiyeda tunanin mai karatu,koda aka kira fire service domin kawo taimakon gaggawa duka dukan gidan yacinye da wuta ba'asamu komai agidan ba face gawawwakinsu dasuka koma babu kyan gani,A lokacin Ammi da su hassana da husaina kamar su fad'a cikin wutar dakyar akasamu suka natsu bayan anrirrike su, musamman Ammar Inka ganshi yakoma kamar zararre duk da karancinsa,kowa kagani alokacin tashin hankalinsa Abayayne yake musamman na rashin ganin komai da yashafi yarsu kwaya d'aya tilo a duniya yar shekara biyu da ba'ayi ba sai tokar,mutun d'aya zuwa biyu wayen da suka nuna ko inkula akan kaddarar da ta farma su Sarki umar ,shine muhammad (Malan) Da mahaifiyarsa fulani duk da yadda suka nuna ko ajikinsa Amma babu wanda ya zarge su akan wani abu,duk da anyi bincike ba, angano sanadiyyar tashin wutar tahanyar jin kamshin fetur acikin sashen nasu wanda aka tabbatar zubasa akayi kuma shine sanadiyyar tashin wutar, kowa yayi mamakin kasancewar fetur din acikin gidan hankalinsu ne yakara tashi fahimtar kamar akwai wani abu akasa...

Anyi zaman makoki an watse lafiya wanda har lokacin Ammar bai koma dai dai ba tun bayan da yaji yaga yadda wuta ke cin gidan uncle dinsa,kuma yaji ance gabaki d'aya sun mutu har Auntynsa da norah, duk da yadda akayi kokarin boyemusu shida mahir da Al amin,yayi suma yayi biyar ana ukun ne yayi doguwar suma wadda bai farfado ba har saida akayi ukun su sannan,Tun alokacin yafara mugun mafarki naban tsoro agigice yake farkawa sai kuma yafara yadawo yafara yin na k'aramar yarinya na kuka tana neman taimakon sa wuta na cin jikinta sai yaje taimakon ta sai ta zille ta karasa fadawa cikin wutar bata bari yarik'o ta haka yake mafarkin kullum har mahaifiyarsa da mahaifinsa suka gane abunda yake faruwa agaresa bai dawo dai dai ba sai da akayi wata biyu,wanda Alokacin Al Alamin ne mai lallashin sa ko mahaifiyarsa inda zuwa lokacin mafarkin nasa yazamo yabar ganin karamar yarinyar acikin wuta..

A baya A kullum yakan yawaita furta uncle dinsa ba mutuba da auntynsa da norah d'insa sunyi tafiya ne,inda sai da ka tayarmasa tsaye aka dage da Addu'a yadawo normal ganin abun yafara tabasa yakusa zame masa hauka,Bayan samuwar kansa sai aka tura su k'aasar india ganin cewa idan yanisanta da gida zaifi dawo wa dai dai yasake kamar kowa,Achan suka cigaba da karatunsu tundaga primary three din da suke a nigeria,sai dai kamar yadda kayi tsammani bayan zuwansu kasar india nadan lokaci,suka ga yara ire irensu ga wuraren wasanni nan kuma karatun su suke ba wasa sai Ammar yafara mantawa yafara sakin jikinsa ga sauran makarantar tasu domin boarding ce,wanda kuwa afarkon zuwansu Al amin kadai yake mu,amala dashi,A lokacin ne mafarkin daya keyi achan baya yadawo masa,A wanchan lokacin yana ganinta cikin kuka ayanzu kuwa cikin tafiyarta irinta ta yara masu wayo yake ganin tana wasarta tana dariyar ta gwanin bugewa,bata ma kulasa duk da yana ganinta tana ganinsa.

Tun mutuwar nora dinsa yace bayason yin karatun likitanci bayan tabbatar da cewa dai tatafi domin dama danta zaiyi,shi burinsa dayatashi dashi shine karatun pilot waton matukin jirgi,wanda shikuma Al Amin nasa burin keman yayi karatun likitanci,wanda sai da mahaifinsa yabashi baki yace yayi yataimaki Al ummah saboda Alllah itama dasu uncle dinsa zasu samu lada wannan kenan.

Kaji dalilin zaman yayanku doctor akasar india, da kuma dalilin dayasa yayan ku yake zama india shida Al Amin har yazamana sun zamo manyan likitota akasar da batasu ba...

****

****

****

"Sarki Ali ne yaci gaba da maganarsa D'an uwana sarki umar a wanchan lokacin shine ya mulkar masarautar nan,yana "yaa norah wadda taci sunan kakarku hajiya sai kuma matarsa lailat ina fa'd'a make kawai duk da nasan kasani yadda zakaji komai yadda yake alabarin ne..yakai karshen maganar cikin wani yanayi yana jin komai yadawo masa sabo...

Hawayene Suka zubo a idanun mahir dasu yuhanis,da sumee da zuwansu kenan aka fara bada labarin sai da babu wanda ya lura dasu,sunyi sallama sai dai ba'a amsa musu ba shine dalilin dayasa suka shiga falon kaitsaye,Haka itama unni hawaye take zubarwa mai zafi maimartaba sarki Ali shine mai lallashin su,shine yafara lura dasu Nisa A tsayen dasuke ido jage jage da hawaye kyafato su yyi tahanyar yimusu Alama..

A hankali suka taka inda suka zauna akusa dashi suka sanya sa tsakiya,suna masu cigaba da zubar da hawayen su,domin su ana goyonsu ne lokacin basu san komai akan labarin ba sai yau duk Ammi na yawan furta musu sumusu Addu'a..

Share musu hawayen yayu yana furta musu kudaina kuka kunji "ya "yan Unni,kai suka d'aga masa da alamar toh,suna masu sake share hawayensu,"kara furtamusu yayi kumusu Addu'A kunji ita suke buk'ata agareku..

Yau ansamu long page😎

https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one□,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!□□

MASU SON A TALLA TA MASU HAJARSU

SHOULD CONTACT ME VIA

+2348069059746

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE27

TYPING□□□

Bayan dukkaninsu sun samu natsuwa sai Sarki Ali yatambaye su daga ina suke gida ko schl

YAr bak'ar wadda take kama da Dr.Ammar sosai ce ta furta" Abba muntaso daga school ne shine muka ce driver yakawo mu nan muganku.

Murmushi sarki Ali yayi yana furta" su sumayya uwayen yawo",sumayya datake d'an satar kallon mahir tad'an kawar da kanta gefe cikin jin kunya tana furta

"Allah Abba bana da yawo,Nisa ce tace sai munzo nan kuma gashi bamu ma gaya wa Ummi ba".

mugun duka Nisa takai mata Abaya Bayan jin kazafin da tayi mata, cikin shagwab'a Nisa ta furta Allah ni Abba ba ruwana itace tace muzo zata karbi sako gurin yaya mahir.

Abbah da jin wannan magana ta Nisa sai yayi murmushi irin nasu na manya dan dama dazu yaga yadda Sumy ke satar kallon Mahir Din sai dai bai kawo komai ba aransa,Murmushi yakarayi irin na jin dadi,sannan A hankali ya furta"Sumayya wani irin sako ne halan?sumayya dake cikin zullumi dama tana tsoron hakan tafaru dan tasa halin nisa wani lokacin bakinta baida sayi,shiyasa tun amota sai data kwatse ta,Dan ta girme ma nisa da shekara daya kuma tafita wayau ita nisa surutu ne dai bai wani sha mata kai ba kamar sumy d'in.

Gabanta ne yafad'i da jin tambayar da sarki Ali yayi mata in ina tafara Alamar rashin gaskiya sai kuma ta donar da kanta kasa,tayi danasanin cewa nisa gurin yaya mahir zata karbi sako dama cemata tayi suje sugaida Unni da duk haka bata faru ba,Kwadayin ganin mahir din take shiyasa tace sako zata karba awajensa,saboda yakwana biyu baije gurin Ummi ba saboda schl data rikesa.

Shiko mahir duk da yana kusa kuma yana jin komai dake wakana bai nuna ko a fuskarsa ba Alamar dasunan shi azancen..

''''''ganin taki basa amsa,sai ya juya akalar tambayar sa ga mahir shiru mahir yayi duk da yaji tambayar da mahaifinsa yamasa "wane sako ne halan zaka bata"itace

tambayar da yamasa,da gayya sarki Ali ya furta masa tambayar,kara furta masa yayi cikin raha kodai sakon sirri ne yana d'an kallon sumy dake gefensa,Ai dasauri ta mik'e cikin jin kunya tayi hanyar Babban falo,Dariya sarki Ali yayi irin tasu ta manya yana girgiza kansa.

Shiko mahir tunjin furucin mahaifinsa na karshe ya sunkuyar da kansa yana mai turar labb'ansa yana furta " nifa Abba bawani sakon sirri bane kawai dama yaya Aj ne yace zaiyi magana da ita ne"

"Touh itakuma wayar Umminku fa,ko bata da amfani ne " inji sarki Ali,bakinsa yakara turowa jin k'aryar tasa bata hauva,Amma akarfin hali irin nasa sai ya furta Abbah inaga ta lalace ne,Murmushi Unni tayi kawai ita da sarki Ali suna girgiza kansu ganin soyayyar ta yaran zamani.

Ahankali Unni ta furta tashi kaje Babana kasha magani ka kwanta tunda kaki cin abinci,Hararar Nisa Yayi dake jinhgine da kafad'ar mahaifinsu tana dariya kasa kasa na muguntar da tayiwa Sumy.

Ahankali mahir ya furta " Unni kinganta koh,wallahi yarinyar chan bata jin magana duk Abba da yaya Dr A suka sakanta ta "murmushi Unni tayi tana mai fad'in kyaleta kaji ai kaima unni ta sakantaka koh,Murmushi sarki Ali yayi ganin ydda zuri'ar tashi suke cikin farinciki yana jin ina ma Akwai Ammar dinsa akusa.MganarUnni ce data furta wa mahir ai kai Autan Unni Ne,ta tsayar masa da maganar zucinsa..

Autan Unni din da Unni ta furta ne yasanya yuhanis ta taso da sauri tana ita wallahi bata yadda itace autar Unni har Da Ummi ma tana maganar tana matso hawayen shwagwaba,tana mai zaunawa a d'ayan gefen Unni Sarki Ali murmushi yakarayi yana furta kyaleshi maji dadi na kinji ai ni ke kadaice AUtanah bada yaya dr ba bada yaya mahir ba,kivar Unni chan danata tarkacen kidawo nankinji yakai karshen maganr cikin wani yanayi dalilin saka sunan Dr Ammar,sbd haka suke kiransa yaya dr,Ita kanta Unni wani yanayi tashiga mai dadi jin karo nabiyu yakara sanya nur d'inta cikin zancen sa.

Nisa kuwa da sauri takoma inda Abban tana dariya tare furta yawwa Abbana ni kadai bada yaya rigammenme ba,ganin mahir na kokarin yimata rankwashi akai jin takirasa rigamamme.

Kyafci mahir yayi yana mai mikewa tsaye sallama yayi musu,sannan yayi ma Nisa Alamar zamu had'u,yayi fucewarsa yana murmushi.

A b'angaren sumy kuwa bayan ficewarta daga dakin sai tayi zamanta afalon jin zaman y isheta kuma tana jin nauyin komawa ciki ganin tabada kanta,dan taji kunya sosaiii,sai tayi ficewarta daga sashen fitar ta kenan ta hango motarsu Abdallah da yusuf tashigo Jikokin fulani,Abdallah d'an gurun yaya mustapha shikuma yusuf d'an wurin malan,Yayyen su Unni.

A hankali suke firarsu ta yan uwa shida sumy bayan gama parkng motar A chan achan Babban parking space dake a fadar yusuf ya wuce nasu sashen bayan gaisawa da sumy,shiko Abdallah yatsaya domin su gaisa kwana biyu basu had'u ba...

A bangaren Mahir kuwa bayan fitowarsa daga dakin yaduba falo baiga sumy sai yafito gaba d'aya cikin sashen ckin mamakin ina ta tafi kuma,a compound din sashen nasu yahango su ita Abdallah Akan wasu chairs suanat firarsu gwanin burgewa kamar wasu masoya,wani kololon bakin cikin ciki ne ya ziyarci mahir daganin Babban Abokin nasa da sumy zaune sunata raharsu,takawa yayi zuwa inda suke yayi,ya yyi tsaye,Abdallah ne yafara lura da tsayuwarsa Abayan sumy dake ta maganarta hankali kwance,lura da yanayin fusakarsa ne yasanya Abdallah tambayar bros lafiya dai koh?sai alokacin sumy ta gansa dasauri ta mike ta fara kame kamen rashin gaskiya... cikin "sanyin muryarsa ya furta lafiya qlau".Unni ce tace inkira mata wannan yarinyar,ohk Abdallah yafurta yana fadin" big girl sai anjima ko dan nasan dakyar mukara had'uwa kila.. inkoma gida kigayar mun da Ummi da husnat"toh tace tana mai rab'a mahir tawuce cikin gidan..

Abdallah ne yakara furta ma mahir yakannaka bros?kasha magani?eh kawai mahir ya furta wucewarsa cikin jin haushin Abdallah,bai tab'a jin haushin big girl din da Abdallah ke kiran sumy dashi ba sai yau,sauri sauru yacimmata Sumy da har tashiga falon..

Ke yadakatar da ita daga kokarin bude kofar second falon datake kokarin yi A hankali ta juyo suka had'a ido dashi yana mai kafeta da dara daran idanunsa masu yanayi dana da Dr ammar,Saurin duk'arcda kanta ta tayi kasa ganin irin kallon dayake jifarta dashi,wanda bazata iya jurewa bah,muryarshi ce tadaki dodon kunnenta,yana furta "wane sako ne zaki karba hannu na"? rass gabanta yafadi nan tafara kame kame duk da bata furta komai ba,ganin yanayin da tashiga yasanyashi dauke kansa,yana kawar da wanchna zancen ta hanyar tambayar ta maganar me sukeyi da Abdallah?

niko nace mahir kamanta da yan uwata kai ne 😄

Kanta tayi saurin dagowa danjin tambayar da yayi mata ido suka kara had'awa dashi tayi saurin janye nata ganin uwar hararar da ya sakar mata,murmushi ne ya subuce mata wanda ganin irin hararar da yayi mata sai taga yakara yimata kyau,Amsa masa tayi A hankali "yaya mahir gaisawa ce mukayi sai kuma firar school din mu danake basa,"ke uwar bada labari koh"shiru tayi jin abunda abunda yafurta girgiza masa kanta kadai tayi tana kara sakin murmushi a fakaice,Bata san cewa yaganta ba,shima ana bangaren murmushin gefen baki yasaki yana mai furta "meye na murmushi"kai takara girgizawa tana kokarin bud'a bakin ta kenan taji tafi abayanta raff raff ....

Waye kuke tunani kenan ya musu kutse suna tsaka da shan love 😍?shin ko dai mahir ya fad'a ne?

Like,share and comment pls.

Idan kina bukatar daga farko zaki iya tuntuba ta....

https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one□,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!✌✌□□

masu son a tallata musu hajarsu should contact me via

call +2348069059746

chat +2348066995473

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE28

TYPING□□□

Duk da bata juyo ba tasan aikin waye,Nisa ce ke sakin karamar dariyarta tana tare da tafa hannayen ta a hankali bayan isowarta kusa da sumy ta furta acikin kunnenta "me kika gayawa yaya mahir naga yana sakin murmushi"

Aiko da jin maganar ta Nisa sumy ta kai mata d'an karamin dundu abayanta,da sauri ta Nisa ta juya dagudu bayan jin dundun da takai mata tana furta sai nagayawa Unni da Abba soyayya kukeyi,ai kafin takai ga bude kofar Second falon na Unni har mahir ya chafko hannunta ido ya raina fata Nisa A hannun mahir dan tasan bawai wani raga mata yakeyi ba take ta raina kanta hawayen karya tafara matsowa tana bashi hakuri tun kan ya kai ga hukunta ta ta.

Kansa kawai ya girgiza yana mai furta "mai kikace zaki fadawa su Unni ne "?

Shiru tayi sai dai faman girgiza kanta kawai takeyi tana cigaba da kakalo hawaye,warning ya buga mata akan kar ta yadda tasanarwa da kowa tagansa tsaye da sumy,Sannan yasake hannunta yana furta stubborn girl.

,,,,,,sai da ta bud'a kofar shiga falon sannna ta juyo ta murgud'a masa baki.

Itakam sumy dariyar ta kawai takeyi kasa kasa.

Bayan wucewar Nisa ya kalli sumy kallo irin na zamu had'u,ya juya ya yayi hanyar nashi dakin wanda yake chan jere shidasu dr Ammar A wani lungu da yashiga ta falon unnin.

Bayan wucewarsa itama sumy ta taka afalon na unni da tunani barkatai aranta.

A bangaren Abdallah kuwa yanayin yadda mahir ya amsa masa ne bai masa ba,Amma sai bai kawo komai aransa ba,face tunanin kila ciwon kannasa ne ya sanya sa zama haka

BUG

Abangaren su halee kuwa wallahi mijin ki zaiyi faman da khady ta furta ne,yasanya Halee data debo yar madaidiciyar loma a spoon tagaza kai ta kan d'an karamin bakinta wanda yake d'auke da pink lips,dasuke shekin maik'o dan maganar ta Khady ita dariya tabata,sai da takai lomar abakinta tana tauna a hankaali sannan cikin sanyin muryar da zame maata jiki ta furta"meya sa kikace haka"?

Cikin zakuwa khady tafara jero mata halayenta wayenda suka zame mata jiki ko ince wayenda aka halicceta da su ,"kinga na farko ni ban masan yadda zaiyi dake ba mutun kullum ciki hijab tafurta cikin dariya ni na namatsu in ganki gidan mijinki inga yadda zaki yi"

A bangaren Halee murmushi kadai ke wanzuwa akan kyakkyawar fuskarta tana cigaba da cin abincnta hankali kwance,khady ce ta cigaba da maganar ta"mutun inkayi magana bai baka amsa ina lafiya" wannan karon Halee sai da tadara harda rike ciki,wanda sai da fararen hakoranta suka bayyana, itama khady dariyar takeyi ganin yar uwarta na farin ciki.

A hankali ta furta bayan gama dariyarta "to me kike so ince ne yar karamar harara khady ta watsa mata chan takara furtawa "bari kiji mama dije cikin d'an murmushi wanda ya fito da side dimple dinta da ya lob'a gwanin burgewa ta ce ni bari kiji koda nayi Aure babu wanda ya isa ya hana ni sanya hijab dina,sai maganar dake cinki ta biyu dan naga kina kalllon filet dina,kinfi kowa sanin ban cika son cin abinci mai nauyi ba saboda bana son inyi kiba inkoma mama dije tulluka gaki nan kina ta zama lukutarki takai karshen maganar cikin sakin karamar dariya,itama khady dariyar tayi tana furta nice yar lukuta,zan rama ,ai gashi nan ke kuma kina ta zama iccen kara mutun kamar iska yakwashesa inbanda wannann abun da wannana abun da bakomai cikin ki tana nuna breast dinta da hips dariya dukkan su suka kwashe da ita musamman Halee da maganar ta bata dariya...

Bayan gama cin abincinsu ne, Khady tafara yiwa Halee kalabar dogon gashinta mai santsi da dubara,ana take shaida mata....

Ai Baba Asabe ta fita tun karfe takwas tayi wurin zaman makoki mamaar Babar Aminiyarta larai,sai maraice tace mata zata dawo.

Niko nace kaga su Baba Asabe an zake dayawa sai kace masu wata hidima ta biki tun safe sai maraice,ko da yake yanzu haka nan akeyi musamman ingidan mutuwar akwai maiko Allah yasa mudace muyi kyakkyawan karshe.

Hamdala Halee tayi A zuciyarta na farinciki jin wannnan labari na Khady ganin yau zata wala,Tambayar khady tayi cikin yanayin farin ciki "to amma meyasa baki tada ni ba nayi ayyukka na"

"yau ni tace in yi Ayyukkan bake ba" khady tace mata hakan ne kawai.

Halee dai tasan sarai karya khady ta fad'a mata dan tasan wacece baba Asabe,Tunano yadda sukayi da Bba Asabe tayi ajiya kan kawai ta dade ba kawo ko sawu daya na ruwa ba domin harda marinta tayi wanda ita kuma jira ta tarar a bohol din....

Hawaye ne shar suka silalo mata a ido tayi saurin gogewa gudun kar khady ta gani,sai dai khady ta riga taganta kai kawai ta iya girgizawa tare da share nata hawayen daya zubo mata na tausayin yar uwarta.

.....Mganar Baba Asabe ce ta fad'o mata arai kafin fitar ta zuwa gidan gaisuwa Halimatu!Halimatu shine sunan da BAba Asabe take ta kwad'a kira,wanda sautin neya farkar da Khady jin Bba Asabe na doso d'akin nasu ta mike da sauri bayan bude idanun nata kazazam ta yi saurin lullub'awa Halee bed sheet dake tsakanin filonta da na Haee Sannan ta isa bakin kofar da sauri alokacin itama Baba asabe takawo bakin kofar....

Gaidata ta Amsa mata cikin sakin fuska

Sannnan ta furta" ina yar iskar yarinyar nan take bataji ina kiran sunan ta bane ko wani sabon iskan ci ne ta tsiro dashi ehh"?takai karshen maganar tana kokarin yaye labulen dakin sai dai Khady ta hanata ta hanyar kara kare bakin kofar tana ta faman susar kai na rashin gaskiya Baba asabe kuwa kafeta da idanu kawai tayi ganin wani sabon iskancin gun yarta furta wa Baba Asabe tayi innata tashiga toilet ne,Uhm meye na kare mun kofa eh sannan uban mi takeyi acikin toilet din tabarni inata turar labb'a ga yar iska,Ganin tana neman tada HAlee da hayaniyar ta yasanya ta marairaicewa tana furta innata kaina ke ciwo gashi kinata d'aga mun murya aka.

Sassauta murya Baba asabe tayi tana furta inta fito kigaya mata tadaura miki abun karin kumallo da ruwan zafi sannan ta gyara mini d'akina na Alhaji nasan basai nace ba ashare agoge ko ina ,harda toilet,sannan intagama acika kwannan gidann nan kuma akaimani ruwa makewayi na,saura kuma ki sanya mata hannu tunda nasaka ki tana gama maganar ta fuuu ta fice daga gidan har ta kusa ficewa khady ta furta inna ta inazaki tunda safen nan,gidan larai zani mahaifiyarta tsohuwa ta cika dazu anfada amasallaci,Ayyah khady ta furta" Allah yajikanta da rahama" Amin Ta furta tasa kai ta fice gidan.

KAI BABA ASABE AJI TSORON ALLAH WANNAN SONKAI YAYI YAWA.

Bayan fitar ta ne khady tayi dukanin ayyukan da Baba asabe yar sonkai ta lissafawa Halee domin tasamu koda hutu yaune kafun dawowar Baba

Adee.

Bayan Gama wannan tunanin sai ta fara jan Halee da fira duk da ba duka take amsawa ba domin har yanzu akwai sauran tunanin mafarkin nan aranta dakuma zaginta da Baba asabe ke yi.

GUSAU

A Bangaren sarki Ali kuwa bayan ficewar Nisa A dakin ne ya furtawa Unni "ya "yanki fa kamar akwai wani al amari atattare dasu ni gashi tuni har nafarawa ba indiyen yaronki kame,sai kuma naci karo da wannan sabon al amari yakai karshen maganr yana murmushi,murmushi Unni tasaki itama tana furta to dad'a yaran yanzu ba,a

gane cikin su ta yuyu akwai wani abun atsakanin su amma suna boye wa ne duk da nasan Baaba na baida nuk'u nuk'u a irin wannan maganar kamar Ammar wanda har yanzu ko budurwa baida ita gasu girma nata zuwar musu gaskiya insuka dawo ka nema musu mata ko cikin ya yan kawayenka ne na matsu inga jikokinmu takai karshen maganar cikin dan murmushi najinin larabawa da fulanida ke yawo ajikinta,shikansa sarki Ali murmushi yayi yana furta gaskiya kam dole in nemo musu mata tunda har gimbiya sarautar mata tafara maganar jikoki agabana yakai karshen maganar yana leken fuskar Unni data sunnar kasa na kunya.

Wallahi soyayyar tsofaffin nan na burgeni...😄

Sai da taga yajanye daga kallon ta dayake yi sannan tacigaba da magana,maganar Ammaar mu kyaleta kawai Adili kabar ta bamusan Alkhairin da ke shirin shiga atsakaninsu ba wanda Allah ne kadai yabar wa kansa sani.

Hakane sarki Ali ya furta sannan yakara furtawa su mutanen india mubarsu sudawo muga inbasu fitar ba sai anema musu, shi yarima inbanda kaddara ai dayanzu da matar shi ahannu Allah ya jikanki norah keda mahaifanki,Ameeen suka amsa su duka cikin wani yanayi shikuma Al amin Auta ta zan bashi inyanaso..Yakai karshen maganar yana murmushi,itama Unni murmushin kadai tayi tana furta Allah yatabbatar da Alkhairi,Ameen sarki Ali ya Amsa.

yana mai Mikewa tsaye rawaninsa yanad'a wanda da taimakon Unni yadaurasa sannan ya sanya alkyabbarsa wata colour maroon mai stone da wata zaiba abun sai wanda yagani.

Shigowar Nisa da minti kusan Uku sai ga Sumy tashigo,A hankali sarki dake gyaran Alkyabbarsa yabfurta y"a yan ummi nizan koma fada,yaushe zaku wuce ne,cikin sauri Nisa ta Amsa da Abban Yanzu tana zunburarar baki dan duk gidan ya gundureta tunda mahir yayi mata rankwashi akai,

Murmushi kawai Unni tayi tana fadin har angaji damu kenan?kai ta girgizawa unni tana mai kara turo d'an karamin bakinta gaba.

Sarki Ali kuwa yar dariyah yayi yana furta waya tab'a mun Auta nah yana murmush,ai kamar jiran tambayar tasa takeyi sai ta fashe masa da kuka,jawota yayi yana lallashi yana kara tambayar ta meya faru?.

In sha Allah ayanzu har weekend zaku rika samun update domin namatsu mu gama book one.

DAGA ALKALAMIN✍

□FA'EEH BG□

Pls like,share and

comme

A MAFARKI NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

Mun kusa gama free pages in sha Allah,Da mungama book one,Episode one kenan za,a fara payment,na episode two!!!✌✌

masu son a tallata musu hajarsu should contact me via

Call+2348069059746

chat+2348066995743

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Pen*is migthier than the sword **

EPISODE1

FREE PAGE29&30

TYPING□□□

Shiru tamasa tana mai share guntun hawayenta dake d'iga a bisa beautiful face dinta,Auta meya faru halan waya tab'aki?shiru tamasa.

Abangaren sumy kuwa cikinta har ya d'uri ruwa tsoron guda kar Nisa tamata b'anbarma a gurin,

Ido suka had'a da nisa sai ta maraairaice mata,ita nisa abun ma dariya yabata sai ta dauke knta kamar bata ga rokon datake mata ba ba ido.

A hankali Nisa ta furtawa sarki Ali cewa"Abba ni Ummi kawai nake son gani ni ba'a mun komai ba.

to yar Ummi ku dauko jakunkunanku driver yakaiku sai in saka fadawa su raka ku basai kun kira drivern ku yazo ba,toh sukace,sallama sukayi wa Unni bayan sun dauki jakunkunansu,suna fice dga sashen D'ai daga cikin manyan motocin masarautar suka shiga tare da mota biyu wadda taraka su,shima sarki Ali bayan wucewarsu masallaci yanufa dan gabatar da sallar la'asar data gabato.

Bayan fitar su dakin na Unni sai ta d'aga waya ta kira Ummi bayan ta bada Umurnin gyara inda sarki Ali ya ci Abinci da tattatare kayan da akayi amfani dasu.

Dialing numban da akayi saving da sister tayi,ringing biyu ba'a d'aga ba ana ukun ne aka daga muryace irin ta Unni sak tayi sallama Bayan Unni ta amsa mata ta dayan b'angaren aka kara furta yaya yakike?Lfy lau! yagida daga bangaren Unni,Lfylau Ummi ta furta Ya Hamma Aliyu yake? lafiya kalau yake yanzu ma yagama ji da rigimar ta gidanki'Murmushi Bangaren Ummi tayi bayan jin maganar da Unni d'in tayi tana furta ai yuhanis rigimar ta sai ita yaya.

Murmushi ta d'ayan b'angaren Unni tayi tana furta ai gasu nan ma sun kamo hanyar dawowa.

ohk! da har sunce ma driver yadawo bayan isha'i Ashe ba dadewa zasuyi ba.

Unni ce tace wallahi sister yar kice tasaka rigima tana son taganki,dariya dukkaninsu sukayi na sakalcin Nisa shekara goma sha tara Amma har yanzu kamar yar goye intana wasu abubuwan.

Tsaigaita dariyar tasu sukayi Bayan Unni ta katse firar tasu ta Nisa ta hanyar furta Albishirinki sister tana murmushi ta d'ayan bangaren Ummi ma murmushin tayi tana furta goro fari,kuma na bawa Ammie ta cinye,tana dariya, itama Unni dariya tayi tana furta kinma kankuwa huta bari inkoma da labarina takai karshen maganar ckin murmushi...

Yayah!yayah!tawa yi hak'uri Ta b'angaren Ummi ta furta.

furucinta duk sai yasaka su yin shiru saboda wadannan kalmomin sune kanwarsu laila ke yawan furta ta agaresu musamman intayi musu laifi,A hankali ta bangaren Unni ta furta Allah yajikanki da rahama laila da dukkan kulluhin musulmi,Ameen Ummi ta furta cikin yanayin da suka tsinci kansu aciki bayan tunano da yar uwar tasu.

.....cikin farinciki Ummi take furta Alhmdllh Allah mungode maka bayan gama jin maganar ta Unni akan maganar su Ammar,In sha Allah kuwa yaya bazasu sanda komai ba sai lokacin da yadace Ta furta cikin murmushin ta daya kasa tsayuwa, sallama sukayi kowa ya ajiye wayar tasa cikin farinciki.

Unguwa ce Babba tamasu kud'i ana naga motar da ta dauko su Nisa ta shiga inda ta parker a wani tangamemen gida wanda tun daga gate din zaka san naira ta zauna Ma masu gidan,Horn drivern sarki yayi sai ga wani gabjejen soja ya lek'o bayan ya shaida suwaye aciki motocin har yan rakiyarsu,sai

Wangale musu katon gate din,Gida ne na alfarma ko ina tsaf komai atsare tundaga parkinga spqce dake shake da manyan motoci na alfarma ga shuke nan masu kawata gida,sojoji ne birjik kowa datasa kalar suna shawagi acikin babban compound na gidan,D'ai daga cikin sune yataso yana kokarin bud'e musu k'ofar motar,Nisa Dalla masa harara tana kowa ya saka ka ka kicifaffe,shidai sojan nan bai takan taba face komawa sashen da Sumy take ya bud'e mata,Itama Nisa budewa tayi dakanta inda ta fito tana harare hararen sojan nan murmushi yayi kawai yana rigimammiyar tadawo cikin ransa dan ba damar fitowa fili afad'a duk da yasan ba abunda zatayi masa domin bata da matsalarkomai kawai dai rigimarce wadda kuma ba kullum take yintaba.

Juyawa motocin da suka kawo su sukayi suna barin gidaN.

Da gudu fad'a acikin had'adden falon gidan bayan sumy ta gaisa da Sauran sojojin

Ummmi! Ummmi! shine sunan dasuke ta kwalawa kira wata matace ta fito daga wani daki daga chan upstair tana takawa ahankali tana furta har kun iso kenan,Macece kyakkyawa kamar Unni fara tass komai nasu iri d'aya har muryar ma tasu identical twins kenan kafin ka shaida d'aya sai ka d'anyi dogon nazari.

Cikin murmushi dukkaninsu suka rungumeta itama murmushin tasaki tana furta sannun ku da zuwa "ya "yana shine ba sanarwa sai kukayi gidaan Unninku kuka turo mun driver kawai.

Dariua sukayi dukkansu har Ummin.

Nisa na bud'a baki zata furta ai yya mahir....Sumy ta mintsileta gudun karta sakammata layi,fahimtar hakan da Nisa tayi sai tace Ummi yaya mahir yace agaisheki,ina amsawa ta furta tana raba jikinta da nasu itama sumy ta furta Ummi yya Abdallah ma yce agaisheki duka ina amsawa tace duk da sun gujeni kwana biyu...

cigaba da magana tayi yau Ina cikin farinciki yayan Unni da Ummi duk sai suka had'a baki gurin tambayar mene ne yasanki farinciki haka Ummi ko dadyyadawo ne bamu sani ba duk da bamuga motarsa ba acompound girgiza musu kai tayi cikin murmushi tana furta aah,BAi dawo ba Amma karku damu zakuji komai nan gaba,Tana wucewar ta kitchen.

Wanka tace suje suyi suci abinci toh suka ce suna takawa upstair d'in ...

Wata kyakkyawar yarinyace fara kamar ta sak da Alamin da sumy sai dai batayi hasken su ba,da gudu ta taho ta rungume yayyen nata bayan sun idasa take kan step din tana furta shine kuka je gidan Unni yau badani ba koh'tana maganar tana neman bare musu baki tasaka kuka,Nisa ce tajawo ta ta na furta kinason zuwa wurin Unni koh,kai tad'aga mata, toh kibari juma'a tayi sai muje koh har Ummi,ai kinga juma'ar takusa zagayowa koh kai takara d'aga mata,yawwa An Husna ta muje kema inmiki wanka ko,suna wuce wa ta sashen da rooms nasu yake.

HOSPITALISED

INDIA

Maharastra 24hrs Hospital mumbai

Zaune yake akan chair dinsa mai juyawa acikin kayataccen office d'insa mai kyau bayan ya cire labcoat dinsa yasargafe ta a had'addiyar hangern office din nasa, bayan yagama duba outpatient.

Katon office ne kamar wani falo guda komai yaji komai na kawa, windows dinsa gaba daya gilas ne ga katuwar lockern sa ta ajiyar takardu da document,da haddaen fridge d'an karami wanda yakarawa office din ado, sai d'an madaidaicin gado na duba marar lafiya tareda sauran kayan amfani irin su spring cover d.S,sai kofar toilet da wata kofa danake tunanin bedroom ne,komai masha Allah ba wani tarkace.

,,,,,,game Yake bugawa a had'addiyar wayartasa kirara 15promax(iphone) sanyin A.C na office d'in yahad'e da k'amshin turaren sa mai dadi BETTER MAN na kamfanin "yosen"domin kowa yasan dr Ammar ma'abocin sanya turare ne.

Had'adden table din dake gaban sa yana dauke da wani tambarin na kwalbar zinari kamar na award an rubuta Dr.Abdul rashid Aliyu Ahmad,cikin tsari mai kyau,ga kayan aikinan masu quality da kyau na aikin su irin su Bp

apparatus,spygmanometer...Thermometer abun awon pulse da dai sauransu sai wasu yan d'ai d'ai kun takardu na amfani wayenda bukatar su kan taso ga patient...

K'arar door bell ce tasanyasa Ahankali cikin tak'ama ya furta come in,Kyakkyawr budurwace tabayyana acikin office din nasa,Dr.Malini kenan kyakkyawar ba indiya ruwa biyu jinin larabawa da indiyawa,kykkywace ajin karshe sanye take da sari ja da labcoat ajikin ta inda naga anrubuta dr malini arorah,takowa tayi Ahankali tazauna akujerar da taje gefen table din tana mai furta masa barka cikin harshen india tare k'awata fuskarta da murmushi....

kamar bazai tanka ba sai kuma ya furta yawwa Atakaice cikin yaren idia shima, yana cigaba da buga game dinshi,tun shigowarta da yamata kallo d'aya yani itace bai ka'ara kallon taba,koda sashen datake.

A hankali ta k'ara furta masa cikin harshne nasu,yazo sufita cin abinci suje bakin ruwa,,,,Bakin ruwan da furta ne yasanya gabansa muguwar fad'uwa daya tunano mafarkinsa da yayi jiya wanda har yau baisanarwa da kowa ba.

A hankali cikin tak'ama da izza irinta jinin sarauta masu ji da ita ajikinsu Bayan tsai da tunaninsa akan mafarkinda yatsaya masa arai,ya mayar mata da Amsa ''I am not interested"

atakaice maganar ta kona wa dr malini zuciya sai dai sanin halinsa sai ta basar bata k'ara furta masa komai ba domin inda sabo tasaba da irin cin kashin da yake mata,wanda ita taja wa kanta,wanda su achan kasar su ba komai bane is nrml thing.

daMa mazan yanzu ya aka kare koshi yace yana sonki bare ke kika kai kanki,abun sai anrika had'awa da Addua,inkin zurfafa yar uwa,sannan karki bayyanar da soyyayr nan har yagane kina iya vada ranki saboda shi,domin wasun su suna amfani da wannan damar su cutar da mu,Allah yabamu masoya nagari

Ganin da yayi bata k'ara yin magana ba kuma bta fice ba yasanyasa d'ago dara daran idanunsa yayi duba na second daya agareta,yana dauke kansa cikin cije leb'ensa na kasa,yayi danasanin d'agowa yakalleta harsuka had'a ido,domin hawayene yagani suna a idanunta wasu na turereniya da wasu,D'an karamin bakinsa yakara tsukewa dan yatsani ganin hawayen mace domin take yake rikicewa,Tabbas a wannan gab'ar dr malini tayi nasara domin zata janye hankalinsa in har tagano lagon.

Ayanzu haka ma yakar zuciyarsa yakeyi data fara darsa tausayin Dr malini wanda kuma shi haknne bayaso yafaru.....

Karaamar tsuka yaja wadda iyakarta kan labbansa yana ajiye wayartasa akan desk,handkerchief dinsa fari k'ar dora mata agefen da ta kife kanta tun bayan had'a idon da sukayi tana cigaba da kukan ta kasa kasa,Saurin Dagowa tayi A hankli ta kallesa cikin wani yanayi ganin ya ajiye mata hanky kallonsa take da mamaki da alajabi domin yauce rana ta farko da yafara nuna mata kulawa,take ta tsinci kanta acikin farin ciki marar misaltuwa ita a tunanin ta yafara sonta,tunda su dab'iar su ce

in har saurayi yabawa budurwa handky tashare hawayenta kamar alamar soyayya ce tunda shima wannan kulawa ce.....

Hmmmm Nikam nace DR.MALINI Kenan.

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

FREE PAGE31

TYPING□□□

"Sorry" ya furta mata ayangance,duk da yadda Kalmar kemasa nauyi ahankali ganin tana share hawayenta Wanda har fuskarta tad'anyi jaa fuskar ta chanza alamar kuka

abunka da farar Fata.kai kad'ai Dr.malini tad'aga masa,Bayan share hawayenta da kyakkyawan handkerchief Nasa fari kar mai kamshi.

A hankali ya buda bakin sa dakyar cikin tattausan lafazi da muryar mai sanyi da nuna izzarsa ya furta mata acikin harshen turanci, I have a lot of appointment today,so thats why I have told u I can't go with you,ya furta mata hakan ne kawai ganin hawayenta, yanaso tasaki fuskarta bazai so ace kullum cikin kuntata mata yakeyi ba yasan cewa soyayyar gaskiya take masa sai dai shi bata cikin Ra,ayinsa har yanzu.

Shiru yayi bayan gama maganar jin bata CE komai ba yakara furta i'm sorry ohk!

D'aga masa kanta tayi tana tashi tsaye da lab coat d'inta da tacire kafin ta zauna,hanky d'insa ta ajiyemasa No,

Ya furta da ita "you can go with it"murmushi tayi har cikin ranta jin furucinsa taji dad'in kulawar da ya bata yau kad'ai akaro na farko wadda tadauke ta amatsayin wata nasara ta ta.

Bye tamasa Tana takonta d'ai d'ai na big ladies masu ji da Kansu tako wanne fanni k'arar high hill dinta ne kad'ai yake tashi duk inda ta wulga sai an mata kallo uku saboda haduwarta.

Dr.Am dayaga wucewar Dr malini tana ta faman sakin murmushi ne abunta,kansa yad'aure masa kai,dama ga office d'insa ganasa,yana bud'o k'ofa yaga wulgawar ta sai dai bata lura dashi ba. ida rufe kofar tasa yayi ya doshi kofar ta Dr.Ammar ko neman iso baiyi ba ya bud'e door d'in yashiga ciki,ko ba,a fad'a ba yasan Al amin ne yashigo saboda shi kad'aine Wanda baya tsayawa Neman iso ta hanyar danna door bell.

Idanunsa a rufe ya furta wai lafiya kamun tsaye akai, Dr.Am bai ce masa komai ba duk da yaji furucinsa,sai ma kara gyara tsayuwarsa da yayi yana mai rungume hannyensa akirji,tsawuyar minti uku yayi babu Wanda ya furta k'ala ga dan uwansa,Dr aj sai ma karantarsa da yake yi.Aj ne yakatse Shirun nasu ta hanyar furta ma Dr.ammar" meye damuwarka na fahimce ka tun safe kamar kawai Abunda ke damunka azuciya,kuma inada yakinin bazai wuce mafarkin da kasaba yine kayi sai dai ban sani ba,ko wannan ya chanza daga Wanda suka sani ganin kamar yana kokarin boyesa ne.

Shiru Dr.Ammar yayi kamar baiji Abunda da Dr aj yafad'a ba saima kara tsumewarsa da yayi akan had'addiyar kujerar tasa mai rotating ,ganin baida niyyar magana yasanya Dr aj kawar da shirun ta hanyar furta...

"Mekasanar wa Dr.malini ne naga ta fita tana tasakin murmushi kodai kabar hak'ar ta ta cimma ruwa ne duk suna maganar ne da yaren India din.

Murmushin da bai shirya yinsa bane ya subuce masa akan kyakkyawar fuskarsa jin abunda Dr aj ya furta idanunsa ya bud'e ahankali tar akan Dr aj yana kallonsa da

murmushi a fuskarshi,sai kuma yakawar da idanun nasa masu kaifi ganin Dr aj ya daure fuska ta Yar dariyar da ta fito masa ta rainin hankali duk da bai tsawaita ba.

A hankali ya mike daga zaunen da yake yatako A hankali dai dai inda aj yake tsaye nan ya tsaya suka jera gwanin burgewa sunsha fararen riguna da maroon colour trouser kowa ya tsuke da belt maroon sai kuma hadaddun boat dinsu masu kyau far are kar dagani dai sunji naira,yau anko sukayi dama mafiyawancin lokutta anko sukayi domin duka Rabin kayansu iri daya ne da juna sai dai kala CE wani lokacin take banbanta,tsayuwarsa data Dr.Aj gwanin burgewa ne Daya yafi daya tsawo,Dr ammar shine mai tsawon,duk sun saka hannayensu a aljihu Wanda ke facing bangon da yake na gilas Wanda dukkan abun hawan dake wuce wa a express way dama mutane suna gani tar.

Tsayuwarsa da minti ya juyo ya dafa aj akafad'a Wanda har yanzu fuskar nan take mur,tsulum yayi yakoma gaban sa suna fuskantar juna, cikin izza da yanga.

Wani killer smile yake ta sakarmasa Wanda ke iya haddasa gubar soyayyarsa acikin second daya acikin zuciyar yan mata,shiko aj ganin sa a gabansa yasanyasa ja da baya yana sakarmasa katuwar harara wadda tasanya Dr.ammar sakin kayataccen murmushi Wanda har sai da fararen tass jerararrun hakoransa suka bayyana.Aj ne ya furta Dan iska kawai haka kakayi wa yan yayan mutane suna fad'awa daga kallon daya cikin kara sakar masa harara.Dr ammar kuwa murmushin sa yakara fad'ad'awa jin abunda aj ya furta masa.

Ahankali ya mayar masa da amsa cikin kasallaliyar muryasa ta gwarazan maza,kar damu likita yanzu duk zan baka amsar tambayoyinka duk da bayanzu naso kaji wasu daga amsoshinka ba,yana mai kara gyara tsayuwarsa,Kwantacciyar sumar kansa yashafo sannan ya cigaba da magana a hankali "tabbas mafarki na ya chanza kamar yadda kayi hasashe .....labari yabasa na yadda mafarkin ya wakana domin dama tin asali basa boyewa juna sirri duk da dama shi aj yasan mafarkin saboda some time lokacin suna kwana daki d'aya yakan ji shi yana magana k'asa kasa cikin baccinsa,Wanda dama yasan yana yin wannan mafarkin.

Ta gwayen ajiyar zuciya yake sauke wa,Wanda har sai da Aj yaji,bayan yagama basa labarin.

Tausayinsa ne Yakama Aj ruwan sanyi yadauko a fridge dake a office din tsiya ya masa yayi acikin glass cup mai kyau dake jere awata locker daga gafen fridge din.

Ahankali yakai cup din saiti dan karami bakinsa kurb'a d'aya yayi yasauke gilas d'in ya rike a ahnnunsa yana sakin nannauyar ajiyar zuciya cikin wani yanayi marar fassaruwa, jin yadda sanyin ruwan ya ratsa Dukkanin sassa na jikinsa,Bayan kamar

minti Uku yacigaba da maganarsa yana furtawa Aj" Dr.malini Arorah bata isa tasamu gurbi acikin kirjina ba ko yanzu kawai Dan tausayi tabani ne ganin hawayenta na zuba abanza,saboda ni kai kanka kasan bana son ganin hawayen mace bare ma ace ta sanadi na suke zuba.

wato abanza Dr😘☹.Hmmm maza

wasu wallahi tausayinsu ragagge ne *baiwar Allah nata wahala shekaru araru amma ayanzu hawayenta ma na banza nesabd haba dr.Namu,*

Dr.AMMAR FANS nidai gaskiya mutumenku yafara wuce gona da iri dan bazan dauki wulakanci ga miss malini ba baiwar Allah☹Allah karabamu da son maso wani,da soyyayar bangare d'aya.□□

"Tabbas da badan kwallar da nagani ba babu abunda zaisa inkula ta har inbata abunda zatay wiping na tears nata,saboda bata cikin tsarin matan da nakeso and kuma she's too young for me yana kai karshen maganars da yatsinar fuska yana kara furta bama kuma Aladun mu d'aya kuma ba Addinin mu d'aya nasan kasan da haka maganar hak'ar ta ta cimma ruwa har abada yana lumshe idanunsa s ai kuma a hankali ya na bude su.

Dr Aj ikon Allah kad'ai yake kallo atare Dr Ammar yana mai yana mai mamakin hali da da taurin zuciyh irin na d'an uwansa ace mutun kaifi d'aya ne ba chanji domin yakamata ace yanzu ya fara kula al amarin Dr.Malini saboda shekarun da tadauka tana bibiyarsa da soyayyarta,.''kaji tsoron Allah Dude,bayan yagma maganar zucinsa, na jin zantukan Dr Ammar d'in. yar karamar harara yasakar masa yana mai kau da kansa gefe,Aj ne yaci gaba da magana yanzu ita Dr malini d'ince yarinya just bai wuce kabata shekaru uku ba fa domin bazan manta ba when last birthday nata danaje ishirin da biyar tayi celebrating Amma shine kake kiranta da yarinya sannan bata cikin tsarin matan da kake so kake iya aure koh !!! hmm Dude kenan inbanda so yana haka me Dr.Malini zatayi dakai dubeka skin dinka kamar zumar dataji wuta ta kone,yakai karshen maganar cikin dan yin dariyar mugunta domin yasan Ammar yatsani wannan furucin.

Karamar harara Ammmar yasakar wa dr aj dan dagaske yatsani kalmar nan dan aj nayawan furtamasa ita duk da yasan wasa yakeyi masa fatarsa normal take kuma ahakan mugun sonta yakeyi.

Murmushi Dr.AJ yayi yana cigaba da maganar sa,"ga mace har mace Amma so na walagigiya da ita gaskiya Dude da zakaji shawarata da ka karb'i Dr.Malini saboda kaima shaida ne tayi maka son gaskiya kuma bugu da kari ta had'a duKkanin Abunda Daaa namiji zai bukata ga mace,kuma duk jarabarka nasan malini zata iya dauka domin nasan halinka inaga ka raina girmanta ne,ina kara baka shawara karkayi watsi da damarka toh!!!!!!yakai karshen maganar tasa yana dariya tare da kanne masa ido d'aya.

Dr.Ammar da ke kallonsa k'uri da ido ne Yayi D'an murmushin gefen baki sai kuma ya murtuke kyakyawar fuskarsa jin furucin aj d'in na karshe domin nafarkon bai bashi haushi ba face ma mere baki da yayi.

"cikin tsuke fuska ya furta Wai yaushe ka koma hakane bansani ba naga alamar idanunka sun bud'e fa,murmushi ne ya subuce masa tuna furucin wai malini zata iya daukar sa abu na kayan wanki,dakuma amsar datazo kansa kan maganar malinin wadda zai mayarwa da aj d'in wadda zaiji zafin ta domin tabbas yaji haushin furucinsa na karshe wai zata iya d....Kasa ida karasa tunanin yayi ta sanadiyyar zuciyarsa da tafara hasaso masa yadda komai na malini yake duk da ba wani kallon tsaf yakemata,subhanallah ya furta azuciyarsa yana lumshe idanunsa tare da bud'esu

yana cigaba da magana kace Dr.Malini Dr.Malini tacika mace ;Am nace ko zaka gwada sa,a ba ko zaka samu cikakkiyar macen tunda naga har ka hango cikarta yakai karshen maganar tasa cikin yana kanne ma Dr.Aj ido Daya kamar yadda yamasa,tare da sakin wani killer smile, aj wqnda daga farkon maganar ta Dr.Ammar murmushi yakeyi sai wannan furucin na karshe yasanyasa turb'ene fuska wata katuwar harara Dr.Aj yasakar masa wadda sai da tasanya Dr .A murmushi wanda yasanya two side dimple dinsa bayyana gwanin burgewa,tsinin hancinsa ya lakata yana mai k'ara sakin murmushi ganin shan tokar da Aj d'in.

A bangaren aj maganar ta bashi haushi matuka domin yadda suke da ammar soyayyar dayake masa bazai iya son abunda yakeson dr .Ammar dinba koda shi bayaso kamar dr malini haka..

Ya bud'a baki da niyyar yin magana sai yayi shiru, karar wayarsa da yaji tadakatar dashi daga abunda abunda yake niyyar furtawa,cirota yayi daga aljihun wandonsa na baya dan ganin wanda ke kiran nasa wanda alokacin har wani sabon kiran yashigo nafarkon yakatse saurin d'agawa kiran yayi Bayan duba sunan mai kiran nasa UNNI

sunan da ya fito baro baro da manyan rubutu.....

□A MAFARKI NASANTA□

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

□A MAFARKI NASANTA□

YAZAMA FREE BOOK

Nama mayar muku dashi free book akan wani dalili nawa inason duk Wanda yaji dad'i yamun Addu'a,Allah ya biya mini da dukkanin buk'atuna

Ina godiya da hakurin da kukayi dani har na tsawon sati biyu koma fiye

Ina alfahari daku masoyan Amafarki nasanta,kud'in na daban ne agareni

---

---

*PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

Pen*is migthier than the sword *

EPISODE1

PAGE32

TYPING

©°••••••••••••••••••••••••••••••°©

Sallamar da akayi A dayan b'angaren ce ya amsa yana sakin murmushi,Unni yakike? ya gida?'sunan da aj ya furtane yasanya gaban Dr.Ammar fad'uwa idanu ya tsurawa Aj dake wayarsa da unni a tsanake cikin girmamawa cikin ladabi.A d'ayan b'angaren Unni ta tambayi Aj ya aiki ? bayan ta amsa masa duka gaisuwarsa,Alhmdllh ta furta ya furta yana mai sake fad'in Unni ai yanzu haka ma muna hospital d'in yau bamu tashi da wuri ba...

Ohk tau Allah yataimaka"ta furta masa,A hankali ta furta" Nur na kusa"ehh ya bata amsa atakaice yana mai d'aga idanunsa ya kalli Dr. Ammar da ya tsuramasa idanunsa masu kaifi Ba ko kyaftawa tunda yaji sunan Unni ya fito bakin dr aj gaban shi ke k'ara faduwa.

Unni ce ta juye harshen ta a yaren fulatanci,tana tambayarsa har yanzu Ammar yana nan kan bakansa ne?bazai karb'i sarautar ba,fahimtar da yayi bata son Dr Ammar d'in yagane zancen da suke yi yasanya sa shima chanja shima zuwa fulatanci,dan duk sun san Dr.Ammar baijin sa tun suna yara akayi koya musu yaren inji kakarsu Ammie gimbiya fatima,wanda itama ga mijinta margayi sarki Hamza ta iya sa da kuma kawar tata HAjiya,har ya" yan ta ma,shi yak'i maida hankali ya iya ne shiyasa bai iya yaren ba.

"Amsawa unni yayi da tabbas dai kam Unni yana nan kan bakansa,Unni bata nuna komai ba duk da amsar tasa tad'anji ba dadi ganin kafiyar yaron nata duk da tasan baizubar bane haka mahaifinsa yake da kafiya.furta masa tayi " kyalesa kar ka k'ara masa maganar komai yazo karshe in sha Allah.Sosai Aj yayi mamkin sosai da jin maganar da unni tayi dakuma rashin nuna damuwa da batayi ba kamar sauran lokutta,sai dai bai tambaye ta dalili ba saboda yanajin nauyin ya yar ta mahaifiyarsa fiye da mahaifiyartasa.Tambayar da ta masa ce ta katse tunanin zucin nasa"•••••••••

Ranar nace ka kirani inkazama less busy Amma Aminullah shiru babu kiranka,da yake haka take kiransa some times itada Sarki Ali ko son,shiru yayi na rashin gaskiya dan tabbas yana sane yak'i kiran nata gudun tambayoyin nata game da Dr.Ammar d'in akan rigimarsa da mahaifinsa,saboda kuma bayaso ya rik'a yawan yiwa Ammar maganar dan duk lokacinda ya masa magaanar sai yaga damuwa karara akan fuskar d'an uwannasa shikuma hakanne bayaso duk da yasan cewa yana cikin damuwar da shi kansa bazai iya boyeta ba a wasu lokuttan ba duk da jarumtar da yakeyi,shiyasa tun ranar da suka fito meeting d'in bai kirata ba,A yanzu ma koda yad'aga kiran yana d'ar darr ne a zuciyarsa duk da yasan unni mace ce marar daukar zafi,sai kuma yaji akasin Abunda yake tunani,yazata yaga ta nuna damuwa ko b'acin rai ko tayi fushi ma dasu.

A hankali ya furtama sorry unni kinsan aikin namu ne,shiyasa bansamu na kiraki ba,Murmushi kad'ai Unni tayi dan tasan tabbas gan gan yaki kiran nata domin baison takurawa AMmar d'in dan tana basa umurni ya tambayesa in yajanye domin ita ko takirasa shiru yake mata,DA kuma yarika convincing nasa har yajanye ra'ayinsa duk da tassan abu ne mai wuya.Shima Aj murmushin kad'ai yayi

dan yagane dalilin murmushin na unni akan maganarsa.

°©••••••••••••••••••••©°

Bayan minti biyu dukkaninsu suka yi shiru,Unni ce ta takatse shirun nasu ta hanyar tambayarsa game da mafarkin da Ammar yasabayi tun yana k'arami wanda anyi neman taimako akai Amma ba,a dace ba kusan shekara ishirin da yan kai.

Amsa mata yayi da ehh yanayi Unni ma a wasu lokuttan kad'ai dan yasan Ammar bazai masa karyaba in yayi saboda shak'uwar dake tsakaninsu.

labarin last mafarkinn nasa yabata wanda ya banbanta da saura duk a harshenn na fulatanci suke maganar.

Ta B'angaren Ammar ido kad'ai ne ya zubama Aj din dan dukkanin abunda suke fad'a baya fahimtar komai inbanda gaisuwar daga cikin yaren,kuma tabbas yaji ajikinsa duk akansa ne suke magana sai dai bai gane kan zancenba,A hankali Ya lumshe idanunsa tare budesu wadanda suka d'an sauya daga farin madararsu yanayin nasa kamar mai jin bacci wanda haka kawai yake jin kasala na saukarmasa ta rashiin dalili.

'Ta B'angaren Unni ta razana sosai da jin labarin mafarkin da dr Ammar yayi,sosai hankalinta yatashi,Kwantar mata hankali Aj Yayi yana furta "unni karki manta fa ba duka mafarki yake zama gaskiya ba agaremu, Annabin mu muhammad saw shine kad'ai wanda yakeyin mafarki kuma ya tabbata dan haka karkisa damuwa dan sun furta zasu dawo kansa bashi ke nuna ko suwaye zasuyi nasara akansa ba Unni kawai kisanya duka wannan mafarkin nasa amizaninb sharrin shaid'an (la'anannen Allah) ba abunda zai iya zama gaske ba,sannann UNNI Addu'o'in ku natare damu mezaisa ki razana,ayanzu ya mayarda maganar sa da hausa inda duk maganar da sukeyi yanaji rad'am akunnensa.

Ajiyar zuciya Unni ta sauke abangaren ta cikin jin dadin furucin na dr aj wanda yasanyata jin sanyi aranta. wanda akullum take k'ara jin sa kamar ma ita ta sunb'ulosa duniya saboda kusan halinsu guda da aj a tabangaren iya sarrafa zance na fahimta da nutsuwa, Ahankali ta furta hakane son muna kai kam addu,a kuma kudage da Addu,a kaji,kai yad'aga mata inda takara furta Allah ya muku Albarka yakare gabanku da bayanku,Ameeen ya amsa mata cikin jin dadi har tamasa sallama Aj yamaza yatare ta daga shirin yanke kiran Unni pls karki sanarwa da kowa harda Abbah,in sha Allah ta furta suna yanke kiran.

Ajiyar zuciya kad'ai yake saukewa a jere cikin kara lumshe idanunsa kansa ya dafe jin yana juyamasa kad'an,A hankali ya bud'esu tar yakoma a mazauninsa daga d'an tsayen da yake tun dazu wanda su bakomai bane agaresu yin irin wannna tsayin saboda yanayin aikinsu na likitota.

Idanunnsa yak'ara lumshewa dasuka k'ara yin d'an jaaa na damuwa

Mafarkin nasa ne yadawo masa akai bayan zaman nasa wanda maganar da yaji aj nayi ce tak'ara dawo masa dashi sabo duk da yana ransa ne har yanzu baisan meyasa yake jin kashe yarinyar da akayi a mafarkin nasa ba yake jinsa har cikin ransa idan ya tuna da sun kashe masa ita jiyake kamar ya yi ta yin kukan da babu mai iya rarrashinsa,tambayar kansa yayi wai dagaske ne kwa?sun kashe masa dream girl d'insa,kansa ya girgiza da karfi yana furta nooo baki mutu ba Cikin d'aga murya irin tsawa d'in nan ta rashin tabbas Kan abu....

©°••••••••••••••••••••••••••••••°©

Ikon Allah kad'ai Aj ke kallo dan Shi Al amarin Ammar nabashi mamaki anya kuwa ba aljana ce ta Auresa ba ko ta shiga jikinsa take zomasa a mafarki kamar yadda su unni suka zata abaya sai dai duk iya binciken da manyan malammai sukayi masa ta hanyar yimasa rak'iya babu alamar hakan atare dashi.

Kuma yanaji ajikinsa kamar ma soyayya yakeyi da aljanar ko sonta yakeyi .Dan tabbas Alamu ya fara nuna son yarinyar yakeyi inma ba soyayya sukeyi din ba,domin ba tun yauba yana ganin wasu alamu agaresa duk da bai tabbatar ba.

Kallon Ammar yakeyi kallo na tausayi da mamaki,ganin kallon da yakemasa shima bayan bud'e idanun nasa da ke

a lumshe jin yayi sub'util kalam,yasan kallo ne yake masa na tuhuma duk da yafi hango tausayin sa acikin idanun na d'an uwansa,maganar da ke zuciyarsa ta fito fili yasan cewa sai Aj ya tuhumesa shikuma hakanne bayaso,kauda kansa gefe yayi daga kallon da sukeyi wa juna shida aj d'in yana mai tsuke d'an karamin bakinsa kar Dr .aj yaga damar sa har iya yimasa wata magana kan zancen.

Dr.Aj k'aramar dariya yayi duk da ya fahimci Ammar d'in sai yayi kamar bai gane nufinsa ba,A hankali Aj yadan duk'o da kansa yana mai furta masa anya kuwa ba son wannan aljanar kakeyi ba domin Kuwa nikam nafi tunanin ALJANA CE (oum Amjad) yakai k'arshen maganar tasa yana sakin karamar dariya,Dasauri Ammar yad'ago Dara Daran idanunsa yana sakarwa Aj wani irin kallo da idanunsa da suka kara girma kallo ne wanda sai da Aj yaja baya,shima yana kallon Ammar d'in da mamaki take zuciyarsa ta kara tabbatarwa da aljanace Ammar din yake tare da ita.

Ran Ammar ya b'ace sosai matuka wanda har sai da labbansa suka kara yin jan wahala na taunar da suka sha sanadin bacin ran da yasame sa na furucin Aj,Huci yake fitar wa mai zafi wanda shikansa aj sai da yayi danasanin maganar yakara yadda tabbas aljanace ke tare da Ammar d'in shiyasa yake wulakanta ire irensu dr malini.

Bayan kamar minti shida yafara sauka daga fushinsa A hankali ya bud'e bakinsa da kyar kamar wanda bayason yin maganar ya furtawa aj "yanzu nizaka had'a da aljannu halittar da muke neman tsari daga gareta,kuma wannnan baiwar Allahn itace Aljanar dude harararsa yayi yana furta kuma ni ba sonta nakeyi ba kawai dai inajin badadi ne sannan ita ba aljana bace then karka kara kiranta da aljana pls mutunce itama kamar kai inada yakinin tabbas mutunce duk da bansan sunantaba har yanzu bansan a ina take ba.

Kallonsa kawai Aj keyi baki asake,Addu,a kad'ai yayi aransa Allah yabawa Ammar lafiya,domin shi gani yake wannan Abu bana hankali bane.

Aiko insunje Nigeria zai sanarwa su Unni aljannu nan kamar ya kamata kara dubashi agani,anema masa magani kar abun yak'arayin girma ganin irin bacin ran da Ammar ya shiga kan furucinsa.kai kawai yak'ara kad'awa yana mai furta ohk!nagane,Amma fa dude kabani tsoro wannnan fushi haka daga kawai na furta Al.....Dr Ammar murmushin da baiyi niyyar fitomasa ba yasaki jin aj yayi furucin Aljanna yakasa idasawa kenan bazai k'ara furta masa hakan ba,har ransa yaji dad'i yadda d'an uwan nasa yake gudun b'acin ransa tun kuwa suna kanana.

Aj wanda yayi shiru jin zai kara sub'util kalami ya furta baki yabawa Ammar hakuri sannann ya kara furta"nasan kaji wayar damukayi da Unni har naroketa karta sanarwa da sarki gudun fad'awa tashin hankalinsa"kallonsa kawai Dr Ammar keyi bece dashi komai ba.

Dr aj samun kansa kawai yayi shima dayin murmushi,ganin yadda yake ta kallonsa kamar wata sabuwar halitta.

Hadadden Rolex din dake daure akan tsintsiyar yakalla ganin lokacin sallar azahar yagabato yasanyasa mikewa dukkanninsu suka dauro alwallah suna dan gabatar da sallar alokacin ta.

NIGERIA

ZAMFARA GUSAU

Uwar ranar da ake kwatsawa ce ta ruwa tasanya dukkanin wani mai abun nawa yake gaggawa ya is a gida don ganin hadarin da had'u lokaci d'aya gudun shan kashin ruwa musamman masu babura.

Baba Adee ne ke ta k'ok'arin barin babban fuel station na nnpc bayan yasha man da zai kaisa garinsu Bungud'u,mashin d'insa ne d'ai daga cikin dankara dankaran motocin dake shigowa a gidan man ne,ya buge mashin d'in na Baba Adee sanadin shigar da sukayi ba dai dai ba.

Fadawan dake cikin motar ne suka fito dasauri suka rik'a masa mashin d'in nasa suna masa sannu tare da duba lafiyar mashin d'in NASA dan tabbatar lafiyar sa suna kara basa hakuri kan d'an karamin had'arin da ya auku sanadinsu,shiko yana furta musu bakomai cikin dattako.

A lokacin ne kyakkyawan dattijon dake cikin motar da duk tafi daukar hankali tafi sauran kyau kirar range rover fara tass new design yasauke glass a hankali dan son yin magana da Wanda accident din ya so faruwa kansa dan yabashi taimako a lokaci nne shikuma Baba Adee ya juyo A hankali daniyar duba bayansa yadda zai fita batare da ya buge wani ba da mashin d'in sa sai yayi dai dai da d'ago kan maimartaba sarki Aliyu Murai da ya sauke glass d'insa gabansa ne yayi mummunar fad'uwa ganin Wanda yahad'a ido dashi sak k'anensa Abdul rashid,sai dai d'an yanayin manyan taka dake tare dashi bakamar lokacin da yana saurayi ba. Wanda har yau basu San meyafaru dashi ba,sai dai kawai anwayi gari da rashinsa anyi nemansa ba,agansa ba.

Sarki Ali kuwa ido yasakar masa ganin bai nuna alamar cewa yagane saba,sai abun yabashi mamaki da alajabi Wanda har yasanya sa tunanin anya shine kuwa shine,kodai bashi bane mai kama dashi ne ,har Baba Adee yayi wucewarsa baisani ba da d'aya daga cikin fadawansa ya furta Allah yataimake sarki shin ko kasan wannan bawan Allah ne sai dai kuma gashi har ya wuce ai,sai lokacin ne hankalinsa yadawo kansa cikin tashi hankali bafaden ne cikin rashin hango tashin hankalinda sarki Ali yashiga ya furta Allah ya taimake ka har ma kama kuke dashi fa,Amma sai dai shi farar Fata ne duk da zafin ranar da ya d'an k'onasa a na hango farinsa....

Ganin samu da rashin da yake shirin yi alokaci d'aya duk da baya da tabbacin cewa shi din ne,Umurni yabawa d'ai daga cikin fadawansa cikin gaggawa da subi mutumin daya fita yanzu Wanda suka buge wa mashin,dasauri suka ja motar d'aya suka bisa.

A MAFARKI NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Pen*is migthier than the sword **

Free

EPISODE1

PAGE33

TYPING

°©••°©

Fitowa motocin sukayi daga gidan man suka parker a gefe gwanin burgewa dama mota biyar ce d'aya tabi mashin d'in Baba Adee,Bayan kamar mintuna goma sai gasu sundawo,sunyi rashin sa,ar ganinsa,sarki Ali Bayan dawowarsu da wannnan mummunan labari labari hankalinsa yak'ara tashi sosai sun sanar masa wata mota ce

ta tsaya ta shiga gabansu kuma sai ta lalace,....maimaraba sarki Ali baice musu komai ba face umurtarsu dayin reverse sukama hanyar Gida (fada).

Abunda yafaru Alokacin da Baba Adee yake tafiyar sa hankali cikin rashin kwanciyar hankali ganin hadarin da ya had'u yana so ya isa gida lafiya batare da yasha kashin ruwa ba... sai dai kuma baima lura da motar da ke bibiyarsa Abaya ba, kuma Alokacin da suka bi bayansa kad'an saboda d'an cunkosan da akasamu sai dai suna hangosa kad'an yana tafiyarsa akan babur d'in kasancewar sa bama gudu da abun hawa bane,wata katuwar mota ce jif bak'a wulik mai tinted glass tashiga gaban motar fadawan atsiyace,wanda dukkaninsu sai da suka razana yadda motar ta kutso agabansu bayan barin guraren da cunkuso yake,abun haushi kuma wanda ke cikin motar ne yak'i fitowa duk da jin k'arar horn d'in da fadawan ke ta sakar masa,d'ai daga cikin fadawan ya fito cikin yanayin masifa yana kwankwasa gilas d'in motar,A hankali glass din motar yake zugewa izuwa k'asa wata matashiyar kyakkyawar budurwa ce da taji bleaching ta bayyana a driver seat d'in wanda da alama ita kad'ai ce acikin motar yanayin ta kamar arazane Amma bai hana ta taunar cingum d'inta ba.

'Magana bafaden yayi cikin nuna bacin ransa"meyasa zaki tare muna hanya kinsan aikin da ke gaban mu ne,Alamun kuka ta fara cikin kissa tana furta masa motar ce fa ta kucce mata kuma she try to control it but takasa sannan ta daura da basa hakuri,sannann kuma yanzu taki tashi ma,Cikin d'an yanayin gamsuwa bafaden ya furta bakomai yan mata amma akara kulawa da irin gudun sa za'ayi domin mafi yawancin haka mota ta kufcewa mutun to ta iya yuyuwa mugun gudu yakeyi da ita ko kuma d'an koyo ne,kai ta d'aga masa cikin kara yimasa godiya,tana mai kara gwada tada motar da farko bata tashi ba na biyu ma sai a na uku ta tashi cikin murna tad'ago tana ma bafaden murmushi da yabata umurnin ta tada motar akaro na biyu taga ko zata tashi,Hannu tad'aga masa cikin sakin fuska sannan ta fisgi motar tana yin gaba abunta,suma fadawan da basu fahimci komai ba suka juya ganin tabbasa Baba Adee ya kubce masa basu ga ko ku'rar sa ba Yasa suka koma gurin sarki domin isarda sako...

©°••••••••••••••••••••••••••••••°©

Gudu motar tayi kamar na barin Duniya sai gata a wani tangamemen gida,Bayan wangale mata k'aton gate d'in inda ta shiga aguje suna parker motar a inda yadace maimakon mace ta fito sai wani saurayi ne yafito a driver seat din wanda daga ninsa dai kaga d'an hau,dariya kad'ai yake tik'a yana furta ashe dai lawisa zaki iya sana'ar film wannan acting haka kinga yadda kikayi kuwa wallahi kad'an yarage dariya ta tafito fili a bayan nan da nake kwance. budurwar da naji ankira lawisa ce ta fito a extra seat itama tana ta tik'ar dariya harda rik'e ciki ashe ma itace budurwar da tashiga gaban motar fadawan sarki...

FA'EEH BG

FIRST LADY

"Muryar tace take tashi tana furta kace kaso katona mana asiri jimmy sugane da gan gan muka shiga gabansu takai k'arshen maganar tana dariya,tak'ara furta jimmy Amma fa nima naso in d'an kwafsa dan namance kwata kwata inbar taunar cingum dinan tana mai kara yin wani k'aton kwai da cingum d'in,dasauri saurayin da aka kira jimmy ya furta wallahi kuwa taunar cingum d'in nan naki yaso yabadamu dan naga kamar bafaden nan yana miki wani kallo duk da nasan bai fahimci komai ba,dariya tayi tana furta yau da aikin mu baiyi kyau ba da oga ya hana muna na sharholiyar mu na kusan sati gashi yau muna da party a club takare maganar da shewa hannayen su suka bige irin na jin dadin nan.

'Jimmy ne yak'ara furta a wanchan karon makinsan anso samun matsala da sai sunga juna tun lokacin,kuma kinsan oga yace da sunyi magana shikenan komai zai lalace shiyasa ma nakara sanya su gaja su su kara saka mana ido kan wanchan tsohon,dana rasa dalilin da yasanya oga bai bada damar akashe masa shi ba na rasa dalilin da yasanya yasa ake kular masa da shiga da ficen tsohon cikin garin nan,duk da ni bazan iya wannan kasadar ba....

Firar su suka cigaba dayi suna lakkame da juna har suka shiga kofar Babban shigarsu su acikin tangamemen falon tabani damar kare musu kallo,lawisa dai irin karuwan nan ne masu lasisi dan tundaga shigar jikinta zaka gane hakan yadda kana nan kayan jikinta sukayi tieting din ta babu inda ba,a gani najikinta abun ba kyan gani,ga uban attach da zuba akanta da nail zago zago kamar wata horanya farace tass kalar farin bleaching,shima jimmy dai da ka gansa kaga d'an wanka ne kuma rikakken d'an shaye shaye bakinsa yayi bak'i alamar shan taba da sauran kayan maye tundaga yanain maganar sa zaka gane,shikam dai bak'ar fata ne irin tamu bakamar lawisa mai bleaching ba.

Su lawisa anji kunya domin ba,a godewa Allah ba shine aka koma neman kyaun kanti.

*gareku "yan matan mu kuji tsoron Allah kudaina fita tsirara kuna sakin siffar jikinku ga mutanen kan hanya,domin kuwa Allah yatanadar da azaba mai tsanani ga masu irin wannan shiga,Dan Allah arage yin irin kayan nan masu matse jiki,iyaye kuma hakkin ku ne ku hana ya yanku saka irin wannan sutura domin ko zunubi suka samu a danaku kason indai dasanin ku suka sanya,teloli kuma kuji tsoron Allah kudaina yiwa yayan mutane dinkin da kuka san bazaku iya barin ya yanku da k'annenku..Allah yasa mudace yakare mu daga sharrrin shaid'an dana zuciya *

©°••••••••••••••••••••••••°©

Hayaak'i ne ya turnek'e falon inda nakai duba na a tsakiyar falon inda na hangi jimmy da lawisa manne da juna,Ance mannau😁Nida cingum..

suna zukar shisha hankalinsu kwance,hannu jimmy d'aya akan kirjin lawisa daya kuma rik'e da tiyo mai kyau nashisha,kar'ar wayar sa ce dake a hannun kujera yasanyasa cire hannun nasa akirjin lawisa yana duba mai kiran nasa sunan oga

yabayya akan screen dinsa dasauri yayi picking call yana karawa akunnensa,A ad'ayan bangaren oganne yake furta jimmy inata kiranku shiru inji in aiki yayi kyau,cikin muryar maye maye jimmy ya furta ya oga na ka kwantar da hankalinka ai kasan ko yaushe mune da nasara indai tawanann fannin ne yakai karshen magaanar cikin sakin dariyarsu irin ta yan hau,A bangaren oga shima dariyar yayi yana furta nakasa zaama tun d'azu yanzu hankali na yakwanta domin tin lokacin da yashigo akasanar mini yakara furta kace yau akwai party kenan aikin ku na kyau zakuji alert din miliyan biyar yanzu yanzu shewa jimmy yakeyi lawisa na tayasa da duk taji komai tare da furta godiya mukeyi oga sannan suka datse kiran,dasauri lawisa ta mike cikin farinciki ta kwaso kwalaben giya dake kan dinning ta tile agabansu da kwayoyin maye,

*SAY NO TO DRUGS ABUSE□□

.*YAN UWA MUGUJI TA AMMALI DA MIYAGUN KWAYOYI DOMIN ILLANE GA RAYUWARMU*□□

A hankali suke bin kwalaben da'i dai suna shanyewa tare da kora wasu kwayun da ga su ga kamar ko kyan kallo baabu,take dukkaninsu suka sake rikicewa kai yad'au chaji kamar wasu mahaukata haka suka kara had'ewa da juna suka fara masha'ar su da suka saba cikin maye kamar wasu dabbobi

(wal iya zubillah)Nidai ganin haka yasa na fece kar inyi mugun gani.

Allah kashirya muna zuri'ar mu□

Allah yakare mu daga kusantar zina□

A ba'ngaren sarki Ali kuwa tunda yakoma gida hankalinsa yagaza kwanciya ko fada bai je ba sai safa da marwa yakeyi akatafaren dakinsa dake sashen unni kuma kuma ya hana kowa yashigo masa sashen duk da yasan gimbiya hassanat da Amintacciyar masarauta kadai ne sai yan yansa ke iya shigo masa kai tsaye. k'arar wayar sa ce ta tsayar dashi da zagayen da yakeyi uwar dakin nasa daukar wayar yayi dan ganin mai kiransa khadijan hajiya yagani yabayyana a screen d'in,bakowa bace wannan khadija sai autarsu dake aure a kano picking call din inda cikin d'an tashin hankali take masa bayani bayan sun gaisa...

"(Hajiyar safkare) ce gimbiya halimatu. mahaifiyarsu Suce dake wurinta ta tada hankalinta sai tadawo zamfara yau saboda mafarkin da tayi na Abdul rashid dinta yadawo gida....

Hankalinsa Ne yakara tashi sosai sai dai bai bayyanar afili ba gudun kara tashin nata hankalin,A yanzu ma tana masa bayanin ne kamar zatayi kuka domin hajiya ta sako ta gaba,lallashinta yayi tare da bata umurnin taje tabawa hajiyar waya...

tafiya kadan tayi zuwa hadadde d'akin da hajiya take bayan tayi sallama an amsa mata wayar ta makala mata a kunne A hankali yar tsohuwar dake kan sallaya tana ta jan charbi tasanya hannunta ta dafe wayar da mama dije ta daura mata sunan da yaran ke kiranta dashi kenan.

Muryar Sarki ali ce ta doke kunnenta sai ta fashe da kuka wanda dama haka yake fama da ita kullum indai zai kira ta,ta dalilin abu guda biyu muryoyin su umar da Abdulrashid take tunowa a duk lokacin da tayi taji muryarsa Takance Ali Allah kabayyanar da haske acikin duhu dan haka take kiransa..

Dama dalilin da yasa tazabi tadawo wurin mama dije da zama shine sanadin tun lokacin da aka nemi Abdul rashid aka rasa taji masarautar ta ta isheta da ma jihar har zuwa lokacin da umar yakone da iyalansa alokacin da mama dije tayi Aure a garin kano sai tanemi takoma gurin ta da zama babu yadda sarki Ali da rashin yan uwansa yadamesa zaiyi haka yabar ta ta koma chan da zama sai dai aka rufe sashen ta domin yafahimci kamar hankalinta zaifi kwanciya chan, kuma duk abunda mahaifiyarsu keso shine abun da suke so tun suna yara.

Kuka take sosai cikin jin radadin abunda baka da yadda zakayi dashi sai dai fatan Allah yayi maka mafita yakawo maka karshen komai,acewar ta muryoyinsu duka iri d'aya ne tun suna yara shine dalilin kukan nata sai aduk lokacin da suka yi magana dashi.

Ta bangaren sarki Ai shima hawayen kawai yake zubarwa na tausayin mahaifiyarsa dake cikin damuwa cikin raunin ta da yafara bayyana wanda take kokarn boyewa na shekara talatin da takwas dan ma Allah yasa hajiya macece mai tawakalli dasai hawan jini yakamata da wasu cututtukan.

Bayan tagama kukan yakara lallashinta yana furya Umma kiyi hakuri inaji ajiki na komai zai bayyana in sha Allah kuma komai yakusa zuwa karshe wanda duk suke da sa hannu akan cutar damu Allah zai tona musu asiri,kanta kadai take iya d'aga masa cikin kara jin natsuwa na saukar mata,mama dije dake zaune bakin gado itama taci kukan ta dan yau dukkaninsu abun yadawo musu kamar sabo sai kallon mahaifiyar tata takeyi cikin tausayi...

hakuri yakara bawa hajiya tabar tafiyar sai gobe za,a turk private jet yadauko ta saboda ynzu baisauko ba yana kasar paris da wakillan kasuwancinsa sukaje taro na manyan yan kasuwa da suka wakilcesa,Amma zai sauka da daddare.

©°••••••••••••••••••••••••••••••••°©

FIRST LADY

A bangaren hajiya kuwa tacije tsaf bata son jirgin a mota take so tazo dole ba yadda ya iya Ya amince maata da zuwan ta mota sallama sukayi ta mikawa mama dije

wayar tare da sakar mata haraara na kiran sarki Ali da tayi taso ace sai dai aganta tsididit a masarautar,wayar mama dije takarba tana mai sunkuyar da kanta cikin d'an sakin murmushi domin tasan dalilin hararar da tasamu D'akin ta fice cikin d'an rashin gaskiya..

BAyan fitar tane sai ga wani kiran na sarki Ali yana mai sanar mata zai turo mota biyu yau gobe tunda sassafe sai su taso tunda bata son tabiyo jirgin,ki shirya mata kayanta touh Hamma tace,tambayar ta yayi ina inayah?tana makaranta tabasa amsa dayake ma yau suke yin hutu shiyasa bata dawo da wuri ba,kigaishe ta ya furta cikin kulawa sallama sukayi tana furta zataji

Tare da yanke kiran...

Fa'eeh Bg

FIRST LADY

kai amma fa nayi kokari yau babatun manaji duk da bani lafiya kunsamu long page.. Kusanya ni a addu'ar ku ina fama zazzabi ne.

Kuyi sharing pls.

Kuyi muna like,da comment...

https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRInZ0yKim

A MAFARKI NASANTA

In my dream I know her

By

Pha'eezah Almustapha

Daga Alkalamin✍✍

Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

*Pen*is migthier than the sword **

Free book □

EPISODE1

PAGE34

TYPING□□□

BUG

©°••••••••••••••••••••••••°©

A bangaren Baba Adee ya isa gida lafiya inda ya tarar da su Halee sun dawo makarantar boko har sun chanza kaya izuwa na gida saboda ba,a islamiyya yau alhamis,khady na ma Halee fira itakuma tana ta wankinta na kayan Baba Asabe dake zaune agefen barandar tanashan redion ta...

Sallamar sa ta mik'ar da Baba Asabe daga zaunen datake tana kame kame,domin ita ko karar babur dinsa bataji ba,turus yayi ganin abunda baiyi zato ba waton dai har yanzu bata bar cutar Da yarinyar nan ba ya furta acikin zuciyarsa,

su Halee ne dake masa sannu da zuwa ne suka dawo dashi dai dai daga maganar zucin da Dayakeyi Amsa musu yayi yayi cikin d'an sakin fuska sannan dakin sa bayan ya ajiye ledar da yashigo musu da ita.

'Baba Asabe da batayi tsammanin dawowar sa yanzu bane tasha jinin jikinta tana masa sannu da zuwan da yak'i Amsa mata,Baba Adee ne bayan shigar sa dakin nasa ya kwala kiran Lauratu ! Lauratu ! Amsa masa tayi jiki Amace dan tasan yau ta k'ara ballo ruwa, aiko shigar ta dakin kenan yahau ta dafad'a dan me zata bar Halee cikin

wannan uwar rana rana wanki gashi tasan bata isasshiyar lafiya,take ana jikinta zai iya chanzawa sai kuma ankoma yawon ganin likita.

Shiru tamasa shikuma yacigaba da fadansa yana furta kiji tsoron Allah Lauratu yarinyar nan kinsan cewa Wata babbar Amana ce agurin mu karki bari ubangiji yakama ki da laifin cuta mata dan bata miki komai ba hasalima akoda yaushe cikin kyautata miki take.

nasha fada miki irin son da nake wa yarinyar nan batun yau ba tabbas inajin ta Araina kamar yar da na haifa tawa tajini na,domin nafi jinta araina fiye da khadija saboda maraicin ta,yanzu ko dan ni baza ki rike ta Da gaskiya ba kamar yarcikin ki.

Baba Asabe dake jin fadan nasa a cikin kunnuwan ta kamar ta saki ihu take jin ya had'a da yakeyiwa Halee dana Khady ranta ya mugun b'aci sosai sai dai ba halin nunawa, A hankali kamar zancen yashiga kunnenta ta fara basa hakuri tana furta ai Halimatun ce tace inbata zatayi ka tambaye ta kaji,ta furta hakan ne domin tasan Halee bazata tab'a karyata taba.

murmushin bakin ciki yasaki tare da girgiza kansa domin ya fahimci manufarta tanason kare kanta ne A hankali ya tunda kince ita tace kije ki karb'i wankin ki iyar da kanki ko kibawa khadija ko kira almajiran da kewankin.Amsa masa tayi da toh,sannan ta fice daga d'akin tana guna gunai kasa kasa cikin ranta afili kuwa badamar fitarwa,Dai inda Halee ke duk'e cikin rana tana wanki wanda bayan fakon idon na Baba Asabe khady ta taso ta rika mata dan kayan nada yawa,jin motsin fitowar tane daga d'akin Baba Adeen ne yasanya khady runtumawa aguje zuwa d'akinsu wanda har sai da Halee tayi d'an murmushi duk da yanayin da take ciki na kuncin zuciya,domin kuwa khady bata mance da kashedin da tamata ba na inta sanya hannunta cikin wankin sai lakad'amata na jaki.....

ooh ni fa'izatu ke kam wannan Baba Asabe anyi futinanniya,har da yar son taki ma baki ragawa to kenan koni mai kwaso rahoton baza ragawa in ankamani kai aiko bari inyi takaina inkara boye kaina.😆

"ke ta furta bayan tsayuwar ta gaban Haleen ki Aje wankin nan ki kira min su idi suzo su idasa shi takai karshen maganar tana sakar mata harara Kinyi arziki Amma ko yanzu akwai wata rana zamu hadu zaki idasa aikin ki takara furwa Halee kasa kasa,A hankali Haee tajawo dogon hijab d'in blue dake mak'ale a igiya tasanya adan karamin dake jikinta cikin dan yanayin sanyin jiki tafice gidan wanda sai da takai zagayen gidan sannan wasu hawaye masu zafi suka samu damar silalo mata tana sharar zufan data tara acikin ranar mai kyaifi da tasha,share hawayen take da gefen hijab dinta aranta tana Addu,ar Allah yabayyanar da iyayenta in suna raye da ahalinta baki d'aya,sannan tafice bayan tsai da hawayen nata.

Wasu yarane guda biyu daKe zaune achan gefen barandar masallacun dakE unguwar tasu ta kyafato da alamar su zo,biyota sukayi har cikin gidan Alokacin Baba Asabe duk ta hada musu kayan dan fita dasu idi almajiri zasuyi ,direct bohol din unguwar sukayi Domin idasa wankin bayan kwasar kayan.

Halee dakinsu ta wuce achan ta tarar da khady na assignment din da aka basu,dashigar ta d'akin ta fad'a toilet dan yin wanka wanda kuma achan cikin bayin ne ta darji kukanta kamar ranta zai fita gwanin tausayi khady tayi tayi tabud'e kofar ta lallasheta ta yi banza da ita hasalima da ta murd'a handle din arufe kofan yake ansanya sakata dole takyale ta tayi mai isarta..

Wankan ta tadauro tare da dauro alwallar la,asar bayan ta lallashi kanta

'karar bud'e kofa ne yasanya khady bud'e idanunta dake rufe wanda dama tsumayin fitowarta takeyi bare datas

Ji shiru.kyakkyawar Halee ta kalla datayi jawur da ita sosai abun ka da jar fata abun sai yabaka tsoro yadda eyes dinta sukayi luhu luhu dasu,gab gab d'in da jikinta keyi ne da khady tagani yasanya ta mikewa da sauri tana taimaka mata tazaunar da ita kan katifarsu tana rika mata kayan ta da tacire a toilet din,taba goshinta khady tayi rau da zafi taji shi,mai ta d'auko ta shafa mata alallausar fatar ta ganin alamun bata iya komai sannan ta fito mata da kayan da zata saka mata mai dan nauyi wanda zai taimaka wurin rage mata sanyin jikinta,dakyar ta amince ta taimaka mata ta sanya mata kayan jikinta zuwa wata rigar yadi mai d'an nauyi da rigar sanyi mai hula da dan hijab din ta baki.

(hijabban gado)😉hijaban gado mana kullum mutun cikin hijab bawani shan iska Allah ni masu wannan dabi'ar tausayi suke bani da dariya kai bawa kullum kamar matar liman ko matan malan ai suna cirewa agaban malan bare ke da ba matar mai sittin ba😂su Halee araga wa kai sako ne sako ne fans nata ku isar dashi koma samu hasken

FA'EEH BG

FIRSTLADY

ALLAH YA JIKAN IYAYENMU DA RAHAMARKA YAA ALLAH WAYENDA MUKA RASA😭 DA WAYENDA KE A RAYE

turare tasanya mata sannan tabata paracetamol dan tasamu relief dawuri da kuma bacci,Bayan sunyi rigima gurin shan maganin dan bata son ganin ko kwalin kwayar magani ne Ko allura,tamata dolene wurin shansa ta hanyar furta mata zata sanarwa da (daddy)Baba Adee dakyar ta karba tasha tana ya mutsar fuska.

Allah sarki Ashe muna😩 da yawa Halee shan magani ko wahala😹Allurar ma basauki kai Allah yakara muna lafiya mai inganci

Bargo khady ta lullub'a mata tana mata Addu'ar samun waraka kamar yadda annabi saw ya yadda sahabbai suka samodaga garesa idan kaje ganin mara lafiya idan har ciwon bana ajali bane to za,a warke da yardar ubangiji bayan Ankaranta ta sau

bakwai akusa da marar lafiyar wannan Addu,a sahihiyace domin tazo alittafan hadisi da dama irin su umdatul ahkam,hakkul mubin,gulubul mara .Da dai sauransu...

Ga Addu,ar kamar haka .....

"AS ALUL HAHUL AZIM RABBAL ARSHIL AZIM,AN YASFI YAKA"Face sai Allah ya yayema masa,sahih ne abu dawud ya ruwaito sa..

wannan lamirin namiji ne in macece za,a ce anyash fiyaki...

kiduba acikin kitabul hakkul mubin na hud'u hadith no.100:cif

a page 10.

zaki samu dayar addu'ar ma wadda annabin yakasance yanayi in yaje ganin mara lafiya apage din..

Allah ne mafi sanin daidai

Allah yasa mudace

Sannan tacigaba da solving din assignment dinda aka basu yau inji malamin maths,A hankali dake kwance tana kallon yar uwar tata cikin so da kauna, cikin yanayin zazzabinta bacci yakwashe ta

WACECE HALEE

cikakken sunanta halimatu sadiya umar,tana zama garin bungud'u ita kamar Amana ce a gidan Baba Adee domin kuwa halee yar tsintuwa ce tsintuwa mafi daraja agaresa shiyasa kullum yake jin tausayinta na rashin bayyanar iyayenta,Halee dai kyakkyawa ce takarshe ga shagwab'a da saurin kuka.Halee tasamu gwargwadon karatun arabia duk da yadda Baba Asabe ke addabar ta duk da wani lokcin bata samun damar tafiya islamiyar ma bare boko,ta haddace wani kaso acikin alqur,ani mai girma,kuma tayi manyan littafan fiquhi da hadisai da sauran su domin Halee akwai hazak'a tako ina da ace tasamu bground na kwarai da sai ta fi haka.Halee takasance bata da yawan son magana shiru shiru ce inkaga maganar ta mai tsawo da to Baba Adee ne ko khady,tana musgunawa sosai agurin Baba Asabe sai kuma Allah yasanya mata wani irin hakuri na ban mamaki da tausayi,Baba Adee yanason ta sosai shiyasa komai zai musu ita da khady yakeyi shiyasa har a makarantarsu ma kawayen su da wasu daga cikin malanmansu yan biyu suke kiran su duk da jin ba sunan uba d'ay suke amfani dashi ba amma ganin yar kamar dasuke da juna da kuma shakuwar da tsakaninsu sai ba,a dauki Banbancin sunan uban da komai ba sai suka barshi amatsayin may be sunan wani ne na familynsu take amfani dashi,suma halee su sun san suna kamar dan wasu lokuttan sukan tsaya gaban madubi sudubi kansu tun lokacin da aka fara furta musu suna kama amakaranatar dan kara tabbatarwa dakansu sai dai suma basu daukesa komaiba,Suna kama kam tabbas sai dai banbancin dake tsakanisu na fata ita Halee fara ce tass kamar farin nan na larabawa mai kyau kamar ka k'wanta jini ya fito sabanin itakuma khady black ce ko ince chocolate irin mai kyau d'in nan,khady bata da bata wani saurayi agefe duk da yadda samarin ke musu turu turuwa saidai suna bin umurnin Baba Adee ne da yace

sai sungama secondry sannan zasu fara tsayawa da wani wanda itakam dama halee bata tab'a tunanin tasamu damar tsayawa da kowa ba domin acewar basu ne gabanta ba,iyayenta sune abu nagaba da takeson ganawa dasu idan har suna raye awannan duniyar.

wannan kenan agaba zan warware muku komai munma kusa kaiwa inda yadace kuji asalinta da yadda akayi tazamo yar ysintuwa mafi daraja agurin Baba Adee har yake kiranta da Amana agaresa.

©°••••••••••••••••••••••••••••••••°©

©°••••••••••••••••••••••••••••••••°©

□FA'EEH BG□

FIRST LADY □

IN THE BUILDING□ EYYH DJ KARAMUN VOLUME□□

au ashe typing □nakeyi Allah yashiyeni□□

Allah ya muku Albarka fans□□□

KHADY

itama yakamata mubata nata shafin,ko dan yadda tadamu da Haleen mu.

Khadija Abdul rashid shine cikkaken sunanta Haifaffiyar garin bungud'u lg a unguwar sarki mahaifin khadija Abdul rashid ana kiransa da Da Baba Adee inji mutanen unguwar yara da samari yana aiki a talatar mafara wanda duk kwanakki yake dawo wa gida yana aikin taimakon likitoci a chan wanda ada kawai matsayin warda servant security ne mai tsaron kofa sai kuma aka fahimci yana da wani talent kan abunda yashafi tiyata da dai sauran ayyukan likitota sai suka dawo dashi cikin ward din yana taimaka musu da wasu ayyukan,sannan yana d'an madaidaicin kanti achan na saida provision.

Khady ita kad'ai Allah yabawa su Baba Adee da Baba Asabe wadda sunanta na asali yake Lauratu sunyi Auren soyayya da Baba Adee Alokacin yaje yin aikin noma agonar mahaifinsu a kauyen na bungud'u mai suna (gada) gada gadajen Allah kauyen akwai dadi arado.

Ya had'u da ita ne achan lokacin takawo musu tallan fura tun alokacin soyayya mai zafi ta shiga tsakaninsu wanda dan danan manya suka shiga maganar tasu.

Anyi Aure Amarya ta tare agidan da mahaifinsa yabasu wanda sai bayan kusan shekara biyar Allah yabasu haihuwa ta ya mace inda yarinya taci suna khadija,dan shine sunanda Baba Adee ya zab'a duk da saida akayi rigima da mutuniyar fafur bata son sunan,tun alokacin Baba Adee yafara takawa abun burki yakuma san Lauratu bata mutunci dama lunbu lumbu tamasa,take kuwa shima ya bure mata.

Khady itama dai kyakkyawa ce yar black beauty kamar yadda nasanar muku alabarin Halee sai dai kuma ta d'an d'ara Halee girman jiki, A yanzu shekarar ta goma sha takwas a duniya da yan watanni sabanin halee mai shekara goma sha tara cif da wata biyar.

Khady takasance tana mugun son HAlee tana jinta kamar yar uwar ta tajini tasha furta ma Halee ni inajifa kamar tsatso d'aya muke dake inaji jininki na yawo ajiki na sai dai kawai Halee tayi murmushi tace nima haka. duk wata Damuwar halee tasani sai dai bata yadda zatayi,dan lokacinda ta fahimci itama Halee ba innarta ta haifetaba sai tausayin ta yadarsu azuciyarta mai girma wanda shine yake tasiri haryanzu.

itama gwargwado tasamu ilimin arabiya dana boko dan kamar ma komai d'aya sukeyi da Haleen duk da yadda Baba Asabe ke son sakanta ta hakan ya faskara itama tasamu gwargwadon tarbiyya awurin Baba Adee.ta fannin samari babu dokar dai ta mahaifinsu na aiki.

WAZAI MINI TYPING

muje zuwa

GUSAU

A bangaren sarki Ali yasanarwa da Unni game da dawowar Hajiyar safkare tayi farinciki sosai dan danan takira Ummi tasanar mata farincikin su bai b'oyuwa awannan rana take aka fara shirye shiryen gyara mata sashenta da yakasance arufe duk da duk bayan dan lokaci ana gyaransa,ayanzu ankara kimtsa komai dan jiran dawowarta wanda dama shine kowa ke tsumayi domin hajiya mutunce mai kima a idon Al ummar masarautar don macece mai son mutane.Duk wanda yaga irin gyaran da akeyiwa sai yaji fariciki domin kuwa sun san tabbas dawowa zatayi.UMMI ce takira Ammie dake k'asar jidda tasanar mata,Ammie tayi farinciki sosai jin wannan abun farinciki take itama anan tasanarwa da Ummi zata dawo itama karshen wata sai dai ta gargad'i Ummi da kar tagayawa kowa tanason basu suprise ne,farin cikin da Ummi tashiga baya faduwa yanke wayar sukayi cikin farinciki..

labarin dawowar hajiyar safkare ya karade masarauta har ya isa kunnen gimbiya fulani matar tsohon sarki mai rasuwa wanda itama yanzu mustapha Yashigo yake sanarmata bata wani nuna jin dadinta face Addu,ar sauka lafiya datamata,tana mai furta ita taje ita tadawo bayan fitar mustapha daga gidan,tana mai kyab'e baki irin yadda tsofaffin masifaffun nan keyi Wayenda suka ga jiya sukaga yau.

FULANI TAMU••••••••

Shima muhammad(malan) dayaga irin gyaran da akeyiwa sashen bakinsa yashiga tabewa yana wucewa sashen fulani da shigarsa ko sallama babu ya furta Fulani ki tsaida khairyya daga zuwa gidan nan bansan ubanda zatazo yi ba kawai dan hajiya zata dawo shine itama zata wani kwaso kafafu,kallonsa kadai takeyi tana taunar

goronta,cigaba da magana yayi jin bata tanka masa ba.ta kirani fa wai inturo mata kud'in mota saboda bata dasu kuma mijinta baya nan,tafiya kamar ta dole natambayeta mezatayi da kud'in wai mota zata shigo tazo tarbon hajiya,tunda hajiya uwar tace yakai karshen maganar cikin jan guntun tsaki,nace bazan turamata ba indai dan hajiya zatazo shine dan iskanci takira yaya mustapha dan tasan dole ma ya tura mata yakai karshen maganar cikin b'acin rai.

Kallon sa kadai keyi bayan gama jin zancen sa rai b'ace.

Mikomun wayata gata chan kan madubi ta furta cikin wani bacin ran da yakara taso mata,wayar ya mika mata tasanya gilass dinta tana mai dialing numban da aka saving da Auta,ringing biyu ana uku tad'aga cikin shesshekar kuka khairiyyah ke furta na shiga uku fulani abun na alhj har ya kai yafara shigo mini da karuwai cikin gida kuka take kasharban har tana shid'ewa saboda bak'incikin dake cin zuciyarta,fulani ma data kira da niyyar masifa dakarfi take raunar goronta cikin bakincikin da ke turneke ta,sai kuma tasamu kanta da yin shiru, dan tun Auren khairiyya shekara talatin yanzu da yan kai babu cigaba,kuma shegen mijin yaki sakar mata "yaa wanda kuma ita dakanta ta had'a auren rayi danasani marar iyaka ga rashin haihuwa da bayayi ga kashin da yake bata da rashin kula domin ko abinci wannann dakyar khairiyya take samu duk da kasancewar alhjin mai tarin dukiya.

Muryar khairiyya ce tadawo da da ita daga maganr zucin da takeyi i nda take furta Fulani zuciya cikin kara fashewa da kuka mai tsuma zuciyar mai saurare..✍✍

Wayyoh khairiyyar fulani ke kuma taki kaddarar kenan😩

Nasan dai kungane wannan khairiyyar koh..Domin sai da namuku kwatta kwatta na labarin tundaga kakanni.Kuma nayi haka ne don kugane dakyau.✍

ko zai faru da khairiyya Allah dai yasa ba zuciyarta ce take shirin bugawa....

Yawan likes yawan comment yawan page....✍

Like,share and comment pls

[3/27, 10:05 PM] Fa'eehbg writer: □A MAFARKI NASANTA□
In my dream I know her
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

IDAN KINA BUK'ATAR UPDATE DINA DA ZARAN NAYI TO KIYI JOINNING GROUP DINA MATA KAWAI✍

https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

FIRSTLADY

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

*ESSENTIAL WRITER'S**

*Pen*is migthier than the sword **

*Free book**

EPISODE1
PAGE35

TYPING

••
not edited..

A hankali ta lallasheta tana mai tambayar ta ya bata umurnin zuwan da zatayi duk "A ah"ta bata amsa bayan ta tsaida kukan nata,kara tambayarta tayi kudin na isar ta eh ta furta tare da kara furta ai dubu hamsin ne ya turo mini cikin mutuwar jiki,umurtar ta tayi da tabishi a alalama dan tasamu gobe yabarta ko jibi tazo,touh tace sukayi sallama.

Fulani ce ta umurci malan cikin wani yanayi da yabata maganinta na hawan jini dake cikin lockern drowern ta na gado dauko mata yayyi tare da jarkar swan mara sanyi yana furta ai duk ke kika ja mata tunda tun farko sai da nace karki had'ata da wanchan tsohon kika kika k'iji tun kafin murabata da Abdul rashid nace miki kibari tasamu wani kika k'i ke ga d'an uwan k'awarki mai kud'i alhaji ai ga irinta nan,Bayan tasha maganin kallonsa take da mamaki jin furucinsa wai duk laifintane,kamar ba dashi da ita sukayi komai ba yanzu kenan ita zai bari ciki tasan idan har khairiyya taji ai tasan ta rasa ta dan zata iya barinta har abada gashi Allah yadora mata son khairiyya kasancewarta itakad'ai mace agareta da kuma Auta,da maln shima tana son sa saboda tasu tazo d'aya shine abokin shawararta amma yanzu jibi yadda yake mata fad'a kamar baisan komai ba kamar kuma ba ita ta haifesa ba.

YAA ALLAH KAR KA BAMU IKON HAIFA "YA "YAN DA ZASU RIKA YIMUNA FAD'A KAMAR SU SUKA HAIFEMU AMEEN

Uffan batace masa ba har ya gama yimata fad'ansa yafice.
Take nadamar da ta dade tana tare da ita ta taso mata na raba Ummulkhairi da Abdul rashid a yanzu da komai ya chabe,hawayenta ta share na tausayin khairiyyah.

A kano kuwa b'angaren Hajiyar safkare sun taso daga kano lafiya tun safe cikin jahar zamfara wuraren karfe sha biyu da rabi na ranar Alhamis,sun samu tarba ta musamman dan duka ahalin babu wanda baizo ba sai mutanen india, girke girke kala kala aka musu da sanya hannun Unni da Ummi.

Farincikin su Nisa da Sumy bai Fad'uwa lokacin da suka hajiyar dan basu san da zuwanta ba Ummi tadai ce su shirya yau zasu je Wurin Unni,Dad'i biyu kuma Inayah tare da ita dan sun saba da Inayah sosai a lokutta da dama su mama dije kan kawo musu ziyara itada hajiya,kuma suna waya da ita awayar Unni ko Ummi.

Janye Inayah sukayi zuwa d'akin Nisa dake chan akusa dana sarki Ali fira sukeyimata kala kala duk rabi ta yaya Abdallah ce dan sun san lokacin baya bata da wani wayau Allah yadaura mata sonsa sai dai shi besani ba har kawo wa yanzu.

Sauraren su take kawai insun fadi abun dariya tayi dariya na murmushi ta murmusa babu wadda ke bata dariya Irin Nisa,Dan Harda Gulmar sumy ta kawo mata a kunne kuma agaban sumy d'in akan mahir inda take shaida mata wai har iyaye sun shiga ciki da sungama karatu za'ayi bikin,k'aton rank'washi sumy tayi mata tana furta wallahi Inayah k'arya take miki,sai kuma suka koma dariyar Nisa dake zubar da hawayen rankwashin da Sumy tayi mata,Inayah ce tajawo ta tana lallashi,sai kuma ta warware jin tambayar da Inayah tama ta na " ina Yah Al amin??

Amsa tabata yana india man sai kuma ta dafe kanta tana furta gosh! tare da rufe bakinta tana furta Nabani Amma dai Aunty Sumy Munafuka kike badai kingaya mata bah,tana k'ara b'are baki zatayi kuka Inayah ce ta jawota ta rungume tana lallashi sannan ta rad'a wata magana akunne da bansan ko ta mece ce ba,dukkaninsu suka sanya dariya.

K'wank'wasa k'ofar da akayi ce tasanya su yin shiru,"waye"cewar Sumy, Muryar Husna ce tasanya su yin shiru inda ta furta nice fa Anty tana turo k'ofar tayi jin ance tashigo,da gudu tashigo bako sallama sumy ce tadakatar da ita ta hanyar furta sallamar fa tana hararar ta komawa tayi da baya tayi sallamar suka amsa mata atare,ya akayi ne Husna ta Halan?inji inayah,hajiya ce take kiran ku,kuzo kuci abinci tabasu Amsa,mik'ewa dukkaninsu sukayi suka fice daga d'akin.

FIRST LADY

A had'adden dinning table d'in dake part d'in Unni dukkaninsu suka iske iyayen nasu,tundaga Su Unni da su mahir har kan sarki Ali da sauran su Abdallah dasu yusuf,isowar su wurin yasanya dukkaninsu suka ja kujeru akusa da hajiya suna saka ta a tsakiya itakuma inaya tana akusa da Abdallah da Husnat,kowa shi yake zab'ar abun da za'a zuba masa..
Had'addiyar fried rice jallof ce da taji naman hanta da kuma white rice da stew ta chicken mai hade da cos low da yaji kayan had'i,sai kuma wainar shinkafa da taji had'i,hajiya ce mai son waina itada nisa saboda ita kayita musamman.drinks ne kala kala.

Bayan hajiya Dukkanin su daga mai fried rice sai mai coslow suka zab'a.
Ahankali suke cin abincin su tun bayan saving dinsu da masu aikin na Unni sukayi,sai su Nisa ne dake k'us k'us din zaman zaman Inayah kusada Abdallah sukeyi kasa kasa Bayan Hajiya duk da hajiya tanaji bata tanka musu ba.

A hankali dukkaninsu suka fara watsewa suna komawa falo sai yarage daga Nisa sai Sumy suka rage da suka tsaya gulma sai inayah dake tsakurar Abincinta saboda jin ta uncomfortable a wurin,Abdallah ne ya furta mata Ahankali Inayah lafiya kuwa? Dasauri tad'ago manyan dara daran idanunta tana sauke su kansa arazane jin yadda yakira sunan nata ba yadda tasaba ji ba,Murmushi ne ya sub'ucewa masa abazata sai kuma ya d'an sauya murmshin ta hanyar furta Allah yasa dai ba tsoro nabaki ba kai ta girgiza masa tana mai sauke idanunta k'asa,Muryar shi ta tsinkayo yana furta bari inbarki kici Abincin ki koh madamm!

Yabar wajen dinning din yana sakin murmushi ya wuce dakin mahir inda suka dosa suma shida Yusuf.

'Su Nisa dake kallon su kamar status gulma ta yi dad'i A hankali suka shek'e da dariya wadda sai da duka su Unni dake firar yaushe gamo suka juyo suna kallonsu,kai kawai Ummi ta girgiza itada hajiya suna masu fad'in Aikin ku kenan Haijya ce ta furta waisu wayen nan yaran yaushe zasu gama boko ne,Murmushi Unni tayi tana furta Hajiya boko ai ba,a gama sa sai dai kai iya yinka, kyab'e baki hajiya tayi,Ganin reaction d'inta sai Unni tayi murmushi ta furta shekarar nan ne ai Hajiya,to ai kam dasun gama makaranta zan zauna da iyayensu amusu Auren sai ahade da inaya itama,kallon hajiya kawai su Unni keyi dan sun san su nisa ko samarin basu dasu bare akai ga fira duk da basu sani ba ko duk suna da wayenda suke so,Dan D'an yau ba'a shaidar shi...

Unni ce ta furta to ai shikenan hajiya ita sumayya yar gida ma za,ayi inaga tana dariyar jin kunyar maganar tata,basu dai tambayeta dawa ba,Amma ita kam Ummi tagane tunda har Unni kejin kunyar maganar toh da mahir take nufin za,ayi yar gidan Murmushi ne yasubuce mata cikin farin ciki sai ta girgiza kai kawai. Muryar Hajiya ce ke furta itama Inaya kamar akwai nata hadin anan dan naji wadanchan ja'iran na maganar wai akalli Inayah da Abdullahi sun dace sun zata banji su ba murmushi dukkaninsu sukayi suna furta Allah yatabbatar da Alkhairi acikin wannan zur'i a tasu Ameeen nikam nace harda mu...

Muryar hajiya ce takara furta da yanzu takwarata NORAH tana duniya da harda ita sai a had'ata da bak'in likitan turai Ammar take nufi haka take cemasa Shikuma Aj bak'in likita.

A hankali takara furtawa cikin sanyin jikin da yasameta Allah yajik'anki da rahama Sadiyaa keda iyayenki,Dukkaninsu suka Amsa cikin yanayin damuwa,sannan suka cigaba da Firarsu har zuwa lokacin da sarki Ali yadawo shida Husnat bayan fitar su falon.
"Inayah ce ke harara su Sumy taana furta gulmaAjali in ba'ayiba a mutu tana mik'ewa daga zaunen datake kan dinning suma mikewar sukayi suna dariya k'asa k'asa suna mata gwalo,falon dukkaninsu sukayi suka jone dasu hajiya aka cigaba da firar yaushe gamo wanda hardasu mahir dasuka fito yanzu aka cigaba dasu.

 A Mafarki Nasanta
Daga Alkalamin Fa'eeh BG
FIRSTLADY

©°••••••••••••••••••••••••••••••••••°©

INDIA MUMBAI
AMDAVAD

Amdavad unguwace Babba tana d'ai daga cikin manyan unguwanni agarin mumbai kasancewar ta tara manyan masu muk'aman gwamnati masu fd'a aji.Babban gida ne wanda yake flat katon gate ne golden inda naga wata mota ta shara ro da gudu tana buga horn mai gadin dake gadin gate d'in ne ya wangale mata gate din inda motar batayi tsinke ako ina ba sai a parking space na gidan ko dai daita parking d'in motar ba'ayi ba wata kyakkyawar yarinya ce yar kimanin shekara goma cikin shigar jeans da t shirt masu kyau ta fito da gudu a bayan motar tana kuka,tana nufar kofar dazata sadaka da babban falon gidan dasauri itama wata yar matashiyar budurwa wadda

bazata wuce 16yrs ba ta gaban motar a extra seat tana k'wala kiran Lubna! Lubna! Amma ina yarinyar tuni yarinyar ta shige cikin falon.

"Ziyadah k'yaleta kawai naji an fad'a daga bayanta inji yaron da yafito a driver seat shima dai kyakkyawan yarone fari tasa kamar dai yarinyar da aka kira da ziyadah da kuma Lubna,shima dai bazai wuce 16yrs kamar ziyadah inaga yan biyu domin kamar su daya hatta tsawon su sai dai banbancin shi ya d'an fita zama Babba saboda Banbancin jinsi.
Juyo tayi cikin yar damuwa ta furta Ziyad kasan fa halin yarinyar chan yanzu zata iya zuwa tagayawa Appah da Aunty laila karya da gaskiya yadda ranta yake bace din nan, yaron da takira Ziyad ne shima A hankali ya furta manta da ita kawai twin sis ai nasan Dukkanin su sauraren ta kawai zasu yi tunda sun san Lubna da karauniy,kuma ma ta tafi tafad'i fad'a ne kawai Appah zaiyi mukam babu ta yarda za'ayi mu yarda tabi mutumin da bata sanshi ba muma bamu sansa ba,bamu tab'a ganinsa ba sai yau.Har sun fara tafiya Ziyadah tace kaga tasa mun manta ma da icce cream namu amota juyawa tayi dasauri tabude bayan motar tad'auko wasu hadaddun shoprite bags sannan ta rufe motar.

Sallamar su ce wata matashiyar kyakkyawar mata da shekarunta baza wuce talatin da biyar ba fara tass da ita kamar balaaraba,gaidata sukayi da yaren indiyanci inda itama ta amsa musu da yaren sannaan ta musu sannu da zuwa.

Tambayar ta sukayi ina lubna bayan sun zazzauna aka tafaren falon dayasha kayan armashi komai na falon milky and white colour manyan hotuna ne makale akaton falon da fuskar wani farin dattijo wanda shima dai bazai wuce 57yrs ba a hoton shida wannana kykkyawar matar tare da ziyada da ziyad agefe da gefensu sai kuma lubna dake zaune ak'afafun tsohon dakuma wani karamin hoto na zane wanda ke d'auke da wata itama kyakkyawar yarinya yar shekara daya duk da azane ne amma duk tafi su ziyad kyau lubna ce mai d'an kama da ita ma,rik'e a hannun kyakkaywar matar nan,yarinyar na murmushi a hoton gwanin burgewa a happy family wanda dukkaninsu suma murmushin sukayi,sai nasu kowa shikad'ai,sai na zanen yarinyar kuma wanda ahoton bazata wuce shekara daya ba da yan watanni ita kad'ai hotunann dan duk nata sunfi yawa wani tana rarrafe wani tana dariya wani tana rarrafe,wani kuma ta wangale d'an karamin bakinta ta had'a hannayenta Alamun tafi gwanin burgewa....

Muryar ziyad ce tadawo dani daga kallon tsaf din danake yiwa hotunan yarinyar mai saurin shiga rai,Anty laila ina Appa? Murmushi kyakkaywar matar dasuka kira Aunty laila da alama dai mahaifiyar su ce,A hankali cikin cikin murmushi ta furta yana nan yana bedroom dinsa naga lubnar dakuke tambaya tashigo tana kuka mai kuka mata?kallon juna sukayi tsakanin ziyad da ziyaada suna masu sunne kansu kasa A hankali ta matso garesu ta zauna garesu ta zauna atsakanin su tana mai sanya hannayen ta ta rike nasu cikin sanyinta ta furta kugayamun zan fahimceku kunji "ya"yana,muryar ziyad ce cikin d'an damuwa ya furta Aunty laila ina lubna take tana gurin Appah ku tana shigowa chan tayi tsinke tabasu amsa ziyad yakara furta kinga Aunty laila sai da kikace kar mufita yau mubar tafiyar nan sai gobe saturday,Amma wacchan uwar rigimar ta matsa sai da muka fita,Uhmm Aunty Laila ta tace tana kara fadar na sani kufito direct kufad'a kugayamun ziyadah,ziyad sai yan kwane kwane yakeyi,Ahankali ziyada tafara bata labarin abunda yafaru bayan fitarsu siyen icce cream din..Maimaita maganar kawai Anty laila keyi aranta har inda ziyada take furta AUnty laila yana kama da didinmu fa harda muma sai dai shi chocolate skin garesa kuma shima baki ga yadda ya rike lubna ba kamar kar yasaketa....✍✍

ko wane ne wannan da Lubna ta lik'e??
Su kuma wayen nan daga ina ????

Chakwakiya to bari dai mubi yarima musha kid'a adai juri zuwa rafi...✍✍

Next pge tommorrow

Naji sauki sosai ina godiya da Addu'o'inku wayen da suka nuna kulawa dama wayen da basu nuna ba,Allah yabar zumunci.Ameen ✍✍

pls Like share and comment...
[3/27, 10:05 PM] Fa'eehbg writer: □A MAFARKI NASANTA□
In my dream I know her
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

FIRSTLADY□

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

*Pen is migthier than the sword *

Free Book□

EPISODE1
PAGE36

TYPING□□□

<><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><><>

.....Koda muka zo inda yake rik'e da ita Baki ga yadda yake ta kallon mu ba har muka gaisa.. tambayar kanta ta k'ara yi Shin wane ne wannan wanda yake kama da Norah d'inta da kuma lubna wanda har lubna zata iya kiranshi da BAYYA Indian lang,(yaya) har take son sai yakaita gurin DIDIN SU(DIDI indian lang YAYA MACE) da ahoto kad'ai taganta ta tab'a ganinta,Muryar kyakkyawan tsohon ce take ratsa tsakiyar falon inda yake furta meyasa kuka k'i barinta ta bishi?,D'ago manyan idanun su sukayi irin na mahaifiyarsu har ita Anty laila d'in suka kallonsa dan son tabbatar da indagaske yakeyin maganar dan sun san Appah yana yawan goyawa lubna baya..

Zama yayi A falon tare da Lubna da ke ta tsiyayar da hawayenta yayi lallashi har ya gaji tun bayan shigar ta bedroom nasa d'in .akan d'ai daga cikin manyan rugs d'in falon ya zauna kara jawota yayi jikinsa ya rungume yana shafa lallausar sumar kanta data sha gyara ba,ayi kitso ba kamar dai yadda indiyawa keyi.

Murmushi kawai Aunty Laila tayi tana mai tasowa daga kujerar da take ita dasu ziyad,hannu tasanya bayan ta zauna a gefan Lubnah dake hawaye har yanZu ta rik'o hannunta tana furta "Nima haka nace musu meyasa basu barta tabi ya" y"anta ba tana yin maganar tana kallon Lubna me matso hawaye harda na dole..."Ko zai kaita gurin didinta,Murmushi tsohon yayi afakaice,har dasu ziyad ma Aunty Laila ce tacigaba da magana,Yan zu ke Lubna baby in inbanda ke ya za,ayi ki gane didinku wadda a zane kad'ai kika santa kika tab'a ganinta tana murmushi kuma har kika iya yarda yana tare da didinku,didinku da take Nigeria,Dasauri Lubna ta bud'a baki Tana Furta Allah Aunty Laila nikam na yarda dashi tana maganar cikin sakalci dagani kasan yarinyar akwai wayau "ai shima yana kama da mutanen kasar, Aunty black ne fa shima ni shiyasa ma nak'ara lak'esa ai dan ya tabbatar mun zai kaini gunta tunda yasanta baki gansa ba fa Aunty Laila wallahi kamar sa da didin sosai yakeyi Amma shine su Aunty ziyadah suka hanani binsa da yanzu naga didi na ni na matsu naganta.... kuka Ne yakara kubce mata bayan gama furucinta na karshe.

Sukam su ziyad sunyi zugum suna kallon mahaifiyar tasu da kanwar tasu jin yadda take ta zaro zance kamar an rera shi acikin kanta,jin mahaifiyartasu tana lallashinta Lubna din ne yasanya ziyad furtawa lubna ai sai ki shirya Gobe ma sai mukai ki in Appah ya yarda ya furta hakan ne ganin signal d'in da Appah yamasa domin yasan hakan ne kawai zai kashe wutar domin kuwa ya k'agu yaji komai gun Aunty Laila domin haka kawai tun fara bayanin na Lubna wanda achan duk bata masa shi ba yaji gabansa yana mugun faduwa hankalinsa ya dugunzuma gaba d'aya..

Ai ko da jin furucin ziyad take lubna ta share guntun hawayen ta wanda har yafara kafewa cikin farin ciki ta kalli Appah kallon bani AMsa kai yad'aga mata shima cikin murmushi dukkaninsu murmushi sukayi.

Bayan samun saukowar tane suka wuce nasu dakin itada ziyada don yin fresh up shima ziyadah ya wuce nasa dake farkon nasu.

©°••°©

A falo kuwa Bayan wucewar nasu ne Aunty Laila takamo hannun mijinta dan son tabbatar da yanayin da yashiga A hankali ta furta ABBAN NORAH !!!!
D'ago rinannun idanuwansa yayi wayenda suka sauya tun bayan da aka ambaci nigeria yaji wani k'olon mashi yachaki zuciyarsa na bakin ciki,da kuma yana yin tausayin norah da yazame musu jiki akoda yaushe.

A hankali itama Aunty Laila ganin yanayin nasa sai taji hawaye sun taru a idonta natausayin tilon yarsu dasu kansu basu san a ina take ba,a wani hali take sai dai hope dasuke dashi kasancewarsu iyaye suna fatan ace yarsu lafiya lau take, cikin gargada muryar kuka ta k'ara furta Abban Norah lokaci yayi da zamu bayyanar da kanmu ga ahalinnmu lubna tana son ganin ahalinta haka ma su ziyad wayenda ma suka fita wayau ada mun boye musu norah amatsayin yar uwarsu da muka fahimci hakan bai da amfani munsanar musu matsayinta agaresu duk da bakomai muka sanar musu ba, ni ina ji ajiki na wannan wanda Lubna suka gani jinin mu ne.

Dasauri Appah yak'ara d'ago rinannun idanunsa cikin razanar jin furucin matar tasa,kai ta d'aga masa cikin tabbatarwa,' wanda su Lubna suka gani jininsu ne to wanene wannan kenan?nanata kalmar yayi wurin sau uku ko fiye ma daga karshe babu mai bashi amsa,A hankali Aunty Laila ta bashi labarin dasu ziyad suka bata,ganin shock din da yashiga yahasa yin wani motsi sannan takara masa da wanda Lubna tafadi yanzu wanda ta san hardashi ne yasanya kansa yin zafi damuwar

ta mishi Yawa ganin lubna kiri kiri ta nuna tana son ganin yar uwarta wanda sauran maganar tata duk shirme yadauketa a farko sai yanzu da aka bude masa komai....

Kallonta yakeyi kamar yasamu camera bako kyaftawa cikin shock din da k'ara shigarsa,bayan na farkon da yashigesa tun lokacin da tafara basa labarin maganganun ne ke dawo masa akai kamar gabansa akayi komai hango yaron yakeyi a idanunsa,musamman inda tace sunce yana kama da Lubna da Norah mamaki ne yak'ara kamasa sosai yau tsawon shekara talatin da "yan kai basu tare da yan uwansu akan zaluncin wasu azzaluman mutane suna ta b'oyon kansu a wannan k'asa yau gashi rana daya Allah zai nuna nashi iko akansu dama mutanen dake kokarin b'oye su ga ahalin nasu wanda basu san dalilinsu ba nayin hakan duk da taimakon da suka musu na farko wanda kuma su shaida ne ba mutanen Ba Azzalumai bane na kirki ne.

A hankali cikin wani farin ciki da ya mamaye zuciyarsa ya furta tabbas wannan wanda suka gani bakowa ba ne face jinin.....

Yaya Aliyu!!!!!!!!!!! Ne

Dan tunda suka ce wanda sukagani ba fari bane tabbas daga tsatson d'an uwana ne domin shine baki acikin mu,sannan in na chan ka Ammar ne suka gani domin shine mai irin fatar yaya,dan mahir fata nace zance ko taki sai kuma jaririyar da muka bar ta aciki ita bamu san kalar taba.....

Yau yaji labarin da yamasa dadi tun bayan na norah din,Kurumm yana Cikin maganar dariya ta subuce masa hadi da murmushi harda guntun hawayen da yadade baiyi ba na hango nesar su ta matso kusa mahaifiyarsa yake so yagani ruwa ajallo yana begen yaga ahalinsu a haka ma shidayake namiji mai karfaffiyar zuciya inaga Aunty Laila wadda kullum sai tayi kuka aboye bakowa ta kwallafa rai akan son gani ba sai yar ta nora wadda bata san a ina take ba tadai san tana cikin nigeria...

Allah sarki uwa mai dad'i
Allah yasaka ma iyayen mu da aljannar fiddausi.Ameen!

Itama Aunty Laila dariyar take yi had'i da murmushi na farinciki musamman da taga yana yin mijin nata yau da yafara komawa asalin walwalarsa,ikon Allah take ta nanatawa aranta kenan Ammar d'inta ne suka gani yau sai kuma tayi murmshin ta mai kyau tana kasa boye farin cikinta itama....

A hankali ta furta " Allah sarki Norah ko a wane hali take yanzu yata girma shekara ishirin da d'ai da yan watanni ai nasan yanzu duk inda take sun mata Aure takai karshen maganar cikin d'an sanyin jiki yadda ta kwallafa rai da norah sai gashi ashe batare zasu rayu ba kaddara ta rabasu..

Muryar Appah ce ke magana yana furta"wannan bawan Allahn ya tabbatar muna da tana hannun kirki ni nayarda dashi domin ke kan ki shaida ce da taimakon Allah da taimakon sa muke rayuwa to dan haka karki saka damuwa aranki kinji oum norah da nur yakai karshen maganr da yin murmushi itama murmushin tayi cikin farin cikin datakara tsintar kanta jin yahada harda sunan Ammar wanda Unni ke kiransa dashi sai kuma ita a wasu lokuttan.

Cigaba da magana yayi "kuma da ace an mata Aure da ya sanar muna fatana kawai Allah yakara mata lafiya,ya tsare muna ita..Kuma ya bayyanar muna da Autan maza

kafin mu koma nigeria ko don farin cikin hajiya yadawwama,kuma ya tonawa wayenda suke da hannu gurin cutar damu sukayi sanadiyyar rabamu da ahalin mu kasar mu,Ameen Aunty Laila ta Amsa.

Fitowar su ziyada ne da lubna sun chanja kaya izuwa na hausa Atamfa chiganvy jaa da bak'i dogayen riguna A shape sun masu kyau gwanin burgewa,da veil baki masha Allah kamar yan nigeria masu zama acikinta,shima ziyad yafito tsaff cikin shigar maroon colour yadi mai taushi harda hular zannan bukar bak'a mai daukar ido kamar wnda zaije gasar kyau.Dama duk ran friday shigar mu ta hausawa sukeyi saboda yadda iyayen nasu suka sabar musu Masha Allah Aunty Laila ta furta tana mai k'ara gyara ma lubna d'aurin ta irin na zahra buhari wanda ziyada tamata wanda Aunty Laila takoyamata.

Shaf shaf shima Appah yaje yashiryo cikin yadi maroon irin na ziyad,suka fice zuwa masallaci dan gabatar da sallar juma,a cikin jam'i har da ziyada ma Aunty Laila kad'ai aka bari tana cigaba da aikin gidan da bawani aiki bane girki ne kad'ai Sai yan gyare gyare dan ko ina tsaf kamar ba yara agidan.

FIRSTLADY

AMDAVAD
> >>>>>>>>> >>>>>
Yau indian dishes ne agaban Amma shi yakasa tab'a koda wani gefe na abin cin dake kan dinning din,tandori chicken ne da pani puri sai kuma pakora sai tashin kamshi sukeyi yaushi ne abunda kukunsu ya girka domin shine a list na girkin yau na rana,DR AJ ne yasanya pock da knife ya yanko tandori chicken sai turu ri takeyi na kamshi bakinsa yakai yana kallon Dr.AMMAR da tambayoyi abakinsa,d'auke kansa yayi daga kallon da yake masa,yadauki pani puri d'aya yakara cusawa a bakinsa yana mai furta "narasa gane maka tunda mukaje shoprite d'in nan har yanzu baka dawo dai dai ba kamar akwai abunda yayi shocking naka agurin,tun dazu fa abincin nan yake gaban ka Amma ko kad'an baka tab'a ba.D'ago Manyan idanunsa yayi masu cike da yanayi na bacci a lumshe yasauke akan Aj dake ta faman cusa pakora abakinsa.

A hankali kamar wanda akayiwa dole maganar cikin dan yatsinar fuska ya furta" yanzu idan nacemaka idan na fad'a maka naga yarinyar mafarki na zaka yadda.....Yakai karshen maganar cikin wani yanayi.

Ai Dasauri AJ yad'auki ruwa ya kora sanadiyyar shakewar da Ya fara da pani puri jin furucin na Dr.AMMAR,Kwalalo idanun sa yayi wanda har Dr.Ammar Sai da yayi dan guntun murmushi mai k'ara k'awata kyakkyawar fuskarsa ganin reaction din Aj.

A hankali yacigaba da magana cikin dakewa kamar wanda akayiwa dole yaa furta "mai kama da ita nagani sai dai wannan yarinyace dan bazata wuce ten yrs ba akalla kallonsa kawai Aj keyi kamar ya ga bakon halitta,cigaba da maganar sa yayi cikin natsuwa "kasan kuma dakyar yarinyar tasaki hannu na.....

Labari yafara bawa aj.....
Zan bisu in samo muku rahoton.....

Nima zan baku labarin in naga ruwan like da comment.

share pls
[3/27, 10:05 PM] Fa'eehbg writer: https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRInZ0yKim
Join my novel group for the new update✍✍

https://m.tiktok.com/h5/share/usr/6984456997898863621.html?_d=e8bi3m3l87dmll&sec_uid=MS4wLjABAAAAGOaScTEd7igAj6auum-Z_v0cxncjX7iFemXzcdWjbEL3FLsbTFXlRmOFLgVSMg1a&share_author_id=6984456997898863621&sharer_language=en&u_code=djg8gfjgkd6lbm

□A MAFARKI NASANTA□
In my dream I know her
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

BANYARDA ATAB'A MINI WANI B'ANGARE NA LITTAFI BA.INKUMA KIKAYI MINI GANGANCI NABARKI DA RABBA....

BAN YARDA A KARANTA MINI SHI AYOUTUBE BA SAI DA IZINI NA.

MASU TAMBAYAR COMPLETE BAN KAMMALA LABARIN BA YANZU NAKE TYPING....

Note editing...

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

*Penis migthier than the sword *

Free book□

EPISODE1
PAGE37

WANNAN PAGE NAKI NE SISTER AYEESHAT ABDULLAHI MUHAMMAD□ KIYI YADDA KIKE SO DASHI

TYPING□□□

••

.....Bayan nabaroka cikin shoprite din na fito in yi picking call bayan nagama amsa call din injuyo kawai sai naci karo da yarinya tsaye abaya na tana ta sakar mini

murmushi,ida juyo wa ta kenan,A hankali yarinyar ta furta mun cikin harshen india bayya! cikin murmushi. ganin yanayin yarinyar yasaka nima nasaki fuskata wanda har zuwa lokacin mamaki da alajabi bai sake ni ba naganin kamannin yarinyar da nake yawan mafarkinta..

"Yaya zaka kaini gurin didin mu yanzu koh" da ta furta shine yasanya ni k'ara saita natsuwa ta.Kai kad'ai na d'aga mata badan nasan wacece yayar tasu ba,muna nan tsaye tana zuba mini surutu sai ga wasu samari mace da namiji inaga dai twins ne su sun doso inda muke suma kuma baka ga yadda suke kallo na ba kamar ydda nake kallonsu wanda ninasan kalllon rashin sani ne suke mini gani na tare da kanwar ta su da ko sunan ta bansani Ba dan naga suna kama da yarinyar Sosai.

Gaisawa mukayi dasu Sannan suka nemi in basu kanwar tasu A hankali nazare hannu na dake cikin nata wanda ta rike gamm,rigima suka sha da ita dan tadage sai tabini nakaita gurin didin ta harda kuka sai da na lallasheta sannan nace taje zamu hadu gobe in kaita Amma duk da haka sai da namijin ya fisgi hannun ta tana kuka tana waige na harsuka sanyata bayan seat suka tada motar su,d'an nisawa yayi sannan ya furta a hankali cikin wani kalar sanyi "kaina ne ya daure shiyasa nakasa komawa cikin shoprite din
Yakai karshen maganar cikin sauke katuwar ajiyar zuciya na doguwar maganar da yayi.

Kallonsa kawai Aj keyi har yadauki ruwa ya tsiyaya yakai abakinsa",yau nakara shaida son da kakeyiwa wannan yarinyar mai yawa ne,ace har ka iya kallon yarinya yar shekara goma siffarta to ko dai yar shekarar goman zaka Aura yakai karshen maganar cikin kanne ido d'aya "kaga sai muyi rainota...Yakai karshen maganar yana sakin karamar dariyar shakiyyanci aj ke furucin.

Hararsa Ammar yayi sai kuma yasaki dan karamin murmushi yana girgiza kansa na furucin Dr.Aj yana mai yankar tandori chiken A hankali yake taunar naman kazar bayan ya saka bakinsa Tare da lumshe manyan idanunsa da yake jin sun dan masa nauyi kasancewar rashin samun isasshen bacci da baisamu ba jiya a asibiti.

••
MUJE ZUWA

Tun alokacin kusan kullum sai Dr.Ammar ya tsiri zuwa shoprite din ko zai ga mai kama da su lubna sai da yashare kwana goma bai hadu dasu ba sai arana ta sha d'aya ne ya hangi lubna itada ziyadah hannunsu rike da juna amma ita sai waige waige takeyi kamar tana neman wani abu kamar ance ta waigo daga gefen da yake tsaye ya rungume hannayensa.

'cikin masifaffen gudu ta zare hannunta cikin na ziyadah tana zuwa ta fad'a jikinsa ta rungume sa sai kuma tasaki kuka itakam ziyada sai ikon Allah take kallo,Ajiyar zuciya yasauke a hankali kamar wanda yaron da yake neman uwarsa sai da yaci wuya yaganta sannan ahankali yacigaba da lallashinta yana shafa sumar kanta."Bayya"ta furta cikin sanyi da dariya mai nuna farin cikinta.dama lubna tasha wa Kowa kai gidan su na rashin kara had'uwa dashi da batayi ba kusan kwana uku kenan duk aka tadosu makaranta sai sun kawota gurin Amma sai dai har su bar gurin basa ganinsa saboda suna shan ban ban wurin wani lokaci da rana yake zuwa sometimes kuma da dare su kuma bayan antaso skull ne.

A hankali cikin kara kawata fuskarsa da murmushi ya furta can I know ur your Name cikin harshen india suke maganar "LUBNA BABY " ta furta aunty nace mini haka Appah ma nace mini yaya ziyad ne da ziyadah kadai basa cemun baby murmushi

yakarayi sannan yashafa kanta yana dagota daga rungumar da yayi mata ayanzu kan kafadarsa.

Itama ziyada zuwa tayi suka gaisa dashi cikin sakin fuska a hankali tunda yaji sunanta gurin lubna yafurtawa ziyada ya schl Lafiya lau ta amsa mishi cikin girmamawa duk da mamakin jin sunanta abakinsa.

Tattakawa yayi dasu har inda rantsasiyar motar tasa take kirar Benz kamfanin lenovo dan bai fitowa da ko daya daga yaransu inzai zo nan,front seat ya bude yajawo wata katuwar teddy pink colour da tacika extra seat na motar an rubuta mata baby Akan band mai kamar katifa din dake kan ta da ruwan gold.Mikawa lubna yayi cikin sakar mata murmushinsa.Ba lubna ba hatta ziyadah da ziyad da fitowar sa harabar wurin yahango su shine ya shima yafito a motar da yake zaune teddyn ta burgesu ko ni mai kwaso rahoto ta burgeni matuka.

Farincikin lubna yakasa boyuwa tsalle kadai takeyi a wurin bayan takara rungumesa tana furta thanks you Bayya.

Bayan motar yakara bud'ewa ahankali ya fiddo da wasu big bags na shoprite din masu kyau d'auke da hoton chocolate,wanda kusan kullum sai yasayesu sai dai yakyautar inbai ga su lubna ba teddyn ce dai guda tun da yasaye ta saboda tamasa kyau sai ya ajiyewa lubna.Mikawa ziyadah ledodin yayi yana furta keda twins brother naki daya, daya kuma na lubna baby ne ita kadai tsalle ta k'ara dakawa cikin farin cikin wannan kyautar da tasamu ga trddyn ta rungume ajikin ta,Sai ma tamanta da maganar kaita gun didinta.

Godiya ziyad yamasa sosai bayan sun gaiisa sannan sukayi sallama dashi har inda motarsu take Har suka shiga mota tana waigen sa tana daga masa hannu shima yana daga maata har ziyad yatada mota ta dakatar dashi da gudu ta fito da tap dinta ta buga game da karatu kirar samsung ahannu ta inda ake saka numbers tashiga duk da wayan ba mai simcard bace ta furta

"Bayya sanya mun numbanka kar ka kara guduwa baka kaini gurin didi bah"

Murmushi kadai yayi yakarb'i tap din rubuta mata nine digit nasa sannan tayi saving da bayya tana rugawa da gudu tashiga mota ta rufe tana d'aga masa hannu har kanta ta ke leko wa ta glass tana sakar masa murmushi...

Sai da yabar ganin kurarsu sannan yayi murmushi yanajin kansa cikin farin ciki marar misaltuwa naganin lubna hardasu ziyad ma akaro na biyu..

Shima daukar motar sa yayi sai gida dama ga abunda yakawo sa kuma yasamu.

<<<<<<<<<<<<<<<< <<<<<<<<<<<<<<<<
□FA'EEH BG□
FIRSTLADY□

shigowarsa baiyi tsinke ko ina ba sai akan katon dinning space nasu a hankali yasanya hannunsa ya wanke akan sink,sannan yazauna a d'ai daga cikin manyan hadaddun dining chairs din dake dinning area din masu kyau
••Butter chichken yajawo dake daure da raping sheet mai kyalli ya bud'e a hankali kamshin hadin hadaddiyar kazar da taji hadi na musamman yabugi hancinsa ne yasanya sa lumshe manyan idanunsa masu haske,A hankali ya yago kazar da pock

da knife yakai bakinsa ya tauna a hankali harda kad'a kai saboda yadda d'and'anon da yagame bakinsa,Bhulpuri yajawo dake cikin katuwar food flask mai kyau ya zuba bakinsa yasanya yana taunawa ahankali Dr Aj da yanzu yazauna kan dinning din ne ya furta" acicin banza tun d'azu ina nan ina jiranka shine daga zuwan ka kazame nan maimakon kaje kakirani ko kasanya sabirkhan Ya kirani shiru bai tanka masa ba har sai da yaji cikin sa ya dauka domin Ammar bai wasa da cikinsa ko kad'an,ruwa yasha da lemu sannan yayi hamdala tare da mikewa yana furta cikin arrogant voice nasa" kanka akeji uban mita"yakai karshen maganar yana sakin kayataccen murmushinsa irin wanda ke kular da aj domin smiling ne mai ma,anoni da yawa aciki harda rainin hankali upstair ya wucewar sa dan yin wanka.

yau aj ya ga farin ciki akan fuskar Dr. Ammar kuma yana da tabbacin cewa ya had'u da yarinyar da yake ta zagayen fita yasake gani,murmushi shima yayi kawai yana cigaba da cin abincinsa.

NIGERIA ZAMFARA
GUSAU
Ta sambo!!!!

kuyi manage ba yawa.
[3/27, 10:05 PM] Fa'eehbg writer: IDAN KINA SON KARANTA LITTAFIN AMAFARKI NASANTA ASAUKAKE KAWAI KIYI JOINING LINK DIN GROUP D'INA
https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

A MAFARKI NASANTA
In my dream I know her
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Penis migthier than the sword *

Free book

EPISODE1
PAGE38

Kema ganaki kawar arziki wannan page din sadaukar wa ne agareki siddiqa muhammad na'ibiluv u lodi lodi

TYPING□□□

<<<<<<<< < <<<<<<<< < <<<<<<<<<<<<

Khairiyyah d'iyar fulani ce tashigo sashen unni dan gaida hajiya, bayan sun gaisa da unni da mahir da ya gaida ita sannan ta ke tambayar unni ina hajiyar unni ce ta furta "ai takoma sashenta tun shekaranjiya,sallamar su nisa ce da sumy,inayah takatse maganar da Khairiyyah ke son yi

'ina wuni mama khairiyyah dukkaninsu suka had'a baki gurin gaisheta cikin sakin fuska ta karba musu da lafiya lau aa inayan dija harda ke hajiya tazo kenan

"eeh "inayah ta furta cikin murmushi tana mai sunne kan ta kasa.
" ya kuka baro dija din lafiya take koh?Mama khairiyya takara furtawa

"lafiya lau"Inaya ta amsa mata.

Allah sarki yara duk sun girma mama khairiyya ta furta bayan wucewarsu daga falon,inda shima mahir tuni yabar falon.

'Hawaye ne shar suka tsiyayo abisa idanunta gwanin tausayi lallashinta unni tayi cikin tausayin rayuwar da mama khairiyyar ta tsinci kanta ciki,anan ta sanar mata ai mijinta yanzu yamata saki daya kuma dama ita kanta ta gaji da hakurin da takeyi.

Hakuri unni takara bata tare da kara lallashinta...

Kukane ya kubce mata,cikin ruwan hawaye da shesshekar kuka take furta duk wanda yarabani da hamma Abdul rashid bazan tab'a yafe masa ba domin nasan farraqu akayi mani dashi,inaji ajiki na komai da akayi masa sanadi nane.....

'Kukane yaci karfin ta, cikin shesshekar kukan tane taci gaba da magana Allah yabayyanar muna da kai, Allah kaine kasan Abunda yake B'oye Allah kakawo muna sauyin Al amurra cikin gaggawa takai karshen maganar cikin k'ara sakin wani mahaukacin kuka tana jin kamar yanzu komai ya faru na rabuwarta da masoyinta nata.

Itakanta unni kukan takeyi cikin jin zafin alamurran dasuka shud'e musu wayend ke wuyar mantawa azukatansu duk da koma mene ne Allah ya riga ya rubuta sa ne Bawa baya taba wuce kaddararsa duk zille zillensa.

Abunda yafaru chan baya .....

Tun bayan dawaowar Abdul rashid daga sudan bayan ya had'o degreen sa akasar sudan na fannin likitanci .

Soyayya mai tsanani ta shiga tsakaninsa da ummulkhairi(mama khairiyyah)yar wajen fulani wadda take warinsu unni ce auta ga fulani...

Soyayyyarsu gwanin burgewa Amma fulani batason had'in nasu,sai da sukayi makarkashiya itada muhammad (malan)suka raba mama khairiyya da Abdul rashid domin cire masa ita akayi a zuciyarsa gaba d'aya wanda suka je a wurin wani katoton boka yayi musu aikin aka cire masa ita azuciya.

Ahaka mama khairiyya sai da tayi jinya ganin ba itace agabansa ba,kuma fulani ta gargade ta da karta k'ara kulashi tunda yabarsonta ya yaudareta, Bayan rabuwarsu sai kuma aka wayi gari an nemi Abdul rashid Ba'a gansa ba har ciigiyarsa anbada a kafafen sadarwa ba 'a sameshi ba babu wani labarinsa domin kamar an masa kurciya wannan kenan....

Shigowar sarki Ali ce tasanya dukkaninsu yin shiru Bayan lallashin su da yayi da basu baki wanda shima karfin hali ne kadai yayi kasancewarsa namiji,Fira suka d'an fara tab'awa dan kawar da damuwar da ta addabi kowannensu .....

Jakunkunansu suka fito dasu suduka ukun unni ce ta lura dasu A hankali bayan kare musu kallo ta furta"kai lafiya kuka fito da bags haka "

Ehh unni gidan ummi zamu suka hada baki wurin bata amsa "kudawa ,Kuma kun ma hajiya sallama ne " takara tambaya dan taga kamar ma sun dade da shirya tafiyar duk da ba wani nesa bane.

Ehh ai daga sashen ta muka fito d'azu kuma su yaya Abdallah ne zasu kaimu.

Mahir da shigowarsa falon kenan kunnunwansa suka jiye masa maganar da nisa da sumy suka furtawa Unni
ai dasauri yakoma inda yayi shigewarsa mota yayi zamansa batare da su Abdallah sun lura dashi ba

Sallama sukayi ma kowa dake falon sannnan suka juya suka fice bayan yimusu Addu'ar sauka lafiya dasukaYi.

Direct compound din gidan suka fito basu doshi ko ina ba sai inda Abdallah da yusuf da yake gaban motar sukayi parking motarsu .

mahir da yaga dai alamar shiga motar sumy zatayi yayi kaza zam ya fito cikin motar yana kwala ma Nisa kira
Dukkaninsu sunyi mamaki domin basu yi tsammanin yana cikin motar ba.

"Gani yaya ta furta bayan isowarta inda yake tsaye agaban motarsa cikin daure fuska.

"bake naki raba " ya fad'a cikin da'ure fuska,sakake nisa tayi tana kallonsa jin furucinsa

Cikin jin haushin rainin hankalin na mahir ta furta " NISA fa naji ka kira yaya irin ma fa kiran nan na mafarauta"
Cikinta yayo zai kai mata rankwashi ta kwasa aguje tana tikar dariya ...

"Sumy yaya nakira" sumy da har ta zauna ne tafito jin furucin nisa,BAyan fitar Sumy nisa ta furta "Yya Abdallah kumuje kawai,zai kawota daga baya sak'o zai bata,Abdallah da yusuf murmushi kad'ai sukayi Abdallah cikin zuciyarsa yafurta no wonder yanzu nagane murmushi yakarayi sannna yafigi motar suna ficewa daga gidan bayan ma'aikatan dake tsaron katon gate din sun wangale musu katon gate din....

Sumy kuwa ganin motar ta wuce ne kuma gashi tayi tsayin kusan minti uku baice mata komai ba abun sai yafara sanyata jin haushi,cikin tsiwar da bata san tana da ita ba,ta furta"wai yaya mahir meye haka har sun wuce fa"

D'ago idanunta ta yi taga yana kallonta ko k'aftawa baya yi sai taga yakoma mata Dr.Ammar Domin dama dashi yake kama sosai samun kanta tayi da k'ara natsuwa bayan hango kamannin ya" yan nasu marar son wargi da tsare gida.

Bayan yagama k'are mata kallo ya furta shiga mota cikin turo bakinta ta bud'e k'ofar baya tashiga har ta gyara tazaman ta ta ga yana tasakar mata harara wadda tasan dalilinta dole ta dawo gaba "Better ya furta sannan ya rufo kofar yana yin reverse na motar suka fice gidan gaba d'aya bayan wangale musu gate din.

BUG
A b'angaren su Halee kuwa yau ta tashi da jikin ciwon kan nata yatashi har cikin ido ko iya bud'e idanunta bata yi,Baba Adee Khady ta kira tasanar masa ta hanyar wayar makota dole ya baro gurin aikinsa.Suka shirya zuwa asibitin Babban Birnin tarayya waton federal medical center gusau An karb'e su cikin mutun tawa sai dai bayan binciken jikin Haleen da yan awannni Baba Adee yaji abunda ya girgizasa tabbas likitoci sun sanar masa ciwon Halee daga cikin hypothalamus dinta yake matsala ce babba domin sai anyi aiki ancire jinin da yake acikin kwakwalwarta wanda jinin ya kume mata sanadiyyar wata buguwa da tatab'a yi likitota sun sanar masa da aikin nata yana buk'atar milion goma dan ceto ranta dan idan ba'ayi saurin cire mata wannan jinin ba da yake yawan sanyata ciwon kai zai kai inda ba'aso kuma hakan ne ba,a so domin zai iya zama sanadiyyar zamowarta psycho mai tabin hankali ta samu mental problem Wanda baida ranar warkewa sai ikon rabba.

Zufane ke ta ketowa Baba Adee Bayan jin bayanin likitocin,Shi d'an talakansa bawan Allah ina zai samu miliyan goma rana tsaka inbadai satar su zaije yayi ba shi bawata kadarar arziki ba tunani ne barkatai ke shigowa kansa awannan lokaci cikin tashin hankali da rashin madafa.

D'ai daga cikin matasan likitotan ne yakira Baba Adee A office dinsa inda yafurta"Baba kozaka iya samu na office dina yanzu inaso zamuyi magana" kai Baba Adee kawai ya iya d'aga masa cikin rashin karfin jiki domin shi kansa yashaida kafafunsa ne suka kaisa office din inda yake biye bayan matashin likitan.

Kujera yajama BAba Adee yana furta"Baba zauna ganin Baba Adee kamar baya cikin hayyacinsa.

cikin sanyin murya matashin likitan ya furta "karka damu kanka da yawa Baba Allah shi keyin komai duk bayanin da akayi maka kawai hasashe ne Amma Allah Ne mai Aiwatarwa in bai nufa zata sha wahala ba zaka ga cikin ikon Allah tayi rayuwarta batare da ko wace irin sifa ba ta alamar mental problem.
Ayanzu ma Baba Adee kai kad'ai ya iya d'aga masa kamar wanda ke d'aukar karatu cikin sagewar guiwa da mik'a wuya Ga ubangiji,Bayan jin maganar ta Dr.Din Inda yaji natsuwa tashigesa.

A hankali bayan yazauna ya cigaba da maganarsa Ni suna na Dr.Yusuf Janyau ana kirana Dr jy. zan taimaka maka yadda za'a yimata aiki cikin sauk'i batare da ko sisin kuba domin na fahimci ta shin hankalin da kashiga Baba na kud'in aikin da aka lissafa maka dakuma abunda zai faru idan ba'a dau mataki da wuri ba.
An gina wata Babbar asibiti ta taimakon Marassa karfi yanzu haka wayenda zasu rik'a asibitin basu cikin kasar nan suna INDIA .....

Achan suke aiki wanda nima achan nayi karatun Amma ba makaranta d'aya mukayi dasu ba inda su suka zabi aiki achan bayan gama karatun namu nikuma nazab'i kasata,duk da haka mukan d'an had'u idan taron dalibbai yatashi na nigeria ko na likitota gaba d'aya inada numban dayansu ta nigeria danshine muke shiri dashi sosai duk da dukkaninsu Abokainane.

In sha Allah da sun dawo nigeria zan kiraka in sanar dakai lokacin Anfara Aiki a asibitin,domin yanzu haka anfara daukar ma'aikata kaga da nasamu aiki achan shikenan ba matsala tunda dukkanin abunda za'a saya akwai shi a asibitin zan tsaya dayardar ubangiji domin tasamu lafiya..

Godiya Baba Adee yak'ara yi masa sosai cikin nuna farin cikinsa da wannan bayani na wannan likita,Cikin murmushi shima Dr.Aj ya furta bakomai Baba yiwa kaine.

Cikin sakin fuska Baba Adee ya furta yusuf sanya mun numbanka anan yana mai mika masa wayansa kirar tecno pop 3 murmushi dr yusuf yayi yakarb'i wayan yasaka numban wayansa sannan yayi dialing sai ga numban Baba Adee ta bayya akan wayar tasa kirar iphone 15 saving yayi da Baba,shima Bba Adee yayi saving da Dr Janyau musabaha suka kara yiwa juna sannan Baba Adee yakara yimasa godiya tare da kara saka masa Albarka..

Khady da Bba Adee yasanar mata da komai afarko ta shiga tashin hankali domin kuka tasanya cikin tausayin yar uwarta wadda ayanzu take kwance akan gadon asibiti cikin ciwo gwanin tausayi,sai daya ga tashin hankalin da tashiga yanason d'ara nasa sannan yasanar mata da dik bayanin da Dr. Janyau yayi masa,take itama ta wartsake cikin farin ciki tana mai sanya wa wannan likita albarka wanda bata sanshi ba A hankali takalli fuskar Halee da takara yin fayau kyakkyawar fuskar ta takara kyau na musammamn kasancewar yar ramar da d'anyi Allah yabaki lafiya yar uwata ta furta.....

Wasu alamomi da Dr.Yusuf yake nuna wa da kulawa a asibitin wurin jinyar Halee shizai tabbatar maka da abunda ke cikin zuciyarsa domin dukkanin Alamomin sa sun nuna son Halee yakeyi. Murna Sosai Bba Adee yayi dan ganin yaron yakasance mai mutunci shidama burinsa kenan Halee tasamu mijin Aure nagari ya aurar da ita ko tasamu salama domin zuciyarsa bata yarda da rikon Baba Asabe ba.

Kwanan su Halee shida aka basu discharge tare da magungunan dazatayi amfani dasu kafin asamu kud'in surgeryn nata.Tunda suka zo asibitin Bba Asabe bata leko ba ko aike, dangin Bba Adee da dama sunzo sunga Halee ciki harda iya da Bba mudi iyayensa da kannensa maza biyu Amma itakam Baba Asabe ko lek'e. wanda hakan bai wani damu Bba Adee ba domin ganin yadda Haleen ke samun kulawa agurin khady mai yin jinyar tata duk da iya taso abarta ta kula da ita....

nikam nace toh Allah ykyauta
Yasa mufi karfin zukatan mu.Ameen

Toh hwa😂 in muku ta hausar mu ta zamfaranci,ku k'ara gyara zama fans munkusa isa inda kuke so fa Haleen mu da alama fa tayi Saurayi ko ince mijin Aure ....

Kai da alama fa mutanen india sunkusa zuwa nigeria..... yeeeeee Can't wait □□□

Me kuke tunani game da soyayyar da Halee zata fara...

[3/27, 10:05 PM] Fa'eehbg writer: https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

□A MAFARKI NASANTA□
In my dream I know her
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

Wannan page naka ne Mahaifina□□taurarona Allah yakara maka tsawon rai Mai albarka tare da lafiya Mai inganci□□

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

*Pen*is migthier than the sword **

Free □

EPISODE1
PAGE39

TYPING□□□

Barkar ku da Shan ruwa fatan ansha ruwa lafiya,Allah yakarba muna ibadar mu

Special thanks goes to the members of A mafarki Nasanta fans group,yan Amana ta luv u Lodi Lodi😍□□

And Big thanks to my sincere people for the support you give me

Anty moon(the writer of abarmu da junanmu and mijin bahijja❤

Oum Amjad(the writer of Yan biyu)❤

My best readers

Yan Amana

Mode❤

Zarah Ibrahim❤
Siddiq Muhammad❤
Halimatu bashar Auki ❤
Fateema A bello♥
Ayeeshat Abdullahi❤

Ina alfahari daku sosai irin ba adadi nan

Fans□□□□□□□
Ina godiya sosai da Jirana da kukayi har natsawon makonni,
Wayenda suka kirani da ma wayenda basu kirani ba Ina godiya, kuyi hakuri banyi mentioned sunanku ba nayi hakan ne sbd Kar mucika page din namu da surutu Ina alfahari daku □

<<<<<<<< >>>>>>>>><<<>>>>>>>>>>>>

✍✍

B'angaren Mahir da Sumee kuwa har sun Kai gidan ummi
Sojojin Dake bakin gate din nan gidan na wangale musu gate babu wata fira tsakaninsu.

Inda Abdallah yayi parking tasa motar Shima ya parker tasa,lock yasanyawa motar ganin alamar sumy fita zatayi, kallonsa tayi cikin son sanin dalilin Saka lock din,.

Tsuke fuska yak'arayi ganin irin kallon da take masa.

Bayan kamar minti uku haka ya furta.. cikin gadara saura saura inkika shiga ciki ki sakarwa Abdallah fuska yakai karshen maganar yana cire lock din.

Kallonsa take da mamaki,Ba halin tambayar dalilin maganarsa ficewa tayi dasauri tana murmushi ita kad'ai bayan wani tunani da yashigo zuciyarta,kenan Yana kishinta inko akwai kishi akwai soyayya kenan Yana Sonta farin ciki ne ya mamaye ta kamar ta daka tsalle sai dai ba hali domin tana Jin idanunsa akanta..

Dakarun Sojojin Dake compound din gidan ne suke mata sannu da zuwa tana amsa musu cikin farinciki har wasu nad'an janta da wasa..

Shigewa cikin gidan tayi da gudu sai falo ta dakata,duka ta tarar dasu atsakiyar falon har mahaifin su colonel jabir Muhammad soja ,Wanda suke Kira (dady soja) suna yin dinner da yadawo gida bayan Yan watannin da ya dauka baya nan.

Duka d'agowa sukayi suna kallonta ganin yadda ta fado dakin fuskar ta sai blushing take Yi tare da sauke numfashi.

cin abincinsu suka cigaba dayi Dan dady soja baya wasa injisu 😆kunsan sojoji fa sakin fuska la la la la□in maku ta bakon balarabe✍

□ FA'EEHBG □
The first lady □□

<<<<< > >>>>>>>>>>>>>>>>>> <<<<<

Joining dinsu tayi cikin kame kame na yadda ta fado dakin suna cigaba da cin abin cinsu.

Bayan sun gama ne tayi ma Dady soja sannu da zuwa ya amsa mata cikin sakin fuska irin tasa.

Bayan wucewarsa daki ne suka cigaba da hirarsu.

ummi ce ta lura da mahir Dake chan tsaye agefen cushion tsayinsa ya rungume hannaye ya kafe sumy da eyes wadda keta zuba fira tana bada labarin su sury kawarta Yan class nasu.

'Murmushi Ummi tayi kawai tana girgiza kanta cikin dattako da sakin fuska ta furta "Ina yini Babana "?

'Sunnar da Kansa yayi Jin gaisuwar da ummi ta masa A hankali yatako cikin Jin nauyinta ya durkusa ya gaishe ta,cikin murmushi da kulawa ta amsa masa.

Manyan food flask din da har an maidasu dining inji Yan matan ne Ummi ta d'auko d'aya tana furta"Baba na nan za,a kawo maka Abincin ne ko anan zakaci kan dinning inyi saving Dinka"

''Nakoshi''Ummi ya furta cikin Jin kunya Dan haka kawai yau yake Jin kunyarta wadda Bai San dalilinta ba.

Nikam nace ba dole ba Maheer ka kama mata "yaa surukantaka wasa ce...duk da bamu tabbatar ba😀😀

Murmushi kawai Ummi tayi bayan gama sauraren sa ganin yadda yake sauke Kai kamar k'adangare.

Sallama sukayi ma ummi suka fice daga falon Yusuf da Abdallah,mahir ne Shima ya biyo su bayan yayima sumayya kallon zamu had'u Yana ficewarsa.

A compound d'in gidan ya had'u da Abdallah da Yusuf suna Jiran fitowarsa.

Musabaha sukayi cikin karrama juna Abdallah ne ya furta "tare zamu koma fa Maheer "

'Shek'e k'e mahir ke kallon sa bayan Jin furucinsa,sai Kuma Ahankali ya ya furta

 "ita motar da ka zo da ita fa"?

'Yusuf ne ya furta zan d'an je gidansu Uun Yana Dan susar keyarsa irin na shed'anar nan,dariya kawai mahir yayi
Yana furta " to sai ka dawo kagayar da ita"

Shima dariyar yayi Dan yagane abunda yake nufi sallama yamusu sannna yafice daga gidan.

A mota Abdallah ne yake d'an jan Maheer da fira duk da mahir baya amsawa sosai sbd haushin sa da Bai sake Saba har yasako zan cen da yakusa tarwatsa zuciyar mahir..

"Friend nifa nagani inaso tun tuni,d'aure fuska mahir yayi,Abdallah ne yacigaba da maganarsa

"Dan haka nikam zanje insanar wa sarki kafin ruwa su cinye ni,Gaban Maheer ne yafadi Wanda har sai da steering ya so kubce masa sai Kuma yayi ta maza ya furta

"Sai ka dawo"atakaice.
Cikin Kara d'aure fuska

Me Abdallah zaiyi inba dariya ba harda rike ciki domin dama yaga yadda steering yaso kufce masa ga Kuma amsar da yabasa..

'kagani ba harka hau Toni ba ita nake nufi ba,Inayah nake magana Akai Dan naga alama kazata da sumy nake Dan da alama ka zurma da yawa...

Farin ciki ne ya ziyarci mahir Mai yawa Wanda tun alokacin da yatabbar Abdallah ba yada wani feeling akan sumy sai yafara bata kulawa.

Soyayya Mai karfi ce ta barke atsakanin sumy da mahir,haka ma Abdallah da Inayah soyayyarsu suke Sha gwanin burgewa wadda har ta bayyana a idon kowa.

INDIA

Anty lailah da Appah sunyi farin ciki daganin kyautar da Ammar ya yiwa su Lubna fiye da tunanin Mai karatu,tun daga lokacin kusan kullum sai su Ziyad sun fita da Lubna domin su gana da Ammar.

Wata shakuwa ce tashiga tsakanin Ammar dasu Lubna,sai dai haryanzu Ammar Bai tab'a had'uwa dasu Appah ba.✍✍

Wassh hannu ✍☹☹

Mu had'u anext page
Muga saukar mutanen India may be agobe Nigeria zatayi manyan Baki
Can't wait □□□

Masu zuwa tarbon Baki ku shirya mu Isa Airport da wuri ayi landing□□ agabanmu□□

Ina Kuma labarin Halee ya ya take ?
□
Shin Baba Asabe taciga da muguntar ta?
Su waye iyayen Lubna ?
Shin Suma Yan Nigeria ne dagaske?

Ina labarin MISS MALINI ???
HMMMM kwamachala kenan inji bahaushe😆

In Sha Allah duk zaku samo amsar tambayoyinku Ahankali kudai cigaba da bibiyar alkalamina ✍✍

Allah yajikanki da rahama kakata yaar Baba☹Allah yasa Aljannace makomarki Allah yakarbi Bakuntarki,ya yalwanta makwancinki yakuma bamu guzurin ishemuku□□

Pls like,share and comment✍
[3/28, 12:02 AM] Fa'eehbg writer: https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dream
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

Allah yajikan iyayen mu wayenda suka Riga mu gidan gaskiya da rahama😭😭

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Pen*is migthier than the sword **

Free

EPISODE1
PAGE40

TYPING

NIGERIA & INDIA

€€€€€€€€€€❤
€€€€€€€€❤
€€€€€€❤
€€€€€❤
€€€❤
€€❤
€❤

A yaune Mai girma sarki Ali ya alkawarta zai Kira Ammar yasanar dashi Babbar Asibitin Daya Gina masa wadda yake so su rike shida D'an uwansa Dr. Aj.

'Kwance yake Ashe Ashe akan had'add'en gadonsa Yana sharar baccinsa hankali kwance fuskar sa sai k'yalli takeyi na madarar kyawu da Hutu,Ajiya zuciyar yake sauke wa A hankali Yana sauke gajiyar da yakwaso adaren jiya na theatre n da

sukayi 6-6 ya duk'unk'une cikin bargo saboda yanayin sanyin garin gashi yakure gudun A. C,Baccinsa yakeyi hankali kwance.....

'Ringing din wayarsa Dake charge akan bed drower tayi k'ara cikin sauti Mai dadi,cikin baccin sa da yayi nauyi yajawo wayartasa yanayin picking call din batare da Duba wake kiransa ba.

'Sallamar Wanda baiyi tsammani bace tasanya sa fincike tattausan blanket dinsa white colour Mai taushi.

Ware manyan idanunsa yayi lumsassu masu cike da bacci akanta ,Yana Mai sauke wayan akunnensa Dan k'ara tabbatarwa..

Ganin tabbas shid'inne ga numbansa nan da code din Nigeria da Kuma yadda yayi saving din ta,sunan Yaya Dady ne ya bayyana rad'am akan akan screen din.

Mai da wayar yayi akunnensa cikin wani yanayi bayan karewa sunan kallon.
Adayan b'angaren Sarki Ali ne Bayan yin Sallamar sa ba,a amsa Masha ba,yake ta Hello! Hello! Tare da furta "Mai sunan K'anena!, Yarima! Dama Haka yake kiransa da wayen nan sunayen Alokutta da Dama.

'Kwalla ce ta taru a idon Ammar na farincikin da yatsinci kansa ciki Yau shekara d'aya da wata hud'u baiji Muryar Mahaifinsa ba sai yau.

'Sassanyar Muryar Mahaifin nasa ce takara ratsa dodon kunnensa Yana Kiran sunansa Dan yasan tabbaas Yana saurarensa yasan halin kayansa sarai inda yake furta" Nurin UNNI"
'' na'am ABBA ya furta cikin wani yanayi na sanyin jiki da farin cikinsa dayake kokarin boyewa da murmushiinsa na dalilin sunan da Mahaifin nasa yakirasa dashi.

Farin ciki ne ya mamaye sarki Ali,Dan ba haka yasaba Kiransa dashi ba, Yaya Dady yake kiransa Dashi,inda sunan ya samo asali. ..Afarko Yana kiransa da Yaya ne kamar yadda k'annen mahifin nasa ke Kiran sarki Alin Daga Baya sai Yak'ara da Dady Bayan yaayi wayau.wannan kenan.

MUJE ZUWA□□□□

Wasan yanzu ya fara....✍✍

A b'angaren Sarki Ali ne yaci gaba da magana Yana furta ''Fatan kana lafiya"?
"Lafiya Lau Alhamdulillah Abba" Ammar ya furta.

D'an murmushi Sarki Ali yayi Jin yanayin maganr sa kamar Wanda ke koyon magana Hausan ma Dai Masha Allah..
Yakwana dubu,? Sarki Ali yakara furtawa..

Dan murmushi Ammar Dr Ammar yayi na tambayar ta mahaifinsa Wanda har saida Sarki yaji sautin fitar sa.
Dariya yayi k'asa k'asa Jin yaron nasa na cikin farin ciki koba komai yasan cewa komai ya wuce tsakaninsu da d'ansa duk da kafiyar da kowannensu keda ita.

Ya aiki ya masa Bayan ya furta Alhmdllh. Cikin farin cikin da yakara mamaye sa Jin dariyar Mahaifin nasa abun kaunarsa ya yakara furta Alhamdulillah..

Ammar ne yake Tambayar Ina Nurul hayat bayan sun gama musayar gaisuwar ta yaushe Gamo,"Nurul hayat Dinka na nan lafiya,Ni yanzu ma Ina Fada ne "sarki Ali yabasa Amsa.

Shiru dukkaninsu sukayi akan furucin sarki Ali na karshen musamman Ammar domin Gaban sane yayi mummunar faduwa A tunanin sa zancen Baya ne zai dawo duk da Bai ga alamar hakan atare da yanayin Mahaifin nasa ba ...

Sarki Ali ne yayi murmushi Jin shirun da Ammar yayi akan furucinsa nakarshe Wanda dama yayi hakan ne Dan yakara ganin Yana yin Ammar din da dauki kiyayyar duniya yadaurawa sarauta.

Katse shirun nasu yayi bayan yagama tu ajjabin Al amarin Ammar din,Anan yasanar Masa da batun janye murabus dinsa har sai lokacin da yaji Yana Ra'ayin ayimasa murabus din,tare da furta Masa ya yafe Masa laifin da yayi Masa na Rashin Neman sa,duk da yasan Shima yana da laifin sa taurin kan ne iri Daya like father like son.😀

Farin ciki ne Mai yawa Ammar ya tsinci kansa aciki Jin Abunda Bai tab'a zato ba agurin Mahaifin nasa,sai Kuma gist na biyu da yakara Sanya sa farin ciki shine katafaren Asibitin da aka Gina da sunansa wadda har an kammalata tun da sarki Ali yafara maganar Ammar ya fincike blanket dinsa k'asa yasauko daga kan had'add'en bed dinsa na Alfarma, k'ak'k'arfar surar jikinsa ta Bayyana tare da kwantaccen gashin kirjinsa da yakara lafewa guri Daya sanadin Hutun Dake jikin sa komai gwanin buurgewa atare dashi abun son kowace mace harta da six spack dinsa dama daga shii sai short ne fari k'al ajikinsa.

Jin cewa mafarkinsu shida d'an uwansa. ya cika nason Gina hospital ta Alfarma anigeria duk da suna da Abunda zasuyi constructing da kansu musamman ma shi Ammar din farin ciki ne kwance akan kyakkyawar fuskarsa and he's speechless about the gist.

Ficewa yayi daga bed room din nasa.
Cikin sassarfar sa ta gwarazan maza yake saukowa daga upstairs din sa har Yana hada steps biyu,Kuma wayar na akunnensa Yana furta thank you ABBA! thank you ABBA! you are the best father in the world cikin shauki na soyayyar mahaifinsa da farin cikin wannan albishir.

Hakuri yabawa mahifin nasa na Rashin Neman sa da baiyi ba cikin natsuwa,cikin farinciki dukkaninsu suka Yanke Kiran bayan sunyi sallama da juna.

Finally dai Ammar ya shirya da mahifin sa yanzu sai maganar dawowa Nigeria ✈✈Allah yasa dai su dawo kasar su ta gado don nikam nagaji da kasar India zafinsu yayi yawa arado

MUJE ZUWA akuya ta sace kura😆.Ko A mafarki Nasan hakan bazai faru ba....Nima nabi maganar bahaushe 😹

Komai Nisan jifa.....

Hasbunallu wa ni'imal wakil
Hasbunallu wa ni'imal wakil
Hasbunallu wa ni'imal wakil

YA ALLAH DUK WANDA YAKE DA WANI SAB'ANI DA IYAYENSA ALLAH KA DAI DAITA TSAKANINSU□□

DOMIN ABUNDA WASUN MU BASU CIKA KULA DASHI BANE BABBAR MATSALACE ARAYUWA YIN FUSHI DA IYAYE DOMIN HAKAN NA SANYA ZUCIYA RAUNI,YAKAN HANA JIN DADIN DUNIYA WALLAHI,FUSHIN IYAYE BALA'I NE.WAL IYAZUBILLAH☹

IYAYE BA ABUN WASA BANE,AKWAI HADISSAI DA DAMA DA SUKAYI MAGANA AKAN HAKKIN IYAYEN MU KUMA INGANTATTU,AKWAI HADISIN ANNABI SAW DA WANI SAHABI YA. RUWAITO INDA HADISIN YAKE CEWA "FUSHIN ALLAH NATARE DA FUSHIN IYAYE "KUJIFA ALLAH MA YANA FUSHI DA WANDA IYAYENSA SUKE FUSHI DASHI TO INAGA WANDA SHI YAKE FUSHI DA NASA SUBHANALLAH..☹

ALLAH KA KARE MU DA WATA MUMMUNAR ZUCIYA□ DAN HAKA MU SAKA HAKURI, DUK ABUNDA SUKAYI MUNA MU MAI DASA BA KOMAI BA IN SHA ALLAH ZAMU GA RIBAR ABUN..
TABBAS DUK ABUNDA MUKAYI MUSU BAZAMU TABA BIYANSU BA A CIKIN WANNAN DUNIYAR ,DAN HAKA MUDAGE DA KYAUTATA MUSU DOMIN SAMUN RIBAR DUNIYA DA LAFIRA DOMIN IDAN KIKA GAMA DA IYAYE KI LAFIYA TO DAYARDAR ALLAH ITAMA DUNIYA KINGAMA DA ITA LAFIYA.
ABUN DA KAWAI BA,A YIWA IYAYE BIYAYYA ACIKIN SA SHINE SABON ALLAH.✍✍

ALLAH YASA MUDACE□
ALLAH KUMA KASAKAWA IYAYENMU DA GIDAN ALJANNAR FIDDAUSI.□
WAYEN DA SUKA RIGA MU GIDAN GASKIYA ALLAH KA HASKAKA KABARINSU KASA HUTUCE AGARESU.

AMIN YA HAYYU YA QAYYUM✍ ✍

□Fa'eehbg □
The first lady □□

Fad'awa dakin Aj yayi cikin yanayin farin ciki Wanda ko sallama Bai tsaya Yi ba adakin na Aj.

Dr Aj da fitowarsa daga bathroom kenan ta cikin mirror yaga mutun atsaye tsakiyar bedroom din nasa...
Cikin mamaki yake kallon ganin Yana ta faman sakin murmushin mai kayatarwa

'Ammar ne yake ta sakin murmushi har ya tako ya rungume Dr.Aj Tsam ajikinsa cikin wani yanayi.
Dr Aj abun yaji sa banbarakwai duk da duk da yasan d'abi'ar Ammar ce Rungumarsa inda sabo yasaba da hakan dan duk lokacin da yake cikin farin ciki yakan yi Masa hakan tun suna Yara yake Masa hakan,har yayi niyyar Ture sa sai ya tuna yanayin da yaga fuskar Ammar din da yanayin farin ciki Dake kwance akan fuskar sa Kuma yasan ayanzu bakaramin Abu zai Sanya sa shiga irin wannan yanayin ba...

Bayan kamar minti uku Ammar yad'ago daga jikin Dr.Aj Yana sakin wani k'ayataccen murmushi "Guess who called me right now"? Ya furta ma Aj cikin kafe sa da manyan idanunsa masu haske cikin zak'uwa Dr. Aj ya furta "su Lubna ne Dan saboda yasanar Masa haduwarsu alokacin da ya rubuta musu numbantasa...

Hararar wasa Dr.Ammar yasakar Masa kamar wata mace eyes ball dinsa har wani kyau suka Kara,sannan ya furta

No cikin yatsinar fuska yana tab'e d'an karamin bakinsa Mai dauke pink lips masu taushi kamar wani karamin yaro
Cikin wani murmushin ya Kara furta guess! guess! Yana Kara ware idanun kan Aj Dake tsaye Yana kallonsa kamar wani hoto yakasa gane Wanda yake nufi....

Ganin Aj Bai gane inda ya dosa bane yasake furta

" guessing" had'add'iyar wayarsa k'irar 15pro max Dake runk'e ahannunsa kamar itace Mahaifin nasa yad'ago yayi showing dinta afuskar Dr.Aj Sunan da Dr Aj ya Gani ne arubuce b'aro b'aro a last call ne yasanya sa rungume Dr.Ammar cikin farin ciki,Yana furta congratulations man tare da taping bayansa kamar karamin yaro Bayan sun gama murnar ne yasanar dashi duk maganar da sukayi da Sarki Ali,Dukkaninsu sun kasan cikin farin ciki a wannan Rana duk ka Kalli fuskokinsu zaka San da hakan.

WATA MATSALAR TAZAMA TARIHI
IN SHA ALLAH✍✍
A HANKALI DAI AHANKALI....✍✍✍
ZAMU JE INDA MUKE SO MU ISA...

□□□□□

NIGERIA
BUG

Yau takasance lahadi,Rana ta farko da dr.yusuf janyau zai fara zuwa gurin Halee,Bayan Neman izinin da yayi gun Baba Adee.
Tarba Mai kyau yasamu garesu.
Shigifar gidan Anan aka shimfid'a Masa k'atuwar dadduma Mai taushi Mai cin mutun hud'u...

Musamman Khady ta girka Masa had'add'iyar jallof ta shinkafa wadda taji kayan Had'i tare da taimakon Halee sai mango juice da suka yimasa da yaji kayan Had'i Shima na musamman da damammiyar fura Mai d'ansd'anon dadi da sanyaya Rai,Anan kan carpet din suka baje Masa madai daciyar kulan da suka shirya Masa da Kuma manyan jugs din da suka shirya Masa kayan sanyaya zuciya.

A d'aki Bayan Khady ta Masa iso,ta dawo d'akin cikin rad'a take furta toh Mrs Yusuf sai ki fito muje ko Kar mushanya angon naki ....
Takai karshen maganar tana sakin karaamar dariyarta .

Halee da Tasha uwar kyau kamar wata sabuwar amarya kamar kasace ta ka gudu cikin Jan material Mai kyau an mata fitted gown yakwanta ajikinta d'ass material din yasaje da fatar fatar ta yakara mata wani kyau na musamman..
.harar Khady Tayi kawai cikin wasa batace mata k'ala ba...

Karamin farin hijab din da Khady ta lura Halee tasanya ne cikin Jin haushi ta furta mata sannunki tana hararar ta,itama Haleen harar Khady Ahankali Kuma cikin zazzakar muryarta ta furta "Yawwa"Dan tasan dalilin wannan maganar ta Khady ,tsuke kyakkyawar fuskarta tayi tare da Kara matse d'an karamin bakinta Dan karma Khady tasamu damar kawo mata wani zancen kan hijab din.

Khady Dake rike da k'ugu ce ta tako cikin tana furta narantse bazaki fita dashi ba,tana Kara murtuke fuska irin dagaske tayi rantsuwar..
Cikin Jin haushin rantsuwar da Khady tayi Halee tacire Da'n madai daicin hijab dinta Wanda yake kullum haka take da Abunta har cikin gidan..

Hijab din tacire tayi wurgi dashi gefe Wanda sanadin hakan yakara bayyanar da albarkatun jikin ta da kyakkyawar surarta wadda ko acikin hijab din bata boyuwa domin Halee irin matan nanne da Allah yayiwa baiwar halitta tako Ina ba makusa.

Itakuwa Khady boyayyen murmushi tayi domin dama tasan inta rantse dole zata cire sa shiyasa ta mata haka nan domin tasan ta da kafiya awasu lokuttan.

K'ugu ta kama irin yadda Khady tayi bayan ta mike daga karamar kujerar Dake Gaban madubin dakin nasu datake zaune akan sa,cikin Jin haushin Khadyn ta furta cikin sanyinta "wai nikam ba yayar ki bace dakike rantse mini tana maganar tana karkad'a jiki irin na masifar nan,Dan kinsan dole zan cire shiyasa kika rantse Koh,Tau gobe in ance ki Kara rantsewa bazaki k'ara ba bazan Kara yarda ba nikam ki ka Kara wata Rana zakiyi kaffara takai karshen maganar cikin kyafci,wai ita nan masifa ce takeyi cikin ruwan sanyi fa take maganar bazaka tab'a zato n ma Fada bane in ba kana kusa da ita ba...Khady Dake ta kallonta da dariyar da tacika mata cikine tana kokarin boye dariyar tadake..
Dasauri ta rike hannun Halee ganin tajawo hijab din zata mayar,Khady ce cikin marairaicewa take furta "Anty Halee sorry;bazan k'ara ba tana maganar tana marairaicewa kamar zatayi kuka dagaske.

Dariya Dukkaninsu suka kece da ita na shiriritarsu,Baba Asabe ce ta lek'o cikin masifa tana fad'in ke Halimatu ubanwa kika barwa bako azaure ne eh!?takarashe maganar cikin Jin zafi da da'ga murya,shirun da Taga sun mata ne yasanya ta Jan katon tsaki mtsww
Tajuya fuuu tabar kofar dakin nasu tare da sakin labule.

Bayan ta wuce ne dukkaninsu suka Kalli juna suna rike Baki na ganin lokacin da suka ja bayan Duba Dan madaidaicin agogon bangon dakin.

Babu tsaitsayawa Khady tajawo Jan gyalen rigar ta Halee dake kan yashe kan katifarsu ta Yi mata rolling dinsa akan yalwataccen gashin kanta da yasha gyara har kalabar da Khady tamata ta warware da kanta saboda santsin gashin ta kitso iyakarsa Yan kwanakki yake fara warwarewa,da sunga hakan kuwa sai su idasa warwaresa su biyu saboda tana da tsawon gashi sosai dole sai da taimako gurin tsifar.

K'ara feffesa mata turare Khady tayi bayan tayi mata rolling gyalen Dan tace batason yafawa tana son ta rufe jikinta.

Sak kuwa tafito kamar wata balarabiyar etopia duk da bawata kwalliya da tayi daga Kajol ne sai powder da pink lipsglow da yakara k'awata small mouth nata Mai dauke da pink lips,eyes lashes dinta sunji mascara sun Kara curewa,gyarar ta kuwa Tasha gyara gwanin buurgewa sai dai muce Masha Allah kyawo ne ke magana Anan...
Dan Allah yayi ma Halee baiwar Kyau...

Flatshoes ta Sanya black da suka k'ara ma kafar ta kyau dukkaninsu sunyi kyau kamar kasace su ka gudu itama Khady tayi shigarta irin ta Halee material Daya sai dai banbanci nata ash color ne sai din ki ita nata straight ce bisa ga Halee dake da fitted gown.

Fitowa sukayi Dan Isa inda yake suna zuba kamshi,musamman Halee kunsan mutuniyar taku akwai son k'amshi....

A b'angaren Dr Yusuf kuwa kallon agogo kadai yake yi duk bayan Dan lokaci ganin har minti biyar ya Shure basu fitoba,bayan Khady tace yabata minti biyu zata kawo masa ita bayan tamasa ison..

hankalin sa yaji ya tashi Yana Jin sagewar gwiwa na zuciyarsa da ta raya Masa kila bata ma son had'uwa dashi...

Hango Khady yayi tafe ..rege rege yafara na Rashin hango Halee,fahimtar hakan da Khady tayi ne yasanyata d'an ja gefe yadda zai hango Halee da kyau Dan ta fahimci ita yake so yagani...

Kyakkyawar fuskarta yahango Mai cike da murmushiinsa Wanda bako yaushe ake samunsa ba sai Alokutta kalilan,tafiyarta takeyi cikin natsuwa tana kallon k'asa,siraran kyawawan yatsunta take ta faman murzawa har suka k'araso gurin fahimtar abun da Khady Dake gabanta tayi da Kuma idanun sa da takeji na yawo ajikin ta duk sai taji jikin ta yayi sanyi tana Jin wani yanayi daban.
Idanunsa akanta Suke ko isowar ta Khady Dake farko Bai Gani ba...

Sallamar da Khady tayi ce tadawo dashi dai dai daga sumar zaunen da yayi na kallon kyakkyawar surarta da ta bayyana duk da rufe jikinta da tasa akayi da Vail dinta ..

Ajiyar zuciya yasauke Mai nauyi aboye Yana amsa Sallamar su harda ta Halee da tayi k'asa k'asa wadda Kuma sarai yajita domin sautin ya Isar Masa har inda baiyi zato .....

Finally dai Haleen zata fara dating❤

Allah yasa anshiga da kafar Dama Dr. Yusuf....

Me kuke hasashe a wannan Rana shinko Halee zata karbi tayin Dr Yusuf?

Baba Asabe zata kyale wannan lamari kuwa ganin tata diyar son shiru...?
Hmmm

Mutanen India ko zasu baro kasar ko kodai?✍✍😑😑

Bakina da goro....
Kudai kucigaba da bibiyar alkalamina*

Message to my big fan♥ this page is belongs to you *maman Abbah*
Allah ya bar k'auna tabbas amafarki Nasanta Shima yana kaunarki kamar yadda kike nuna mishi one love,Allah yabar k'auna✍
Masu korafin short page yau dai ansamu long page narufe bakin magana
Yau nayi typing har na gode Allah
Mu hadu
Anext page

Like share and comment pls
https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

□A MAFARKI NASANTA□
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍□✍□
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

*Pen*is migthier than the sword **

Free □

EPISODE1
PAGE41

TYPING□□□

♥♥♥♥♥♥

Ur are my everything sister sumayya Almustapha Murai□□♥my life is nothing without 😘you indeed this page is belongs to you baby girl □I love you dear.□□

❤❤❤❤❤❤

Barkanku da Shan ruwa fatan kowa yasha ruwa lafiya
Allah yakarb'amuna ibada□□Allah *yabiya wa kowa da bukatun sa na alkhairi,Amin* ✍□✍□✍□

<<<<<<<< >>>>>><<<<<<<<<>>>>>>>>>

D'an murmushi yayi bayan ya Amsa Sallamar tasu Yana furta shine kanwar mu kika shanya ni Baki kawo mun mata ta da wuri ba so kike nayi kuka Anan ne?yakai karshen maganar cikin Kara sakin murmushi Yana yawo da idanunsa akan Halee wadda take a tsaye sagado ba wani kuzari..

Murmushi Khady tayi tana furta Afwan Dr.ka rufamun asiri Kar hukumar lafiya ta duniya tazo yin yaki Dani saboda nasaka Daya daga cikin masu Yiwa Al umma hidima akarkashinta kuka takai karshen maganar tana sakin karamar dariya, Shima

kansa Dr.yusuf dariyar yayi Jin maganar ta Khady,cigaba da magana khady tayi tana furta
" Afwan Dr na tsaya Kara gyara maka matar Kane "....takai karshen maganar tana murmushi.

'Dr Yusuf wani murmushin yasaki najin dadi Mai hade da dariya kana ya furta korafi yakarb'u barrister Khadija yakai karshen maganar kamar irin a court,dariya Dukkaninsu dariya sukayi Jin yadda ya mayar mata da amsar harda wani barrister Khadija.

Harta Halee da tazauna yanzu take jinta akan k'aya kan carpet d'in itaama sai da tad'an Yi k'aramin murmushinta Mai kashe zuciya.

Sallama Khady tayi Masa Bayan sun d'anyi barkwanci ta wucewarta.

A hankali yatsin Muryar Halee tana furta "Ina wuni " cikin wata silent voice Mai Sanya bacci ga Mai sauraro bayan d'an shirun da yabiyo baya tsakaninsu.

K'ara sunne kanta Dake k'asa tayi,Jin yayi shiru Bai amsa ba.
Sautin murmushin sa da taji ne yasanya ta d'an d'ago da kyakkyawar fuskarta Dan ganin Abunda yasanyasa murmushin Had'a idon da tayi dashi ne ne Yakafe ta da idanunsa masu cike da shaukin Sonta da alama Bai baida niyyar amsawa mata gaisuwar,shi yasanya dasauri tak'ara yin k'asa da nata idanun tana sakin guntun murmushi,cikin natsuwa Dr. Yusuf da ya Kara sauke ajiyar zuciya a bayyane wadda har sai da Halee taji sai dai bazata iya d'agowa ta kalle sa ba.

"Masha Allah kinyi kyau har nakasa dauke idanuna akanki,Dan Allah ki rik'a mun irin wannan kwalliyar da murmushin " ya furta.

Kunya maganar sa tabata Dan bata tab'a soyayya da kowanne namiji ba ko tsayuwa da wani duk da turuwar da ake mata damasu tsaidata akan hanya ko masu aikowa agida Baba Adee na dakatar dasu.

Tafin tattausan hannunta ta Sanya tana rufe kyakkyawar fuskarta najin kunya tana Kara sakin murmushinta Mai kyau Wanda har sai da side dimples dinta suka lob'a.fuskar sa yad'an matso da ita kad'an Shima Yana sakin murmushin..

Ta kusurwar Zara Zaran yatsunta ta lek'o sa Had'a idon da sukayi ne tacikin yatsarta Babba yasanya ta duk'unk'une kyakkyawar fuskarta cikin gwiwowinta tana sakin k'aramar dariya Shima kansa dariyar yakeyi na farin ciki Ganin ta cikin wannan yanayi.

Cikin wani yanayi ya koma mazauninsa Yana furta"nidai wannnan kunyar zata takurani yanzu idan munyi Aure haka za'a dinga yimun ana rufe mun wannan kyakkyawar fuskar...samun kanta tayi da d'ago kanta ta kalle sa cikin wani yanayi Jin furucinsa Wanda take jin duka maganganun nasa wani iri kasancewarta farin shiga.. sannan takoma mayar wa k'asa Bayan cire fuskarta ta akan jikinta.

Pls Dan Allah ki d'ago inga kwalliyar nan Koh,ko rowarta za,a Yi mun ne yakai karshen maganar Yana Kara sakin murmushi cikin wani salo shi komai
takeyi burgesa takeyi yasan cewa Allah ne kawai ja daura Masa son Halee Yana Jin ajikinsa Babu irin son ma da yakeyiwa Halee aduniyar nan..

Hmmm Dr.Yusuf kenan da alama kaima fara shiga ne 😹😹

□□□□MUJE ZUWA
Wai ansace jakar b'arawo□

Jin ya Had'a ta da Allah ne yasanyata d'ago da Dara daran idanunta tana sauke su akan kyakkyawar fuskar Dr.yusuf Dan Shima Dr Yusuf ba Baya bane gurin kyau Shima farin bafullace ne Yana da kyau sa gwargwado irin nasa sai dai tsawo ne Bai cika ba...

Subhanallah Masha Allah yake furtawa aransa cikin wani yanayi Ashe duk sauran lokuttan kallon tsoro yamata sai ayanzu ne yake Kara ganin zallar kyawunta zubin da Allah ya mata.

Kallon dataga Yana binta dashine lokacin da tadaura idanunta kan nasa yasanyata Jin tsikar jikinta zuba, cikin cikin wani yanayi na sanyin jiki da yakara dabibayeta ta furta "A zuba maka abincin" tayi hakan ne Dan kawar da yanayin da take ji atattare da ita dakuma kallon da yake yimata,A jiyar zuciya ya Kara sauke wa akaro na biyu Yana k'ara Jin sa acikin kogin soyayyarta acikin zuciyarsa..

A hankali cikin wata sassarkar murya ya furta "Alhamdulillah Allal Ni'imati"tare da furzar da wani iska Mai zafi acikin bakinsa take kasala tasaukar Masa wadda Bai San dalilinta ba,tare da kawar da kansa gefe.

Kai kawai ya iya d'agawa Halee wadda ayanzu ta d'an fara sakewa kad'an ganin ya dauke idanunsa akanta Kuma Baya kallonta,Wanda shikuma yayi hakan ne gudun faruwar wani Abu,shiyasa yayi gaggawar kawar da idanunsa akanta jinsa awani yanayin daban..

kunsan zuciya musamman ga Abunda
take so....

'kai kawai ya iya d'agawa Halee dake Jiran Amsar sa.

Abincin ta zubamasa..
A hankali Bayan yayi Bismillah yake cin abincinsa hankali kwance har ya kammala, Amma duka Rabin hankalinsa na akanta a fakaice.

 Itakuwa Halee baiwar Allah sai faman tankwasar kyawawan yatsunta takeyi tana sakin murmushinta aboye da ita kanta bata San ko na mene ne ba.

Bayan gama cin abincinsa ne yayi hamdala..

Yagabatar da kansa agareta da soyayyarsa da Abunda yake ji agame da ita,D'an shiru yayi Yana sauke ajiyar zuciya sai Kuma Ahankali yacigaba da magana Yana "furta Dan Allah Halimatu sadiya kisoni kinji yakai karshen maganar cikin marairaice fuska kamar wani karamin yaro.

Halee dake sauraron sa ne tunda ya fara magana ta d'ago tana yin dariyar da bata shirya yiba wadda ta fito mata abazata Jin yadda ya marairaice mata.

Anasa bangaren Shima dariyar yakeyi ta farinciki ganin alamun nasara a atattare da lamarin, kyakkyawar fuskarta yake kallo tana dariyar fararen hak'oranta sai walkiya sukeyi gwanin burgewa.
A hankali Yak'ara furta naji dadin Dana Sanya wannan kyakkyawar halittar dariya ma'ana mata ta yakai karshen maganar Yana sakin kyakkyawan murmushiinsa..

Murmushin itama tayi tare da k'ara sunne kanta k'asa Bayan Jin wannan furucin nasa na matarsa Wanda kesakata Jin kunyarsa.

Kawar da wancen zancen yayi Yana tambayarta Amincewarta,shiru tayi tana Jin nauyin tambayar tasa da amsar da zata Basa,Dan tasan tabbas itama tanajin wani Abu akansa duk da bata san ko mene ne ba .

Kamar wata k'adangarwa haka tad'aga Masa kanta cikin Jin nauyinsa da kunyarsa ta furta "tunda ya baka damar zuwa gurina na amince domin Nasan baba bazai mun zaben mij....
Shiru tayi Jin kamar tadauke hanya

Murmushi ne ya subucewa Dr.yusuf

Sai yayi Kuma kamar baiji Abunda tace ba Dan ta iyar da maganar ta...

Ganin Bai nuna alamar yaji bane yasanyata cig aba da maganar ta cikin silent voice nata tana furta "Allah yatabbarmtar muna da alkhairi"

"Amin "
Ya ya furta afili cikin farin ciki duk da baha ka yaso jiba,Amma yasan A hankali hak'arsa zata cimma ruwa..

Firarsu suka d'an tab'a duk da yawan firar shine Mai Yinta ita iyakarta murmushi da uhm,aah sai d'aga Kai ..
A haka sukayi firar inda Bai barta ba harsai da yaga tafara sakin jikinta dashi har sun d'an San wasu daga cikin halayen junansu...

Sallama yayi musu itada Khady bayan Halee ta Kira ta..

Manya manyan jakunkuna ne na Alfarma ya Mik'a wa Khady bayan yaciro su daga cikin motarsa. Dakyar ta karba tana godiya bayan ya tillasta mata karbar ledojin ...shigowarta tayi tabar Halee atsaye bayan sun Kara yin Sallamar akaro na biyu.

Ita yake kallo har ya tada motar sa yakasa dauke idanunsa akanta,ita kuwa tsaye tayi ta kasa tafiya sai faman sunne Kai take Yi Kuma takasa shiga gida..

Har ya fara tafiya da motar tasa yadawo da Baya bayan hango ta da yayi atsaye takasa tafiya tinted glass din sa yasauke sannan Ahankali ya Kira sunanta cikin wata kasalalliyar murya Dan ayanzu har ta juya bata lura da dawowarsu ba.

Chak ta tsaya daga d'an takawar da tafarayi Jin tsayuwar motarsa dakuma sautin kasalalliyar Muryar sa "please Halee Kar ki cire ni a tunaninki,ki soni har k'arshen rayuwarki yakai karshen maganar tasa cikin sakin wani smile,tare da Jan motarsa.

Halee wadda ke tsaye bayan ta juyo Ahankali ta bi motar tasa da ido,takasa yin Koda kwakkaran motsi ne,ta tsaya Chak kamar andasata a gurin Jin furucinsa dakuma irin

kallon da yayi mata,Wanda ta hango wani abu acikin idanun nasa mai wuyar fassaruwa,kallo ne yayi mata Mai kashe mata jiki Wanda har yanzu tana jinsa ajikinta.

'Murmushi tayi A hankali na dalilin da ita kad'an tabarwa kanta sani.
Ahankali tashige gidan ,inda ta tarar da Baba Asabe rungume da ledojin da Khady tashigo dasu da alama kwace su tayi duka,gasu nan duk ta zazzage komai akan tabarma,ga Khady a gefe tsaye tana ta faman turar Baki.

Wani k'aton chocolate ne Wanda akalla zai Kai 30k Baba Asabe ta sungume kwallin ta re da wani biscuits Shima Mai tsada duka sai da ta zab'i Abunda take so tabar sauran nan,bayan ta mike ta furta ke Halimatu zoki kwashi kayan,Halee dake a chan gefe rakub'e ta matso a hankali tana tattara sauran kwalayen chocolate din cikin Rashin nuna damuwarta,Har tajuya ta fara magana tana furtawa Khady "sakarya ai sai kizauna nan ki zama yar aike ko ince yar dako har tarigaki Aure yanzu haka keda dadi ace yar tsintuwa ko yar riko ta Riga yar masu gida goshi,wad'annan kayan da kika Gani ke ya kamata akawo wa su, kece Mai gata ba ita ba gaskiya Hadizatu da sake,yanzu ki duba uwar dukiyar da ya kashe mata Mtssw taja mugun tsaki tana kyabe Baki,ganin yanayin fuskar Halee da Khady tana k'ara furta ai gwara intsira ko da wannan ma takai karshen maganar tana Saka kanta acikin d'akinta har ta shiga tasake dawo da kanta tana furta "ke Halimatu inkin gama tattara kayan nan kije ki debo muna ruwa sannan inkin gama kiyi shara sannan ki d'ora girkin dare,"

"Tou" kawai Halee ta furta
Hawayen Dake kwaranya a idanunta tun lokacinda Baba Asabe ntafara yimata sakin magana tashare tana d'ungumawa Khady ledar guda da saura n kayan da ta Had'a..

A hankali ta wucewarta d'akin su Dan cire kayan kayan jikinta ta sauya wasu Dan Baba Asabe ta Hana ta fita da kaya masu kyau in zata fita in ita kad'ai ce.

Bayan wucewarta d'akin Khady ta tashi dasauri jiki ba kwari ta zube kayan nan ta wuce d'akin Baba Asabe,azaune ta isko ta ta baje manyan kwalayen kan tiles din dakin tana cin chocolate dinta hankali kwance..

Kai Khady ta dafe tare furzar da iska Mai zafi cikin b'acin rai tana furta "Babata hakan Bai dace ba ankawowa yarinya kaya duk kin kwashekke wannan Abun ai Abun kunya ne ma wallahi agareni ,kinsan cewa ko Baki karbi kayan nan ba Halee dole ke zata fara kawowa ki Gani, ko duka kika dauka bazata ce komai ba Babata,kibar hakan yanzu shi wannan cin fuskar duk na mene ne Yan zu duk akaina ne,indai nice banaso wallahi ki barni da yar uwata Kar bakin cikin ki Babata ya kashe mun ita takai karshen maganar kamar zata fashe da kuka..ni wallahi Babata nafison tasamu komai na duniya fiye Dani saboda ita bata San gatan mahaifiya baa ita abar tausayice, meyasa bazaki ji tausayinta tunda Nasan kinsan wacece ita, meyasa bazaki sota kamar ni ba? Meta Miki meta rage Miki wasu hawaye ne masu zafi suka silalo mata...

Wani lafiyayyen Marin da yasauka kan fuskarta ne yasanyata kasa iya furta kowace kalma,Baba Asabe ce ta sauke mata wannan Marin ko tantama batayi Wanda bata tab'a yimata irinsaba domin bata tab'a kwatanta marinta ba sai dai duka saboda yadda takeji da ita,bisa ga Halee da take Shan duka da maruka da tsangwama..

Cikin b'acin rai na maganganun Khady ta furta sakarya kawai tana hararar ta,Khady Dake dafe da kumatun ta tana tsiyayar da hawaye gwanin tausayi...

Cigaba da magana tayi Sha Sha kawai ya za 'ayi ki Had'a kanki da ita eeh takai karshen maganar kamar zata Kara kaimata wani Marin,cigaba da maganar tayi...

Wadda ke yar tsintuwa Kuma Marar asali domin ba,a San asalinta ba, waya sani ma ko yar yar shege ce aka yasar abola Baban ku yakwaso shi Mai zuciyar annabawa,sannan har zaki iya Had'a kanki da ita ke yar halak sannan Zaki Yi mata fatan samun duniya fiye da taki mtssww taja tsaki tana sake furta wawuya kawai,wuce kibani guri ko in tattakaki kinzo kinamun Fada kega uwata,duk zanyi maganin ku Dake har ita sai naga in tare kuka zo DUNIYAR shasha kawai.

Komawa tayi Rai ba'ace na maganganun Khady tacigaba da cin biscuit dinta tana Kara Jan dogon tsaki.

Khady Dake rik'e da kunce ce cikin Rashin kuzari da bakincikin maganganun na mahaifiyarta ta juya tana share hawayenta,Bayan fitowarta ne taci karo da Halee....

Baiwar Allah☹Allah ya kawo Miki mafita✍✍

Yau matuk'a HALIMATU SADIYA tabani tausayi wallahi rayuwarta akwai abun tausayi aciki..

Allah muna rok'on ka Kar ka jarabce mu da Abunda zuciyar mu bazata iya d'auka,idan ko ka jarabce mu ya ubangiji kabamu iKon yin tawakkali
Amin✍✍✍✍✍

In naga comment da yawa gobe zaku
samu long page...

Comment dinki kamar taki yake agareni Ina godiya □

Ayeesha Abdullahi...□

Pls like share and comment...

https://www.wattpad.com/list/1003211273?utm_medium=com.whatsapp.w4b&utm_source=android&utm_content=share_reading_list.

https://chat.whatsapp.com/IjZCle5c6V3BGRlnZ0yKim

□A MAFARKI NASANTA□
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□
Firstlady□□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand

*ESSENTIAL WRITER'S**

*Pen*is migthier than the sword **

Free

EPISODE1
PAGE42

TYPING

~~~~~~
Iftar Mubarak
May our prayers be acceptedo prayers
~~~~~~

Bayan fitowarta ne taci karo Halee tana shara,Bayan d'ebo ruwan,Dan ta tarar babu Jira tagama da wuri har tafara saharar bayan gama debo ruwan.

hawayenta ta k'ara sharewa gudun Kar Halee ta fahimci wani Abu,bata San kuwa ta makaro ba domin dukkanin maganganun Baba Asabe a kunnenta suka sauka tun lokacin da tamari Khadyn ta fara sharar komai data furta agareta yashiga kunnenta harta yar shegen da ta tsani jin sa abakin Baba Asabe taji.

'cikin sagewar gwiwa ta furta Halee Ashe har kingama kwasar ruwan ta Yi hakan ne Dan ta tabbatar da hasashenta
"Ehh" Halee ta furta cikin son danne kukan Dake cinta arai da k'ololon bakin cikin da take ji har cikin mak'oshinta Yana taso mata ji take Yi kamar ta had'iye zuciya ta mutu....

☹☹☹☹

Khady fahimtar yanayin da Halee ke ciki Wanda take da tabbacin maganganun mahaifiyartane sanadin shigarta hakan domin tasan ta da hakuri Amma gashi ayau takasa b'oye abun da takeji aranta,cikin bakin cikin da bata da maganinsa sai Allah ta wucewarta d'aki batare da ta Kara furtawa Halee komai ba tare da kwasar sauran kayan ta wuce dasu wayenda ke yashe ak'asa.

***Bayan wucewar Khady Wani mugun kuka ne ya taso mata Marar control na ban tausayi,Wanda har saida ta Dad'e bakinta gudun karta k'ara b'allowa kanta wata sabuwar masifar gun Baba Asabe,jikinta har gigirza yakeyi tsananin kukan da take Yi haka takoma da tsintsiya ahannunta tana cigaba da kukanta Wanda Babu mai lallashi...

Cigaba da sharar ta tayi bayan tafara samun natsuwa tana Yi tana sharar hawaye gwanin tausayi kyakkyawar fuskar nan tata tak'ara yin jaaa na kuka kyawawan idanunta masu haske ayanzu sun rikid'a sun sauya sanadin kukan da tayi.

Bayan tagama sharar ne tafara shiryen shiryen d'ora musu abincin dare. Khady ce bayan tayi sallar la'asar ta fito tana Taya ta fira duk da bawani kuzarin firar dukkaninsu Suke dashi ba,musamman Halee firar Khady take mata Amma kwata

kwata hankalinta Bai kanta,lura da hakan da kkady tayi tayi ne yasanyata tashi ta d'auko musu chocolate d'aya d'aya Dan dama tana mata firar ne Dan rage mata damuwar da ta Gani kwance akan fuskarta,domin har kukan da tayi Khady ta fito Jin sautinta Amma ganin kukan Shima wata rahamace ta yaye damuwa agurin d'an Adam sai bata lallashe taba, bata Kuma Taya ta aikin ba gudun k'ara b'allo mata wata rigimar datafi wacchan ,Dan duk ranar da tasanya Halee Khady tasanya hannu aciki to dukkanin sai ransu ya b'ace musamman Hale...

Har 'yar son ma BA'A bari ba

Allah ya shirya muna ke gwaggo masifa
Hajiya Laure uwar gidan Baba Adee😹

Kada ku shagala Kuna karatun LITTAFIN AMAFARKI NASANTA
Daga
Alkalamin ✍✍
Fa'eehbg
First lady □□

□□□□□□□□□□□

Chocolate din da ta d'auko ta Mik'a ma Halee bayan ta fasa mata shi Dan dawo da ita a tunaninta,kallonta kawai Halee tayi da idanunta masu girma wayenda suka chanja launi tana Mai girgiza kanta tana furta ...

"Banaci"

Sai Kuma hawaye Shar suka silalo mata abisa kyakkyawar fuskarta,lallashinta Khady tafarayi da Kai tana girgiza kanta,alamar tadaina kukan.. tana share mata hawayen gudun Kar Baba Asabe Taji..
Bayan tad'an natsu sai Kuma Ahankali ta fara tsakurar chocolate din din da Khady tayi forcing dinta ta karb'a,ya mutsar fuska takeyi Ahankali Wanda duk Khady na lura da ita har takai takasa jurewa ta dafe kanta da sauri tana furta" Inna lillahi wa Inna ilaihi raji'un". Jin wata muguwar sabuwar azabar data kunno mata Kai domin kanta ne yayi wani mugun sarawa Wanda har saida tadauke numfashi na wucen gadi..Hankalin Khady yayi mugun tashi naganin yanayin da 'yar uwarta ke ciki...

Kaico tayi da halin mahaifiyarta Dan tasan duk itace sanadiyyar motsawar matsanancin ciwon kan na Halee Wanda sai da likitota suka gargade su da Kar Arik'a barinta cikin damuwa ko b'acin rai domin zai iya Sanya pressure dinta Hawa sannan ya Sanya yawan jinin yak'ara girma daga inda yake har yakai inda ba'aso..

Dasauri tadauko d'ai daga cikin maganin nikkanta da akayi prescribing Wanda Zata Rika Sha idan ciwon ya motsa kafin ayi mata neuro surgery din domin shi zai taimaka mata tak'ara samun karfin neutrons dinta.

Maganin Tasha da taimakon Khady sannann ta Rika ta suka wuce d'aki ta takwantar da ita domin maganin Yana Sanya bacci,Bayan tayi bacci ne ita Kuma ta fito ta cigaba da kula da girkin nasu..
Duk abunda ke faruwa Baba Asabe bata sani ba,ana chan ansanya zak'i gaba sai ancinye.
Allah yasa d'an kanoma yakamaki Baba Asabe,kuce Amin□

Fitowarta kenan taga in Halee Taga ma dukkanin ayyukan da tasaka ta ci karo da Khady na iza murhu cikin madafa

Tsaye tayi rike da k'ugu tana kallon Khady cikin sannan cikin gadara ta furta ke Khadija ! Uban me kikeyi anan ne Ina ita wacchan natattar da bata da zuciya...

Wai nikam bama na hanaki Sanya hannu acikin aikinta ba?Khady Dake kallon Baba Asabe ce cikin Rashin. Jin tsoro da haushin Babar tata ta furta" Ai Babata bata Jin dadin jikinta ne ciwonta kanta ya motsa Kuma kinsan likita ya a da sharudd'a abar yawan sanya mata damuwa da b'ata mata Rai Amma Kuma Kinga Abunda kika janyo yanzu in ba Allah ne ya bata lafiya ba dole inje in Nemo Baba yadawo gida akoma da ita asibiti Allah ma yataimaka tana da maganinta na rage radadi..

Kuma wallahi Baba ta kika Dake ni yanzu sai na fad'a Masa ke kika tado mata da ciwon takai karshen maganar tana turo Baki gaba da hurar hanta..

Khady tamu watan bakin Baya mutuwa duk da Marin da ka Sha dazu

Muje zuwa
□□□□□

Sak'ake Baba Asabe tayi tana hararar khady dan Tasan tabbas zata iya sanar da Baba Adee komai har Wannan zagin da Bai San tanayi ma Halee ba na aiban tata da d'iyar shege da marar asali da Marin da tamata,Aiko da ranar ta bani Dan zai iya kora ta gida yadda yake Jin wannann yar tsintuwar,Yanke shawarar bari ta kyale ta kawai ahad'u wata Rana Dan tana tsoron komawa kauyen nan ayanzu ..bayan gama tunanin zucinta ne ta buga k'yafci tare uwar harara ga Khady, sannan ta fice daga madafar,cikin Jin haushin Khady .

Hamdala Khady tayi bayan wucewar Baba Asabe Dan tasan tabbas zata iya sanar da Baba Adee ne shiyasanya tabar maganar nan,da sai taje ta tado da Halee dake baccin wahala cikin pain .

Bayan sallar magrib ne har Halee ta tashi barcin ta garass kamar bata tab'a Jin ciwon Kai ba,Abincin su sukeci hankali kwance musamman Halee wadda bata son cin abin ci Mai nauyi da dare Kuma bata cin abincin dayawa Wanda dama dabi'arta ce, taliya ce Suke ci yar Hausa wadda taji daddawa da kayan Had'i wadda Halee ta d'ora Khady ta iyarr ...

Bayan gama cin abincin nasu ne suka d'an tab'a fira kad'an
Kiran sallar isha'i ne ya tsayar musu da firarsu inda bayan sun gabatar da sallar ne Halee tadauro wanka tare da yin brush ..towel ne Babba tad'auro ajikinta Wanda duk da girman sa sai da yad'an bayyanar da fararen santala santalan
Cinyoyinta masu d'auke da kwantaccen gashin irin na mata sai guntun hijab dinta red domin tana mugun son jar kala itace favorite dinta,hijab ne Wanda tasaba sakawa inzatayi wanka Wanda tadauke sa al'adarta ce ko ince dabi'arta zama da hijabi Ako Ina shiyasa ma ta nemi k'ana nan domin sakawa cikin gida saboda bata iya zama hakanan kunya take ji..

Kyawawan legs dinta take takowa dasu masu taushi kamar na jariri kamar basu taka k'asa ba Ahankali bayan fitowarta gurin wanka,Wanda duk wahalar da take Sha baisanya wani halitta nata chanzawa ba domin haka Allah yayi ta.

Mai tashafa da turare da man Baki sannan tasanya kayan barcinta wayen da tariga ta fiddo su tare da wani farin hijab din fari Wanda yakara haska kyakkyawar fuskarta ya

bayyanar da kyawon asalinta na jinin larabawa za ce Kona fulanin Sudan,inda hijab din zai Kai yadi uku haka.

Khady da ta Dan fara bacci ne taji kwanciyar Halee abayanta..

gyara kwanciyarta tayi Bayan tahau katifar bayan ta tofa musu Addu'a itada ita khady dan yau Khady tace Agajiye take ko wanka batayi ba,to ko tana da tabbacin dakyar in tayi Addu,o'in kwanciya barci....

Asuba tagari Khady.

'Juye juye take akan katifar takasa runtsawa tun kwanciyarta kan katifarta tayaki tunanin da yake Shirin shigo mata ta kasa,sai ayanzu maganar Dr Yusuf yayi mata da dukkanin firar da sukayi take dawo mata sabuwa..
'murmushi take ta saki ita kad'ai tana tunano da kyawawan kalaman sa da yanayinsa da murmushin da yayi mata na karshe,murmushi tak'ara saki tunano furucinsa da yace taso shi har har k'arshen rayuwarta ma'ana har abada,Kuma tarik'a yimasa murmushinta Mai narke zuciya,Samun kanta tayi da sakin wani narkakken murmushi Mai harzuk'a zuciya Wanda bata San yaushe yafito ba..

Khady da tun d'azu ta farko inda take jin motsin Halee Wanda shi farkar da ita inda har ta juyo gabanta batasani ba ta zurfafa atunani..

Khady cikin mamakin murmushin Da Halee ke ta saki a tsakiyar Daren nan kamar Mai aljanu ta furta "ke Koh lafiya kika kasa bacci sai faman sakin murmushi kikeyi ke kad'ai kamar Mai shafar aljannu .....

Halee da taji maganar daga samane ta furta cikin dakewa "murmushi Kuma ni Kam ba daini ba tana maganar tana kokarin controlling kanta daga yanayin da take ciki domin har yanzu takasa dauke murmushin a fuskar ta sai blushing takeyi,tare da waskewa gudun Kar Khady ta ishe ta da tambayoyi ko tagane yanayinda take ciki domin tasan ta da kwakkwafi,ita kuwa Khady tun lokacin da Halee ta fara magana khady take murmushi Wanda ita Halee bata lura ba sabd bata son ta Had'a da ita tayi saurin ganota hmmm Khady tayi tana furta "Ur in love sisi" nagane Mai kike yiwa murmushin nan ai dama Baki b'oyemun ba domin dole zan gane,cikin son kawar da zancen Halee ta furta " Love " she pretend as she doesn't know whats love means..meye love ne halan da kike Had'a ni da shi ta Kai karshen maganar tana yatsinar fuska..k'wantar ta Khady tayi wadda sai da ta mik'e daga kwancen tana Sosa gurin domin taji zafi 'yar k'aramar fitilar da Suke ajiyewa ad'akin da daddare saboda Halee da bata iya kwanciya aduhu sai da haske ko kad'an ne ,tajawo ta haska gurin da har yayi jaa abunka ga farar fata hawaye tafara k'ak'alowa na Jin zafi tana furta Allah sai na rama cikin sakuwa da tab'e d'an k'aramin bakinta kamar wata karamar yarinya yar shekara shidaa, cikin k'aramar dariya Khady Khady ta furta In nabarki kika rama Zaki sanar Dani Abunda kikewa murmushi Dan Khady ta fahimci maganar take so awatsar,Kai ta d'aga wa Khady cikin turo Dan karamin bakinta sai Kuma tasaki murmushin k'eta irin zata d'ibo rabon ta Dan har ta hango yadda zata yiwa Khady.
Hannnu Khady ta mik'o mata dai dai gurin da tasan ta k'wanta,kallon hannun tayi cikiin turo Baki sai Kuma ta dungure hannun dukkaninsu dariya suka Sanya dama Khady tasan ba ramawar Halee zatayi ba rigima ce kawai.bayan sun gama dariyar Khady ta furta "inajin ki Mrs Yusuf,ko dai kin fad'a ne " idanu Halee ta rufe najin kunya maganar,sai Kuma A hankali abunka ga Sabon shiga bazata iya boyewa ba tad'agawa Khady Kai
Alhamdulillah Khady ta furta,domin dama Abunda take sonji kenan,Amma ba kwanciyar hankali a tare dasu,dan tunda Halee zata Raka Halee sai da ta tabata Baki

kamar ta Masa wulakanci ko taki amincewa dashi domin mutumin kirki ne k'ila Allah yakawo sa cikin rayuwarta ne domin yazame mata jigo Kuma yacika mata gurabun da ta rasa.
Cikin farinciki Khady ta furta "Allah ya tabbatar da Alkhairi can't wait to see your weeding Mr & Mrs Yusuf janyau dariya dukkanin su suka Sanya harda Halee cikin Jin kunya.
Anan Khady tad'an Kara bata wasu shawarwari Dan itama duk da ba soyayyar takeyi ba duk sune,Amma tana d'an tab'a karatun novel a makaranta in class mate nasu sunzo dasu sab'anin Halee da ba wannan ne agabanta ba..
Daga nan suka sakeyin Addu'ar Bacci bayan gama firar tasu suka k'wanta.

Sai muce Asuba tagari.
Amaryar Dr Yusuf
Team Dr Yusuf Ina kuke ne ?✍□□□
Nidai nice ta d'aya □□

NIGERIA

K'ungurmin dajine da yake cikin jahar zamfara.
Wata had'add'iyar mota ce k'irar jif bak'a wulik Mai tinted glass ta faka a chan wani gefe, inda duhun itace ya rufe da dajin,wani Babban mutun ne da ak'alla zai Kai shekara hamsin da Yan Kai ya fito acikin motar da mask na fuska Wanda ya rufe dukkanin ilahirin fuskarsa sai idanunsa da Baki ta yadda baza'a iya shaidasa ba.

Tafiya yayi Mai tsawo Wanda har numfashi yake saukowa kasancewarta Mai Dan jiki..

 Taron Dan dazon wasu kalar mutane kake hangowa shigarsu Babu kyan Gani wasun su sun Sha bak'in kaya da rawani kamar irin na buzaye sun rik'e manyan bindigogi masu sarkuna na albarussai a wuyansu gwanin ban tsoro Taron nasu a lissafin kiyasi zasu Kai d'ari uku kowa ya jingina da Babur dinsa Yara da manyan wayenda iyakar su shekara Tara zuwa goma,Bayan isowar sa inda Suke ne suka fara gaggaisawa cikin sanin juna suna Basa girma kamar wani shugabansu ..

Mashin d'in dai daga cikin su yahau bayan sun gama gaisawa dashi suka kama hanya inda sai da suka Yi tafiyar awa uku sannann suka kawo inda wasu manyan manyan bukkoki Suke da wasu mutanen masu irin shigarsu su gasu nan birjik kamar wata kasuwa da guns rike a hannunsu,ga wasu mutanen nan ad'add'aure da da vest ajikin su wacce ta chanza kala a gefe sun ci wuya har sun chanja kamannin fatar su.

Saukowa sukayi suka hade da wayenda ke gurin wayenda Suma a kiyasi zasu Kai su d'ari bakwai ,suka fara shewa da kuwwa suna murna ga oga ga oga tare da harba bindigoginginsu sama irin na karramawarnan,wani ne cikin hausar da Had'a fulatanci ya furta cikin yin shewa oga yazo oga yazo inda duk sauran Suma suka k'ara dauka ...

Cikin zak'uwa yadakatar dasu ta hanyar furta,su senator Jamil da captain Anas da emir Kabir kurya,minister isyaka muradi sunzo jiya ???
D'ai daga cikin sune ya furta cikin gurb'atacciyar hausar sa" aaah oga Amma munyi waya dashu
Har sun bamu wani aiki Mai "wane kalar aiki kenan? Ya Kara TAMBAYA cikin gadara...

Ehh oga shun bamu damar mu shiga cikin Babban Daji lecal gaimen😸

Ba,a ma iya fad'in local government dinba😂😂 .

Muyo kidmashin d'in yar gidan tsohon gwamna Alhaji mukhtar Maja yanzu ma haka munfara shiri shikin shatin nan jamu tafi,sannan anjima Emir Kabir zai Aiko muna da shabbin bindigogi da makamai wayenda kukai shiyo daga kashar Amirierca wasu shanfurin masu kyau yace ma Ba'a cshika shamunsu a nan kusha ba.duk Yana maganar ne acikin Hausar sa Mai garwaye da fulatanci irin fulatancin nan na kasar Mali,Kenya...

Kai mutumen da suka Kira oga yajinjina

Kana ya furta tabbas aikine Mai kyau suka samo Ashe kamar ansani akayo ordern shabbin makamai ,domin tsohon gwamna Alhaji mukhtar Maja ya saci kud'i sosai Dan za'a samu babban kaso agurinsa ,shewa dukkaninsu suka dauka suna had'awa da kabbara kamar awurin yakin jahadi..

A hankali ya taka iZuwa gurinda mutanen Dake d'aure kamar kayan wanki sun fita hayyacinsu ya furta cikin kwanciyar hankali su wayen na kangararrun har yanzu basu fad'i dalilinsu na k'one gidan ba dakuma Wanda yasanya su ba ,zagaye su Yan ta addan sukayi da manyan bindigogin su Abun tsoro har suna Had'a Baki gurin furta shunk'i magana kangararru ne ai dai kaga yadda shukaci wuya tun lokacin da aka kwasosu nan Amma shunki shewa komai,Dariyar k'eta mutumen da aka Kira oga yayi bayan yagama sauraransu sai Kuma cikin dakewa da Rashin tausayi ya furta ku kawar dasu tunda basu iya magana basu da amfani agare mu... dukkanin wayen nan bayin Allah sai da suka razana cikin tashin hankali Jin furucinsa ,cikin tashin hankali suka shiga rokonsu,Amma Ina Basa ji sharri da mugunta ya Riga ya cika zuciyarsu irinta fir auna,Anan take suka Sanya kan bindigoginsu suka bubbugesu Akai sannan suka jera su layi su biyar jina jina Babu kyan Gani sannan suka bisu da harbi tako Ina ,WAl lYAZUBILLAH ☹
Kashin wulakanci suka musu sannan suka jefa gawawwakinsu ga Namun Daji suka cinye Cikin Rashin Imani da debewar albarka .
Rigunane suka d'auko da ke da baje na kayan police suka cinna Masu wuta ,kayan na ci da wuta suna shewa suna zagayar rigunann Dake ci da wutar ..dukkanin wayen nan bayin Allah basu cika ba sai da sukayi Kalmar shahada sannan suka bar duniya ciki rad'adin uk'uba da zak'in Azaba....

Innalillahi wa Inna ilaihi raji'un□□Allah ka kawo muna mafita acikin wannan k'asa tamu tabbas wannan page yasaka ni zubarda hawaye domin ire iren wannan kisan na wulakanci shine alummar mu Suke fuskanta ayanzu.
Wayen nan bayin Allah sun bani tausayi sosai inajin abun kamar gaske 😭😭😭
Allah yajikan kulluhin musulmi Allah ka Kara yimuna kariya □□

Allah ka kawo muna karshen wannan Rashin tsaro da muke fama dashi acikin jihar mu ta zamfara da ma k'asa Baki daya□,Allah Kuma ka rabam da wayen Azzalumman bayinka,Kar ka basu iKon Had'a hanya damu□□
Allah yajikan wayen nan bayin Allah□

😭😭😭😭Naji mutuwarsu wallahi duk da bansan suba Kuma bagaske bane Amma abun akwai tausayi .....😭

Tambayoyinku
??????????????
...su wayen na nan bayin Allah su waye ne kidnapping boko haram ?

Su waye sukuma wayen nan polisawan meye sanadin zuwan su gurin Azzalumman mutanen nan?

meke tsakaninsu da wayen nan Azzalumman ko ince meya Had'a su mesuke son sani ne,??
Sannan su waye ne wayen nan mutane da mask man ya ambato ajere ,captain Anas ,emir Kabir d.s ???
Zaku samu amsar ku
Ku dai inmuku ta bature yace just follow me.✍✍

Yau naji tausayin Halee
Sai dai nataya ta farincikin sosai...fadawarta asoyayya😂

Finally dai da alama Halee tagama zurmawa duka,sai Shirin buki munyi nasara mu Dr.yusuf's team
Sai dai muce Allahyabaki lafiya Halee

Ina labarin mutanen India???

Amsar tambayoyinku duk zaku same su a gaba in Sha Allah,idan Allah yabamu Aron Rai duk zan warware muku Saka sala✍✍✍

Kudai kucigaba da bibibiyata.✍✍✍

Kuyi comment
Kuyi like
Kuyi sharing Don Allah

Akwai darasi Mai yawa cikin book din shiyasa nake so ku tayani sharing dinsa,Dan Al umma su Amfana ✍✍✍

First lady

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Firstlady

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Pen*is migthier than the sword **

Free □

EPISODE1
PAGE43

TYPING□□□

Bayan rigunann sun ciye da wuta ne ogan yace su rubuta sak'o su turawa duniya cewa sun kashe 'yan sandan nan da ake ta Nema ruwa ajallo wayenda ake Nema tun watanni uku da suka wuce,take Anan kuwa suka watsa hotunan Yan sandan nan da yadda suka kashe su har yadda Namun Daji suka lamushe su suka musu cin gilla Wanda Dama sun Riga da sun Yi d'auka.

Hasbunallu wa ni'imal wakil..

Ogane yaciro wayarsa k'irar iphone 14promax yayi dialing numban din da akayi saving da MY TEAM yakira,Senator Jamil Babuga ne yafara yin magana bayan receiving call din cikin yanayin kamar na maye ya furta "yane oga",Shima Captain Anas Lemu Dake cikin Taron Dan dazon manyan Sojoji ne ya mik'e tsulum ya fice daga d'akin Taron bayan Bada uzurin sa na k'arya,A b'angaren Emir Kabir Saraki ne yad'aga Kiran yanayin sallama bayan tashi da yayi daga cikin iyalan sa,sai Kuma minister Isyaka Muradi da yad'aga nasa Kiran Bayan korar 'yan matan Dake a dakin nasa wayenda ya gayyato agidan shak'atawarsa..Bayan gama gaisawar su ne mutumen da ake Kira da oga ya sanar musu da hukuncin da ya Yanke kaitsaye Bada shawarar su ba,Dukkaninsu sunji Dadin hukuncin kashe wayen nan matasan polisawan domin gudun tonuwar asirin su,Emir Kabir Saraki ne cikin Jin dad'i ya furta Dama ni oga tuntuni naso akashe su karsu kub'uce muna Asirin mu ya K'ara Shirin ban kad'uwa,kunga ita wacchan matsalar tuntuni mun kawar da ita duk da bamu mukayi aikin ba,Kuma namu nakanmu muka so muyi da hannun mu yadda zamu Fi samun kwanciyar hankali,Hakane cewar senator Jamil Babuga sannan yakara furta Nima wallahi tuntuni hankali na yake a tashe,Captain Anas Lemu ne ya furta nifa haryanzu hankalina atashe yake akan mutuwar tsohon ministan tsaro da binciken laifukka Gani nake kamar zai dawo daga mutuwarsa...

Minister Isyaka Muradi ne cikin D'an faduwar gaba da yar damuwa ya furta nidai abar maganar minister of security and investigation crimes (S.I.C) domin tana d'aga mun hankali cikin Jin haushinsu oga ya furta ku wayen na irin mutune ne mutumen da ya k'one k'urmus kuce ya dawo nida kaina naga gawarwakinsu shida matar sa babu kyan gani 'yar su ce kad'ai ba 'asamu tata gawar ba domin ita gaba d'ayanta ta k'one..shine har kuke wani banzan tunani chan yakai karshen maganar cikin wani haushin tuno maganar Captain Anas Lemu mugun tsaki yaja Mtssw sanann ya cigaba da magana "Naji mission din da kuka samo muna Mai kyau domin akwai tsoka aciki,tabbas Yana buk'atar manyan makamai masu kyau irin wayenda bamu dasu a Nigeria wayenda sojan Nigeria Bai tab'a rik'a suba domin munsan masu tsaron gidan sa basu da wasa ko mu Banda sun sanmu da bazasu rik'a bari mugansa ba Dan basu cika yadda da mutane ba..

Emir Kabir ne ya furta ai shiyasa mukasa akawo odern wasu tak'arkashin k'asa Shekaranjiya,munyi Kiran layinka bamu samu ba,sai muka aiwatar domin munsan dama anyi maganar makaman awanchan zaman,oga ne ya furta "na cire layin ne akan k'aramar wayar kasan bamu shiga mutane da kowanne kalar sim card

musamman irin wannan harkar ta sirri ..dariya dukkaninsu suka Sanya cikin annashuwa,Anan ya umurcesu da su shirya su shigo dukkaninsu su had'u anan dabar farko Ranar wani sati Mai zuwa,Amsawa dukkaninsu sukayi da Tau sannan sukayi sallam,wayar ya mayar Acikin aljihunsa,sannan suka d'auke sa suka Mai dasa dabar farko inda suka d'auko sa sannan yayi sallama dasu ya bar dajin...

Allah ya tonawa masu irin halayen ku asiri□□□

INDIA

Zaune yake yana hutawa acikin had'add'en office d'in da yakasance mallakinsa akan had'add'iyar kujerar sa Mai juyawa bayan gama Duba tarin patients,sanyin A.C ne ta ko Ina ga sanyin damuna da ake ciki ya mamaye office din. 'wayarsa ce a hannunsa Yana ta faman dialing numban da Lubna ke kiransa da ita,Amma Kiran Baya shiga wurin sau uku Yana Kira sai dai wata ba indiya tayi Masa yaren su da nufin layin is switch off ,tsoro ne yakamasa in ba wani abune ya faru dasu dan Bai tab'a Kiran wayar aka k'i d'agawaba.Dan "Yan kwanakkin nan sun Saba sosai dasu Lubna har su Ziyad ma,sai dai har yanzu Bai tab'a Jin murya ko ganin d'ai daga cikin iyayensu ba zumuncin dasuka k'ulla suna yin abunsu ne awaje.

Text din da yashigo wayar sa ne yasanya sa bud'e lumsassun idanunsa dasuka yimasa nauyi wayenda ke sanye cikin had'add'en glass nasa irin na likitoci Wanda yakara ma kyakkyawar fuskar sa kwarjini Wanda ba kullum yake Sanya Saba.

A hankali Bayan d'an sauke ajiyar zuciya yashiga bud'e sak'on da yashigo cikin had'add'iyar wayar tasa k'irar iphone 15promaX..sak'on da ya bayyana ne yabashi mamaki,kallon rubutun kad'ai yakeyi wanda aka turo inda nalek'a kaina na lek'o muku Abunda ke ciki Wanda yasanyasa kasa dauke manyan idanunsa Akai..

KA NEMI "YAR UWARKA TANA RAYE
Shine abun da sak'on yak'unsa da manyan kalmomi..
Tun lokacin da aka fara yimasa irin wannan sak'on kansa yake ad'aure yarasa gane wacce yar uwar tasaa ake nufi ,yasan dai duka k'annensa mata suna nan lafiya ko d'azu dasuka Yi waya Da UNNI tashaida Masa duk kowa lafiya Lau yake, Kuma duka k'annensa mata suna nan ai,sai mutun d'aya yar uwarsa wadda ya rasa tun tana k'aramarta ta hanyar gobara toh me hakan ke nufi,Norah d'ince da ko k'ashinta ba'asamu ba za,ace tana Raye girgiza kansa yayi cikin son kawar da tunanin da ke Shirin hargitsa Masa brain ta sanadiyyar Norah din da ya sako acikin tunanin nasa,wata kasalar ce Mai dauke da damuwa Mai yawa wadda take ab'oye acikin zuciyarsa tun Yana k'aramin sa tasaukar Masa duk asanadin wannan tunanin ,mutuwar Antynsa da Uncle dinsa da Norah yake tunano wa Yana Jin kamar alokacin abun yafaru guntun hawayensa yashafe masu zafi asanadiyyar k'unar da zuciyarsa keyi na Rashin wani gurbi na rayuwarsa ,A hankali yasanya kyakkyawan handkerchief Nasa ya goge digon hawaye akarkashin glass nasa,tare da musu Addu'ar samun salama acikin gidajen su na asali wato k'abari sannan yayi Addu'a Allah ya bayyanar da k'anen mahaifin nasa Wanda yaci sunansa..
Nidai nace Amin ✍

Numban da aka turo sak'on da ita ya Duba ta Nigeria ce domin ga code din Nigeria nan amak'ale da ita,sab'anin wanchan sak'on na farko da yake a unknown number deciding yayi bari yakira layin sai dai Jin wayar akashe ne yasanya shi aje wayan akan desk din gabansa Mai dauke da tarin takardu bayan goge sak'on gaba d'aya,Lumshe idanunsa yayi wayenda har sun d'an sauya kalar su ta asali cikin wani yanayi tare da d'an cizar leb'ensa na k'asa Yana Jin mood d'insa yasauya gaba d'aya ..

NIGERIA

A yaune aka Idasa kammala dukkanin tsare tsaren Asibitin har kwararrun ma'aikata Andauka.

Hajiya tayi farin ciki sosai dajin wannan labari na ginin Babbar Asibitin da sarki yasanar mata Dan dama ya alkawarta sai an kammala duka zai sanar da mahaifiyar tasa, albarko tayi ta Sanya musu shida Yan uwansa da zuri'arsu Baki d'aya,duka family n farin cikinsu awannan Rana Bai b'oyuwa.

A yaune Kuma yasanar da Ammar dukkanin komai ya kammala, farin ciki sosai Dr.Ammar yayi najin wannan labarii domin haka kawai ayanzu yake son yakoma Nigeria,Tambayarsa sunan da za'a sanyawa hospital din sarki Ali yayi cikin dogon Tunanin da baigama yinsa ba Bakinsa ya furta" NORAH " sai da yayi maganar ne Kuma sai yayi shiru domin Jin furucin nasa wani iri Dan sunan Dake mak'ale azuciyarsane ya fito batare da yashirya ma hakan ba..

Murmushi sarki Ali yayi domin yasan irin son da Dr.Ammar yakeyiwa Norah tun Bai Kai haka ba,Masha Allah Mai sunan Hajiya tadawo Allah yasanya Alkhairi yasa wannan Hospital tazamo abar da zata kawo sauyi acikin k'asar mu ta Nigeria aharkar lafiya..

Amin Dr Ammar ya furfa A saman lab'bb'ansa cikin yanayin farin cikin da yasamesa ayanzu na amincewar da mahaifinsa yayi da sanyawa hospital din sunan k'anwar tasa mafi soyuwa agaresa wadda duk da bata Raye har yanzu Yana jinta azuciyarsa yarasa dalilin da yasanya yakasa mantawa da komai nata..

Sallama yayi da Mahaifin nasa Bayan yasanar da sarki Ali lokacin dawowar su Nigeria inda zasu dawo ana saura kwana biyu bud'e Babbar hospital din,farin ciki ne yakara mamaye sarki Ali har yarasa Ina zai tsoma zuciyarsa farin cikin sa yakasa b'oyuwa yau gashi Ammar da bakinsa Yana furta zasu dawo Nigeria kasar su ta haihuwa
Awannan Rana dukkaninsu sun kasance acikin farin ciki...

BUG

B'angaren Halee kuwa soyayya tsakaninta da Dr.yusuf ta kankama k'warai soyayyar su Suke Sha gwanin burgewa,ta fannnin matsin da take samu a gurin Baba Asabe kuwa Babu Abunda ya chanza sai ma k'aruwa da yayi tun shigowar Dr.yusuf rayuwarta.

A yau ma haka takasance bayan dawowar su daga makarantar boko ne suna shiryen shiryen zana jarabawar gama secondry school..
Tunda suka dawo kayan jikinsu kad'ai suka chanza Inna Asabe tasanya Halee A gaba cewa ta fito tayi mata wanki da tsakar ranar da ake kwatsawa...

Babu musu ta fito tafara wankin tass take wanke kayan Wanda batare da wata damuwa akan fuskarta ba,firarsu Suke tab'awa itada Khady gwanin burgewa duk da Harare Hararen da Baba Asabe ke yiwa Khady din.
Sallamar Baba Adee ce tasanya Dukkaninsu farinciki Dan yau tafiyar bazata yayi musu Bai sanar da su zai dawo ba Kuma ba yau ne ranar dawowar Saba...
Baba Asabe Dake cikin d'aki taji shigowarsa hankali ta yayi matukar tashi Dan bazata manta sharad'in da ya Saka mata ba kan Sanya Halee wankin kayanta,jikinta ne yadauki rawa tuna yadda ransa ya b'aci a wacchan karon na uku yau ma gana hud'u ank'ara domin tana lissafin,Zufa ce ta keto mata inda ta sharce da hannunta tana

hankad'a labulen d'akinta talek'o hango sa tayi tsaye kamar andasa shi fuskar sa ta nuna alamar b'acin Rai k'arara akanta yadaureta tamau,cikin b'acin Rai ya furta" shalele bar wankin nan"Wanda tunda yashigo yayi sallama baiyi magana har sannu da zuwan da suka Masa Bai karb'a ba,Khady acikin ranta kuwa take furta Allah yak'ara Allah yasa Baba Yadau mugun mataki takai karshen zancen tunanin nata tana sakin murmushin k'eta Dan sai da tabi Mahaifiyar tata d'aki dan Taga ko zata iya ciwo kanta akan wankin dan ta mayar dashi kan almajiran Dake wankakau din Amma tak'i saurarar ta data matsa har dukanta taso Yi ba arziki tabaro dakin cikin Jin haushin Mahaifiyar tata gashi ba damar ta Tanya Halee wankin...

Cikin sanyin jiki Halee ta cire hannayen ta daga cikin ruwan tana gogewa azanenta tare da d'an kallon k'ofar d'akin Baba Asabe afakaice cikin d'ar d'ar "kinci Abinci" ya tambayeta " eh'' ta mayar Masa da amsa cikin son gasgata zancenta ya koma tambayar Khady "hakane khadijatu",Khady da har ta bud'e Baki da niyyar furta Bata ciba ne ta Had'a ido da Halee tana mata alamar karki mun haka domin bata son maganar tazamo wani matsala atsakani Baba Asabe da Baba Adee,ganin hakan ne yasanya Khady furta eh Munci Abinci bayan dawowar mu daga makaranta,kansa yad'aga Yana d'an nuna yardar sa duk da Bai wani gamsu da amsar suba Dan yasan zasu iya b'oye masa,domin yasan Halin lauratu zata iya cewa ko abincin ta Hana wa Halee cinsa har sai tagama wankin Dan mugunta,Kuma tabbas hakane Dan Sallah kad'ai suka gabatar ta fito da Halee duk da gajiyar dasuka kwaso tayin thumbprint yazo kanta ga zafin ranar da akeyi.

"Wuce d'aki ku k'ara cin Abincin ki Dan Nasan Baki wani ci abincin da yawa ba,ke Khadija tafi ki d'ebo mata Abincin..

A hankali Halee ta wuce d'aki cikin Rashin kuzari na gajiya da uwar yunwar da ke kwakularta da Kuma ranar da ta gasata ita Kuma Khady tawuuce kitchen Dan d'ebo abincin Wanda zai ishesu dan itama bata ci ba tana Jiran Halee tagama ne su ci tare ..

Jakar da yazo da ita ce rik'e a hannunsa da ta fito yanzu daga d'akinta take kokarin karba tare da furta sannu da zuwa Baban Hadiza,fisge jakar yayi batare da ya Amsa mata gaisuwar ta ba sannan ya wucewarsa d'aki cikin binta da mugun kallo..

Binsa tayi dakin da sauri cikin faduwar gaba da shigarta kuwa ya rufe ta da fad'a Yana furta " na gaji da cin zalin da kike yiwa yarinyar nan da cin Amanar Allah da kikeyi ,Kuma wallahi yanzu bazan k'ara kwatsarki ba ki cigaba akwai ranar k'in dillanci Ranar da Zaki girba Abunda kika shuka da kanki" yakai karshen maganar cikin zafin Rai da kunar zuci..
Hakurin da tabasa Wanda yasanya sa sassautowa daga fad'an Nasa ganin kamar maganar tashiga kunnenta har yabarta ta Had'a Masa ruwan wanka tare da kawo masa Abincinsa,Anan take jima likitota sun shiga yajin aiki Kuma Baba Adee tare yake Aiki dasu shiyasa yadawo gida yau,wankinta kuwa ita ta Ida Abunta Dan ba,a ga almajiran ba dake wankau ba.

Nidai Kam Allah ya shirya munke Uwar gidan Baba Adee...

A b'angaren Halee kuwa tunda Khady tashigo da abincin take cin Abunta cikin natsuwa duk da yunwar Dake mukurkusar ta Bai Hana ta kwantar da hankalinta ba agurin cin abincin,Abincin ta taci Mai d'an dama domin dama bakarya yunwar takeji karfin Halee ne kawai irin naata,itama Khady Dake cin abin cin ,bin Halee da ido kad'ai takeyi ganin Halee taci Abinci Mai nauyi da yawa ,ta San cewa ba k'aramar yunwa ce ta kamata ba Dan yau ko breakfast din da tahad'a musu bata samu damar cinsaba,saboda aikace aikacen da tayi tunda safe gudun Kar ta Yi latti a school.

Tausayin yar uwar tata ne yakamata Wanda take taji wasu hawaye suna son silalo mata sai dai gudun ta tada mata da hankali yasa ta shanye Abunta...

Nikam Khady kina burgeni
Saboda son da kike yiwa Haleen mu

Geng geng suna hanya fa mu k'ara gyara zama

Ina team Dr .Ammar ku hak'ura kawai Dr.yusuf namu yashige

Wasssh hannu na ✍

Mu had'u a next page

Like share,comment pls

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Firstlady

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Pen*is migthier than the sword **

Free

EPISODE1
PAGE44

Note edited

TYPING

Sorry guyz for keeping you waiting

K'arar wayar Halee ce Dake chan yashe gefen gado wadda Dr Yusuf yasaya mata Dan su rik'a communication,k'irar itel 160 key pad bayan Neman izinin Baba Adee da yayi inda ya umurcesa da k'aramar zai bata ba Babba ba,in har Android din zai saya mata to ya bari sai tagama makaranta,hakan kuwa akayi yakawo mata k'aramar wayar fara Mai kyau tare da Sabon simcard da yayi register da kansa ya kawo mata.

Ahankali ta cire hannunta daga abincin,Dan dama taji cikin nata yad'auka har tana batun yin Amai saboda Rashin Sabon cin abinci Mai nauyi da yawa.

Wani Kiran ne yasake shigowa alokacin wayar na hannunta ta jawo ta. HUBBI ne ya bayyana akan screen din wayar, Kara wayar tayi akunnenta tare da yin sallama cikin zazzak'ar muryarta,Amsawa Ta D'ayan B'angaren akayi inda Muryar Dr Yusuf ta Bayyana cikin farin cikin da annashuwa Jin Muryar ta Mai cike da natsuwa,"Alhamdulillah shine Abunda take ta furtawa Akan tambayoyin da yake mata cikin farin ciki,yajikin mu yak'ara furtawa cikin murmushi inda "Cikin Kara yin k'asa da murya ta furta uhm Naji sauk'i cikin shagwab'a da sakin guntun murmushinta Mai kyau na Jin kunyar maganar tasa..

Masha Allah,Allah ya K'ara muna lafiya.. ya furta cikin wani yanayin da ya tsinci kansa na Jin sakuwar da tayi Masa wadda har ya fara sabawa da ita domin Halee akwai shagwab'a dama ce kawai da bata samu.

"Amin"

Halee ta furta cikin natsatsiyar voice dinta

Shiru ne ya biyo Baya a tsakaninsu..

A hankali ta tsinkayi Muryar sa yana furta Luv Baki Yi missing d'ina ba Koh??

Cikin d'an Jin kunya da shauk'in soyayya ta furta" nayi man takai karshen maganar tana rufe fuskar ta kamar tana gabansa..

Murmushi yasaki

Sannan ya K'ara furta meyasa kik'a mun flash ko ki Kira ni Dana ce kimun bayan kundawo school yakai karshen maganar cikin Jiran Amsar da zata fito bakinta..

"Aiki ne ya rik'e ni"ta furta Masa cikin sanyinta Wanda sai yanzu Kuma taji wani rauni yataso mata.

Duk da bata fad'a Masa ko wane irin aiki bane yasan tabbas na wahala ne domin A d'an zaman da sukayi ya fahimci Halee ba 'yar Baba Adee bace sai dai ko d'iyar D'an Danginsa sace,Dan dukan da take Sha da tsangwama agurin Baba Asabe yasan kaso guda acikin Uku,domin A wasu lokuttan in ya Kira yana samunta cikin k'uncin yanayi, wani lokacin har takan kasa iya d'aga Kiran nasa,Kuma idan tasamu Iko ta kan d'an sanar dashi wani abun in yafaru,sai dai A duk lokacin da irin hakan yafaru yakan kwantar mata da hankali,shiyasa Ya d'au Alwashi ko ta Halin k'ak'a sai ya Mallaki Halee A matsayin matar sa uwar ya yansa data gama secondry school ko Dan yarabata da zaman gidan hak'urin da takeyi da matar wan na mahaifinta a cewarsa, Ajiyar yasauke a boye ba tare da yak'ara furta mata komai ba kan aiki da tace tayi...
Bayan gama tunanin zucinsa da magana.

A hankali suka cigaba da firarsu ta soyayya gwanin burgewa Wanda yasanya har ta manta da damuwar Dake cikin ranta.

Tin dawowar Baba Adee Gida Halee tasamu Hutu da natsuwa a gidan hankalinta kwance babu wata tsangwama . sai Abunda ba,a rasa ba nadamuwar Dake mak'ale azuciyarta da ruhinta.....

A yau kwana goma da fara yajin aikin da k'ungiyar likitota suka shiga,Kuma ayaune Allah yakawo k'arshen sa sunyi breaking.

Tunda Halee Taga Baba Adee Yana shirye shiryen komawa hankalinta in yayi dubu ya tashi Dan tasan Baba Asabe sai ta rankamata duk wani aikin da bata Yi akwana goman da tayi da Hutu.
Sallama yayi musu harda k'ara yiwa Baba Asabe Nasihar kula da Amanar Da Aka Basa ta Halee m,Kuma ta tabbatar Masa da zata kula sannan yakama hanyar Mafara ya bar su cikin kewa musamman Halee da kejin sanyinsa fiye da Khady.

Tun bayan wucewarsa Halee ta fara Cin karo da mugayen kalamai da habaice habaice abakin Baba Asabe,Aiki kuwa har Wanda Bai zama dole ba aranar Sai da Halee tayi taci wuya sosai.

GUSAU

Mama khairiyya ce zaune a d'akin hajiya suna tafirarsu gwanin burgewa,Anan ne mama khairiyya take Sanarwa da hajiyar safkare sakin da mijinta yabata guda,duk da Dama hajiya taji abakin Yaya Mustapha yayan khairiyyar,Hakuri hajiya tabata sannan ta umurce da ta komawa mijinta kowacce mace hakuri takeyi agidan ta,Kuma ta rufe idonta ga Al amurransa.
Godiya tayiwa hajiya cikin share guntun hawayen da ya silalo mata na sanadiyyar wani tunani da ya zauna azuciyarta,sannna tayi mata sallama tana barin sashen.

A yaune Inayah takoma Kano tabar su sumy da su hajiya cikin kewarta Nisa harda kukan rabuwa kamar irin bazata daawo ba,Yaya Abdallah shi yarakata har garin Kano kwanan sa d'aya a wurin Mama dije yabaro garin, yabaro masoyiyar sa cikin kewar sa domin harda kuka tayi sai da yayi ta lallashinta haka ya tafi Shima cikin kewar Inayarsa.....

Sarki Ali ne yake sanarwa da UNNI dawowarsu Ammar Nigeria,cikin farinciki ta Yi tsalle ta d'ahe sa kamar wata yarinya saboda murna, ta rasa Ina Zata Saka zuciyarta Jin har sun shirya Kuma,kuka ne Mara sauti ya sub'uce mata Wanda yasanya ta k'ara k'ank'ame mijin nata cikin wani yanayi na farin ciki Jin Abunda batayi tsammani ba ayanzu sanin halin mijin nata da yaronta.

Sarki Ali kuwa dariya kad'ai yake yimata cikin wani farin cikin da yakara mamaye sa ganin irin tsallen da tayi kamar wata baby girl... A hankali Yak'ara furta Am sorry oum Noor tare da taping bayanta irin na lallashi cikin soyayyar junansu.

Soyayyar tsofi gwanin burgewa□□

□□□□□□□□□

Muje zuwa

A cikin hakan ne Kuma yak'ara sanar mata sunan da Ammar ya zab'a ma Asibitin Bayan ta d'an samu natsuwa..

Farin ciki sosai ta nuna a wannan gab'ar ma cikin tausayin Dr.Ammar da k'anwarta Laila Addu'a tayi agare su Allah yakai haske acikin k'abarinsu..
Amin sarki Ali ya Amsa Shima cikin wani yanayi...

Nikam nace Da dukkan kulluhin musulmi ✍
Amin

'Labarin dawowar su Ammar ya zagaye masarauta dangi kowa murna ce fal acikin sa tunda fuskokinsu zakagane hakan,wasu kuwa bakin ciki ne a ransu na sanyawa Rai,domin kuwa lokacin da labarin ya iske Muhammad (malan) ya tsinci kansa cikin bak'in ciki marar misaltuwa domin atuninsa murabus ne zai dawo da Da Ammar Nigeria take Anan kuwa yafara sak'a da warwarar kalar tuggun da zai shirya,Bayan gama dogon nazarinsa da tuninsa yayi wani mugun murmushi Yana ficewa daga d'akin nasa..

Mudai sai dai muce MALAN
Ak'ulla alkhairi Kar abiyewa sharrin zuciya, .

INDIA

Lubna ce k'eta faman daddana waya tana k'okarin Kiran layin Da akayi saving da Bayya, ringing biyu ana uku aka d'aga Kiran,cikin farin ciki ta furta Dr. Bayya
Shine ko Kane me ni Dr.Ammar Shima ana sa b'angaren. Murmushi yayi sannan ya furta Lubna ta abun Babu ko sallama,yayi maganar cikin hausar mu dan iZuwa yanzu ya fahimci suma su Lubna ba asalin indiyawa bane akwai Abunda yakawo su nan India,sannnan awasu lokuttan suna d'an sako gurb'atacciyar Hausar su cikin magana wadda bako iyata sukayi ba,duk da su Aunty basu barsu sun yarda dukkanin Al adar mu ta Hausawa ba.

rufe bakinta tayi cikin yarinta data gano kuskurenta nak'in yin sallamar harda kallon kofa gudun Kar Aunty Laila tajiya cewa batayi sallama ba kamar irin ana Jin muryar Mai magana acikin wayar, wadda kullum sai an mata fad'an Yinta domin ko makaranta Suka dawo haka take fadowa gid... chan Kuma sai tayi sallama ya Amsa mata cikin sakin fuska da Furta yawwa Lubna baby ta fara hankali...yakai karshen maganar cikin murmushi ..

Dadi ne ya mamaye Lubna Jin ance tayi hankali Wanda yasa ahankli ta k'ara furta Masa cikin hausar ta dabata wani fita sai kayi dakyar ka gane..
Bayya yaushe zaka zo kaga Su Appah na da aunty na ??? Pls Bayya don't say no Pleaseeee taja maganar cikin shagwab'arta irinta Yara.

D'an Jim yayi cikin mamakin wayon yarinyar ya furta duk randa kika so Lubna I am always free for you farin ciki ne yak'ara kama Lubna cikin sauri kuwa ta furta "Tomorrow Bayya "Bai Musa mata ba yace ta turo Masa da Address na gidan,sannan ya fara tambayar ta Ina su Ziyad da bata ma bari yasu damar tambayar yasuke ba.

"Suna school " Nima yau karyar Rashin lafiya nayi Dan nayi ta Kiran wayar ka yau ko zata shiga ta furta

K'ayataccen murmushiinsa yasaki Mai Kara k'awata kyakkyawar fuskar sa Jin furucinta sannan a hankali ya furta kidena k'arya kinji Lubna Baby Babu kyau Mai k'arya wuta ake Saka shi...Tau ta furta tare da Furta Bazan k'ara ba. Bayya good girl ya Furta

Sannan yasanar mata da yayi ta Kiran wayan su Bai samu ba "Anan tasanar Masa da ai wayan Aunty Laila ce taci screen da ta yardar ak'asa gurin yin game Kuma aunty tace baza'a gyara ba domin bashine barna ta farko ba,duk da tana da nata tap din .

Kai ya girgiza kawai cikin murmushi Yana Furta aunty ta kyauta tunda Lubna baby bataji,Allah Bayya inajin magana ta Furta kamar zatayi kuka murmushi yakara saki sannna ya Furta to naji my Baby Ki kula kinji abar yiwa Aunty barna,sallama sukayi bayan ya umurceta da Kar ta sanarwa dasu ziyadah har dasu Appah ma zuwansa promise ya Furta itama ta mayar Masa promise sannna sukayi hangup na Kiran cikin farin da annashuwa.

GUSAU

Taron samarine da yan mata acikin club din suna ta faman Raye Raye da "Yan shafe shafe kowa da tasa kalar shiga wasu kamar basu Sanya sutura ba,ga kwalaben giya nan birjik sai faman kwalbewa sukeyi ga wasu agefe chan masu yawa,sai Kuma jerin wasu gun gun na samari suna ta faman Shan shisha hayaki ne ta koma ya turnek'e wurin Wanda idan kana yar k'aramar Asamar ka zata iya motsawa atake,a ko Ina haske ke ta lighting dinsu haske na musamman Mai kalar green, purple,red then white a gurin.

Jimmy na hango da lawisa tana rungume akan k'afafunsa suna ta faman aikin shafar juna suna d'an kora alcohol aciki..
Vibrating din wayar lawisa ne Dake cikin damammne aljihun wandonta ne yasanyata cire bakinta Dake cikin na jimmy tare da Jan dogon tsaki na katse mata jin dadi da akayi domin bata Ida fita hayyacinta ba,kamar jimmy da yashawu da yawa cikin d'an yanayin maye ta d'aga Kiran bayan Duba Wanda yayi Kiran..

Sunan oga ne ya bayyana akan screen din wato Mai gidansu da Suke Kira oga..
Wayar takaara akunnenta kirar iPhone 12 pro max A hankali tad'aga wayar batare da sallama ba ta Furta oga yane cikin yanayin maye daga D'ayan b'angaren oga ne ya Furta lawisa kizo gidan shak'atawa ta yanzu Ina buk'atar ki cikin gaggawa da sauri ta amsa da ohk! Oga Gani nan tafe
Dan tasan yau zata Rika manyan kaya Dan kudi yake bata ba na wasa ba,cikin azama ta cire hannayen jimmy dake kan breast dinta Yana ta faman shafarsu,cikin dai daga ciki. Yan matan Dake ta rawa ta jawo d'aya daga cikinsu ta d'ora akan k'afafun jimmy..

Cikin sauri ta Had'a dukkanin kayan ta acikin k'aramar pose,bata tsaya yiwa jimmy wata maganar ba ganin Baya hayyacinsa tayi ficewarta Cikin Babban club din..

Direct inda motar da suka zo da ita ita da jimmy ta shiga atsiyace ta bar harabar wurin cikin minti talatin ta iso Bakin katon gate din gidan shakatawar na oga horn tayi Mai gadi na wangale mata gate gaisawa sukayi da Mai gadin kamar yadda kullum in tazo ita kad'ai ko ita da jimmy sai sun gaisa Har take d'an Masa alkhairi
Yayi ta Sanya mata albarka yana binta da Addu'ar shiriya....

Parking d'in motar tayi a parking space sannan ta fito ta rufe tana rangwad'a d'ai d'ai ko Ina na jikinta Yana motsawa Dan lawisa Babaya ba gurin zubin halitta ga kayan jikinta Babu kyau sun d'ame ta sosai.
Ko sallama batayi ba ta fad'a cikin Babban falon
Nasa ..

Babban mutun ne zaune akan kujerar yar two sitter ya rufe idanunsa yabawa k'ofar shigowa falon Baya,Dagashi sai short da singleti,k'amshin turaren lawisa da takon takalminta yasanya shi juyowa Yana ware idanunsa akan ta bakowa bane wannan mutumen face kuwa Muhammad (malan)
Fuskarsa ce ta Bayyana wadda take yana
yi dasu sarki Ali ..

Kallon lawisa yakeyi kamar wani maye Yana lasar Baki Yana sakin munafukin murmushi,ita kuwa ganin haka sai k'ara rausaya takeyi tana girgiza na shanunta har ta k'araso inda yake zaune,da zuwanta bata Yi wata wata ba ta d'ane kan cinyoyinsa,shafe shafe suka fara da tsotse inda take dukkaninsu suka fita hayyacinsu ba Abunda ke tashi acikin falon sai nishin su kiss din juna sukeyi kamar wayenda suka samu alewa,Jin kujerar ba ta musu balance ba yasa yasunkuce lawisa Bai dire ta a ko Ina ba sai akan k'aton gadonsa inda take ya bita Yana k'okarin zuge ....Wanda dama shi yayi saura ajikinta,inda Shima yazame nasa,suka cigaba da mu'amalantar juna,gurnanin su kad'ai Kake ji adakin kamar kar Nuka da kananun Nishin lawisa nidake bakin kofa na fito gudun Kar inyi mugun Gani,ganin Abun nasu bana wasa bane na bar gurin gaba d'aya nakomawa ta falo.....✍

Allah ka kare mu daga kusantar Zina
Amin ya hayyu ya qayyumm ✍

First lady

Sun dauki minti talatin kafin dukkaninsu su dawo hayyacinsu.
Kimtsa kansu sukayi bayan fitowarsu daga wanka,a tare Kuma suka fito falo rungume da juna suna tikar dariyarsu kamar wasu zararri,basu zame ko Ina ba sai A Babban dining table na falon had'add'en abincine sukaci na fried rice da sultan chips tare da lemuka masu dadi suka ci suka koshi,ko awurin cin abin cin ma a ya mutse sukayi shi basu ko gama ba suka koma kan network

WAl IYAZUBILLAH
Allah kamuna ka tangar tsari da mugayen kaddarori
Allah Kar kabamu iKon Had'a hanya da zina
Ya Allah na rok'e ka ka tsarkake muna zukatan mu..
;;;

haihuwar uwarsa,bugu takai Masa Acinya ganin tabbas yadawo normal Wanda yasanyasa zabura,tashi yayi zaune Yana ta faman ya mutsar fuska na katse mishi bacci da akayi,Dan san da suka gama tasu hidimar shida budurwar da lawisa ta had'asu baccin yakwashesa,hararar sa tayi tana Furta tashi muje 12 ta kusa Kuma kasan kame akeyi,saukowa yayi daga kan gadon yasanya kayan sa,Babu wani tsarkake jiki suka fice daga club hotel din Baki d'aya..

A mota lawisa ke sanar dashi oga yabata sak'o yace domin Ansanar dashi kwanakkin baya Baba Adee yashigo GUSAU a Asibiti yakawo yarsa da bata da lafiya..
Sannan tabashi dubu dari uku daga cikin Abunda ogan nasu yabata,Karb'a yayi Yana furta zamu k'ara kula indai zai sakar muna kud'i,ai gaja ma yakirani yasanar Dani yaga lokacinda Baba Adee yashiga Asibitin suna biye dashi alokacin,cigaba da magana yayi cikin b'acin Rai yake furta lawisa nace kibar kula oganmu,yanzu ace ban isheki ba me na rage ki dashi me oga yafi ni dashi...

Kinsan inason ki lawisa wallahi Ina kishinki sosai Amma Nasan ke bazaki gane ba duk yadda zan Miki bayani,wallahi bana son ganin kina mu Amala da kowa inba ni ba yakai karshen maganar cikin d'acin Rai Wanda ke nuna maganar har cikin zuciyarsa tafito.

Lawisa kuwa cikin zak'uwa kamar Jira takeyi yakai Aya ta Furta hmm jimmy kenan bazaka gane ba yanzu bagashi naso muna Nashan minti b, Ina kula sa ne kawai Dan na fahimci awannan harkar kud'insa sun Fi zuwa hannunmu,Kuma da Kake cewa haka meyasa duk In na baka kudin Kake karbewa takai karshen maganar cikin kafe sa da idanu..

Shiru jimmy yayi kamar baiji ta ba domin baida amsar bata yasan gaskiya ta fad'a kudin na taimaka musu sosai musamman shi Dan kamar Dan shi take Neman Haram din ,cikin Jin haushi lawisa tak'ara Furta Kuma Daka ke ke cewa nabar mu'amala da malan Kai ya na isko ka ne ehh! Shiru yak'arayi Bai tankamata ba Dan ayanzun ma baida amsar bata,Kuma maganar kula mata bazai iya dainawa ba sai Ahankali, sai dai shi iyakar gaskiyarsa yanason ta Kuma so bana wasa ba.shiru motar ta tayi bayan gama maganar tata kowa da abun da yake sak'awa aransa.

YAKU "YAN UWA KUCI DAGA HALALIYARKU DOMIN ITACE MAI AMFANIN KU ADUNIYA DA LAHIRA✍
HARAM KUWA WUTA CE,SANNAN GUBA CE MAI KARYA GARKUWAR JIKIN D'AN ADAM ATAKE TA HANYAR K'ONA KO WANE SASHE DA WUTAR JAHANNAMA✍

SUBHANALLAH ALLAH KA KARE MU DAGA SHIGA WUTAR JAHANNAMA KA KUMA KARE MU DAGA CIN HARAM KO FAD'AWA HARAM,ALLAH KACIGABA DA HAD'A MU DA HALALIYARMU

A yaune su Sumy da Nisa suka kammala zana jarabawarsu ta neco da waec sai Jiran sakamako.
Murna sosai Nisa tayi Jin labarin dawowar Yaya AA (Dr Ammar) banda gobe,da yake haka take cemasa musamman da ta tuna alkawarin da yayi musu nasaya musu waya itada Sumy in sungama school,tun da tashigo gidan yanzu taji maganar dawowar Dr Ammar takasa zaune ta kasa tsaye farin ciki kamar me ji take Yi kamar ta jawo jibin yanzu....

...Kalmar hasbunallahu wa ni'imal wakil ce a bakinsa bayan falkawarsa daga mafarkin da yayi,bakowa bane face sarki Ali,tunanin mafarkin yakeyi na Abunda yagani acikin barcin nasa inda yaga d'an uwansa Umar yazo garesa Yana Furta kacire da muwa d'an uwa ban mutu ba Ina nan dawowa gareku...wannan sune kalmomin da ya ji Dan uwan sa ya ambata Wanda yasanya sa Jin wani kuzari ajikinsa,koba komai yau Allah ya nuna Masa Dan uwansa a mafarki Wanda ya Dad'e Bai Sanya sa a ido ba yau shekara ishirin da d'aya kenan..
Mikewa yayi bayan gama tunanin nasa akan mafarkin Nasa yayo alwallah Raka'at Biyu yayi Yana Mai musu Addu'ar bayyanar in har suna Raye din danshi Bai Ida yarda sun k'one ba sai dai baida tabbacin cewa ko suna a Raye din ko amace duk da Bai tab'a sanarwa da kowa Rashin ganin zoben d'an uwan nasa ba Wanda wuta bata chanza shi..
Bai d'aga daga kan sallayar ba har sai da yayi Addu,o,l masu yawa agare su da Kuma d'an uwansa Abdul Rashid da Alummar duniya Baki d'aya..

Haka ake so mutun mumini yakasance idan zaiyi Addu'a yayi ta a jam'i domin Yana d'aya daga cikin Ladduban da ake karbar Addu'ar bawa atake gurin✍

Kiran sallar asuba ne da akayi masallacin masarautar yasanya sa nad'e sallayar Yana ficewa daga d'akin nasa,su mahir ya fara tadowa da Abdallah sannan suma su Nisa ya tadosu sannan ya fice masallacin batare da ya tsaya Jiran su mahir din b a.

Bayan sungama sallar ne yake gaggaisawa da Yan uwa inda wannan dai daga cikin dabi un sarki Ali ne ta hanyar musabuha.
Hannu ya Mika ma malan,inda malan yaki mayar Masa da Sallamar Kuma ya ki Basa hannu ,murmushi kawai sarki Ali yayi Yana mikawa Yaya Mustapha hannu sukayi musabaha cikin karrama juna.
Ba yan zu sarki Ali yasaba da irin wannan da bi'a ta malan ba yasamo asali ne tun suna Yara haka yake kyamatar duk wani na familyn nasu inka cire Yaya Mustapha da Mama khairiyya suda su da ya ke ciki Daya suka fito dashi..
Shiyasa sarki Ali baidamu ba,komawarsa gida yayi sashensa inda yakwana yayi shirin shiga fada.

Bai sanarwa da kowa mafarkin da yayi ba har unni da hajiya sai dai yacigaba da Addu'a ga Ubangiji Allah ya tabbatar musu da alkhairi.

Gyare gyare ne ake tayi acikin masarautar fadawane da ma'aikata ta ko Ina ke Kai kawo na dawowarsu Dr Ammar nigeria gobe,Ank'ara gyara part dinsu dayake asashen unni shida Dr Aj domin fara d'aya Suke rabawa tun suna Yara sai dai kowa da nasa bedroom,achan gidan lieutenant jabir Muhammad soja ma haka Suke wannan shiri na tarbon manyan bak'i angyara musu komai nasu achan din..

Sai Jiran dawowarsu..

For more info
Contacts□□
WhatsApp& Telegram+2348069059746

Please like share and comment✍

□A MAFARKI NASANTA□

I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Firstlady

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Pen*is migthier than the sword **

Free

EPISODE1
PAGE45

TYPING

Noted edited

INDIA

Zaune suke cikin motarsa shida Dr Aj sunata Bada horn abakin wani makeken gate na Alfarma,Bayan d'an lokaci sai ga wani tsoho ba indiye ya fito daga cikin gidan Yana Furta Aah d'an yaro kasake dawowa cikin sakin fuska da harshen India yake maganar inda yak'ara furtawa bayan Dr Ammar ya Amsa da ehh tare da gaida tsohon cikin mutunci shida Aj,"Har yanzu Dai Ba'a sallamo sir ba",cikin yar damuwa Aj ya Furta yanzu baka San Hospital din da yake ba ma'ana inda akayi admitting nasa,"ehh gaskiya bansani ba
Kuma d'azu da hajiya tadawo mancewa nayi in tambaye ta".

Kai Dr Aj yad'aga sannan suka sake yin musabuha tare da barin unguwar gaba d'aya,suna Hawa kan titi...

A Cikin motar Aj ne ke ndriving sun Sanya k'ira'ar shekh Muhammad afif suna sauraro..cikin Jan k'aramar tsuka Dr Ammar ya Furta naso ace kafin mubar garin nan nagana da iyayen su Lubna,duk sai nake Jin ba dad'i araina yakai karshen maganar cikin sauke wata ajiyar zuciya,cikin damuwa Shima Aj ya Furta gaskiya yakamata ace munyi sallama dasu kafin mubar k'asar nan.Dan Shima Aj yad'an Saba dasu Lubna

sosai Kuma Shima ya hango kamar Ammar dasu Lubna d'in tun lokacin da suka fara had'uwa,sai dai kowa yasan yadda Allah ke nuna iKon sa ta hanyar yin kamannin Yan Adam iri d'aya wasu idan kagansu zaka ce tawaye ne sai dai ko jini basu had'aba hasalima mabanbantan k'asashe Suka fito.

Maharashtra 24hrs hospital suka zarce Dan Bada resignation letter d'insu,cikin jimamin Rashin ganin su Lubna.
Bayan shigarsu Asibitin ne Suma bodyguard dinsu suka parker nasu motocin agefen harabar Asibitin dan suna biye dasu dama,sai dai su sukayi driving da kansu ta hanyar nunawa drivers din nasu Rashin Ra'ayin tuk'in nasu.

Basu zarce ko Ina ba sai office d'in medical director na hospital din Wanda yake shine shugaban likitota awannan hospital din
Suka Bada takardar barin aiki sannan sukayi signing suka fito,kowannen su office dinsa ya zame,Dan d'aukar Abunda yake Mai mahimmaci ne agare su.

DR . AMMAR ne tsaye acikin office dinsa, tsaye akan wata had'add'iyar locker,Yana binciken wasu takardu,locker ce Mai kyau
wadda ta k'ara k'awata office din.cikin shigarsa ta bak'in trouser da t-shirt fara ya tsuke abunsa gwanin burgewa a irin shigar da dai kuka San Doctors nayi,sai shoes bak'ake Samfurin boot suma masu kyau...

A hankali ya dakatar da Abunda yakeyi Jin an fad'o Masa office ba Neman izininsa bare sallama,A hankali kuwa ya juyo Dan ganin wani isasshen ne,Domin bayan Dr Aj yasan Babu wani Mai Masa irin haka.

Da kyakkyawar fuskarta Dr.Malini ya ci karo inda dama zarginsa na itace ya tabbata ta hanyar Jin k'amshin turaren mata a office din nasa da yasan dai nurses basu shigowa Kai tsaye, sai dai ko a telephone a Kira idan wata matsalar ta taso kafin a isko sa a office din.

Kallo guda yayi mata Ya d'auke kansa yacigaba da aikin da yakeyi,ganin yanayin da tashigo dashi kamar hankalinta atashe yake,Cikin yanayin damuwa da tashin hankali wannan kyakkyawar ba indiyar Dr MALINI ta Furtama Dr Ammar cikin yaren Indian....

Kuch ta he hoti Mera sardiye ho
Ajne bat Mera sarti.bat Hoya he...😂😂😂😂

Ina indiayawan mu fatan kungane yaren..😂😂

.."Dagaske ne My Doctor kunyi resignation Kuma gobe zaku bar India?,da yake haka nan take kiransa awasu lokuttan..

NABI MY DOCTOR DA GUDU ،

Cikin wata kasalalliyar muryatasa da Rashin damuwa da yanayinta ya Furta mata "yeah" atak'aice batare da ya aje aikin da yake Yi ba.
Hawaye ne suka kwaranyo daga cikin idanunta gwanin ban tausayi inda tun tanayi acikin zuciya har yakai ya fito Fili.
Jin shesshekar kukan nata Yama sa yawa ne yasanyasa idasa kwashe takardun da ya Had'a guri d'aya tare da rufe lockern Yana Jan k'aramar tsuka Marar sauti dama a Yan kwanakkin nan Tasha Masa Kai ba office ba ba gida ba,Dan inta kira wayarsa bai d'aga ba direct gidansu take isko sa,tun d'an sakin fuskar da yafara nuna mata wadda ayanzu yake danasani.k'ara kallonta yayi a fakaice na second d'aya kana Yada'uke idanunsa da sauri akanta ganin irin shigar da ke jikinta wadda sai yanzu ya

lura da ita,shigace ta English wears Riga da wando d'amamme rigar iyakar ta rufe breast bata Kai ga cibiya ba irin rigunann ne na fasion da ake d'aurewa a tsakiya abar cibiya sake da tommy zuwa k'ugu,dama shigarta ce wannan tana mugun son irin shigar..
Kamar dai yadda kuka San Shraddha Kapoor na shigarta ta cikin film din student of the year ko ABCD,any body can dance..

Korar shaid'an yayi bayan k'yallo ma idonsa shafaffen cikinta da cibiyarta Dake manne,zama yayi akan kujerar sa Bai kula ta ba,bayan kamar minti D'aya ya bud'e idanunsa da ke Lumshe a hankali.
Dr.malini kuwa ganin yak'i kulata ne cikin ruwan hawayenta da Muryar ta Dake shaking ta Kara furta yanzu my doctor in ka tafi shikenan bazaku dawo ba...

Yanayin da tayi maganar sai tabashi tausayi cikin d'an ya mutse fuskar sa domin tabbas ta takura masa ba kad'an ba
Cikin yangarsa da arrogant voice nasa Mai nuna iKo da mazan taka ya Furta I'm sorry
Yana Lumshe manyan idanunsa da yake Jin wani iri acikin su,wani irin sanyi ne ya ziyarci zuciyar ta Jin Kalmar hakurin da ta fito daga bakinsa ayanzu akaro na biyu hawayenta tak'ara sharewa da handkerchief din da yatab'a bata Wanda dama tana tare dashi Ako da yaushe yazame mata abokin tafiya.

A hankali ya Kara tabbatar mata da Abunda take son sani gobe zasu bar India Kuma insun tafi bazasu dawo ba sai in wani aikin yataso Wanda dole ana Neman taimakon su agurin,yakuma sanar mata da Babbar Asibitin da mahaifin sa yagina musu wadda har an kammala ayanzu ma chan zasu cigaba da saving live's ..

Congratulations ta Furta cikin wani yanayi da ta kasa fassara shi na farin cikine ko na bakin ciki...
Thanks ya Furta
Inda tak'ara Basa amsa tana Furta
"It's my pleasure" farin ciki ne Kuma taji ya mamaye ta yau sunyi doguwar magana dashi inda Kuma tak'ara tuno maganar tasa da yace zasu Rika shigowa in ta taso Wanda tasan Kuma dole ne ko sun je su dawo tunda ba'a basu damar yin tafiyar din din ba...

Cikin Rashin kuzari ta Furta I love you my doctor sai dai bansan dalilin da yasa baka Sona ba,nidai ko da baza ka soni ba zan iya biyoka Nigeria murayu tare hakan ,Kuma gaskiya idan dai har naga kadade baka zo India ba zan biyoka nigeria Dan bazan iya jure Rashin ka ba har na tsawon lokaci...

Kallonta yakeyi Ahankali ganin yadda kyakkyawar fuskarta tayi jawur abunka da Jan kosai na kukan da Tasha duk akansa,Kalmar so da ta k'ara Furta masa ce ta k'ara Sanya ya gwiwowinsa cikin kasalalliyar muryar ya Furta mata" karki
Damu ai zamu rik'a communication ohk!" Tare da dauke idanunsa kan fuskar ta,inda ya Furta mata hakan ne Dan kwantar mata da hankali,dan ayanzu tausayi take Basa.

Kai ta d'aga Masa alamar gamsuwa da furucinsa,Kad'an suka tab'a fira har da Dr Aj da yashigo yanzu Wanda duk Rabin firar Aj ne da malini keyi shikam ogan iyakarsa juyi a kujerar sa tare da Lumshe idanunsa kamar wani Mai bacci..

Sallama sukayi da dukkanin colleques nasu,inda harda Taron karraamawa aka Had'a musu na musamman daga gwamnatin India na nuna jajircewarsu a wannan asibiiti Mai d'inbin tarihi duk da kasancewarsu Yan Africa, sun samu kyaututtuka da Dama a wurin bukin karramawar tasu da ya gudana adare musamman Dr Ammar.gwamnatin

India ta nuna alhinin Rashin gwarazan likitota masu d'in bin tarihi azukatansu dama sauran k'asashen dasuke mak'wabtaka dasu.
Gwamnatin India ta Kuma k'ara tabbatar musu da zasu cigaba da biyansu albashin su ba wani chanji har na tsawon shekara arba 'in akan hidimar dasuka Yi da k'asar gurin samun cigaba a fannin lafiya,sannan. Suka tabbatar musu zasu nemesu in wani aikin yaci karfinsu kamar yadda sukayi da MD na Asibitin Maharashtra,a take Kuma Anan suka k'ara sanar musu gidan da Suke zaune acikinsa sun mallaka musu shi halak malak,wanda yake dama na gwamanti ne,duk da yake suna da nasu gidajen na Alfarma akasar sun Fi son na gwamnatin Wanda ta Ginasa musamman Dan su ...

Allah sarki
Kunsan indiawa fa akwai karramawa indai ka musu to insuka tashi mayar Maka zaka Sha mamaki..Dan lokacin da nayi zama India haka suka mini naji kamar kar inbaro □😹□□□

Farin cikin su Dr.Ammar a wannan Rana Bai b'oyuwa.Har body guard dinsu da sauran ma'aikatan su sunyi sallama dasu cikin kewar juna,dukkaninsu suka koma barrack Dan dama mafi yawansu Sojoji ne masu farin kaya.

NIGERIA
Unni ce da masu aikin sashen nata ke ta Kai kawo acikin sashen na kitchen dinta ,sunata shirin tarbar manyan Baki da zasu sauka, yau girkin da akayi musu kala kala ne na musamman, musamman unni ta Nemo wadda ta iya abincin India aka Had'a musu irin su Pani puri shawarma da had'add'iyar basmatic rice dataji kayan Had'i na musamman,da farfesun kaji da had'add'iyar suyar kaji ,sai coconut juice da Madara tare da manyan exotics drinks,aka jere akan dining din da manyan kuloli na Alfarma masu d'an Karan kyau wayenda suka k'ara k'awata dining space din saboda farare ne Kar tass. tsayawa fad'in kalolin abincin zai cika wannan page din idan muka tsaya lissaafo abincin da aka tanadar musu duka zamu iya Cinyesa..

Jere Suke akan dinnng din,kowa kagani ya chab'a ado na musamman tin daga kan k'ana na, su Nisa ansha kwalliya itada sumy har Inayah dasuka zo jiya Dan tarbon manyan Baki itada mama dije,anko sukayi,kowa kagani farin ciki ne shimfid'e akan fuskarsa,Ummi ma tazo itada da Dady soja Dan duk Anan za'ayi tarbon su Anan sashen Unni a Babban falon ta,Sarki Ali yau ko fada ba ' a zauna ba,anyi ma masarautar wani irin gyara na musamman Dan har Sabon fenti sai da aka chanza ko Ina fess fess Masha Allah.

INDIA

Dr.Malini ce ta Raka su har Babban filin jirgin Mumbai India itada sauran colleques nasu da manyan wakillan gwamnatin India Dan k'ara karrama su,sallama sukayi ma dukkaninsu cikin Rashin son rabuwa da juna..

Dr.malini harda hawayen rabuwa da masoyi harda rungumar sa taso yi sai dai ya kauce mata.

Dr.Ammar da Aj sunji damuwa sosai alokacin da suka rabu da abokanan arzikin nasu wayenda basu tab'a nuna musu k'yama ba ta kasancewar su musulmai acikin su,Kuma ba Yan k'asar su ba.

Sanarwar da akayi kowa yagyara jirgi zai tashi ce tasanya Dr.Ammar Dake kusa da Dr Aj a first class,bud'e manyan idanunsa da Dake Lumshe tun bayan shigarsu cikin jirgin...Wanda damuwar Rashin samun su Lubna ce ta dabaibayesa,A hankali Yak'ara

gyara zaman belt din sa tare da zamansa acikin jirgin..tare da Karanto Addu'ar tafiya azuciyarsa.
A take nan jirginsu ya Lula a sararin samaniya..inda jirgin nasu yatashi A Babban filin sauka da jirage da sauka na SHIVAJI Mai suna .....

✈CHHATRAPATI SHIVAJI INTERNATIONAL AIRLINE MUMBAI✈✈✈✈✈✈✈

Mudai sai dai muce Asauka lafiya
Bokayen turai..

NIGERIA

Jirgin da yakwaso manyan bak'i daga k'asar India yasauka karfe uku dai na Rana A Babban filin sauka da tashin jirage Dake Gusau Mai suna...

BAZAMFARE AIRLINE GUSAU ZAMFARA STATE✈✈

Mota shida su Unni sukayi Dan tarbon manyan bak'i..

Sanarwar da akayi jirgin zai sauka ne yasanya su Unni da Ummi dasu Nisa fitowa daga cikin motocin su,zuwa waiting space..

A hankali jirgin yasauka inda bayan Yan mintuna mutanen Dake cikin jirgin suka fara fitowa cikin farin ciki kowannen su rike da yar k'aramar jaka ahannu wasu kuwa trolley bag.
Sai dai har yanzu su Unni na zuba ido ko zasu ga ya Yan nasu shiru

Har sai da mutanen suka kusa k'arewa sannan su Dr Ammar suka fito,Aj ne agaba sargafe da yar madaidaiciyar jakarsa Mai kama da school bag,Yana sanye cikin k'ana nan kaya wando jeans bak'i da Riga jaa,sai Ammar Dake Bayan sa yasha kyau na musamman cikin had'add'en k'ananan kaya Shima cikin shigar blue wando jeans da Riga dark blue anyi mata farin design na rubutu Mai kyau na Kalmar EASY,sai cover shoes fari masu d'an tuli sai farin glass da yasanya a idonsa Wanda yakara k'awata kyakkyawar fuskar sa Mai cike da haiba ,Masha Allah. fatar nan tasa sai sheki takeyi musamman da Rana tad'an hasko sa fresh dinta yak'ara bayyana k'arara,k'aramar jaka ce Shima goye abayansa sai Kuma had'add'iyar trolley dinsa bak'a Mai amfani da na'ura jaye a hannunsa fuskar nan tasa ba wani sakewa irin haka,Kuma ba Shan mur,ba kamar Aj ba da bakinsa yakasa rufuwa tun fitowarsa acikin jirgin ya shak'i k'amshin Nigeria.

Nisa ce ta fara hango Dr.Aj cikin farin ciki da shauk'in soyayya ta watsa wata iriyar k'ara ta farinciki wadda ta jawo hankalinsu Unni dama sauran tsirarrun mutanen Dake wajen,da mugun gudu ta fad'a jikinsa tana k'ank'ame sa sai Kuma kuka ya kubce mata Wanda yake fitowa tundaga zuciyarta,Dr.Aj da Yaji abun wani irine tun fad'owarta a k'irjinsa da yadda yaga farin ciki kwance akan fuskarta yatsinci kansa a wani yanayi Marar misaltuwa... Hannunsa yadaura abayanta Ahankali Yana rarrashinta har tasamu natsuwa,Su Ummi dasuka ga Abunda Yafaru dukkaninsu murmushi sukayi domin sun San sakar cin Nisa,Amma yanayin da tashiga akwai wani Abu ko basu Yi bincike ba.

Dr.Ammar kuwa sumy ne da Husna da su Ummi suka rungumesa cikin farin ciki.....

...Finally dai sundawo yanzu kallo yadawo Nigeria...sai mu Jira muga ya abun zai kasance...

Allah kabamu iKon kammala wannan book lafiya ya ubangiji

Maman Abba
Sis Ayeesha Abdullahi
naga comment dinku

Ina godiya

Allah yabar k'auna

Next page tomorrow in Sha Allah

If you have any suggestions or advice you should contact me via my
Whatsapp&Telegram +2348069059746
Email -faizaalmustapha1940@gmails.com✍✍✍

Like share and comment pls

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Firstlady

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Pen*is migthier than the sword **

Free

NOTED EDITED

✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓✓

EPISODE1
PAGE46

Wannan page sadaukarwa ne agareki Auntyna Kuma abokiyar shawarata k'warin gwuiwataMaman Muhammad (haandy)marubuciyar littafin BAHAR
Thanks for the support I really Appreciate it□□□□□□

TYPING□□□

£££££!□
££££!□
£££!□
££!□
£!□
!!!□
!!□
!□
Mahir ma da hajiya rungumesa sukayi cikin farin ciki,Shima Dr. Aj duk sai da yabisu d'aya bayan D'aya Yana Rungumarsu cikin farin cikin dawowa garesu.

Bayan yagama diramar sa da hajiya Dake ce Masa yazama k'ato ne yarage cin abincin,yaro kamar d'an Dan be kallonta kad'ai yayi tare da yin murmushi Yana Furta bawani nan kedai Kinga santalelen saurayi kyakkyawa Kuma Gani nan bari nan Auren ma da nace zanyi Dake na fasa,dukkaninsu dariya suka Saka ganin yadda hajiya ta kyab'e Bakin.

Unni Dake gefe ma sai data murmusa tana d'an kawar da kanta irin na kunyar nan ta d'an fari ,A hankali ya tako Yana ta faman sakin k'ayataccen murmushinsa Yana dosar inda Unni take tsaye kanta ak'asa Yana zuwa baiyi wata wata ba ya fad'a akan k'irjin mahaifiyartasa ya rungume ta Yana sakin dariyar farin ciki itama Unni dariyar takeyi na farin cikin Jin d'umin jikin yaron nata, Dukkaninsu wani farin ciki ne suka samu kansu ciki Marar misaltuwa Wanda sun Dad'e basu samu kansu ciki ba Marar misaltuwa.

A hankali ya Furta Nurul hayat I 'm back to you kiyi farin ciki Mai yawa,bana son ki k'ara yin Fushi Dani Kona second d'aya kinji..yakai karshen maganar cikin sauke ajiyar zuciya idanunsa na sauyawa daga yanayin daga kalarsu.

Unni kanta kad'ai ta iya d'aga Masa tana taping hannunta akan bayansa alamar lallashinsa Jin ajiyar zuciyar da yasauke,hawayen Daya zubo mata tashare tana Furtawa cikin harshen larabci "marhababika ya Nur",Dan haka take Kiran sa awasu lokuttan,janyesa tayi ajikinta sannan ta d'an d'aga k'afafunta ta sakar Masa kiss a goshinsa cikin farin ciki da murmushi kwance akan fuskarta,kowa Dake kallonsu Unni da Dr.Ammar sun burgesa sosai.

Jikin su Ummi da Nisa yayi sanyi na ganin yanayin da Unni tashiga itada Ammar,A hankali Shima Dr.Aj yatako cikin farin ciki yana rungume Unni barka da zuwa tamasa cikin farinciki itama tana Furta barka da dawowar ka k'asar Haihuwarka Aminullah na,Amsa mata yayi da yawwa Unni cikin farin ciki kamar yadda fuskar ta Unni take wanze da farin ciki,Shima peck ta Masa agoshin sa bayan sa take bubbugawa anatse.

Nisa ce cikin farin ciki ta rungume Dr Ammar tana Furta welcome back Yaya A,cikin farin ciki Shima ya rungume k'anwartasa yana Furta thanks you dear

Cikin farin ciki Mai yawa na ganin junansu.

Dukkaninsu rangama sukayi cikin had'add'un motocin su, mota d'aya suka shiga Dr .Ammar da Aj sai hajiya a front seat wadda mahir ya tuk'o su sai Kuma sauran motocin su Nisa da su Ummi,suka shiga sauran motocin wayenda fadawa suka tuk'o da sauran fadawan da suka zo rakiya.

A motar su Dr.Ammar kuwa hajiyace take ta tsokanar su tunda sun dawo gida sai afara maganar Neman Aure Dan ita Kam duk sun mata tsufa,sai dai Dr Aj ne kad'ai ke tanka mata, cikin Jin haushi ta Furtawa Dr Ammar "wai Kai bak'in likita me ka taka ne waih yau,takai karshen maganar tana rike hab'a, Murmushi kawai Dr.Ammar yayi Yana Furta hajiya mezance Miki , uwar harara ta gallara Masa ta cikin madubi wadda tasanya dukkaninsu dariya har mahir Dake driving,A hankali Dr .Ammar bayan Lumshe idanunsa ya Furta dama danki ta ku rani kikace dole atare zamu koma gida ko,nikam zan k'ara maimaita Miki kin min tsufa sai dai daga nesa, hajiya mere Bakinta tayi tana Furta Allah wadaran naka ya lalace ta cigaba da Jan charbinta batare da ta k'ara Furta masa wani Abu ba, dukkaninsu murmushi sukayi kawai.

Tun dosowar su Babbar masarautar suke Jin tashin busa da algaitu aciikin fadar dan Dr.Ammar ya ce Baya son algaitu su bisa har airport shiyasa aka dakatar dasu cikin masarautar kawai,kid'in gangane ta ko Ina ke tashi,wangale musu k'aton gate din masarautar ne ya basu damar shiga daga cikin Babbar masarautar,jama'ace ta ko Ina fadawa da sauran ma'aikatan ma'ana bayin Dake masarautar,ma'aikatan kowanne Sashe sun fito tundaga sashen Fulani,hajiya,fada,Yaya Mustapha, Muhammad (malan) da sauran dangi,kowa na tsaitsaye a compound d'in masarautar Jiran dawowar yariman masarautar,shigarsu ciki yabada damar fitowarsu daga cikin motocin su.

 had'add'iyar carpet ce Mai taushi aka shimfid'a wadda zata sadaka da sashen Unni,wadda yarima zai hau aka rubuta ur welcome ce shimfid'e agurin, a hankali Dr.Ammar ya d'aura had'add'iyar k'afarsa akan carpet din shida Dr.Aj ma'aikata ne ketayi musu gaisuwa ta hanyar bow,ta hanyar sunkuyar da kansu su d'ora hannayensu akan goshin su hannu d'aya bisa d'aya irin yadda Yan Korea Suke Yi a historical films nasu,hannu kad'ai Dr.Ammar ke d'aga musu shida Aj Har suka shiga Babban falon Unni gaba D'ayan su har su hajiya dasu Nisa,sarki Ali Dake tsaye a Babban falon shida Dady soja ne suka mik'e suka rungume "Ya "yan nasu cikin wani farin ciki sarki Ali ne ya furtawa Ammar Barka da dawowa k'asarka ta haihuwa nayi farin cikin ganin ka Kai da d'an uwanka...Kai Dr Ammar ya d'aga cikin farinciki a hankali Kuma ya furta I 'm sorry Yaya Dady cikin farin ciki sarki ya Furta shiii alamar yayi shiru su. Sun Dade rungume da junansu cikin shauk'in soyayyar D'a da mahaifi,sarki Ali ne ya fara jaye jikinsa daga na Dr Ammar Yana komawa yayi kissing din hannun Ammar din,haka yakoma ya rungume Dr.Aj cikin farin ciki,Shima Dady soja rungume Dr Ammar yayi cikin farin ciki bayan sakin aj Yana Masa barka da zuwa.

Bayan dukkaninsu sungama gaggaisawa aka d'unguma ga gaba d'aya zuwa babban dining Area Dake falon,Nisa ce agefen hajiya tana facing chair din Dr Aj ita Kuma sumy tana a kusa da masoyinta Yaya mahir,sarki Ali da Dady soja suna akusa da juna Unni da Ummi sun Saka Husna atsakiyarsu,sai Dr.Ammar Akusa da Dr Aj Yaya Yusuf da Abdallah ma suna agefen hagun hajiya, dukkaninsu Bismillah sukayi bayan kowa yazab'i Abunda yake so ma'aikatan sunyi saving dinsa.

A hankali Suke cin abincinsa Babu motsin da Kake Jin sai na k'arar cokulla da sautin fillet,Dr.Ammar ne Dake cin had'add'iyar basmatic rice wadda taji had'i na musamman,Wanda Unni ce tayi kokarin Had'a Masa ita kasancewarta d'ai daga cikin

favorite dinsa, kamar ance ya d'aga idonsa yahango k'anwartasa Abar k'aunar sa Nisa ta Tsurawa sashen da Suke da ido Ahankali ya bi inda take kallo da ido Dan yasan dai bashi take kallo ba dan ya tab'a Jin sumayya nagayawa Aj n irin son da yuhanis din ke Masa Kuma agaban sa ma yasha Furtawa sumyn baijin komai akanta tunano da maganar da Aj yayi suna India ,ya yarda cewa k'ila jarabawar k'anwarsa ce kenan kamar yadda Dr.malini take ta wahala da soyayyarsa,Amma shi ko kad'an bayajin soyayyar ta aransa,sunan Dr.malini ne da yashigo kansa yaji tausayinta ya kamashi abin cin ne ya gunduresa na tausayin k'anwarsa,A hankali yazare hannunsa dake rik'e da spoon,Lemu ya tsiyaya A hankali kurb'a biyu yayi Yana mik'ewa,mik'ewar sa tsaye ce tasanya Aj kallon sa da mamaki Dan yasan badai k'oshi yayi ba,cikin yaren India ya Furtamasa "wai harka k'oshi ne "kai kad'ai Dr Ammar yad'aga Masa ya juwarsa Yana furtawa Unni "Nurul hayat natafi inyi fresh up,tambayar sa tak'arayi ya k'oshine ko Akai Masa d'aki dan batasan tambayar ce Aj yamasa ba,eh" ya furtamata atakaice cikin tattausar murya wadda mahaifiyarsa kad'ai kesamun irin wannnan sautin,juyawa yayi yaci gaba da tafiyarsa batare da ya tamkawa hajiya Dake jansa da wasa ba,har ya b'acewa ganinsu yanajin sautin Muryar hajiyar na fad'in kayiwa ubanka Mustapha Dan murmushi kad'ai yayi Yana girgiza kansa,Yaya Mustapha da shigowarsa falon kenan cikin yar dariya ya Furta hajiya me Kuma muka aikata daga dawowarmu yau,kawar da kanta tayi gefe irin Jin haushin nan tana Furta barni da ja 'irin wai ni zai kyale Ina magana Dan shegantaka to ni nama fasa Auren,dukkaninsu dariya suka Sanya,rigimar hajiya da Ammar akwai abun dariya aciki,duk da Baya kula ta ma.

Mik'ewa hajiya tayi Dan dama tagama cin abin cin ne ta k'oshi tare da barin gurin.

Aj da tun d'azu yake lura da irin kallon da Nisa ke Masa ne yad'an kawar da kansa bayan d'an k'ara nazartar ta da tabbatar da zarginsa arai akan tabbas wannan shine dalilin da yasanya Dr Ammar Barin wurin Dan ya tabbatar ba k'oshine ya tadashi ba yasan yadda yake Baya wasa da cikinsa musamman Abunda yake favorite nasa,k'ara d'ago kansa yayi inda karaf idanunsa sai a cikin na Nisa da duk Rabin hankalinta nagunsa,kasa dauke idanunsa yayi sai dai suka cigaba da kallon junansu Babu d'auke ido,Nisa ce ta Yi karfin halin sauke nata Idanun k'asa cikin yar kunyar data kamata,duk abun nan da ke faruwa atsakaninsu Babu Wanda Bai luraba duk su Unni sungani dasu Dady soja,sumy murmushi kad'ai tayi tana fatan Allah ya karkatowa Nisa Hankalin yya Aj,Dama tasan dole zai so Nisar Dan ayanzu kosu kansu sunsan suncika manyan 'yan mata dan duk wata halitta Dake jikiinsu tak'ara Bayyana tasan duk chan Baya fad'e yake Yi bata cikin tsarinsa tasan cewa Dan baiganta bane ayanzu....

Shima Dr Aj kawar da idonsa yayi yanajin nauyin Had'a idon da sukayi da sarki Ali Lemu ya kurb'a a hankali sannan ya mik'e Shima yabar kan dining zuwa sashen su,Murmushi kad'ai sarki Ali yayi bayan wucewar Aj din tare da girgiza kansa.

Nisa da keta ya mutsar abincin Dake gabanta da cokali na Rashin jinta comportable tun lokacin da Dr Aj yakamata tana kallonsa,itama tayi tsam ta bar kan dinning din, sumy dake k'unshe dariyarta ce ta furta jirani Nisa,isko ta tayi inda take tsaye Sannan suka cigaba da tafiya tana tsokanarta da Mrs Al Amin, Murmushi Nisa keta saki Jin sunan da Sumy ta Kira ta dashi bayan isarsu d'akin Nisa ne sumy keta sakin dariyar da take k'unshewa abakinta tana Furta" wai Nisa Kinga irin kallon da Yaya Aj yake Miki duka fa su Ummi sungani Allah ma ya rufa muku asiri hajiya tabar kan dinning yau da sai kunji kunya ba yar kad'an ba Dan Nasan intafara tsoakanar ku takai karshen maganar cikin sakin karamar dariya.....

'Nabani Nisa ta Furta tana d'ora hannayenta biyu akanta sai hawaye yanzu kenan duk su Unni da Abbah sun ganemu hawaye kuwa sai k'ara kwaranya Suke Yi A

idonta,lallashinta sumy farayi tana Furta mata "aikin ma jidadi Nisa hakan komai zai zo dasauki bakyaso kowa yasani ne kamar nida Yaya mahir,Kinga hakan cikin sauk'i sai a Aura Miki Yaya Aj sai ki zama Mrs Al AMIN JM SOJA dariya ce ta sub'ucewa Nisa wadda tasanya kyawawan dimples dinta bayyana masu yanayi da na Dr Ammar cikin murmushi da yar k'aramar dariya kamar wata yarinyar yar Sha uku ta Furta wa sumy " hakane Kuma fa Aunty sumy"

K'aramar harara sumy ta sakarmata tana Furta yau Kuma nak'ara samun auntyn dariya suka Sanya. sannan suka cigaba da hirar su sumy nabata shawara yadda zata janyo Hankalin Yaya Aj kanta asauk'ak'e.

A b'angaren Dr Ammar kuwa tun bayan shigarsa had'add'en d'akin nasa da yaji kayan more rayuwa Wanda yaji white paint da pink k'aton falo ne Wanda yakusa girman falon su na India acikinsa akwai kitchen,da store sannan akwai d'aki biyu Jere da juna Babbar Tv ce ta kamfanin Apple jingine a bangon falon wadda takusa cinye Rabin bangon sai kujeru na Alfarma farare k'ar sabbin zubi da akayi musu,sai labulayye pink colour, sai d'an karamin fridge Shima agefe,
d'akin batarkace ko Ina sai k'amshi ke tashi ko Ina musamman turaren mamallakin d'akin Wanda yakasance kamar dashi aka Gina d'akin sabo da yadda ya kamsashe d'akin da kamshi Mai dad'i, ga sanyin a.c da yak'ara wa d'akin yanayi Mai dad'i.✍

□□□□□

A hankali yake takonsa har yakai k'ofar bedroom nasa d'ai daga cikin k'ofofin Dake ajere yabud'e inda wani daddan d'an k'amshi yaziyarci hancinsa da yasanyasa Lumshe manyan idanunsa Yana sauke su acikin had'add'en bedroom din nasa,Bedroom nasa Shima babbane d'aki ne Wanda yak'unshi makeken gadonsa da wardrobe Mai aiki da controller da taji madubayye ta ko Ina sai walk'iya takeyi kayan d'akin milk ne Shar har labulayye d'akin Masha Allah komai yaji zam zam.

Da shigarsa d'akin ya fara rage kayan jikin sa guntun wandon sa kad'ai yabari.

wani lafiyayyen towel fari k'ar Mai taushi ya jawo bayan bud'e sip din tasa ta hanyar yin amfani da controller nata,A K'ugunsa yadaura inda towel din yakara haskaka surar jikin sa wadda ta Bayyana ta k'ak'k'arfan namiji Mai jini ajika dogo Mai siffar k'arfi kamar d'an wrestling six spacks dinsa sun Bayyana irin na tiger shroff,kayan da yacire ne direct ya wuce dasu toilet,toilet din Masha Allah Shima ya had'u ba kad'an ba fankacece guda,Dan Yana yanayi da na gidan su na India. Kayan yasanya acikin washing machine nasa k'irar k'asar Chinese,busar dasu yayi bayan sunyi tass Dama bawata daud'a ce dasu ba,wankansa yayi acikin had'add'iyar shower dinsa wadda ko Ina tana iya isko ka tare da wanke kwantacciyar sumar sa Mai laushi, wadda gyara ya ratsa ta da sabulu Mai Sanya k'amshi,sannan yak'ara d'auro wani Sabon towel pink Dake mak'ale a hanger d'in toilet d'in,cikin d'ai daga cikin had'add'un towel d'in Dake mak'ale agurin tare da d'an k'aramin towel Wanda yake Dan goge kansa.

Kayan da ya wanke yad'auko a hannunsa da'ya,d'aya Kuma rik'e da towel din da yake goge kansa dashi,Bayan ya fito ne ya a je kayan akan had'add'en gadonsa k'irar Italy.

tsaye yake akan Babban mirror n Nasa Yana goge sumar kansa wadda take Shan gyara Ako da yaushe,Bayan yagama shafe kannasa yasanya Masa mayukkan Dake Jere birjik akan madubin nasa na gyaran Kai masu tsada bayan taje sumar inda take kuwa tad'au shekiyi gwanin burgewa Bayan ya gyara kan nasa yajawo mayukkansa na jiki masu tsada wayenda ke k'ara haskaka chocolate colour skin d'insa,yashafa

adukkanin sassan jikin sa, kyakkyawar fatar sa sai shek'i takeyi gwanin burgewa ko Ina lui lui Masha Allah tafen hannayen sa da k'afafun sa sai walk'iya sukeyi,tsadaddun turarrukansa yajawo ya feffesa na body spray masu dad'in k'amshi,man bakinsa ya shafa (lipsbalm)Wanda ya K'ara haskaka kyakkyawan pink lips dinsa,tare da kyakkyawar fuskarsa Mai cike da kwarjini gwanin burgewa.
Bayan yagama'yan gyare gyarensa da yan shafe shafensa,Ya Sanya kayan da ya wanke acikin sip din sa bayan ya bud'e ta,domin shi mutun ne Mai tsafta Baya son ganin kowane irin tarkace a inda yake,yasansu agefen da ake mak'ale kayan da ba ayi ironing nasu ba.

kayane birjik a cikin wardrobe d'in tun daga kansu vest da panties na maza da short trouser,jeans da t-shirt da suit sai, harda sashen da towel Suke da handkerchief,sai kayan mu na Hausa tundaga kan kaftani shaddodi kala kala irin su gizner,meter d.s ,da yadudduka zubin k'asar Morocco,dakuma had'add'un huluna kala kala duk Wanda kuka San maza na sakawa Babu Wanda babu agurin komai atsare gwanin burgewa abun ba,a cewa komai sai Wanda ya Gani.

Wani tattausan yadi ash colour ya Ciro mara kauri da farar vest da short din sa black..shirinsa yake Yi Ahankali cikin yadin inda ya fito tsaf kamar kasace sa ka gudu dashi kyakkyawar fuskar nan tak'ara haske kamar tauraro acikin taurari idan ka kalle sa Sau d'aya sai k'ara saboda yadda yadin ya k'arbe sa yayi fitting din sa sosai kamar wani ango.

Towels d'in da yayi amfani dasu ya Sanyo acikin washing machine bayan ya ciresu.

Turarrukansa masu k'amshi yak'ara fesawa ajikinsa Yana k'ara Duba kyakkyawar fuskar sa Dake ta shek'i acikin madubi ganin yadda yadin yazauna ajikinsa kasancewar baicika Saka irin wayen nan kayan ba,lakace tsinin hancin sa yayi da dogon ya tsarsa najin wani yanayi Dake shigarsa na farin cikin dawowar sa ga ahalinsa gaba d'aya Yana sakin wani narkakken murmushin da yakusa sumar dani.□ □□□

Kai fa'eeh Arage k'arya haka□□

Ai shi gida na da banne..✍✍
Yo dama ai kowa yabar gida gida yabarsa
A halinka sune komai naka malan a duk inda kaje ka dawo sune dai...

Nigeria k'asar mu tagado muna cikin ta har .....□□□□□□□□□□□□yau da Banda gobe but wani sati zamu koma india😂😂😂😂

Allah kayafe muna□□

Maman Abbah
Maman Muhammad
sis Ayeesha Abdullahi
Ina godiya da kulawar ku Allah ya bar k'auna ✍□□□□□□□□□□❤

If you have any questions
U can chat me on my telegram account
Via dis number
0806905946

Kuyi comment please
Kuyi sharing
Kuyi like.□□□

□A MAFARKI NASANTA□
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Firstlady □□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

*Pen*is migthier than the sword **

Free □

EPISODE1
PAGE47

Idan Baki karantaba ki fara kar abaki Iabari yar uwa,littafin □□□
□□□AMAFARKI NASANTA □□□nadabanne Dan haka nake k'aunar wannan book d'in kasancewarsa haka da yanayin siffar littafin da yadda yazo mini nida masoyansa...✍✍
Inkimason ki tabbar da zancena kawai ki fara bibiyar alkalamina✍✍✍
✓✓✓✓✓✓✓✓✓

TYPING□□□

\\\\\\=\\\\\\=\\\\\\=\\\\\=\\\\\\=\\\\\=\\\\=\\\\\

A b'angaren Aj Shima Bai zarce ko Ina ba sai A bedroom dinsa D'ayan d'akin Dake kusa Dana Dr.Ammar...
Duka yanayin d'akin nasu d'aya ne sai dai kala ce ta banbanta,nasa kayan d'akin purple n lighte da labulayye purple masu haske,wankansa Shima yadauro tare da Alwallar sallar azahar.

Dr.Ammar ne ya fito cikin Shirinsa anan falo ya tarar da Dr.Aj da har ya yashirya cikin blue yadi,da hula jaddara black Mai kyau, da takalmi bak'ake irin na Dr.Ammar.

Kallonsa Dr.Aj yayi Yana tab'e Baki na Rashin ganinsa da hula Bai Yi mamaki ba Dan yasan dama tun suna k'ana bayason Sanya hula akansa acewarsa takurasa takeyi wai.

Cikin tafiyarsa ta mazan jiya ya Furta"kataso muje ko in wuce in barka nan Yana maganar bisa ga har yakai bakin k'ofar fita falon,Aj Dake zaune akan cussion speechless ya Furta "tafiyarka cikin Jin haushin sa,Dan tun d'azu yake jiransa duk da yasan cewa Yana chan Yana shiriritarsa,ganin cewa ya rigasa tasowa dining amma har yanzu Bai shiryo ba.

Hararar bayan sa Dr.Aj yayi tare da tasowa ya biyo bayansa.

Shikuwa Ammar murmushi kad'ai yayi Yana Ida ficewa daga falon,fitowar Aj tasanya Dr Ammar Dake jiransa su wuce tare abakin k'ofa.

Dr.Aj da ya fito ne yayi kamar baiga Ammar ba yacigaba da tafiyarsa,murmushi Dr.Ammar yak'ara saki ganin Abunda Aj yayi Masa,Shima Bai kulasa ba kawai yacigaba da tafiyarsa,har suka jera atare suka Isa Babban falo.

Koda Suka iso falon sun tarar da su Hajiya dasu Unni zazzaune su Dady soja dasu Mahir,Abadallah duk sun wuce masallacin
Gaida su sukayi,sannan suka wuce masallacin fada inda dama already kowannen su yad'auro alwallar sa Dan gabatar da sallar azahar.

Bayan dawowar su daga masallacin sun tarar da mama dije ta iso daga garin Kano itada Inayah,su Nisa sunyi farin ciki sosai da zuwansu.

Mama dije ce bayan tayi masu Ammar Barka da zuwa take tsokanarsu,yanzu Kam tunda andawo gida samarin Aunty sai afito da matayen Aure tunda Allah yakoro muna ku,Dan haka take kiransu dashi inzatayi musu irin wannan wasar sbd gimbiya Laila..,takai karshen maganar tana sakin yar dariya..

Cikin yar dariya Dr Aj ya Furta Aunty dije kizab'o mana matayen kawai Dan duk cikin mu nan babu mai budurwar bare Akai ga mag...yakai k'arshen maganar Yana susar kansa bayan yad'aga hularsa irin na Jin kunya tare da sakin yar dariya...

Dukkani dariyan sukayi ta maganar Dr.Aj,shiko Dr Ammar ko tankamata baiyi ba Bai nuna yasan abun da ake magana ba afalon ko mama dije tayi magana, Hajiya ce ta Furta"Kai kafi k'arfin ka amsawa uwar taka,shegantakar taka har ta shafi uwayenka takai karshen maganar tana hararsa ..

Murmushi kad'ai yayi daga jinginen da yake akan hannun kujera batare da yabawa hajiya Amsa ba sannan A hankali ya Furta "Aunty dije kibar hajiya lokaci na zuwa"
To Allah ya nuna munashi lafiya ta Basa Amsa,Amin dukkaninsu suka Amsa. murmushi tayi Jin ya Furta tabar hajiya..
Hajiya kuwa wata uwar harara tasakar masa tare da kyab'e Baki tana cigaba da Jan charbin ta murmushi dukkanin su sukayi na hararar.

Inayah ce da yanzu ne fitowarsu daga d'akin Nisa ta rugo da gudu ta rungume Ammar cikin farin ciki tana Furta sannu da zuwa Yaya A,Amsa mata yayi da yawwa cikin sakin fuska har da yimata Yan tambayoyin kulawa.
Gurin Dr Aj takoma Shima ta rungumesa tana Masa sannu da zuwa cikin farin ciki kamar yadda tayiwa Ammar shima Yan tambayoyin yayi mata na nuna kulawa agareta.

Bayan takoma tazauna ne inda su sumy Suke ne yad'aga idonta sai acikin na Abdallah wani irin mugun kallo yabita dashi na kishin rungumar da tayiwa yayyen nata,kawar da kanta kawai tayi fahimtar kallon da tayi mata.

Aj ne ke kallon sashen da su Nisa Suke,shi har mamaki yake,magana yake azuciyarsa shin wai har yaushe sukayi wannan girman,girman su yabasa mamaki Dan sun Dad'e basu lek'o Nigeria ba, duk da suna video call dasu Amma ganinsu azahirin girman da sukayi na Fili yabasa mamaki matuk'a....

To kabasu mamakin su man□□□😂da tsegumi😂😂😂😂□

Saurin kawar da kansa yayi Bayan kallo ma kansa da yayi tudun Yan madaidaitan breast din Nisa da suka taso akan akan doguwar rigar tata ...

Dr Ammar Dake kalle dashi ne ya girgiza kansa kawai Yana sakin murmushi Akai kaice tare da yiwa k'anwarsa fatan samun soyayyar Abokin nasa Kuma d'an uwansa.

Firar yaushe Gamo suka cigaba da ita ga ba d'ayansu,Anan sarki Ali yasanar da ginin Babbar Asibitin da ya gimawa su Ammar D'in dukkaninsu sunyi farin ciki sosai,har su Unni da suka San da maganar yasanar musu wani sati za'a bud'e Asibiti..

>>>>>>>>>>>>><<<<<<>>>>>>>>>>>>>>>> Ranshi ab'ace yake magana ta waya da Wanda ke akan layin Kiran..ya akayi Baku same su ba kuka bari suka sub'uce muna, wannan maganar banza ce ace operation bai yuyu ba,tun farko sai da nasanar muku tun A Airport ku farmaki Yan banzan ku kashe min su shida Mahaifin nasa,ta D'ayan b'angaren ne aka Furta masa Ai uban nasa Bai je hililln jirgin ba,inda Muryar wani bafullace ke fidda wannan sauti cikin yar damuwa da b'acin Rai..
Ta D'ayan B'angaren malan ne yak'ara furta yanzu kenan wannan damar ta sub'uce muna mun Rasa wannan Babbar damar yakai karshen maganar cikin kunar Rai kamar kamar zaiyi aman wuta.

Shima bafullacen ta b'angaren sa yak'ara Furta "arado oga baka ga manya manyan shojojin Dake a Airhort ba, 😂wai Airhot
Kashan bamuje da yawa ba mu biyar kad'ai muka she dagani shai k'ira da jan maje da Mai Adda,da zarto,Dan bamuyi jaton zashu mana haka shojojin arado baka ga makamanshu ba, shunfi namu arado Kuma anzuba shu gurin da yawa kamar shuna gadin wani agurin..

Cikin b'acin Rai ya da d'aga murya ya Furta " wai su wane ne Suke muna zagon k'as a suwaye,duk wani shiri namu suna kan gaba suna rusa muna shi,suwaye muna zagon k'asa Mai muni agare mu ya iyar da maganar cikin k'araji tare da Yanke Kiran...

My team yayi dialing cikin b'acin Rai... bayan d'aga Kiran ne muryoyin su suka fara Bada sauti cikin tashin Hankalin Jin muryarsa Jin Ya Furta kusameni gidan shak'atawa

ta yanzu,oga lafiya dukkanin su Suke tambaya inada ya Yanke Kiran batare da yabasu Amsa ba...

Ko minti ishirin ba'ayi ba,sai ga wasu aranayen jif sun shigo gidan bayan wangale musu da aka Yi,parker motocin sukayi a inda yadace.

Babban falon dukkaninsu suka dosa cikin tashin hankali na Rashin sanin Abunda Yafaru Wanda sak'e sak'e yadabaibaye zuciyarsu na dalilin Kiran gaggawar da yasame su...

Samunsa sukayi tsaye ya rungume hannaye abayansa Yana sabbatu shi kad'ai
Yana Furtawa shin wannan Mai muna zagon k'asa taimakon mu yake Yi ko cutarmu,a iya binciken danayi su wad'annan Yan sandan da muka kashe kosu basu San dalilin dayasa aka sanyasu k'one gidan ministan (S.I.C) ba da iyalansa
Sun dai bi umurnin sane kowaye tabbas akwai Wanda yakeda sirrin mu Bayan (S.I.C) minister,dole muk'ara tsaurara Al amurranmu...

Minister iyaka Muradi ne Dake da mugun tsoro ya Furta cikin d'an tsoro da tashin hankali kardai ace fatalwar minster Umar ce tadawo Dan d'aukar fansa duk da bamu muka k'onasu ba,dukkaninsu dariya suka Sanya duk da tashin hankalin da Suke ciki Banda malan,Dan maganar tabasu dariya

Senator Jamil Babuga ne ya Furta haba kaiko minister aimu ko fatalwarsa tadawo muba Abunda zata Yi muna Kai zata Nema tunda kaine d'an rahoton mu Kai ne Mai yimusu kutse da lamarin su Kai da captain Anas Lemu yakai karshen maganar Yana dariya,Shima Captain Anas dariyar yayi Yana Furtawa senator Jamil ai za,a fara dakai Dan kaima Mai laifine,Emir Kabir Saraki ne yadakatar dasu tahanyar Furta ba wannan ba,yanzu dai oga meye abunda ya faru...

Cikin d'an Yana Yin hasala malan yazayyane musu komai Akan farmakin da yasanya Akaiwa Sarki Ali Da Dr Ammar,inda yasanar musu sojojin da akace anbaza awurin Wanda shikansa abun yad'aure Masa Kai na tunanin ubanda ya turo sojojin,dukkaninsu sunji faduwar gaba sosai musamman captain Anas Lemu Dan basu Yi zaton haka ba,Kuma tabbas da gaskiyar ogan nasu akwai wata ak'asa duk agamata tabbas akwai Wanda yasan da Shirin ogan nasu,duk da kosu bai sanar musu da Shirin ba,Dan bazasu manta da yadda wanchan karon aikin da suka Bada da hannunsu ya chanza ba..

TWENTY TWO YEARS BACK ....
WAIWAYE ADON TAFIYA...

A chan Baya...

K'ungiyar "Yan taadda ce da tayi shura ajihar zamfara dama wajajen zamfara ma'ana k'auyukkan zamfara,wadda kusan kullum sai an watsa labarin sunkashe mutane sun tada k'auye,sun sace dabbobi da dukiyoyin Al umma sannna sunyi kidnapping na bayin Allah,Ako dayaushe fama akeyi dasu har yanzu Allah Bai kawo k'arshen su ba..

A bunda ya faru achan Baya.....

Cikin k'ungurmin daji ne da ya kasance d'ai daga cikin manyan dazukkan Dake cikin jihar zamafara Wanda Namun Daji kad'ai ke rayuwa agurin ada, Wanda a yanzu Kuma b'arayi suka maidasa mafakarsu,suna rayuwa aciki su wayen nan "Yan ta daddan.
Zazzaune Suke akan wasu kujeru su biyar oga Afarkon layi,sai senator Jamil Babuga da captain Anas akusa dashi,sai emir Kabir Saraki,sai minister Isyaka Muradi,dukkaninsu face mask ne afuskar su sai wasu irin mutane dazasu Kai dubu yawansu kewaye dasu da manyan bindigogi da sark'okin albarushi shigarsu Babu kyan gani kowa yasha uban rawani kamar wasu sarakuna wasu bula wasu bak'i sai warin suke tashi agurin da warin tabar da Suke zuk'a da ya garwaye wurin Babu dadin shak'a..

Shigace dai Dake nuna alamar su tazamansu Fulani da zabarbarbawa,wasun su sun Tara uban gashi kamar ka kitse sa kamar dai yanayin mutanen Mali,gasu nan dai ba maganar kallo biyu saboda in ka kalle su har wani mazari jikinka zai dauka...

Oga ne yake magana,Yana Furta tabbas duk da yake d'an uwana ne zanyi maganin sa tunda har yanemi ya tona mini asiri a idon duniya ta hanyar bincikensa tabbasa bazan tab'a ragama Masa ba, duk abubuwa da na shanye akan gidan mu na wannnan sarautar datake mallakin mu wallahi bazan tab'a rufe idona akan wannan ba,tun lokacin da minister Isyaka Muradi yasanar Dani cewa sunyi akan wannnan k'ungiya binciken su zaizo kanmu Asirin mu Yana Shirin toniwa, Kuma duk Wanda aka bincike sa Asirin sa take yake bankaduwa a idon duniya,nayanke wa kaina da ya tona muna asiri,gara ayo mani kidnapping na D'an wana Umar da iyalansa in kashe da hannu na sannan in hau karagar mulkin dayake tak'ama da ita shida Wansa,wadda nadade Ina mafarkinta tun kafin rasuwar Mahaifina,Dan shiru yayi sannan ya cigaba da magana Yana kallon wayen nan k'azaman mutanen Ina ga sunyi Rabin shekara jikinus baiga ruwa ba saboda tsaabar warinsu... Na Baku damar ku shiga har fada duk yadda zakuyi ku yo kidnapping nasaa shi shida iyalansa,Amsawa sukayi da zaka ga aiki oga angama.

D'ai daga cikin su ne fuska ba annuri ya Furta ya mutsatsiyar hausarsa da ta Had'a da fulatanci "oga Koda Kisha ne ayi ko wayaso yashiga Sha kanin mu da aikin "
Kai malan yad'aga cikin Bada umurni, Bindigoginsu suka d'aga sama suna harbawa suna ihu Mai ban tsoro ...dakatar dasu Emir Saraki yayi ta hanyar Furta sai kunyi shiri Mai kyau Dan Shima minister Umar wayaune dashi,Amsa Masa sukayi da angama..

Buhuhunan kud'ad'en fansar Al umma ne da Suke k'arbo kwana kwanan nan daga gidan tsohon shugaban k'asa Dr Lukman Murtala Mon na fansar yayansa guda hud'u mata biyu mata uku wayenda akayi kidnapping daga zuwa biki ak'auyen Babban nasu da ya tilasta musu zuwa kasancewarsu Mai son sada zumuci Maison zama da Yan uwansa duk da yabar su achan Yana taimakonsu da biyarsu..

Buhu shida suka jawo na Yan dubu dubu b'arayin suka jawo suka ajiye atsakiyarsu oga Anan take aka zazzage kud'ad'en ana n gurin oga yakasa Kashi bakwai su Kashi d'ai d'aya Yan dabar Kashi biyu,sai na sayen sababbin makamai Kashi d'aya na informer Kashi d'aya ak'alla kowannen su yatashi da million ishirin ishirin,Sauran tumaki da dabbobi suka bar musu amatsayin k'arin ganima agare su murna sukayi sosai ganin tarin dukiyar da aka bar musu..

Bayan watsewar Taron ya ta addan suka fara shirye shiryen shiga fada Banda gobe...

Sai dai Abunda basu sani ba duk wani Abu dasuka tattauna ayanzu Yana recording awata "yar k'aramar na'ura Dake mak'ale a cikin agogon MALAN da matar sa tamasa kyautarshi...

Geng geng
Taufa Al amarin nan yafara rikicewa
Kaji wata sabuwa✍✍✍

Mudai Allah ya Yi muna tsari da wayen na. Ya taaddan Allah karka basu iKon Had'a hanya damu ka Kara kare mu

Mu had'u gobe in Allah yakaimu Dan Jin yadda zata kaya...

Kuyi hakuri ba editing cos am tired Kuma bana da lafiya Ina maneji ne kawai...

Like share pls and comment ✍✍✍✍

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Firstlady

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

P.E.W.A

Home of perfect essential writer's together we stand

ESSENTIAL WRITER'S

*Penis migthier than the sword *

Free

EPISODE1
PAGE48

Kuyi following D'ina A
Arewa books,@Fa'izatou
Wattpad @Fa'iza murai

TYPING

••••••••••Δ••••••••••••Δ••••••••••Δ••••••••••••Δ

××××××××××××××××××××××××××××××××
<<<<<>>><<<<<<<<<<<<<<<<<<<<>>>>>>

.....sun shirya tsaf Dan Kai farmaki a fada,sai dai sunyi Rashin sa,a domin a safiyar data kasance saura kwana d'aya su shiga fadar,suka samu labarin gobara ta tashi agidan minister Umar Wanda agidan babu Abunda aka fitar agidan harsu kansu sai dai gawawwakinsu da duk suka cinye da wuta.

Labarin ya riski oga agidan shak'ata warsa yashiga tashin hankali ma tuk'a domin yasan wannan ba aikin su bane ba shine Abunda suka shirya ba dan k'ara tabbatar wane yayi Kiran sauran Dan Jin yadda akayi,in su suka cinnawa gidan wuta tunda yabasu umurnin kisa,..

Bayan gama sauraren sa Babban b'arawon yasanar Masa da basu chanza komai ba hasalima su yau ko cikin gari basu shigo ba sun tsaya shirye shirye ne,yanzu Suma suka samu labarin wutar daga d'ai daga cikin informers nasu Dake cikin garin, daga nan ne suka Sanya dogon bincike harsuka gano wayen nan "Yan sandan nan guda biyar nada Sanya hannu acikin k'ona gidan sarki Ali Umar murai,minister of security and investigation crimes,har sukayi nasarar kamo Yan San Dan nan suka wahalar dasu ta hanyoyi masu yawa dan duk suyi bayanin dalilin Wanda yasanya su cinnawa gidan wuta dakuma wane ne shi,duk wahalar dasuka Sha kuwa basu sanar musu Wanda yasanya su ba da dalilinsa inda hakan ne yabawa oga damar kashe su duka wannnan kenan.

Emir Saraki ne bayan gama tunanin sa yasauke ajiyar zuciya Yana Furta yanzu dai muk'ara shiri Akan wannan mission d'in na gidan tsohon gwamna Alhaji mukhtar,cigaba da tattaunawa sukayi yadda zasu k'ara b'oye kansu wa duk wani Wanda yake Shirin Yi musu shigo shigo na shigo ba zurfi a alamurransu

A MAFARKI NASANTA DABAN YAKE DA SAURA

••••••••Δ••••••••••Δ••••••••••Δ•••••••••••••Δ••••

BUG

A b'angaren su Halee kuwa, A Ayau ne suka gama zana jarabawar karshe a secondary schl,ta fannin soyayyarsu da Dr.yusuf sai Abunda yak'ara yin gaba,Baba Asabe kuwa har yanzu tana nan tana cigaba yad'awa Halee maganganu tare da wahalarda ita da musguna mata cikin ruwan sanyi.

Yau takasance Lahadi Halee ce Gaban murhu cikin madafa sai faman hura wuta takeyi inda wutar tak'i kamawa saboda kasancewar makamanshin wutar d'anyu ma,ana itace,lu lu eyes dinta sunyi jawur na hayak'in da ke shiga cikin su.

Inna Asabe ce cikin d'aga murya take Furta ke Halimatu wai Dan Rashin mutunci har yanzu kina nan kina iskancin naki da son jiki tun d'azu hura wuta ya gagara eh! Yar iskar yarinya ke komai nasa ka ki sai kin mini shashan ci aciki..

Cikin sanyin jiki da sagewar gwiwa Halee ta Furta"Baba Itacen ne Basa ci"k'aton tsaki Baba Asabe tasaki tana Furta nabaki nan da minti goma ki Had'a ta inba haka ba wallahi sai na lakad'a Miki dukan tsiya agidan nan sakarya kawai Sha Sha tsintacciya yar gaba da fatiha ...har tagama zage zagen ta da fad'anta Halee bata d'ago Kai ta kalle taba,sai dai cikin ranta tana Jin zafin duk wata kalma ta b'atanci

agare ta domin dukkanin kalaman da ta Furta mata ayanzu kalamai ne da ta Saba dasu in dasabo sai dai haryanzu sune abubuwan da takasa sanyawa zuciyar hakuri akansu takanji matsanancin zafi aranta aduk ranar da Baba Asabe ta Furta mata su wasu lokuttan ko baccin kirki bata iyayi take Kuma nan ciwon ta sai ya tashi..

Bayan wucewar Baba Asabe ne tasanya kyawawan yatsunta tashare hawayen fuskarta na bak'inciki da Kunar Rai tana cigaba da huraa wutar har tasamu cikin Ikon Allah wutar ta ruru duk da Itacen yanayi Yana mutuwa inka kalle ta gwanin tausayi kyakkyawar fuskar nan tata duk ta yamutse,ga kwanciyar busashen hawaye nan afuskarta sai dai natsuwar ta da bata gushe ba in ka kalleta zaka ganta so calm kamar babu Abunda ke damunta arai ko yake ci mata Rai..

Khady da tashin ta kenan daga bacci ganin bata ga Halee a gafen ta ba yasanyata fitowa daga cikin d'akin Dan tasan tabbas tana nan tana yin bautar da ta Saba,tasan ko yau Baba Asabe sand'o tayi ta tada Halee d'in.

A hankali ta zauna gefen Halee a Cikin kitchen din wadda ta buga tagumi da a alama bata ma San da zuwan ta gurin ba,Halee Dake cikin dogon tunani Jin anjanye mata hannun a hab'arta yasanyata Duban gefen da Khady take zaune akusa da ita, Had'a idon da sukayi da Halee ne ya bawa hawayen Dake mak'ale a idonta damar fitowa na tausayin yar uwarta naganin yadda fararen kyawawan idanunta suka rune sukayi jaa kamar garwashe,hannu tasanya da sauri ta goge su gudun Kar Halee tagani,sai dai Ina ta makaro domin Halee ta lura da hawayen itama nata hawayen tashare a kaikace,cikin dauriya ta furtawa Khady
" har kin tashi " tausayinta ne ya K'ara kama Khady Kai kawai ta iya d'aga mata b tare da Furta mata komai ba.
Cigaba da hura murhun sukayi atare,Inna Asabe Dake tsaye tana kallonsu ne taja wani mugun tsaki Mtsww Wanda yasanyasu duban inda take tsaye Dan basu San da tsayuwarta gurin ba.

'cikin masifa ta Furta Khady "ke shalele uban wa yakawo ki nan eh"

Cikin tun zurar Baki Khady ta Furta "bakowa" tsaki Baba Asabe tak'ara ja sannan kamar an janyeta tabar wurin fuu tare da yiwa Halee mugun kallo.

••••••••••••••Δ••••••••••Δ••••••••••Δ••••••••••••••Δ

Few minute later in the moment

Baya sungama cin abincin su ne wayarta tayi k'ara
D'agawa tayi cikin yin sallama da zazzak'ar Muryar ta,A D'ayan b'an garen Dr.yusuf Shima k'arba mata yayi cikin farin ciki inda ya Furta " wa ailaiki Salam zaujati " wani kyakkyawan murmushi ta saki Wanda duka gab'b'ansa sai da suka Amsa,Dan tana mugun son ya kirata da wannan sunan,gaisawa sukayi irin ta masoyan nan da suka mutu cikin kaunar junan su,shiru ne ya biyo Baya bayan gama gaisawar tasu inda Ahankali ta tsinkayi muryarsa yana k'ara Furta

" Nurul Qalb na matsu lokacin Auren mu ya zo inganki Gani ga ki kina mun kallon soyayya da kyawawan idanun na naki,nikuma na Miki kallon k'auna" yakai karshen maganar Yana sakin murmushi Mai had'e da dariya.

Murmushi tasaki itama tare da Jin kunya ta Furta " ai lokacin Yana kan hanya ya kusa isowa"
 dariyar yayi sosai na furucinta sannan cikin murmushi ya Furta Allah ? Dagaske

"tabasa" Amsa

Cikin sakin yar karamar dariyar itama.

Cigaba da maganar sa yayi "Kinga yanzu in muka Yi Aure Hankalin ki zai k'wanta domin daga lokacin ko spoon bazaki k'ara d'auka ba nizan dinga girka Miki Abinci in rik'a ciyar Dake in shayar Dake da hannuna ,sannan in Miki wanka in shimfid'ar Dake kamar jaririn k'wai ke komai ma nizan rik'a yimiki sai dai kizamo miji na zamo mata Arik'a Kirana da Mijin Hajiya ....

Duk da kunyar da maganar ta Saka ta ji Bai Hana ta darawa ba saboda sabon da ke tsakaninsu domin kyalkyalewa tayi da dariya kamar ba Halee ba Dan ba kasafai takeyin irin dariyar ba,sai ayanzu da Allah ya jefo Dr .Yusuf cikin rayuwarta.

Firarsu suka cigaba dayi cikin nunawa junansu kulawa da soyayyar junansu gwanin burgewa.

Khady Dake kallon su Halee cikin burgewa ta Furta Azuciyarta itama Allah yabata Miji irin Dr yusuf Wanda zai rik'a nuna mata soyayya irin haka Dan su Halee Soyayyar su na burgeta.

GUSAU
Ayaune za'a yi Taron bud'e Babbar Asibitin .
Shiri na musamman akayi domin bud'e katafariyar Asibitin.
Dukkanin familyn sun hallara a masarautar don Taya murnar bud'eta,kowa kagani yaci ado na musamman tundaga k'anana har manya,girke girke akayi masu Rai da lafiya.

A b'angaren uwayen taro kuwa sun shirya tsaf,dukkaninsu sunyi kyau cikin wasu aranayen suit farare,musamman Ammar sai yazamo kamar wani tauraro acikin taurari duk inda ya wulga sai Anmasa kallo biyu,kyawonsa yak'ara bayyana kyakkyawar fuskar nan ta karayin wani kyau na musamman dogon hancin nan nasa yak'ara tsawo kamar biro chocolate skin d'insa tak'ara yin glowing na musamman,pink lips nasa Suma sai shek'i sukeyi na mask'in man Bakinsa,manyan idanunsa sun k'ara kyau sunyi wani haske kamar an musu wankan Madara sai k'yalli sukeyi acikin su kamar anshafa musu Mai Zara Zaran eyelashes dinsa sun k'ara k'awata idanun nasa kasancewarsu cikakku masu tsawo tare gyarar sa da take kamar anyi shaping nata, mai yawa da ita atsare,Masha Allah kad'ai zamu ce.

Su Nisa da sumy da Inayah sun Sha wani bugaggen less Mai shegen taushi Wanda yaji duwatsu ta ko Ina,su Unni ma less ne sukayi anko dashi su uku Ummi,Mama dije,Dady soja Shima ansha kyau cikin wani had'add'en yadi,sarki Ali Shima yadin ne ajikin sa sai wata had'add'iyar alkyabba da ya d'ora akan yadin sai walk'iya takeyi,su hajiya ma ba,a barsu abaya bah,dasu Yaya mahir,Abdallah da Yusuf kowa kagani yasha kyau.

Zazzaune Suke acikin katafaren filin Asibitin Bayan isowarsu ,komai atsare afilin da aka k'awata musamman yadda kasan wata sabuwar duniya.. sashen maza daban sashen mata da ban kowa an ware Masa gefen sa.

Manyan bak'i ne aka gayyata tundaga
Tunda sarakuna, shugaban k'asar mu na yanzu Mai ci Babanku😁Bola Ahmad tinubu,da Sabon Gwamna Dr.Bello Muhammad matawallen maradon da wasu daga

cikin manyan manyan gwamnonin Arewa, da sauran masu rik'e da muk'aman gwamnati tundaga tundaga kan Yan majalisa da ministota d.s.

Sai shuwagabannin Airforce duk sun halarta gurin Babu kakin da Babu agurin tun daga Sojoji, custom...

Sai shuwagabannin k'asashen waje America, London, China,Korea musamman sunzo Taya wayen nan gwarazan likitota murnar samuwar wannan Babbar Asibiti.

Sai Kuma abokan kasuwancin sarki Ali Dukkaninsu sun hallara A gurin na kasashe da dama Dan Taya sarki Ali Murnar Bude wannan Asibitin, Dukkanin wasu shuwagabannin na manyan asibitotan Dake k'asahen waje sunzo dakuma colleques dinsu Dr.Ammar na India dama na sauran k'asashe,k'ungiyar UNICEF itama takawo jiki Dan tayasu murna.

A b'angaren Dr.Malini bata samu damar halartar Taron ba,sai dai ta turo da sak'on Taya murna inda tasanar Mrs Arorah sigh ce bata da lafiya
Ma'ana matar Babanta.

A b'angaren mata kuwa manyan mata sun halarta,tundaga matar shugaban k'asa,matar gwamna,Mrs Bello Muhammad Matawallen maradon (Mon) Hajiya Hajiya Balkisu Muhammad da sauran matan gwamnonin Mak'otan zamfara kowa kagani agurin sai ka k'ara kallawa,K'ungiyar marubutan Arewa takawo jiki...Chan na hango *Perfect essential writers association*sun kawo jiki,su sister bareemat(Yan biyu macizai),oum Amjad,(Yan biyu)oum Maryam (Ina izzar take),Anty moon(Mijin bahijja),Dr teema,maman Abdallah(Yan kance) Autar Ammi (Aljannar ruwa ce) d.s.
Itama Haandy takawo jiki marubuciyar *Bahaar*
Chan Kuma na hango Boss bature (Abba Sojoji) itama ta kawo jiki tana gaisawa da fans dinta, Yan group na *NOVEL'S KINGDOMS* ma sunzo kungiya guda Dan Taya murna sun Sha Anko,Mai kyau,su sis Ayeesha Abdullahi,Maman Muhammad,Maman Abba,Zarah ibrahim,Jibril,ummu-Salma kabir gagara,Amina janyau,sahura Kabir gagara,Umaima Halliru,baby birnin gwari,Asama'u ibrahim,Halima Bashar da sauran su..in nace duka zan lissafo sunayen ku zan cika page din ne.

An gabatar da taro lafiya bayan bud'e taro da Addu,a tare da national Anthem,anyi jawabai na Bada shawara daga nan aka tashi aka bud'e Asibitin Mai Suna
NORA SPECIALIST HOSPITAL
Wadda Mai girma gwamna Dr BELLO MUHAMMAD MATAWALLEN MARADUN bayan gama Kaddamar da ita daga nan aka d'unguma had'add'en *HALL *Dake cikin *TAULA ARENA*Dake cikin Gusau d'in Dan gabatar da Dinner wadda k'ungiyar likitota ta duniya ta shirya musu Dan tayasu murna Gina wannan katafariyar Asibitin Mai kusan cin gari guda,Asibiti ce da ta k'unshi sassa daban daban tundaga sashen zuciya,sashen k'oda ,sashen kwakwalwa,sashen kula da fata,da dai sauran manyan sassa dama k'ana nan,sannann ta zak'ulo manyan kwararrun ma'aikata dga cikin jiha dama wajen jiha har ma da k'asashen waje,tundaga Doctors,Nurses, Pharmacist, Lab scientist,Public health practitioners da dai sauransu.

An k'awata gurin k'awa ta musamman inda aka manna k'aton hoton Dr.Ammar Da Dr.Al Amin (Aj)sun Sha kyau cikin kayan tiyata na likitota sun sargafe stethoscope awuyansu kowannesu yayi murmushi ya rungume hannayen sa ak'irji sun bawa juna baya,ku kwatan ta kyawon Da Dr.Ammar acikin kayan nan dan bansan yadda zan fasalta muku Shiba,b'ata biro ne ma zayyano muku domin kuwa yayi wata kalar had'uwa ta musamman...

K'aton cake ne ne Mai d'auke hotunan su Dr Ammar aka yanka inda da taimakawar gwamnan jahar zamfara Dr Bello Muhammad Matawallen maradon..anyankansa lafiya inda duk wani ruwa da tsaki sai da yakai bakinsa.
Nima dai na laso yar madarar sa d'in Dana Gani ta mak'ale agefen wata Leda..□□

Anci ansha Agurin Taron,komai gashi nan save your self sai ka zab'a abun da kake so ,agurin Babu kalar Abunda babu sai Abunda Allah yaharamta ci da Sha,Abinci ne kala kala tunda ga kan snack har zuwa sauran girke girke.fannnin lemuka ma gasu nan zube a fridges ba,a cewa komai sai ka zab'a ka darje
,Chan na hango muku Sis Ayeesha Abdullahi Ana ta fisgar nama ansamu Banza...😀
"Yan *GIDAN NOVELS KINGDOM*
Suma ana ta faman ya mutsar hak'ora kowa nata bawa ciki hakkinsa wasu harda Sakawa acikin jaka😂😂 irin su oyi..✍✍

Nima Kam Mai d'aukar rahoton Dana Kai kaice idanun jama'a na Yi maza na cika jaka ta,yo waga banza yak'ita□□□□□😂

Kowa kagani agurin cikin farin ciki yake musamman wannan family Unni Da Ummi dasu hajiya bakin su yakasa rufuwa.

Daga nan aka fara basu gifts na musamman sun samu kyauta Mai yawa wayenda bazasu lissafu ba,tundaga kan manya motoci, gidaje,inda Shima shugaban k'asa kafin tafiyarsa yayi announcement ta hannun protocol nashi,inda yayi Alkawarin zai Sanya hannu gurin Biyan ma'aikata,tafi ne ya tashi cikin hall din raf raf da sound na wooww na farin ciki,inda daga nan UNCEF
Itama tayi nata announcing na mak'udan kudaden data zube da K'ara taimakawa mata da k'ana nan Yara da sauran marasa lafiya,Kuma ta tabbatar zata kafa nata reshe na k'ungiyar ta acikin Asibitin dan k'ara kulawa da Yara da mata..tafi aka Kara d'auka bayan koma Jin wannan abun alkahirin,wata sanarwar ce tak'ara dakatar da mutane daga yayar dasukeyi na wayen nan kyaututtuka ta His excellency Bello Muhammad Matawallen maradon inda yayi Alkawarin Gina sashen marayu da kula dasu acikin Asibitin wowwww Allahu Akbar shine Abunda ke tashi a hall din tare da tafi,A hankali Suma manyan masu kudin dasuka halarta sukayita kawo tasu gudun muwa..
Sarki Ali Da Dr.Ammar Da Dr Aj sun tsinci kansu cikin farin ciki Marar misaltuwa domin ayau idan kaga Dr.Ammar baza kace shine ba yakara yin wani kyau na musamman kasancewar yau fuskar tasa asake take tana ta wanzar da murmushi Mai Kara k'awata fuskarsa,inda Yan mata kuwa kamar su zubda eyes nasu wurin Kallonsa inda shi ko d'aya Bai Gani ba acikin su,ko ince Basa gabansa..cikin su Harda Sis Ayeesha Abdullahi da ta mace kansa.😂□□□□□□□

Subhanallah zoku ga hajiya bakinta kamar gonar auduga harda Yan guntun hawayenta,Unni da Ummi sai hamdala sukeyi azukatansu,su Nisa ba'a magana.

Daga nan aka Sanya kid'a Mai taushi Wanda ko baka Yi niyyar takawa ba sai motsa Koda kafar kace yadda kid'in ke ratsa jiki,chan na hango Anty Moon Ana d'an Rausaya Kai kamar k'adan garuwa...
Musamman Aka Kira *A MAFARKI NASANTA FANs*ma'ana *NOVELS KINGDOM* Suma suka baje suna ta bankan rawayar su,Nima dai na D'an motsa k'afata daga gefe..

Bayan and'an chashe sannan aka rufe taro da Addu'a tare da yin jawabin godiya,taro yawatse lafiya Lau,manyan bak'i Already dama dare yayi an kama musu Hotel anan zasu kwana zuwa gobe su wuce.

A wannan Rana dukkanin kafafen watsa labarai da gidajen telebijin Babu Abunda sukeyi sai haska wannan gagarumin taro domin dukkanin wasu masu yad'ai labari sun halarci gurin, tundaga BBC ,FMs State radio and television,social medias,irinsu tiktokers, Instagram etc,inda take duniya tadauka,masu kud'i nata turo da tasu gudun muwa inda Suma sauran Alumma suka bi Asibitin da Addu,a ta fatan alkhairi da kawo cigaba ga k'asarmu ta Nigeria Baki d'aya dama kewayenta,da fatan wasu masu kud'i ma suyi Koyi da Sarki Ali dasu Dr Ammar wajen Gina Asibitota irin wayen nan da ake zube kud'i Dan taimakon Alumma.

Ayau farin cikin wannan Ahali a wannan Rana Bai b'oyuwa..

Masha Allah
Allah ka yawaita muna irin su Sarki Ali acikin Al ummar mu

Finally dai ankusa had'uwa
Masu son ayi rushing ku k'ara hakuri kad'an ne ya rage...

FA'EEH BG✍✍✍✍✍

Idan kina da shawara ko tambaya Zaki/ka iya tuntub'ar wannan lambar.
Telegram,Whatsapp
08069059746

Follow my accounts
Wattpad @faiza murai
Arewabooks @faizatou
Facebook Pha'eezah Almustapha

Like share pls and comment...✍✍✍✍✍

```https://whatsapp.com/channel/0029VaZmQcv4yltXZ8zJiD3y

https://chat.whatsapp.com/L42Op0Ya7YPDsMhkJtVRbI

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Firstlady 

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai
```


PERFECT ESSENTIAL WRITER'S ASSOCITION

□P.E.W.A□

Home of perfect essential writer's together we stand□

ESSENTIAL WRITER'S□□

*Pen*is migthier than the sword **

Free □

EPISODE1
PAGE49

TYPING□□□

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠

Kyakkyawan Mari ne ya sauke mata akumatun ta da hannu bibbiyu ajere,wasu taurari ne taga suna wulga mata jin Abunda batayi tsammanin jinsa ba,ba kowa bace face Baba Asabe,Wadda taji Marin kamar saukar arado Wanda Baba Adee yasauke mata sanadiyyar dukan da tayiwa Halee har sai da ta Suma.....

INA MA ITAMA KA SUMAR DA ITA😹😹😹MUGUWA MAI KAN GWANGWANJ😁

Tsam ya rungumeta ak'irjinsa kamar wani zai kwace Masa ita yana sauke ajiyar zuciya tare da shafa dogon lallausan dogon gashinta da ya sauka har gadon bayanta..
Jin abun takeyi kamar amafarki duk da ayanzu taso fahimtar me wanene take tare dashi,musamman k'amshin turarensa da ya ziyarci hancin ta Wanda tasan agaresa kad'ai take jin irinsa kamar wani mayen karfe, Ahankali ta fara butsulniya da niyyar kwace kanta agaresa fahimtar hakan da yayi ne yasanya sa jaye ta ajikin sa da kansa cikin wani yanayi da ya riske sa ayanzu sandaiyyar rungumar da yayi mata,idanunta ta zuba Masa masu haske inda sai Kuma hawaye suu suka silalo mata,Dr.Ammar da ke kallon ta da rinannnun idanunsa ne ya Furta MISS MALINI WHAT'S HAPPENED??□□
□□□□□□□□□□□□□□□□
WA KUKE TUNANI MALINI NA TARE DASHI....

YA HAKA KUMA ME KE SHIRIN FARUWA YAKUMA NAJI AN FURTA MALINI😹😹😹□

♣♣♣♣♣♣♣♣♣♣♣♣♣

AM SORRY FANS □□□□❤

THIS IS A FAKE PAGE PLS I BEG RELAX 😂😂😂😂😂😂□□□□□□□□□□□□□

FATAN KUN NISHAD'ANTU
MASU BP NASAN HAR YA TASHI,MASOYAN HALEE RAI YA B'ACI,DA MASOYAN DR.AMMAR IRIN SU OYI□□□□□□

I MADE IT FOR THE ANNOUNCEMENT PLS !!!□□□□□□

ASSALAMU ALAIKUM
MASOYANA ❤❤□ ABABEN KAUNA TA ,DUNIYAR MAFARKI NA□□KUMA MASOYAN LITTAFIN AMAFARKI NASANTA □□

INA MAI FARIN CIKIN SANAR DAKU ZANJE HUTU NA WATA D'AYA BANA UPDATE BECAUSE INA DA EXAMS A MAKARANTA IN UPCOMING 17 DAYS,INA BARAR ADDU,AR KU TA FATAN SA,A,SANNAN INA K'ARA BAKU HAK'URI AKAN YAWAN TSAIKON DA AKE SAMU,HAKAN YASAMO ASALI NE TA RASHIN SAMUN TIME DA BANA DA....INA GODIYA SOSAI DA KULAWAR DA KUKA BANI,INA ALFAHARI DAKU SOSAI KAUNAR KU TA DA BANCE ARAINA D'ARI BISA D'ARI□❤□❤❤❤❤❤❤❤□NASAN ZAKU IYA JIRANA KODA NA SHEKARA NE□ SHIYASA NAK'ARA FAD'A KU NA MUSAMMAN NE AGARE NI KUNE DUNIYAR MAFARKI NA □ DOMIN NIMA A MAFARKI NASANKU□□□□□□□□□□□□□□□□HEART YOU ALL GUYS...✍✍✍

FA'EEH BG
THE WRITER OF AMAFARKI NASANTA

THANKS TO YOU GUYS ONCE AGAIN□□□□□□□□□

LIKE SHARE PLS AND COMMENT

KAR AMANTA AYI FOLLOWING DIN CHANNEL DINA□

.....✍✍✍✍✍✍```

□A MAFARKI NASANTA□
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

□First lady□

_Yar lelen Taskira _ ---
TASKIRA WRITER'S FORUM
□T. W. F□

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA□
_____

بسم الله الرحمن الرحيم...□□□□□

(صل الله عليه وسلم) فيدك، ابي وامي يارسول الله □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

Free □

EPISODE1
PAGE50

TYPING□□□

Alhamdulillah Allah ya nufa mundawo kan aiki lafiya.
Wannan Nasan duka daga cikin Addu,o,in kune Ina godiya sosai masu Kira masu text duka nayi appreciating Allah yabar k'auna Ina alfahari daku□□□□□□□

😇□□□Wata ta tambaye ni wai yaushe zamu gama wannan book din don Allah?,Abunda kawai na iya Furta mata shine komai tsarin ubangiji ne,Kuma kowanne book da yanayinsa yake zuwa,sannan shi irin wannan labarin Mai kwamachala natsuwa yake buk'ata bayason gaggagawa da sai muyi rushing,had'in kanku kawai nake buk'ata,fatana kaawai shine Allah ya bani iKon kammaala sa lafiya□□□□

Sai Kuma Masu Neman complete book,kuyi hakuri bangama Saba yanzu muke typing dinnsa,sai dai kuyi hkr ku rik'a bibiyar update in zaku iya,Ina godiya sosai Allah yabar zumunci□□□□□

WARNING

INA K'ARA JAN KUNNEN KU MASU YIWA MUTANE SHISSHIGI ARUBUTUNSU KAR WADDA TA KARANTA MINI LITTAFI AYOUTUBE,KO AJUYA MINI BOOK TA WATA SIGAR SAI DA IZINI NA,IN KIKA MINI GANGANCI KINYIWA KANKI DAN BAZAN CE NABARKI DA ALLAH BA✍✍

Note edited.

Mafarkin gaske shine cikar buri√√√√√√√
◉◉◉◉◉◉◉◉
♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠

A hankali ya sauke idanunsa akan takardar da Rubutun sa ya Bayyana b'aro b'aro aciki,murmushi yasaki Wanda yak'ara sanyata d'ago idanunta da suke ta tsiyayar da hawaye kamar an bud'e famfo takai dubanta agaresa k'ara samun sa tayi Yana sakin murmushi Mai had'e da Yar k'aramar dariya.Turo d'an k'aramin Bakinta tayi tare da K'ara share hawayen da suka mak'alemata suna Neman saukowa,tare da kau da kanta gefe tana Mai Jin haushin yanayin da tagansa na farin ciki,gashi ita tana cikin halin da bazata iya fassara yanayin k'uncin da take ciki ba Wanda shine silar komai Dan tun lokacin da takardar ta iso hannunta take jin ta tsani kanta zuciyar ta Babu dad'i musamman in ta tuna da Kalmar da ya Furta mafi muni agareta"Ba kya cin tsarin matan da nake,Kuma har abada bazan tab'a son ki ba"wayen furucin yafi

komai tsayawa Nisa arai da za fafa mata zuciya,shiyasa takasa yaga takardar sai nanata Rubutun take Yi kamar Mai yin karatun hadda.

A hankali ta tsinkayi muryarsa yana Furta
"Tashi daga cikin sanyin nan ki dawo nan kar ki min Illa"Ya nuna mata kan lallausar carpet Dake shimfid'e a d'akin akusa da abin cin da ke gabanta.Itakam bata fahimci komai ba a furucinsa na farko sai na biyu Wanda yasa cikin bin umurninsa ta mik'e Ahankali,komawa tayi ta k'ara damb'arewa akan tiles d'in da sauri tuna kayan da ke jikin ta, tare da sunne kanta k'asa kamar k'adangaruwa cikin yar kunyar da ta kwasa.
D'an k'aramin murmushi yayi tare da Kawar da kansa ganin Abunda tayi tare da basarwa kamar Bai ga Abunda tayi ba,Duk da sai da gab'b'an jikin sa suka Amsa ganin santalala santalan cinyoyin ta Suke awaje da Kuma Yan matasan halittun breast nata da suka yo toro a yar k'aramar rigar,hijab d'inta Dake kan gado yajawo ya d'ora mata agabanta,kunya ce tak'ara kamata atunanin bai ga abun da tayi ba,har taji sanyi aranta ayanuz kuwa ta tabbatar har jikin nata ya Gani turo Baki tayi gaba cikin Jin kunya ta d'auki hijab d'in ta Saka sannan A hankali ta mik'e ta koma inda ya nuna mata, soyayyar indomie ya bud'e Dake cikin fillet na Alfarma har tafara hucewa,tare da Furta "
 Kici Abunci ko Kuma yanzu in Miki Allura domin an shaida mun Baki da lafiya haka ne ? Shiru tamasa tana k'unkuni Dan itama kam muna layi d'aya batason Allura sai Kuma rasa amsar da zata Basa ganin tambayar da yayi mata ta Rashin lafiyar ta kaamar akwai dalilin Yinta irin Bai yarda ba,katse mata tunani yayi ta hanyar Furta "Me ya ke damun ki",wasu hawayen ne suka sake silalo mata dasauri tasanya gefen hijab nata ta goge cikin k'unar Rai tuna shine silar komai har light headche da take fama dashi ayanzu...SO BALA'I
ALLAH YA RABAMU DA SO MASO WANI.
AMIN.

Ganin bazata Basa Amsoshin tambayoyin Saba Wanda Dama shi badan ta Basa Amsa yayi mata tambayar ba,rainin hankali ne kawai irin na MAZA KO INCE RAININ HANKALI IRIN NA DR .AJ,KAMAR BAI SAN YADDA MUKE K'AUNAR NISAR MU BANE....MALAN ZAKA SHIGA HANNU FA KA BI A HANKALI 😏

A han ya d'auki spoon da pork Dake gurin yafara D'iba yakai mata bakin ta daniyar bata abaki"Haaa " ya Furta mata k'in bud'a bakin tayi sai da taji ya Furta zai mata d'ure sannan ta bud'e bakinta yafara ciyar da ita ,sai da ta kusa cin rabin sannan ta kawar da kanta gefe ruwa ya tsiyayo a k'aramin glass cup dake kan had'add'en tire na glass Shima Mai kyau da aka jera kayan breakfast din aciki,A Baki ya kafa mata sai da ya tabbatar ta k'oshi yadda zata samu Cikaakkiyar natsuwa sannan ya matsar da kayan gefe tare da d'an k'ara matsowa akusa da ita yana replacing kansa da kayan da ya mayar gefe,A hankali ya Furta "yanzu wannan rubutun ne ya sanyaki kuka,ehh "? Yakai k'arshen maganar tasa cikin kafe ta da ido hawaye ne taji sun k'ara zubo mata ta goge da gefen hannunta,cikin d'an yanayin damuwa Dr.Aj ya Furta "yaa Salam "tare da dafe goshin sa,A hankali Kuma ta tsinkayi muryarsa yana Furta "I'a m sorry kinji hawayen da suka kasa tsayawa yasanya tafin hannunsa yashafe mata tare da K'ara Furta mata "kar in k'ara ganin wayen tsaddun hawayen naki yakai k'arshen maganar cikin Kara kafe ta da idanu ganin yadda kyakkyawar fuskar ta ta chanza jiya zuwa yau cikin tausayinta,d'ago kanta tayi sanadiyyar furucin sa na karshe, kallon sa tayi da yanayin mamaki inda A hankali ya jinjina mata kansa Alamar tabbacin maganar sa,kan ta ta mayar k'asa tana had'iye wasu hawayen wayenda ta rasa ko na mene ne inda Kuma ta tsinci zuciyar ta wani sanyi ya ratsa ta ta sanadin wannan maganar duk da bata da tabbacin abun da zuciyar ta keson nuna mata,ta karda ya Nemo da biro a d'akin,rubutun da yayi a wacchan takardar ya maimata rubutawa a takardar inda daga karshen inda yayi Rubutun INDIA ya mayar dashi da hausar mu, tare da k'arawa da CALM DOWN,sannan pls wayen hawayen masu tsada atsayar dasu

zubar su na k'ona mini Rai ENDOCARDIUM d'ita tare da zanen emojis masu nuna samun natsuwa da ban hak'uri da nuna alamar k'auna,Bayan gama Rubutun ya umurceta da komawa kan gado domin k'ara samun Hutu saboda yasan Unni tabata magani Tasha,komawa kan gadon tayi ta k'wanta tayi lamo blanket ya rufa mata Mai laushi pink colour ajikinta sannan ya yasanyata cire hijab da ke jikin ta cirewa kuwa tayi saboda blanket din yayi covering na jikin ta gaba d'aya,takardar da ya nad'e ya sanya mata atafen hannunta,sai Kuma yad'an sunkuya A hankali sai tin kunnenta ya Furta ki futa lafiya,Kuma ki tsayarmun da expensive tears d'in nan idanunta ta runtse Jin Sabon yanayin da tashiga ta sanadin kusancin da suka samu wanda har take d'an Jin bugun zuciyar sa,tana ji har ya fice ya rufo mata d'akin idanunta arufe sai da ta tabbatar da yafice sannan ta bud'e takardar Daya Sanya mata a hannunta wadda ta matsu taga me ne ne aciki duk da fargabar Rashin makamar Abunda takardar ta k'unsa akaro na biyu irin sak'on takardar farko ta tarar afarko Sai ak'arshe taci karo da Abunda batayi tsammani ba inda ya K'ara da MRS AL AMIN J ki karki yi kuka. wani irin tsalle ta buga har ta manta da zazzab'in da take na ciwon Kai ta duro da karfi akan gado tare da yaye blanket d'in rungume Inayah tayi da shigowata kenan cikin farin ciki Marar misaltuwa ta tsinci kanta ciki,Inayah da bata San Abunda ya faru ba Wanda ya chanza yanayin yar uwar ta ta ba cikin son Jin tabakin Nisa ta Furta naga Yaya Aj ya wuce Yana sakin murmushi shikad'ai kema Kuma naga kina ta murna ,takardar Nisa ta Mik'awa Inayah,Inayah da karanta Rubutun tsaf murmushi tayi Mai had'e da murna na farin cikin samun cikar burin yar uwar ta na samun abincin zuciyarta.SAURA RUWAN ZUCIYA😂😁,RUWA BA,A IYA RAYUWA BABU KAI CHIRR WANNAN SOYAYAYAR SAI A FAGEN FAMA GABA DAI GABA DAI,MUNKUSA ISA INDA ZAKU GA ASALIN SOYAYYAR RUWAN ZUCIYA BASAI NA FAD'I BA NASAN KUN SAN INA NAKE MAGANA,DUK DA BAMU SAN DA WAYE ZA,A JAME BA #DR.AMMAR KO # DR.YUSUF□□□.....KOWA YA FAD'I RA'AYINSA A COMMENT SECTION WAKUKE TUNANI ACIKIN SU YAZAMO RUWAN ZUCIYAR HALEE. ACIKIN GWARAZAN LIKITOTAN NAN✍✍✍✍✍

follows my account
Arewabooks
@Faizatou

Wattpad
@Fai'zaMurai

Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠

Rungume ta Inayah tak'ara Yi tana Furta congratulations sisi,Inayah ce tak'ara furtawa Nisa bayan sun samu natsuwa Kinga shawarar mu ta bayyanar Masa tayi aiki,ni Nasan ko sak'on na farko na farko Bai fad'a ne har zuciyarsa ba,shiyasa nayi ta lallashin ki ki daina kuka domin ni Nasan Yaya Aj zai zamo mallakin ki,wayar Inayah Dake chan gefe tana charge Nisa tajawo tayi dialing numbern Ummi Kira d'aya biyu aka d'aga Muryar sumy ce ke sallama a ta D'ayan b'angaren dama wayan na hannunta bata dad'e da gama waya da Yaya mahir ba Wanda ita Ummi ta Saka ido kawai har ta daina fad'an d'aukar mata waya da takeyi,Bayan sun gaisa ne Nisa tasanar mata da komai da yafaru bata boye mata komai ba duk da tana Jin kunyar Furta wani abun,tsalle sumy ta dinga Yi tare da Furta wooouuuuu cikin farin ciki,Ummi da tayi da taji kwatsatar tayi yawa Adakin Sumy ne ta lek'o a hankali bayan bud'e k'ofar tare da Furta Summayya "lafiya kuwa"?cikin sumayya kuwa cikin farin cikin ta da yakasa b'oyuwa ta Furta wa Ummi " lafiya Lau bakomai fa Ummi" takai karshen maganar tana susar Kai,Yar k'aramar harara Ummi tasakarmata tare da girgiza kanta

tana Furta ni in kingama ki muk'o min wayana, Bayan wucewar Ummi ne suka cigaba da firarsu duka su ukun acikin wayan cikin farin ciki suna k'ara d'aura Nisa a hanya...

****

A chan sashen Unni kuwa Bayan fitar Dr.Aj kwatsam suka ga ana shigowa da manyan - manyan jakun Kuna masu kyau da tsada har akagama shigowa dasu Unni bata iya cewa komai ba Dan bata San ko waye mallakin su ba,duk da yanayin su da tsarin su ya nuna ba na Nigeria bane na saudiyya ne, wadda take hasashen ita ce kuwa bata da tabbas domin tasan ta barsu cikin k'asar nan kenan may be sai ta waya kamar yadda suka Saba.
Sallamar wata Balarabiyar mata ce wadda ak'alla zata Kai shekara saba'in da wani Abu aduniya sai dai tsufan nata ya boye kasancewarta Mai gyara da kula da kanta idan ba fad'a Maka akayi ba bazaka tab'a yarda tayi shejarun nan ba Ammie kenan mahaifiyar Ummi,Unni Laila,inda ga kama nan ta fito k'arara daka Kalli Ammie kasan itace ma mahaifaiyar Yan biyu da Laila wato Ummi da Unni.

'Jin Sallamar wadda basu Yi tsammani ba ayanzu yasanya mahir Dake buga game awayarsa ya wurgar da ita gefe yaje ya rungume Ammie cikin farin ciki domin duk yafi kusa da ita,sannu da zuwa yayi mata cikin farin ciki da harshen larabcin da ba gaba d'aya ya iya ba," marhababika ya ummul khairi" ya Furta mata,sannu da zuwa uwar Alkhairi.itama cikin murmushi take Karb'a Masa tare da yimasa tambayoyin Dake nuna kulawa cikin harshen larabcin da yazauna abakinta rad'am Wanda da ji kasan yarenta ne,hawaye ne ya silalo mata a ido inda tayi saurin gogewa kar su ankara
Sunbatar goshinsa tayi tayi cikin Kara sakin murmushi.
Cikin farin ciki da kewar Mahaifiyar tasu itama Unni ta taho da sauri ta fad'a jikin Ammie cikin farin ciki marar misaltuwa tabata side hug tare da Yi mata barka da zuwa itama cikin harshen Larabci inda Kuma sai hawaye suka sauko mata na kewar Mahaifiyar tasu fahimtar yanayin da Unni take ciki yasanya Ammie bubbuga bayanta alamar rarrashi shiru Unni tayi,Inda Ammie a hankali tasauke mata kiss Aka inda,itama Unni kiss din ta mayar mata dashi a hannun ta,inda hankali Kuma ta kamo hannun Ammie din ta tazaunar da ita cikin d'ai daga cikin had'add'un manyan rugs d'in Dake falon,Cikin mintunan da basu wuce biyar ba aka cika Gaban Ammie da kayan ciye ciye na marmari irin nasu Apple,strawberry,inibi,kankana,date dasauran su saboda Unni tasan sune Abunda Ammie zata so saboda mafi yawa achan sune cimakar su (Makkah,jidda).
Waya Unni ta jawo Tayi dialing numban sister cikin ringing biyu aka d'aga ko gaisawa Unni bata bari sukayi ba,ta sanar da ummi zuwan Ammie d'in Nigeria,farin cikin Ummi Bai b'oyuwa, Alhamdulillah gida yafara had'uwa cikin farin take Furta hakan,K'ara Furta wa Unni d'in tayi "ai dama Yaya tun Kwanakki munyi maganar da ita lokacin da hajiya ta dawowa,tace itama zata dawo Amma kar in Sanar wa da kowa,Ashe kuwa tana kan hanyarta Alhamdulillah Dama yanzu nake son Kiran wayanta,sai gashi kinzo mun da labarin dawowarta,Ammie Dake Jin maganar da Suke Yi ne da yake a handsfree Unni tasaka call d'in ta Furta cikin harshen Larabci surprised na muku cikin d'an murmushi,itama Ummi cikin murmushi ta Furta touh Ammie sannu da zuwa cikin harshen da Ammie tayi magana,"yawwa " Furta da harshen Hausa.ya hanya Ummi ta k'ara yimata daga k'arshe tasanar da ita suna nan tafe yanzu tare da yin sallama suna katse Kiran,Bayan katse Kiran ne Unni ta Furta nikam dai Ammie wannan bazatar bata mun ba fa ta Kai k'arshen maganar cikin yar dariya ganin yadda Ammie tayi da fuska irin to ki Mai Dani inda na futo.ita ma Ammie murmushin tayi tana k'ara jin farin ciki na mamaye ta.✍✍✍

Nima Anan nayi murmushi na dakata
Domin aljannu na sun sanar Dani labari Mai dad'i na page din gobe□□□.....✍

Mafarkin fans na had'uwar boom agobe zai tabbata in Sha Allah ✍✍✍

Inason ganin cooment da yawa yadda zanji dadin Bada page din gobe Mai zafi✍✍

Like pls and comment
Faiza Almustapha
FIRSTLADY
Yar lelen Taskira

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG
Heart touchings story
Jealous
Damuwa
Mafarki Mai yanayin gaske.

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

First lady

_Yar lelen Taskira _ ---
TASKIRA WRITER'S FORUM
T. W. F

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA
_____

بسم الله الرحمن الرحيم...

(صل الله عليه وسلم) فيدك، ابي وامي يارسول الله

Free

EPISODE1
PAGE51

TYPING

YAN KASUWA MASU SON A TALLATA MUSU HAJARSU K'OFA ABUD'E MU NA TALLATA KO WACE IRIN HAJACE AKAN FARASHI MAI SAUK'i
Zaku iya mun magana ta wannan
Layin +2348069059746

_____

follow me please
On
@Arewabooks
@Faizatou

Wattpad
@Fai'zaMurai

Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

_____

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠

Cikin mintina da basu wuce talatin ba Unni tasa ank'ara gyarawa Ammie sasashenta Dake kusa Dana Fulani Wanda Dama ba,a barshi haka ba,ana gyaran Sa duk sati duk da kasancewar ba kowa aciki.

Sarki Ali ne da Unni ta aika Masa da sak'on zuwan Ammie yashigo cikin farin ciki tare da sallama abakin sa yasha rawani da wata had'add'iyar Alkyabba Dake nuna irin kud'in da ke tattare da ita har k'asa ya durk'usa yagaida surukarta tasa Kuma Mahaifiyar sa,cikin farin cikin ganinsa Ammie ke Karb'a gaisuwar tasa, Sallamar Hajiya ce itada Mama Dije da suma sak'on ya Isar musu na zuwan Ammie, rungume Ammie hajiya tayi harda Yan hawayenta tana Furta Ashe Rai kan ga Rai Fatima cikin farin ciki Ammie take Furta Allah ya Nufa Gimbiya Halimatu itama tana sharar nata hawayen yanayin da suka shiga duk sai da suka bawa duk Wanda ke gurin tausayi,Dan su Unni sun San irin shak'uwar Dake tsakanin su na k'awance a chan lokuttan Baya da suka shud'e,Sallamar su Nisa ce da K'arar da suka Saka ce ta farin ciki wadda gaba d'aya Muryar Nisa tafi d'agawa da tasanya kowa duban k'ofar shigowa da gudu suka fad'a kan Ammie da suke tsaye itada hajiya suka rungumeta suna mata sannu da zuwa cikin farin ciki harda Saka mata kuka lallashin su take Yi cikin murmushi da farinciki,tare da Karb'a musu barka da zuwan da Suke mata, congratulations ta k'ara furtawa Nisa Ashe an girma har angama makaranta Yan matan Su Hassana ,murmushi Nisa tayi kawai tana k'ara lafewa kan jikin Ammie,Ammie ce tak'ara Furta Amma dai za,ayi muna walima Koh?Kai Nisa ta d'aga mata,Unni ce cikin d'an wasa ta Furta Ammie su d'aga Miki Ajiki kar su iyar muna Dake cikin murmushi da dattako Ammie da har ta zauna a inda ta tashi zuwan hajiya ta Furta k'yalesu Hassana in basu zauna ba a Ina zasu zauna Abunda zan musu Kenan naji dad'i Dan nasan irin yadda sukayi kewata,d'an hawaye ta share afakaice tare k'ara k'awata fuskarta da murmushi.

Dr.Ammar da Dr Aj Dake a falon zaune ne suna tab'a fira sama sama wadda Aj ne Mai kokarin Yinta shi uban gayyar uhm ne sai Aah yan misklillancin sun motsa,k'arar da Nisa ta saka ce tasanya Dr Aj Furta subhanallah tare da Jin gabansa ya fad'i domin shi har ga Allah ta Nisa kad'ai yaji,Dr.Ammar da Shima yaji sautin ne nata itada Inayah tare da Jin surutun mutane ak'asa yayi kamar baiji ba,Cikin yar damuwa Dr.Aj ya Furta Dude muje muga Abunda ke faruwa inba jikin Yuhanis ne ya tashi ba,kallon

k'asa k'asa Dr Ammar yayi Masa tare da Furta sai kadawo mugun kallo Dr Aj yayi Masa Yana ficewa daga d'akin tunda ya doso falon yagane Ammie ce ta hanyar Muryar ta yaji da bata chanza ba,duk da yanayin tsufa cikin farin ciki Dr.Aj ya Furta marhababiki ya Ammie,ya hanya yamata,sannu A hankali take ka'bawa cikin farin ciki tare da K'ara tayasu murnar bud'e Asibiti da Kuma k'ara yimusu barka da dawowa gida duk da ta musu A waya,tambayar sa take Ina D'ayan Bokon turan ....

Dr Ammar Dake tsaye a chan gefe rungume da hannayen sa ak'irji tun bayan fitowarsa daga nesa ya hango gefen fuskarta kyakkyawar tsohuwa zubin larabawa Yar gaye Tasha jar abaya tayi rolling gyalen irin yadda dai sukeyi Achan k'asa Mai tsarki,matsowarsa kusa ne inda yaji sautin Muryar ta da yaji tana tambayar sa,Jin sautin Muryar ta yak'ara tabbatar Masa da ita d'ince dai kamar yadda ya ayyana aransa,cikin takonsa na k'asaita da yangarsa ya k'araso falon da ayanzu ya fara cika Dan har su Ummi sun iso itada su sumy da husnat, hannayen sa zube acikin aljihunsa ya k'araso fuskar nan dai ba laifi ba dariya ba sakin fuska.

A hankali yayi Sallamar da ba kowa yaji ba inda iyakarta labb'ansa Unni ma kad'ai taji itada tasan halin kayanta sai Aj,A hankali Ammie da ke kallonsa kamar tasamu hoto ne gajin yadda yazama k'ato Kamar d'an wrestling har yafi ma Aj da take ta mamaki haryanzu ta Furta" Kai kafi k'arfin ka gaishe ni ne"? D'an sakin fuskar sa yayi A hankali cikin takon k'asaita ya ida k'arasowa Anan tsakiyar falon "Yana Furta idan kika Yi hak'uri zanzo har k'asa na duk'usa na gaisheki "yakai k'arshen maganar cikin sakin Dan guntun murmushi Mai k'awata fuskarsa cikin tab'e bakinta ta Furta ni bama sai ka durk'usa ba tunda naga kazama k'ato kar kaje tashi ka buge ni Ina maleji da sauran tsufa na,Dariya dukkanin falon suka Sanya,anasa b'angaren Shima sai da ya murmusa kad'an na furucin Ammie d'in,A hankali ya Kai dubansa gunda hajiya take zaune tana Jan charbin ta da tsokana ya Furta "Kinga inda Hajiya tafiki Ammie da itace baza tamun magana ba iyakarta tasaka mini ido taga iya shirun nawa"yakai karshen maganar Yana kashe wa hajiya ido d'aya irin na tsokana.K'atuwar hararar da hajiya tasakar masa ce tasanya sa yin guntun murmushi, sai Kuma ta bud'e Baki kamar anbata amsar abun da zata ce Masa ta Furta KAYI WA UWARKA DIJE WANNAN ABUN,kashe idon da yayi take Kira wannan abun,Aiko gaba d'aya falon dariya aka Sanya Mama dije itama cikin dariya ta Furta kagani Abdul kaja mana magana tsakar Rana muna zaman mu lafiya,Ammie ce cikin dariyar farin cikin wanzuwarta cikin ahalinta ta Furta ai shiyasa nake mugun son Jan bokan turai Dan yafika kunya Dan tsabar Rashin ta ido hajiyar Kake yiwa haka tayi yadda yayi ta wani mak'alk'ale ido d'aya wai adole misali zatayi yadda ya kashe idon mezasuyi falon in ba dariya ba,ita ma kanta Ammie sai da tadara,hajiya kuwa murmushi kad'ai tayi tare da Furta Bar ni da ja'irin.

Cikin murmushin Shima ya furtawa Ammie barka da zuwa kamar an Masa dole "yawwa"ta Amsa tare da mere bakinta tana Furta daga Baya kenan, murmushi kad'ai yayi sannu da zuwa ta Masa kamar yadda tayi wa Aj da Taya sa murna.
Kowa ya shigo yagaida Ammie yayi mata barka da zuwa,hatta matar Yaya Mustapha ma yauta shiga tayiwa hajiya barka da zuwa,Banda malan da Fulani,har mama khairiyya ma da ta kwana biyu da komawa gidan mijinta ta Kira waya tayima Ammie sannu da zuwa.Labarin da yariski Fulani bata nuna komai akan fuskarta ba na farin ciki ko akasin sa,Malan kuwa Dama baida wani case da ita ko ajikinsa.

Bayan sati biyu Mama dije ta komawarta Kano itada Inayah,Aiki ya kankama A NORAH SPECIALIST HOSPITAL majinyata ne ta ko wanne Sashen suna samun kulawa ta musamman kamar ak'asar turai baza ka tab'a cewa a k'asar mu bane inba dai b'ak'ar fatar mu Dake wulgawa ba.

Shirye shiryen bikin su Nisa ne ake tayi na murnar gama school Wanda aka Had'a harda na Mahir da Abdallah da suka kammala degree d'insu na biyu wato masters Anan HUDA PRIVATE UNIVERSITY GUSAU,an k'awata masarautar k'awata ta musamman gwanin burgewa musamman aka d'auko mai decorations wadda ake ji da ita a fad'in Nigeria zainabu Abu decorations center.ko Ina ka Duba samari ne da Yan mata masu aji wayenda na'ura ta zauna musu sunsha kyau cikin shiga ta Alfarma,uwayen taron sunyi shiga ta musamman ta wasu dark blue riguna masu bajewa har suna ja ak'asa sunsha light make up kamar ka sace su ka gudu,Suma mazan sunsha kyau cikin wasu suit masu kyau light blue and dark,Shima Dr Ammar da Aj anko sukayi cikin wasu arniyen suit su ma masu kyau da d'aukar hankali kamar wasu angwaye inda suka Saka black and white, musamman Dr Ammar yayi wani irin kyau na tada hankalin Mai kallonsa kamar wani black American,duk inda ya wulga sai an Masa kallo biyu,Yan matan Dake gurin take duk suka rud'e k'awayen su Nisa sai dai kwarjininsa bazai barsu su iya tunkarar Saba.

Anci ansha anyi Raye Raye sun samu gift sosai,bayan nan taro ya watse ne suka fara bubbud'e kyaututtuka da suka samu d'aya bayan d'aya,kyauta ta k'arshe da suka bud'e ce ganin Abunda ke ciki yasanya su rungume juna itada sumy domin kuwa lafiyayyun wayoyi ne masu tsada k'irar IPhone 14 pro max masu kyau ya basu ne amatsyin gift ya cika alkwari kamar yadda ya alkawarta musu in suka gama makaranta zai basu wayoyin, colour Daya ya basu red sai walk'iya sukeyi.

Wani d'an k'aramin box ne suka bud'e inda aka rubuta Y ajikin sa kenan a na nufin Yuhanis yasaka su bud'e sa cikin sauri dan ganin Abunda ke ciki ganin yadda kwallin ma shi kan sa yake walk'iya,Sumy ce da ta k'wace kwalin hannun Nisa yanzu ganin kamar su biyu sun kasa bud'esa, ta fito da wani had'add'en zoben zinari da yasha Yar k'aramar kwalliya sai walk'iya yakeyi daga Saman sa anrubuta AY cikin tsari Mai kyau anhad'e haruffan guri guda,wow Sumy ta Furta itakuwa Nisa rufe bakinta tayi gudun kar aji k'arar ta ta farinciki ganin Rubutun da zoben ke d'auke dashi,inda take kwakwalwarta ta Had'a mata ma,anar haruffan Alamin & Yuhanis, A hankali Nisa tad'aga manyan idanunta masu kama da na Dr. Ammar zuwa gefen da su Dr.Ammar Suke zaune a falon ta Kalli gefen da Dr.aj yake kanne mata ido d'aya yayi Yana murmushi,Alamar godiya tamasa da ido inda ya d'aga kansa Shima cikin murmushi Dan yanzu Kam soyayyar su Suke Sha baka ma hannun yaro kowa yasanda Soyayyar Dake tsakaninsu agidan,Alamar tasaka yayi mata take kuwa tasaka shi Ad'an yatsarta na uku inda yazauna d'ass hannun ta nuna Masa yayi mata alamar yayi kyau kunya taji ya dasauri ta rufe idonta ganin sun Had'a ido da Dr Ammar da yake kallon komai Dake faruwa agurin yayi kamar bai gurin ma,kuwwa duka suka Sanya falon inji su Mahir dasu Yusuf,wani box din suka Kara haduwa dashi Shima Mai kyau irin na Nisa an rubuta MS akan sa inda Ms din yake nufin Summayya & Mahir da sauri suka bud'esa cikin farin ciki Sumy ta rungume d'an Uwanta tare da Yi Masa godiya na wannan kyauta, anbude ktautukka da dama tundaga nasu hajiya su sarki Ali Dady soja,komai Masha Allah sai kyauta ta k'arshe ta mahir da suka bud'e inda ta k'unshi sark'a da Yan kunne ,zobe na zinari masu kyau dukkaninsu iri d'aya ba Banbanci,Suma su mahir sun bud'e nasu komai anyi sa cikin tsari na burgewa, a wannan Rana sun kasance cikin farin ciki musamman ganin wayoyinsu ahannun su godiya kuwa Dr Ammar yashata.

Da Inayah taga videon partyn harda kuka domin bata samu damar zuwa ba sabda jarabawar da suka fara a makarantar su.

.BUG.

A B'angaren su Halee kuwa yau Dr. Yusuf yasanya ranar da zasu fara zuwa Norah specialist hospital Dan ganin Babban likitan da ke kula da irin matsalarta.
Baba Adee ya shirya tsaf don zuwa hospital din ayau.

Yau takasance litanin ranar da kowanne ma'aikaci,Yan kasuwa da d'alibbai Suke shakkarta Kuma yake sauri dan ya Isa akan lokaci saboda cunkosn abun Hawa.
yau tun safe take jin gabanta na fad'uwa kirjin ta na bugawa Wanda ta rasa dalili faruwar haka agareta.Sanyi sanyin jikin ta da Khady taga yak'aru ne ya sanyata Furta mata "wai Halee lafiya kuwa,Koda dai bakya son zuwa Asibitin ne ganin likitan" takai k'arshen maganar cikin yar damuwa.

Halee da har hawaye ya cika manyan fararen idanunta ne muryar ta na cracking kamar zata fashe da kuka ta Furtawa Khady"k'irjina ke d'agawa na rasa dalili inajin abun har acikin jikina,Ina tsoron faruwar wani mummunan Abu agareni" takai karshen maganar cikin wani yanayi tare da janyo hannun khady ta d'aura adaidai inda zuciyarta take cigaba da bugawa bugu Kuma ba na wasa ba domin ko daga nesa kad'an zaka iya hango yadda k'irjinta yake d'agawa,D'ibb D'ibb din da Khady taji ne na chanjin bugun zuciyar Halee ya bata mamaki da tsoro cikin yar damuwa da take k'okarin b'oyewa Haleen Dan ta kwantar mata da hankali itama ta Furtamata "kar ki Sanya damuwa aranki bakomai da zai faru sai Alkahiri, in Sha Allah Alkhairi zai same ki karki k'ara yin irin wani tunani akasin haka,ki cigaba da Ambaton sunan Allah zai daina kinji,janye hannunta tayi akan k'irjin na Halee tare da d'an bata side hug tana d'an bubbuga bayanta irin na lallashi ganin yadda ta tada hankalin ta lokaci d'aya,duk da itama taji nata hankalin yad'aga Jin yadda zuciyar Halee ke bugawa ba a k'a Ida ba domin bazata manta ba a makaranta malamin Basic science ya Musu heart har da yadda take bugun k'a Ida, da Wanda bana lafiya ba,an sanar musu har practical an Musu inda aka Saka kowa yasaurari tad'an uwansa,an ma ita tabar shi amatsayi Alkahirin ne zai faru da Yar uwarta duk da bata San ta Ina alkhairin zai bullo ba.

Muryar Baba Adee ce ke sanar dasu su fito in sun shirya tun d'azu motar ta iso,gashi Dr yusuf yasanar Masa da Likitotan har sun fito,wasu Riga da Zane na atamfa ta Sanya da madaidaicin hijab milk colour Wanda yakara k'awata kyakkyawar fatar jikinta,tak'ara Yin wani haske kamar wadda akeyiwa wanka da ruwan Madara,Wanda duk wahalar nan da Baba Asabe ke bata baisa ta chanza ba, Koda ace kuwa ta chanza bazaka tab'a ganewa ba idan ba zaune kake da ita ba kullum,ita kanta Baba Asabe har mamaki takeyi na zubin halittar Halee a lokuttan da Dama takan tambayi kanta Anya kuwa Halee ba yar larabawa bace ta yuyu ta jirgin sama ta fad'o ba asani,kanki dai ake ji Baba Asabe😉ganin Halee dai bata chanza wa duk wahalar da take bata Koda kuwa ace ta chanza na D'an lokacine zata dawo normal,dalilin hakan ma ne yasaka take turata kichnen cikin hayak'i,nikam nace raba kanki Baba Asabe su Halee su ake Kira jiki duk Madara na Asalin komai zakiyi a hakan Zaki ganta,sai in abun ya tsananta.

Dukkaninsu hijab suka saka,mota suka shiga wadda Baba Adee yayi musu shatar ta Dan baison gwamatson nan da maza a mota,hanyar Gusau suka kama..
Mudai sai muce Asauka lafiya..

.GUSAU.

A B'angaren Dr.Ammar kuwa yau tun safe yatashi da muguwar faduwar gaba wadda tak'ara sanya sa Rashin kuzari yafara laziness din sa,Bai je Asibitin ba sai wajajen karfe goma instead ace k'arfe Tara.

Warda round suka fara gabatarwa zagayar d'akunan marasa lafiya kenan a hausance don Duba yadda suke,inda suka fara yin discharge ma'ana sallama,suka sallami na sallama wayenda jikinsu yayi karfi,suka chanzama masu buk'atar chanjin ward, ma,ana d'aki wayenda suka fara Jin dama dama,domin Emergency ne da I C U yafi kulawa domin channe da critical conditions, shiyasa nan Suke fara dubawa a matsayinsu na masu hakk'i da Asibitin sai da duk sukayi Abunda yadace har sauran wasu ward din sun zagaye irin su FMW,MSW,MMW,MSW da sauran su sunyi sallamar masu dama dama wayenda za,a Karawa magani ko chanjin magani an Musu wayen da nasu ne yak'are duk an sake rubuta Musu Wanda Yada'uke su awa biyu sannnan kowa ya kama hanyar office dinsa.

Dr Aj Dake kula da duk wani motsin Dr Ammar ne Yana ganin yadda yake ta yatsinar kyakkyawar fuskarsa kamar yaga Kashi tare da d'an sauke numfashi Bayan d'an lokaci ne,yakasa hakuri sun kama hanyar office nasu ne ya ke furtama Dr.Ammar "Me yake damunka wai "hannayen sa ya ware Masa alamar Shima Bai sani ba tare da tab'e d'an k'aramin bakinsa da ke ta shek'i na maik'on man baki kamar na mace inda har wani pinky pinky yak'ara Yi Mai kyau,kallon sa kawai Dr.Aj yayi tare da girgiza kansa dai dai yakawo office nasa Wanda aka rubutawa consultant 2 yayi shigewarsa,Shima Dr Ammar nasa office d'in ya tura Wanda ke dauke da consultant 1 asaman sa kamar na Aj.sanyin office d'in ne yayi Masa sallama, k'aton office ne da yake da fad'i da girma tsit Kake ji sai sanyin Ac da yak'ara wa office d'in Armashi ga k'amshin room freshener Mai Sanya natsuwa Wanda ya had'e da dadd'an turaren sa sai had'add'iyar fan ta tsaye Mai kyau k'irar china Dake ta aiki cikin kwanciyar hankali tana Bada iska Mai dad'i Kuma mai Sanya bacci ba' a ankara ba,K'aton table ne agabansa Wanda yak'ara k'awata office d'in, Yana d'auke da wata had'add'iyar system k'irar company Apple Mai kyau sai wasu takardu da files da wasu daga cikin kayan aikin su irin su Bp apparatus, thermometer, pulse oximeter,da sauran su wayenda buk'atar su kan taso in case Koda yanason Kara confirming d'in result din da nurses suka kawo.office ne da ya k'unshi madaidaicin gado na Duba mara lafiya tare da spreen cover atsaye gefensa Wanda har an bud'e sa ,sai Kuma wata yar madaidaiciyar locker itama wadda ta k'unshi takardu,akusa da ita akwai madaidaicin fridge Mai kyau,sai hot and cool shima ana sa gefen,sai k'ofar toilet Dake chan d'an lungu kusa da wata k'ofa inda nafi tunanin bedroom ne Mai d'auke da gado na kwanciyar aikin dare wato CALL DUTY..komai dai yaji a office d'in kamar na India d'in su.

Tun bayan shigarsa office d'in ne yad'an huta na kamar minti goma, yabada umurnin afara turo patients,A hankali yake tambayar su matsalolinsu d'aya bayan d'aya har ya kammala,Halee ce ta k'arshe kasancewar sun d'anzo late saboda cun kuson abun Hawa da aka Samu.

zaman ta gurin da aka tanadarwa marasa lafiya da relatives nasu taji bugun zuciyar ta yak'aru fiye da lokacin da Sanya idanunta akan sunan Dake mak'ale a symbol din Asibitin da Kuma Wanda tafara ji agida hankalinta ya tashi domin bata tab'a tsintar kanta acikin wannan yanayi ba ko makamancinsa wani sanyi take ji Yana shigarta na musamman sai dai zuciyar tata bata tare da ita domin tayi Nisa nason zak'ulo abun da yake damunta ko yake Shirin faruwa da ita,dukkanin wasu alamomin damuwa sun Bayyana atattare da ita kyakkyawar fuskarta ta Yi wani kyau na musamman Wanda idanunta sunyi wani haske da yad'an garwaya da ruwan hawayen da ke Neman saukowa na yanayin da take ciki,A hankali ta rik'e dai dai saiti zuciyarta dake gudu kamar zata b'allo Riga ta fito saboda yadda take gudu gabanta kuwa faduwa yake bana wasa ba baiwar Allah tsikar jikinta duk ta tashi saboda tashin hankali da take ciki,Kiran sunan ta da akayi ne ya dawo da ita daga matsanancin yanayin da tashiga na tunani ,jikinta ne yad'auki rawa gab gab kamar mazari sai hawaye shar suka zubo wayenda ke mak'ale a cikin idonta,suna zubowa suna turereniya da wasu gwanin

tausayi hannun Khady ta rik'e gamm kamar zata tsere mata,Kai Khady kawai ta girgiza mata alamar tadaina tare da share mata hawayen ta Dake ta zuba wadda gaba d'aya tausayin Yar uwarta yakamata tun d'azu ta zuba mata ido tana kallon iKon Allah,Baba Adee Dake chan gefen da maza Suke ne Yana kallon duk abunda ke faruwa tun d'azu Yana kallon halin da Halee take ciki yataso A hankali cikin kamalar sa ya Furta shalele kanta ta d'ago ta zuba Masa manyan idanunta da sukayi jage jage da hawaye eyelashes d'in ta sun cure guri d'aya sanadin ruwan hawayen da suka jik'a su,idanun nata har sun sauya launi inda Kuma launin ya k'ara k'awata ainahin kyawonta.
A hankali ya Furta mata " Baki son kiga likitan ne "Kai ta girgiza Masa,k'ara Furta mata yayi to meye na kuka tunda bayanzu ma za'ayi aikin ba ganin likitan kad'ai zamuyi mukoma gida" shiru tayi ita kad'ai tasan yanayin da take ciki tun Sanya k'afarta acikin wannan Asibiti take Jin komai yak'ara kwancemata duk yadda zata fassara ma wani yanayin da take ciki bazai gane ba domin ita kanta Babban aiki ne agareta fad'in yanayin da take ciki ayanzu yanayi ne Mai cike da fargaba tsoro shakku damuwa domin kuwa in aka ce Maka zuciya na bugu ba ak'a idaba Kai ma kasan ma mallakin wannan zuciyar awani yanayi yake Wanda shi kansa bazai iya Bayyana yanayin da yake ciki ba.
Baba Adee ne ya Furta "cikin Yar damuwa bari in Kira Dr.yusuf in Sanar dashi kawai mu zamu koma gida tun da bakya son ganin likitan"Kai ta girgizawa Baba Adee bisa ga har ya yayi dialing numban tasa ringing d'aya biyu Dr yusuf yad'aga sallama Baba Adee yayi Masa, Amsa Masa Dr yusuf yy cikin mutunci da girgimamawa, a hankali Baba Adee ya sanarwa da Dr.yusuf halin da ake ciki,Halee kuwa ganin dagaske dai Baba Adee Dr yusuf yakira d'in ta Mik'e Ahankali cikin Rashin k'arfin jiki ta Kama hanyar office nasa inda taga mutane na shiga duk Wanda aka Kira sunan sa Anan gefen da Suke,Dan ita atunanin ta maganar komawa gidan ce Baba Adee zaiyiwa Dr yusuf din kaitsaye kamar yadda ya Furta mata ita Kuma bazata so hakan ba duk k'okarin da dadyn yakeyi yaje abanza domin tasan wannan duk ita akeyiwa Dan samun ingantacciyar lafiyarta.

Khady Kai kawai ta girgiza tana bin Halee da idanu wacce ke tafiya kamar d'awisu kamar tana tsoron taka k'asar,cikin tausayin ta.

A hankali take share hawayen ta da bayan hannunta inda duk takon ta d'aya sai k'irjinta ya buga,bugun zuciyarta ya ninkaya har takai tana lissafin takonta domin tako d'aya kamar ana k'ara zarewa gangar jikinta kuzari na bugun da k'irjinta keyi.

In kunason dogon page agobe kuyi comment da yawa✍
Yawan comment da like yawan tsawon page

Like pls and comment
Faiza Almustapha
FIRSTLADY
Yar lelen Taskira

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*

https://chat.whatsapp.com/H60CWiGISVFKEFT6NedEUw

Join for new update□□□□□□

https://whatsapp.com/channel/0029VaZmQcv4yltXZ8zJiD3y

Hajiya idan kina buk'atar daga farkon Book Dina ki Yi following channel Dita,Anan Zaki same sa asauk'ak'e Kisha karatunki lafiya □ basai kin Nema agurin FA'EEH 😍 ba, ga link Asama□□□□□

□A MAFARKI NASANTA□
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

□First lady□

Yar lelen Taskira ----------
TASKIRA WRITER'S FORUM
□T. W. F□

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA□

بسم الله الرحمن الرحيم...

فيدك، ابي وامي يارسول الله (صل الله عليه وسلم) □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

Free □

EPISODE1
PAGE52

TYPING□□□

Masu son son Ayi musu Advertising Kuna iya mun magana ta wannan lambar
08069059746

---

follow me please on

@Arewabooks
@Faizatou

Wattpad
@Fai'zaMurai

TikTok
Fa'eeh Bg

Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

LAFIYA AKE MAGANA♨♨♨□□□□

KI YAWAITA SHAN RUWA□□□□□DOMIN RUWA SUNE ABU MAFI MAHIMMANCI AJIKIN D'AN ADAM,MUSAMMAN ALOKACIN DA AKE WATSA RANA DA ZAFI JIKIN KI YANA BUK'ATAR SU SOSAI YAR UWA.
IDAN BAKI SANI BA KI SANI RUWA SUNE ABU NA FARKO DA JIKI YAKE BUK'ATA,RUWA NA TAIMAKA MA JIKI TA HANYOYI DA BANDABAN NA FARKO K'ODARKI TANA BUK'ATAR SU SOSAI KUMA KINSAN ITACE MAFI RINJAYEN ORGANS AJIKIN MU DAKE AIKI AJIKI DUKA AKODA YAUSHE IN KI KA CIRE ZUCIYA, DOMIN DUK WANI WASTE PRODUCT DA AKE FITAR WA AJIKI IRINSU ZUFA,FITSARI D.S AIKINTA NE ITA KE TACEWA TA FITAR,TA BAWA JIKI MAI AMFANI,DAGA LOKACIN DA TA TSAYA TA DAINA FUNCTIONING JIKI YASAMU RAUNI.DAN HAKA AKULA□□□ARIKA SHAN RUWA MAI YAWA DOMIN SUNA KARAWA WANNAN ORGAN LAFIYA,SUNA HANA MASA KAMUWA DA CUTAR NAN MAI SUNA (KIDNEY STONES OR KIDNEY BEANS)□□□□

_____
Kuyi hakuri da Rashin update na jiya nayi sa so Ashe banyi save ba narasa sa duka shiyasa kuka ki samun update yau akan lokaci□

_____
Happy Eid Kabir
Allah ya nuna muna wata shekaran lafiya,Kuma ya Karb'a muna ibada□
Abani Kuma Yan barka ta da sallah□□
÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷

A B'angaren Dr.Ammar kuwa tun lokacin da ya Isa ga file d'inta ya duddubasa bayan anyi Kiran sunanta,yayi Jiran ta batazo ba ransa ne ya fara b'aci Dan ya tsani delay bare Kuma sunan mace ne afile d'in,Dan yaga sunan da ke mak'ale ajikin file din na Halimatu sadiya Umar,Bayan karanta sunan sai da ya nanata sa Sau kusan uku Yana Furta nice name aransa domin sunan ya masa sak Dana k'anwar sa da ta yi rayuwa adoron duniya ashekarun Baya da suka shud'e,Sallamar Dr.Aj ce tasanya sa Ajiye file din akan achan gefen desk din achan gefe.
D'ai daga cikin kujerun Dake a office d'in Aj yazauna Yana furta "wash wallahi na gaji da yawa yau ansamu tarin patient".

A hankali Dr .Ammar Dake d'an sauraren sa ne Bayan Amsa ma Aj din sallamarsa yayi tsaki tare da Furta "patient d'aya ta rage mun gashi ta b'ata wa kanta lokaci wallahi da badan na ga condition din nata is so worst ba da ba zan Duba ta ba sai dai cikin ku wani ya dubata ko na koreta sai next week.gashi ma transfer patient ce yakai k'arshen maganar Yana sauke ajiyar zuciya da numfashi Mai nauyi na doguwar maganar da yayi sai Kuma A hankali ya Lumshe narkakkun idanunsa masu cike da haiba da Annuri.

Dr.Aj ne Dake kallonsa da sauraren sa cikin mamaki ganin yadda lokaci d'aya temper din Dr Ammar ta tashi ayau Kuma ganin haka yasan cewa tabbas akwai abun da yake

damunsa Dan yasan ba haka yake ba akan patients Yana da Sanya sosai Yana tausayin su. domin duk abunda yake Yana kallon sa acikin ward dazu yasan cewa tabbas akwai Abunda ke damun Dr Ammar wanda yake ta k'okarin b'oye wa,Dan tun d'azu yake ta lura da yadda Dr.Ammar ke sauke ajiyar zuciya,kansa kawai yagirgiza kawai sannan ya Furta Masa" may be jikin patient din ne yayi nauyi shiyasa ta fiyar tata ta kasance haka.
Yar k'aramar tsuka yasauke wadda iyakarta labb'ansa Yana k'ara Lumshe idanunsa tare da Jin b'acin Rai na cigaba da mamaye zuciyarsa na zaman Jiran wannan patient tasa,A b'angare d'aya Kuma zuciyarsa bata da sukuni sai faman beating take kamar ana kad'a ganga.

Halee Dake tsaye a bakin k'ofa ne takasa shiga cikin office d'in wadda ta kusa minti hud'u tsaye agurin ji take kamar kar tashiga ta juya kawai sai dai Ina ta Riga ta iso Kuma bazata so Baba Adee da Suke k'okari kanta suji ba dad'i ba bisa da kari ma ita kanta ta na son samun lafiyarta gudun faruwar wani abun Mai muni agare ta Anan gaba,ta D'ayan b'angaren Kuma bugun zuciyarta na k'aruwa fiye da duka sauran lokuttan d'azu ayanzu haka jikinta shaking yake Wanda sai ka nutsu zaka iya Gano yanayin da take ciki, hasbunallahi wa niimal walkil take ta nanatawa har ta d'an fara samun natsuwa Azuciyarta.
A hankali bayan ta fara dai daita natsuwar ta tasanya Zara Zaran yatsun hannunta ta murd'a handle k'ofar tana sakin sallama cikin "Yar k'aramar muryar ta Mai sanyi da kwantar da zuciyar Mai sauraro,Dr.Aj Dake magana ne Yana bawa Dr.Ammar labarin wata patient da yayi Attending yanzu Mai breast cancer,Yana Furta Wallahi mata na bani mamaki kullum cikin fad'akar wa ake Amma abanza bazasu iya zuwa Asibiti ba sai ciwo ya fara cin jikinsu baka ga matar nan ba d'azu haka nayi ta ma ta fad'a Kuma in ba wani iKon Allah ba bazata dawo Asibiti ba alokacin da na umurceta tadawo,Kamar basu San ciwon kansu ba,kazauna da ciwo ajikinka har yakai wani mataki ita wannan ma Allah yataimake ta tana first stage ne da bansan yadda zatayi ba cancer mugun Abu ce Basa ganewa shiyasa Suke b'oyewa basu san cewa da ta kama ka sai wani ikon rabbi ba, shiyasa muke ce musu da kaji wani alamomi kazo Asibiti,in baka manta ba alokacin da muna India matar nan Mai cancer wallahi ta bani tausayi har yanzu tana zuciya ta ta bani tausayi gata da k'ana nan shekaru Kuma fa a history nata na disease din ya fara daga breast lumps ne (K'OLOLON NONO) ace da k'ana nan shekarun ka mijin ka ma bare yayanka Basu more ka ba,an Yanke duka nonuwa biyu Kai matar nan ta bani tausayi wallahi sosai Babu yar kawar nan ta mata,akwai wata itama da mukayi attending lokacin baka nan matar nan fa bata Yi surviving ba taci wahala sosai Amma Babu yadda muka iya munyi iya kokarin mu baiyi Aiki ba saboda tariga takai last stage of cancer mataki na karshe kenan,mata na bani mamaki wai wasun su kunya ke Hana su zuwa Asibiti fa ni idan nine su wallahi akan lafiyata bazan iya zama na zura ido Ina kallon disease na girma ajiki na ba,kasan Kuma fa har maza na yin cancer ta breast sai dai ba kasafai ake samu ba,shiyasa muke bawa mata shawara da su rik'a yawaita yin breast self examination don kare lafiyarsu daka ga wata alamar ka ziyarci Asibiti.

TSOKACI
Breast lump (k'ololon nono,ko k'arin mama)ana samun sa a cikin nonon mata musamman Yan mata wayenda basu Yi Aure ba breast lump Yana faruwa ne bayan yin Al ada,Wanda aduk lokacin da kike menstruation naki wannan k'olon yakan Yi tsiro acikin breast naki Wanda hormones Dake secreting milk abreast yake Samar dashi yasanya tissues su daina functioning, idan akasamu yawan hormones acikin breast din sai asamu wannan lumps d'in to daga nan idan Baki rik'a dubawa ba zai tsaya yayi ta girma, shiyasa an fison idan kina Al,ada ma ki rik'a dubawa domin tantancewa ko akwai wanzuwarsa domin alokacin yake Bayyana,Kuma idan anyi sa,a kina gama Al 'ada zai wargaje kamar Bai tab'a zama ba . breast self examination itace hanya mafi sauk'i da Zaki tsayu da kanki ki Duba lafiyar breast naki,ba lalacewa

bace kallon breast naki da kanki a madubi ba,no karki ji kunya Yar uwa ki tsayu ki rik'a duba breast naki Dan kariyar lafiyarki anso duk bayan d'an lokaci kamar mako mako haka bayan kin Yi alada ki bincika ta hanyar yin breast self examination ku shiga YouTube kuyi searching (breast self examination)zaku ga yadda ake yin sa ku kalla da kyau domin Yana da matukar Amfani ke uwa idan kin wuce wannan level na samuwarsa Zaki iya kallo ki koyawa "ya'yan ki Koda kuwa Yan shekara goma ne ko k'asan haka,domin yafi farawa ta haka ga mata San Yan mata,nace kuje ku kalle sa a YouTube ne saboda Anan bayaninsa zai mun wahala,Kuma kunsan bahaushe yace Gani da ido ya Kore ji,nafi son kowacce ku tasan yadda akeyinsa ta yadda har zata iya koyar da wasu matan Wala Allah Yan Uwanta ne ko k'annenta ko ko d'alibabbanta na,islamiyya ko boko,domin Ayanzu Abunda yafi yawa kenan idan kika je Asibiti zaki ga Yan mata da yawa da kwailaye da manyan mata suna layi akan wannan matsalar wallahi sosai.
Breast cancer Yana daga cikin kashe kashen cancer wadda muke Kira *CARCINOMA* domin tissues Dake growing mara amfani.

Abubuwan da Zaki Yi Dan kare kanki daga samuwar breast lump ko girman sa ajikinki,dakuma kulawa

_Ki daina yawan zama da breziya alokacin Al ada,domin alokacin ne ake yawaitar samun excessive milk a breast Zaki ga nonuwan ki sun ciko kamar zasu fashe wasu har zafi sukeyi musu da nauyi kuma Kinga breast Basa son takura alokacin gashi ke Kuma kina ta matse su acikin breziya,ke bama alokacin kad'ai ba tun asali haka Suke Basa son amatse su atakure su da yawa,saboda veins Dake rike dashi Basa da karfi sosai take aka takura ma breast sai kiga ya zube flat kamar silifas yayi collapse jijiyoyin sun saki,wannan da masu yawan d'aurin kirji nake inzaku Yi ku Rika sassauta daurin Dan wallahi Kuna takurawa jijiyoyin nan.

_ki daina kwana da breziya Yar uwa
_adaina barin datti Ak'asan nono musamman masu halittarsa da yawa,ma,ana masu randuna✍
_sannann ki kula da yawaita yin breast self examination duk bayan d'an lokaci.

Alamomin da Zaki gane kina dashi acikin breast naki bayan yin self examination

- jin k'olon acikin nono mara girma haka
- some times in yadade ajiki yakan danyi zafi zafi sai dai ba dayawa (severe pain),Kuma Yana chanza position domin haka yake kamar iska,domin wasu lokuttan ma In aka je surgery akan nemesa arasa sai dai ak'ara dibar miki lokaci kije ki dawo idan yak'ara bullowa.
- chanjin girman nono (Abnormal growth)
Chanjin ba wani Mai yawa ba
_ Jin Nauyin breast ba a lokacin aka al ada ba.
ꕥꕥꕥꕥꕥꕥꕥꕥꕥꕥ
Alamomin da Zaki gane kina dauke da cancer wayenda Suke abayyane,awasu lokuttan Kuma ana samun d'an kuskuren Rashin ganinta a irin wayen nan alamomin,Amma dai da kyar gaskiya wayen nan su bayyana ba,asameki da cancer ba may be stage na farko ko biyu

_fitar ruwa Mai d'an kauri da jini jini a A nono (Nipple discharge) Wanda har wari sukeyi.
_girman nono na Rashin k'a Ida Wanda har ya Bayyana afili Zaki ga d'aya yayi Babba d'aya kuwa Yana nan cif cikin koshin lafiyarsa (Abnormal growth of the breast) Yana faruwa ta sanadin wannan (tumor) din Dake cikin breast din Wanda shine yakawo wannan girman a nonon naki inda yake Saka tissues suyi ta growth bana lafiya

ba,shikuma tumor din shine cancer domin acikin sa take,sune ke hargitsa tiisue sai asamu excessive fluid Wanda take sai kiga nono yayi hi him girma Mai muni daga nan sai kiga breast yayi mugun girma har yazama abun tsoro ga Mai shi.
_ kumburi Wanda yake k'unshe da excessive fluid (Edematous)bayanin kamar na farko ne.
_kuraje masu ruwa (wound discharge) ko Maruru Mai girma Wanda yake zubar da ruwa.
_chanjin kalar nono,Zaki ga yayi red red haka
_ko rashes masu k'aikayi
_ chanjin Kan nono
_ nauyin nono ba alokacin Al ada ba

.....
Breast mastitis (kumburin NoNo) wata matsalar ce ta breast ga mata Sai dai anfi samunsa agurin masu shayarwa ko wayenda suka Yi yaye,ko masu sabuwar haihuwa Shima some times yakanzama matsala har aikin sa sai anyi,idan yayi worst har nipple akan cire,shiyasa ake so da ka ji chanji akan breast naka ka ziyarci Asibiti Dan saurin kawar da matsalar Dake damunka ko yar kankanuwa ce.

Take note please✍
Idan ance kina da breast lumps karki tada hankalinki sis
Bawai ana nufin kina da breast cancer ba no shi dai breast lumps shiyake leading to breast cancer ma,ana (shiyake Kai mutun izuwa matakin cancer)in ba,a dau mataki ba da wuri ba.
Shiyasa zaku ga kamar suna kama da juna ta alamomin su Dan ko Asibiti kika je da matsalar kina jin k'ololo abreast naki,ma,ana matsalar lumps sai Doctor ya Miki tambayoyin sign na cancer kafin su d'au matakin Duba Lumps Dan tabbatar wa.

Sannan shi breast lumps ciresa akeyi Dama na fad'a muku k'ololo ne to cire sa akeyi Kuma cirewar sa ba Mai wahala bane ana gama Miki ma Zaki iya Saka rigar ki sannan ba zaman Asibiti akeyi ba gida ake wucewa acigaba da Shan magani Dan haka in kika ga wata matsalar kije Asibiti because is not a big deal Abu ne Mai sauk'i,sannna karki ji kunya lafiyarki itace rayuwarki wallahi da Zaran ta kubce Miki Baki da wani sauran Jin dadi aduniya sai dai kad'an kad'an.
HI my sis nace karki ji kunya×3 kije kiga likita Sister na ki cire kunya domin Anan gefen bata da Amfani agareki ko nono d'aya kika rasa kin nakasa domin Babu namiji da zai kwasheki da breast Daya sai Wanda yaga Allah kunsan yadda mazan yanzu suke basai na fad'a muku ba,nidai na rok'e ku da Allah Arik'a self breast examination,madubi badan kwalliya kad'ai ba Ture ya k'era muna shi ba harda Duba lafiyar mu,Dan haka ki zama Mai kula akoda yaushe,ta kowanne gefe ma ajikin ki ki tantance yadda yake ta yadda da Zaran Kinga chanji ajikin ki Zaki gane atake.

Sannnan karki ga nononki d'aya yafi d'aya girma ki tada hankalin ki😇😅Natural haka halittar Su take sai dai girman ba wani bane,Zaki ga mafi yawancin Yan mata na hagu yafi girma but anasamun na dama,Amma ni duk wasu cases da nagani na hagu ne Dan haka karki damu hilliss,inkika lura ko halittar mu ba D'aya ba ce ba akalar fata ma wani zaki gansa jaaa,wani bak'i bak'i bak'i
Wani fari fari fari,wani fari wani Jan k'osai,wani ko kamar duhun tukunya haka yake,A halittar jikin mu ma in kika Duba hannayen ki guda biyu kika jera su Zaki ga d'aya yafi d'aya girma ko kafafunki ke ko barin jikin ki fa Daya yafi daya girma hajiya haka Ubangiji yake abunsa yayi haka ne Dan ya nuna muna iKon sa akanmu,Kuma yayi mu different a halitta Allahu Akbar Allah abun godiya
Allah ka k'ara muna lafiya
Ina fatan wannan bayani zai Amfani yan uwa mata masu karatun novels da wayenda Basa Yi ta hanyar yin tak'aitaccen bayaninsa ga agare su Kuma ya gamsar dasu..

Domin nasan in Sha Allah
Wannan bayanin zai gamsar daku har ku iya yiwa wani bayanin sa□□□□□□

Kuyi hakuri na cika muku page da surutu Nasan Zaku ji dadin bayanin ne,Kuma Mai amfanin mune□

BACK TO OUR BUSINESS✍✍

Yayi saurin Furta Masha Allah aransa ganin kyakkyawar yarinyar Dake tsaye abakin k'ofar zubin kyawawan fulanin ethopia ko larabawan makka,tare da Karb'a mata sallamar ta.

Itakuwa Halee Dake tsaye abakin k'ofar kamar andasata Jin wani irin bugu da k'irjin ta ya Kara yi kyawawan idanunta ta Dan runtse da karfi sai Kuma ta bud'e a hankali cikin wani yanayi da taka sa ko motsin kirki sai faman tab'a kyawawan Yan yatsunta take Yi kamar tana neman wani abun acikin su kanta ak'asa...

Acikin yanayin da take cikine ta tsinci Muryar Dr.Aj Yana Furta Halimatu sadiya Umar Koh cikin d'an murmushi Dan haka kawai zuciyarsa ta raya Masa itace domin da ma ya d'an nazarci file din nata,Dasauri Ta d'ago kanta ta zuba Masa kyawa wan idanunta masu Kaifi da haiba wayenda suka Kara kyau na d'an sauran hawayen da ke cikin su wayenda ta tsayar tun abakin k'ofar eyelshes dinta kuwa sun k'ara curewa guri d'aya gwanin burgewa,cikin k'ak'alo kyakkyawan murmushin ta na son b'oye yanayin da take ciki Wanda Dama ba take ake gane saba kasancewar kwarjini nin kyawon ta da yake b'oye sa Wanda sai Wanda yasanta sosai zai iya gane damuwar da ke kwance akan fuskar ta,murmushi tayi Mai K'arawa fuskarta kyawu na musamman da fito ainihin kyawonta ta gya'd'a Masa Kai.

Masha Allah Dr.Aj ya K'ara furtawa akaro na biyu azuciyarsa. A Bayyane kuwa gurin zama ya nuna mata inda yakasance mara lafiya na zama in sunzo ganawa da likita wanda kujerar Aj ya gyara mata itane adai dai saitin inda Dr Ammar yake zaune sai faman dannan wayar sa yakeyi batare da yasan ma taka maiman Abunda yake Yi ba shi dai yasan game yake bugawa tun daga lokacin da tayi sallama cikin daddad'an sautin ta komai ya kunce masa zuciyar sa ta kwad'aita da son k'arajin Muryar ta da Kuma ganin kyakkyawar fuskar mamallakiyar muryar, A d'ayan b'angaren Kuma tun shigowarta kirjinsa yayi wani mahaukacin bugawa Wanda sai da yarazana Wanda da ace hankalin Aj nakansa da zai fahimci yanayin da yake ciki duk kuwa da yadda yake k'okarin boye Masa,kunsan mutumin naku jarumi ne haka ya yayi shiru yana cigaba da pressing wayar sa sai idanunsa da yake ta faman lumshewa masu dauke da gajia da da Rashin isasshen bacci aduk Dan lokaci.

A hankali Halee cikin wata kalar murya ta furtawa Dr.Aj nagode Atak'aice.
Jin wannna sautin akaro na biyu shi yad'an sanyaya Masa Abunda yakeji azuciyarsa da Kuma mintsinin da take Masa na son fallasa halin da yake ciki
A boye yasauke ajiyar zuciya tare da K'arasa shigewa acikin kujerar sa ta Alfarma wadda take rotating ya fara juyawa Ahankali Yana juya bayansa.

A hankali ta Tako iZuwa kujerar da ya nuna mata wanda duk Tako d'aya sai zuk'atan nan guda biyu sun motsa sai sunji ajikinsu, jikin Halee kuwa yak'ara yin sanyi kamar wadda k'wai yafashewa aciki,har ta zauna kuwa kanta ak'asa yake ta kasa Kara iya dago kanta tun dagowar da tayi lokacinda Aj ya ambaci sunanta.

Bayan zaman ta kuwa sai office d'in ya d'auki shiru yayi tsif dama Aj ne Mai Yi. Firar rabi da kwata gogan iyakarsa ya Lumshe ido yayi d'an yi tak'aitacciya magana.

Dr.Aj ne Dake d'an nazartar yanayin sa kamar akwai Abunda ke damunsa Mai girma,sai dai yaga alamar yau Yan sarautar sun motsa ko ya tambaye sa ba lallai ya fad'a Masa ba kamar dai Amsar farko yasan haka zai k'ara maimaita Masa irin ta d'azu.yashaida hakanne ganin Dr.Ammar ya basu Baya kamar shi kad'ai ne a office d'in Wanda Kuma ba dabi'arsa ce yiwa Aj din haka ko ma waninsa ba,ba Abunda kake hangowa kuwa sai faffad'an bayansa da kwantacciyar sumar sa Dake kwance ak'eyarsa wadda ke Shan gyara akoda yaushe.

"Ya furta dude ga patients Dinka na ta jiranka fa cikin son tunatar da Shi wanzuwar Halee agurin duk da yasan Yana sane da ita ramuwa ce yake Yi kamar yadda ta k'i zuwa kan lokaci haka Shima bazai Duba ta kan lokaci ba,
A hankali suka tsinkayi sautin Muryar sa cikin wata irin Golden voice tasa ya Furta

"Nasan da ita Atak'aice"yanayin yadda yayi maganar sai da ya tab'a gangar jiki da zuciyar Halee duk da kuwa kalmomin da yayi Amfani da su basu wuce kalma uku zuwa hud'u ba.

Kai Dr. Aj ya girgiza kawai Yana Furtawa aransa dama Nasan za'a Rina.

A B'angaren Halee wadda ke zaune sai faman lankwasar Yan yatsun ta take Yi kamar abisa k'aya ta k'ara Jin jikinta ya mutu mutu Tus ta sanadin wannan Muryar da taji wadda har yanzu take maata Amsa kuwwa a kunnuwanta k'irjin ta ne ya buga a lokaci guda Jin Muryar kamar ta San ta sai dai Rashin sanin ko tuna a inda ta santa yasa ta kawar da dogon tunanin da zuciyar ta keson dulmiyata na Rashin tabbas sai ta watsar da tunanin wane bagire na zuciyarta tayiwa Muryar matsu gunni.
Sai Kuma haushin sa yakamata najin abun da ya Furta bayan barin ta da yayi zaune ya shanyata d'an k'aramin Bakinta ta cunno gaba na huce haushinsa duk da bata ga fuskarsa ba,kwantaccen sajen sa kad'ai ne ta kyallo da idanunta tun lokacin da ta shigo office d'in akansa ne tafara sauke fuskar ta sai dai ko kallon second bata Masa ba tadauke kanta Wanda shine yabata damar ganin gefen fuskarsa, Amma ta shaida izzarsa jin yadda ko maganar take Masa wahala kamar wani sarki a fadarsa,A hankali taji tana son ganin full face nasa Dake d'auke da complete kwantaccen sajen sa da ta hango ad'azu kasancewar ya Dan Yi k'asa da kansa a lokacin Kuma bata yi Masa kallon tsaf ba domin bazata iya ba saboda Rashin Jin ta comportable tun shigowarta office d'in.

Bayan kamar minti goma kowa da Abunda zuciyarsa ke sak'a Masa .shidai Dr.Aj kan wayar sa yakoma Yana chatting abunsa da masoyiyarsa.

A hankali ya juyo da kujerar sa a gabansu da idanunsa da Suke a Lumshe wayenda har sun d'an sauya launi sun yi wani fari fari maroon d'in su yak'ara yin duhu ya bud'e su A hankali Yana batare da yakalli Halee Dake facing dinsa ba.

Yana Sanya kyawawan Zara Zaran ya tsunsa masu dauke da kyakkyawan zoben zinari Mai kyau Mai dauke da da tambarin AH cikin tsari Mai kyau Wanda sai ka Sanya idanu da kyau zaka tabbar da Abunda ke dauke azoben ya jawo files dinta Dake gabanta Wanda Aj ya ajiye ad'azu.

Zara Zaran yatsun sa da idanunta suka k'yallo mata ne yak'ara Sanya mata kwadayin son ganin fuskarsa da Kuma golden voice tasa Dake ta Kai kawo akwakwalwarta duk da tana kokarin ya kice ta.

Takarda yasanya acikin file din nata ya fara Yan rubuce rubucensu irin na likitota na game da Abunda ya Gani acikin file din sannnan A hankali ya d'ago da kansa cikin

bin umurnin da zuciyarsa ke Basa batare da ya ankare ba ya sauke su akan kyakkyawar fuskar Halee da ke Ad'an sunne kad'an.

Halee wadda haka kawai tasamu kanta da Sauke wani kalar murmushi da ta kan iya a cewa ta dade bata Yi Shiba ta Wanda ko ita bata San dalilin yinsa ba tad'ago kanta da sauri Jin kamar an Saka mata wata irin kura Mai karfi ajiki na idanunsa da taji akanta..

Dr Ammar da sai da gabansa ya fad'i na ganin murmushinta Wanda alokacin bata d'ago kanta ba.

D'ago kan da tayi ne yabasa damar ganin kyakkyawar full face dinta Mai dauke da murmushin da takeyi Mai bayyanar da two side dimples dinta Wanda har yanzu Bai gushe ba Akai.

'Zabura yayi da karfi tare da nuna ta da Yar siririn manuninsa cikin razana Amma bazaka tab'a iya hango razanar Kai tsaye ba kasancewar kamalarsa da ta lullube kyakkyawar fuskar sa,sai Kuma A hankali yasanya duka hannayensa ya goge kyawawan idanunsa Dan k'ara tabbatar da abun da yake Gani agabansa, da K'ara tabbatar wa da kansa idan ba mafarkin da yasaba Yi bane,A hankali Kuma jikinsa yayi sanyi sai ya koma yazauna tare da Furta *NORAH* cikin Yar kasalliyar murya wadda Wanda ya iyarda furucin sunan ta hanyar yin ajiyar zuciya wadda duka Halee kad'ai tajisa.

Jikin sa ne ya K'ara yin sanyi bayan tabbatar wa da kansa ita dince dai,sai dai Abunda ya Kara sanyaya Masa jiki shine sunan *NORAH* da ya Kira Bai ga Alamar ta nuna itace mamallakiyar sunan ba ko itadin ce ba,sai dai manyan idanunta da ta sakar Masa wad'an da yake jinsu har tsakiyar kansa yanaji suna cigaba da yawo ajikinsa,A hankali cikin wani yanayi na musamman kamar ana fisgarsa ya furta Wanda ko shi baisan yanayin me ne ne yake ji ba,ya Furta cikin golden voice din sa "kallon ya Isa haka" da muryar da ita kad'ai zataji sa.
Saurin yin k'asa tayi da kanta tana cunno Dan k'aramin Bakinta cikin Jin kunya,ita bakomai yasa takasa dauke idanu akansa ba face yanayin da taga yashiga lokacin da suka Had'a idanu Wanda inzata iya kwatantawa kamar taga razana atattare dashi wadda bata San dalilin sa ba,da Kuma ganin kyakkyawar fuskar sa da ta kwad'aita da son kallon ta tun d'azu,Shima Anasa b'angaren dakyar ya iya saita kansa yajanye kyakkyawar fuskar sa akan tata kyakkyawar fuskar, fuskar da yake Gani akoda yaushe fuskar da ta zame Masa k'awa,fuskar da ta maye Masa gurbin Rashin da yayi na shekaru yau itace agabansa wani sanyi yaji ya ratsa zuciyar sa Jin lokaci d'aya kamar anjaye Masa duka damuwar da ke addabar sa ayau da ta shekaru aru aru, A hankali ya furta acikin zuciyarsa" afili ma tafi kyau"sai Kuma yasamu kansa da Sauke wani irin silent smile Mai K'arawa kyakkyawar fuskar sa kyau na musamman hango ta da yayi ta cunno bakinta gaba Wanda ke nuna alamar kunyar da taji na maganar da yayi mata ayanzu.

Dr.Aj Dake zaune ayanzu Yana kallonsu kamar yasamu Tv ne tun farkon mik'ewar Dr.Ammar Hankalinsa yadawo kansa razanar da yayi ce ta bashi mamaki na ganin Halee yasan cewa tabbas akwai dalili Kuma abune Mai girma ya alkawarta zai tambayesa in ta fita,Koda bazai fad'a Masa ba Dan yasan halin kayan nasa,sai Kuma murmushin da yaga ya wanzu afuskar Dr Ammar din da yakan iya rantsewa ya Dade Bai gansa akan fuskar Saba,da Kuma furucin da yayi ma yarinyar na kallon sa da yakamata tana Yi Jin yadda yayi maganar cikin yanayi na musamman Mai nuna kulawa da wani b'oyayyen Abunda ke zuciya,murmushi ne ya kubce Masa Jin wani tunani da yazo azuciyarsa lokaci d'aya tana ayyana Masa wani Abu.

A B'angaren Halee da Dr.doctor Ammar dukkaninsu bugun zuciyoyin su ya dai daita tun bayan wannan eyes contact da suka samu,wani yanayi ne na daban dukkanin su suka tsinci kansu,A hankali Dr.Ammar ya kemata Yan tambayoyi tana Amsawa cikin d'an yanayin sanyin jikin ta da har yanzu ya kasa sakin jikinta.

A B'angaren Dr.yusuf kuwa Koda Baba Adee ya Kira sa Shima Yana kan duba patients ne Amma ya kusa gamawa iyaka patients uku suka rage Masa,yasanarwa Baba Adee gashinan zuwa bayan yagama da patient din A lallasheta taje taga likitan zai biyo bayanta daga Baya.
Bayan ya gama ne ya fito cikin sassarfar sa ya iso inda Baba Adee yake tsaye yakasa zama tun bayan wucewar Haleen Anan yake sanar Masa da ta wuce tun d'azu har yanzu bata fito,Kuma tun lokacin da suna waya a d'azu ta Isa office d'in.

Zuciyar Dr.yusuf ce tad'an tab'u na Jin bayanin Baba Adee, Ahankali ya Furta Baba bari naje na Dubata.kama hanyar office d'in yayi tare da tunanin wulakancin Dr.Ammmar ne ya Kawo kan Halee kenan a zuciyarsa sai Kuma wasu sak'e sak'en da suka wanzu aransa har ya Isa office din na Dr Ammar din Yana sak'awa da kuncewa.

Da sallama dauke a bakinsa ya tura k'ofar office din cin karo da Halee yayi wadda itama take k'okarin fitowa office d'in bayan gama Amsa Yan tambayoyin da Dr.Ammar yayi mata..

goshin ta ne ya bugu akan k'irjin sa yar k'aramar K'ara tasaki cikin shagwab'a tana Furta "wayyo zafi" da Yar k'aramar muryar ta tayi furucin, Subhanallah ya Furta cikin Yar damuwa da Kuma Jin zuciyarsa ta wanke na Ganin su su uku a office d'in Dan haka kawai yaji zuciyar sa na son d'arsa Masa wani Abu akan Ammar da Halee d'in ganinsu haka yasan dai wata magana bazata tab'a shiga tsakanin Ammar da Halee din sa ba.

"Cikin Yar damuwar buguwar da Halee tayi a goshin ta ya furta "SORRY Wifey" cikin shauk'in soyayya da kaunar masoyiyar tasa,Yana Mai Sanya hannunsa a goshinta yafara lulayawa,Halee da taji zuwan Abun bazata ta fisge goshin ta tare da rik'e hannun nasa Wanda bata San yadda akayi ba itama ta rik'a hannun nasa, b'ata beautiful face dinta tayi cikin dan tsuke dan k'aramin Bakinta, dan haka kawai taji abun da yayi Bai wani burgeta ba nasanya hannunsa akan goshinta duk da kulawa ce ya nuna mata,Kuma tasan Bai tab'a Kai hannunsa ajikinta ba sai yau ita kanta bata San dalilin sa nayin hakan ba duk da tasan tabbas akwai dalili tunda tasan ba halin sa bane,Dan tasan halin kayanta ciki da Bai.

Sakin hannun sa tayi da sauri ,tana d'an tab'a goshin ta,Dr yusuf ne ya Furta luv cikin murya Mai nuna tausayi da begen masoyiyar tasa,Kalmar luv ce ta sanyata sakin fuskarta tare da sakin k'ayataccen murmushinta Wanda har dimples dinta ya Bayyana gwanin burgewa domin tana son sunayen nan da yake kiranta dasu, Dan Dr Aj Kam Shima ba Baya gurin soyayya,Kuma yasan ta hakan zai iya shawo kan abarsa ganin kamar ta nuna Rashin Jin dadin ta kan Abunda ya faru yanzu ganin yadda ta tsuke kyakkyawar fuskarta,Shima murmushin yasaki ganin murmushin masoyiyar tasa Yana Furta "raguwa kawai "Kai ta sunkuyar k'asa cikin murmushin ta Mai kyau,"ya Dena ciwo Koh,Kai ta d'aga Masa sannan
Cikin bata Umurni ya Furta "kitafi Gani nan zuwa yanzu zan fito" tare da bata hanya, har tasanya k'afar ta daniyar fita office din sai Kuma tasamu kanta da son juyowa tak'ara kallon kyakkyawar fuskar sa domin haka kawai ta ji alamar kamar idanunsa na akanta,juyawar da zatayi kuwa cikin sa,a idanunta sai acikin nasa kallon second Daya ta Masa ta Ida ficewa tana barin office din Baki d'aya.

Dr.Ammar Dake Jin zuciyar sa kamar zatayi bindiga ne tun lokacin da Dr.yusuf yasanya hannu ajikin Halee din da Kuma hannayen su da suka hade alokacin da ta rike hannun na Dr yusuf har da Yar shagwab'ar da tayi Masa da Kuma k'arar da Saka wadda tasanya sa Jin kamar yaje yaa rungumeta ya lallasheta ya Duba goshin nata, wata boyayyiyar Ajiyar zuciya ya sauke Mai nauyi Wanda take idanunsa suka chanza launi,tare da Jin zuciyarsa na wani irin zugi kamar zata kama da wuta Wanda yarasa dalilin da yasa yake Jin haka duk da yasan shirmen da idanunsa suka gane Masa ne.

Gabansa ne yaji yayi wata irin muguwar fad'uwa Jin Dr.Aj Yana Furtawa Dr yusuf ko itace uwar gidan tamu Dr?Bayan sun gaisa din,Amsar da Dr yusuf yabawa Dr Aj itace Abunda ya tayar Masa da hankali har yayi sanadaiyyar faduwar k'irjin sa.
Dr.yusuf kuwa cikin d'an Sosa keyarsa da Yar k'aramar dariyar farin cikin tambayar ta Dr Aj ya Furta "in Sha Allah fatiha kada'ai ta rage kushafa"

Masha Allah Dr Aj ya Furta Yana Furta Allah yakai mu lokaci lafiya,Amin Dr.yusuf y Furta cikin farin Addu,ar ta Aj Yana zama akujerar da Halee ta d'aga Yana mik'awa Dr.Ammar hannu alamar musabaha,Dr. Ammar Wanda yayi kamar baisan da shigowar ta Dr Yusuf ba da duk maganar da Suke yi da Aj din.kallon hannun na Dr.yusuf yakeyi cikin wani yanayi ba abun da yake hangowa face hannun kwance akan fuskar Halee da Kuma hannayen su da suka had'u, d'an kawar da kansa yayi cikin dakiyarsa da basarwa Yana ji kamar yasaka adda ko zarto ya yanka hannun na Dr.yusuf,ga Kuma wifey da yaji ya kira Wanda sai da gabansa yafadi alokacin. A hankali Kuma kome ya tuna sai ya Mik'a Masa hannun nasa cikin dakewa da jarumtarsa yanaji kamar zuciyarsa zatayi bindiga alokacin Wanda har wani suka yakeji tanayi Masa wanda yarasa dalilin faruwar hakan,musabaha sukayi cikin Rashin sakewa da juna suka gaisa kowa da Abunda yake sakawa azuciyarsa bama kamar Dr.Ammar domin yaji zafin Abunda yafaru sosai Wanda har yanzu yarasa dalilin faruwar hakan agaresa,meyasa yake jin zafin abun,Dr yusuf kuwa baida mu ba domin dama ba wani sakewa sukeyi da juna ba tun asali duk da kasancewar su friends achan Baya Dan ko lokacin da suna India suna medical school Aj ne kad'ai Wanda Suke Dan sakewa dashi shiyasa in yaje Kai musu ziyara da shi kad'ai Suke D'an tab'a fira,ko ayanzu contact ta Aj kad'ai yake da ita.✍

Finally dai munzo gurin hankalinku ya kwanta a daina takura fa'eeh da ma na fad'a muku komai a sannu yake tafiya to yau dai gashi an had'e
Al amarin yazo da zafi karon farin anfara wasar 😋😉😉😉
Anan yak'in zai fara zamu ga Mai rabo □□□□□ Aciki.

MEYE haka likita shin mi Kake nufi haka daga Ganin sarkin fawa sai Miya tayi zak'i
Mudai kabi mu Ahankali Dan mukam mun wuce gurin Dr.yusuf ya shige ciki

teams Dr Yusuf how far□
teams Dr Ammar how far□□□□

Yau Nasan sai comment ya gundure ni

In Kuma kuka watsan k'asa a ido Babu long a page gobe,domin wannan ma in Kun lura page biyu ne na had'a muku ✍✍✍x
Faiza Almustapha
FIRSTLADY□
Yar lelen Taskira □ □

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG
heart touching story

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*

https://chat.whatsapp.com/H60CWiGISVFKEFT6NedEUw
Sabon update acikin group□□

https://whatsapp.com/channel/0029VaZmQcv4yltXZ8zJiD3y

Zaki samu farko a channel kiyi following kawai□□

□A MAFARKI NASANTA□
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

□First lady□

_Yar lelen Taskira _ ---
TASKIRA WRITER'S FORUM
□T. W. F□

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA□
_____

بسم الله الرحمن الرحيم...

(صل الله عليه وسلم) فيدك، ابي وامي يارسول الله □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

Free □

EPISODE1
PAGE53

TYPING□□□

السَّلاَمُ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَةُ اللهِ وَبَرَكَاتُهُ.
عيدكم مبارك وكل عام وانتم بخير
تقبل الله منا ومنكم صالح الأعمال
Taqabbalallahu Minna wa Minkum.

May Allah SWT accept all our prayers, supplications, and good deeds and forgive us and grant us success in this life and hereafter (Ameen).
"Eid Mubarak".✍

♦♦ *Happy Eid Kabir*□□□♦♦

follow me please on
@Arewabooks
@Faizatou

Wattpad
@Fai'zaMurai

Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

_____

♣♣♣♣♣♣♣♣♣♣♣♣♣

Dr.yusuf kuwa,File d'in Halee yajawo Dake Aje a Saman sauran files din kasancewar shine karshe,Sannan cikin Rashin damuwa da yanayin na Dr.Ammar ya Furta ohk three weeks ka bata kenan?
Dr.Ammar da ke Lumshe da idanunsa ne shiru kamar bazai tankasa ba, a ganinsa meye na takura komai gashi nan arubuce, A hankali ya d'aga Masa kansa tare da Furta A tabbatar tana Shan maganunnukan ta please kan lokaci,domin sune zasu taimaka gurin had'e gudajen jinin Dake guri guda wanda zai taimaka muna gurin yin aikin nata,har ita yataimaka mata gurin samun ingantacciyar lafiyarta,yakai k'arshen maganar cikin sauke numfashi na doguwar maganar da yayi wadda Kuma ya ke Yinta k'ire k'ire kamar an Masa dole,Wanda Dama Yana Neman Relatives nata ne da zai yiwa gamsasshen bayani gurin kula da Shan maganin ta akan k'a Ida Kuma,yayi wa Yusuf bayanin ne saboda Bai da wani zab'i ne Bai ga wani nata yashigo bayan ta ba sai shi,yakai k'arshen maganar cikin sauke boyayyiyar ajiyar zuciyah tare da Lumshe manyan idanunsa.

Dr yusuf Dake kallonsa ne sake da Baki da mamaki Jin yadda yake ta Basa bayani cikin kulawa harda wani please na munafurci kamar ba yanzu ya so yayi Masa Rashin mutunci ba to Kuma me yasa ya chan za lokaci d'aya haka agaresa duk da yasan ba dashi yake ba,har yake magana cikin kulawa hmmm Niko nace Kai dai Yusufa bar zancen nan haka..

Dr yusuf Ficewa yayi daga office d'in bayan gama Jin bayanin na Dr Ammar suna sake yin musabaha da Dr Aj Dake kallon su kamar yasamu wani show..

Da fitar sa kuwa Dr Aj kamar Jira yakeyi yasauke tambayoyin Dake bakinsa,A hankali yadawo kan kujerar da Dr.ysuf yad'aga Yana Furta wai ni Kam dude me yake damunka ne yau?Jin yayi Masa shiru yaki tankasa ne idanunsa arufe, yabasa damar Kara Furta zan tambaye ka pls kabani Amsa bro, Dr .Ammar Dake sauraren sa ne ya bud'e manyan idanunsa yasauke su akan Aj batare da ya Furta Masa komai ba,ganin hakan yasa Aj yakara Jin karfin yi Masa tambayoyin Dake abakinsa,ganin yabasa hankalin sa kamar shi kad'ai yake Jira yaji ta bakinsa,Furta Masa yayi "meya razanar dakai agame da wannan patient din taka Mai suna halimatu sadiya Umar?,Sai

tambaya ta ta biyu me yasanya ka yin murmushin da ka shekara baka Yi irinsa ba agaban wannan yarinyar?murmushin da ko Dr.malini bata samu makamancin Saba,sai ta uku,meye dalilin ka na shawa Yusuf k'amshi kamar yayi Maka wani Abun ko akwai wani Abu atsakanin ku duk da nasan dama Baku Saba da juna ba,Amma Nasan ba haka Ka Saba treating din Sa ba,duk akan meye ne?yakai k'arshen maganar cikin son Jin karin bayani.

Dr Ammar Dake sauraren sa ne Wanda ya kafesa da manyan idanun nan nasa masu Kaifi ya Kara sauke ajiyar zuciya,bayan Yan sakanni har Dr.Aj yaci re Rai da Jiran Amsar sa sannan A hankali kamar bazai Yi magana ba Dr Aj ya tsinkaye sa Yana furta Masa cikin golden voice dinsa Mai sanyi wadda ayanzu tak'ara yin taushi na yanayin da ke nukurkursar zuciyarsa,"zaka samu Amsar ka ta farko kawai D'an jarida",Murmushi shi Dr Aj yayi kawai Tare da Furta Masa "naji dai" Atak'aice

Shiru ne yak'ara biyo Baya kamar bazaiyi magana ba sai Kuma A hankali ya furtawa Aj"ita wannan yarinyar da ta razanar Dani,naga fuskar sani atattare da ita ne"cikin son k'arin bayani Dr Aj ya Furta Fuskar sani toh A Ina kasan tane.

Dr. Ammar Dake lumshe da idanun sa Yana d'an juya kujerar sa A hankali ne Yana ta Kuma sauke numfashi Wanda yake fisgosa da kyar ta sanadin yadda zuciyarsa tayi Masa nauyi,ya ware su tare da kallon Aj Da ya matsu yaji ta bakin Ammar din,sannan A hankali kamar Mai Jin tsoron yin furucin Wanda yake ji har makoshin sa kamar yadaina aiki Na wucin gadi,da sanyin Jikin da yasaukar Masa lokaci d'aya da faduwar gaba ya Furtawa Dr.aj ...

*A MAFARKI NASANTA*itace yarinyar da nake yawan Gani acikin bacci na,itace yarinyar da nasabu da ita acikin MAFARKI NA, tin da nayi growing itace abokiyar fira ta Mai d'ebe mini kewa,Dan shiru yayi cikin wani yanayi Yana sauke numfashi,sannan A hankali ya cigaba da magana ,bakomai ya razanar Dani ba face ganin wanann yarinyar Mai yawon zomin Amafarki wadda ka Furta mun cewa ALJANNA CE (AUTAR AMMIE),ko maganar ka tabbas ce,itadin ce Aljannar,ko gizo ne take mun kamar yadda tasaba Yi mun akoda yaushe,ko bacci ne nakeyi da ido asake.sai dai ta wani b'angare had'uwa ta da su Lubna ya k'arfafa mini gwaiwata yasa na fara Addu,ar Allah ya bayyanar mun da ita A Fili a ko wanne irin yanayi take Koda kuwa ace tana dauke da cutar hauka ne,Domin na shaida tun da har akasamu Mai kama da ita za,a iya samun wanzuwarta aduniya,awata k'asar daban kamar yadda ubangiji ke Hallitarsa a mabanbantan gurare da siffar kamar Yan Adam.
Sai dai abun da yakara sanyaya mini gwuiwata ayanzu bani da wani tabbacin itadin ce ko ba ita ba ce,duk da na ambaci sunan da ta tab'a furta mun a MAFARKI Amma Banga alamar cewa itadin ce mallakin sunan ba,Yakai karshen maganar cikin Dan taune lips d'in sa na k'asa da suka k'ara Yin pink sai shek'i sukeyi,cikin wani yanayi tare da sauke ajiyar zuciya Mai nauyi da d'an tab'e k'aramin bakinsa Jin kan sa yyi Masa nauyi na doguwar maganar da yayi yanzu.

Dr aj da yayi mutuwar zaune ne Wanda saida Dr Ammar yayi taping hannayen sa akan fuskar sa sannan ya Furta cikin tunuma,kenan duka wannan Shan k'amshin da kake yiwa Dr.Yusuf akanta ne, Dr .Ammar kuwa "hannayensa ya wara Masa alamar Bai sani ba kamar d'azu,Kai Dr.Aj ya girgiza kawai Yana Furtawa aransa kenan duka wayen nan tambayoyin nasa amsar farko ta wadatar Masa domin shi mutun ne Mai saurin fahimta,afili kuwa Aj K'ara furtawa Dr Ammar yayi iKon Allah abun akwai mamaki dude Abu kamar a series films ko a novels wannan akwai alajabi acikin wannan lamari, ban tab'a ji ba sai yau da na gani da kaina,achan Baya haukar ka nake gani Ashe nine mahaukacin...

Daga haka Aj Bai k'ara Furta Masa komai ba ganin kamar Baya cikin son K'ara cigaba da yin naganar,face ma Lumshe idanunsa da yayi kamar Mai baccin gaske,office d'in ne ya d'auki shiru tunanika sun mamaye zukata rauni na cigaba da zak'ulo kansa jiki ya sanyaya.

WASAN YANZU AKA FARA✍✍

FA'EEHHHHHHHHH BG

Dr.aj kuwa Cikin zuciyar sa Tausayin d'an uwan nasa ne ya kamasa da Kuma mamakin wannan lamari da yaki sakin sa,ace mafarki yazame gaske Wanda ba kasafai ake samun haka ba,mafarkin ma irin wannan nad'an uwansa Mai wahalarwa,wanda Suke tunanin Aljanna ta Aure sa,tunda duk lokacinda yayi sa baida natsuwar zuciya sai a rasa gane ma kansa,wai ace mafarkin nan da yazamewa Dan uwansa jiki Wanda kusan kullum sai tazo Masa Amma yau gashi Allah ya nuna Masa yarinyar afili yaganta ido da ido Allahu Akbar ya Furta murya ciki cki,Yana tunano yanayin da yaga d'an uwansa yashiga alokacin da su Halee suka kayi kicibus da juna inda Yusuf yad'ora hannunsa akan goshinta alokacin ...
Dan sai yanzu wasu abubuwan yake d'an kawo su akansa duk da Bai Saka ido akansu ba,kansa kawai yagirgiza Yana k'ara Jin tausayin d'an uwan nasa,naganin reaction din sa alokacin inda zai iya rantsewa kishi ne Mai tsanani yagani kwance akan fuskar sa tun shigowar Dr yusuf din, Alamomi sun nuna akwai soyayyar yarinyar aransa tun bayan da yafara cire soyayyar margayiyar k'anwarsa Norah aransa wadda ya Saba da ita fiye da kowa acikin k'annen nasu tun lokacin da Yana da kuruciyar sa,Bazai manta ba lokacin da suna India yatab'a Kiran yarinyar da Aljanna har ya nuna ransa ya b'aci Wanda ke nuna alamar yasaka ta aransa ko akwai wani Abu tsakanin sa dream girl din tasa wadda kowa yake tunanin Aljanna ce ta Aure sa take je Masa a MAFARKI.
Tausayin sa yaji ya kara mamaye sa bayan gama tunanin zucin game da maganar da Dr. Yusuf din ya mayar Masa a kan Halee d'in "fatiha kad'ai ta rage ku shafa"jikinsa ne yaji yak'ara yin sanyi alokaci guda na Abunda yake hasasowa zai faru,gashi dai Dr Ammar yaga samu yaga Rashi duk da yasan har yanzu Bai wani yarda da son yarinyar yakeyi ba kamar yadda gangar jikinsa ta kasa b'oyewa.

A B'angaren Dr Ammar kuwa Wanda idanunsa ke rufe haryanzu Babu Abunda ke Masa gizo face murmushinta da ya fara cin karo dashi abisa kyakkyawar fuskarta,tare da K'ara tunano kallon da tayi Masa kafin ta fice daga office din,Wanda kallo ne da bazai iya fassara ma,anar sa kasancewar bashi acikin natsuwar sa alokacin,Amma tabbas yanaji wannan eyes contact din da sukayi na Rabin second har cikin jikinsa gab'ansa sukan girgiza aduk kwakwalwarsa ta hasko Masa kallon,inda duka wayen nan moment din nasu haka yake ganinsu acikin idanunsa kamar an jona masa tv, A hankali yasauke wata munafukar ajiyar zuciya tare da hade dukkanin leb'ansa agurin guda d'aya akan d'aya sai Kuma ya ware su tare da cije leb'ensa na k'asa Wanda yak'ara yin pink sai shinning yake Yi na sauran danshin lips balm Dake mak'ale akansu.

A B'angaren Halee kuwa haka kawai take Jin ba dadi azuciyar ta na barowar ta office din.
Sannu Halee kinji ai sai kije chan ki kwana Koh

A B'angare D'aya kuwa Babu Abunda ke mata gizo a kwakwalwarta Wanda ke isarwa idanun ta face kallon da sukayi cikin ido da ido kafin ta fito,wani kalar tausayii ne ta Gani kwance akan kwayar idanunsa Mai nuna alamar kiji tausayina,Da Kuma mai Neman taimako,da wani Abunda bazata iya fassara shi ba akan Rashin sanin taka maiman mizanin da zata aje sa.

A hankali take takawa kamar wadda kwai ya fashe wa a ciki,cikin Rashin kuzarinta Wanda ya K'ara raguwa fiye da d'azu sanyin jikinta yakara Bayyana alokaci Daya Mai had'e da rauni,Wanda bakomai ya haddasa mata wannan yanayi ba face wayen nan moment din musamman razanar da ta Gani atattare dashi da Kuma golden voice nasa wadda har yanzu take jinta acikin kwakwalwarta tana yawo.

Har ta iso gurin da su Baba Adee Suke bata sani ba,har ta d'an gota su khaady Dake zaune tadawo da ita Baya ta hanyar riko hijab d'inta fahimtar cewa ba ta masan ta iso a kusa dasu ba.
Cikin yin k'asa da kanta kamar bata fahimci Abunda tayi ba ta nemi guri ta zauna cikin natsuwarta da Kuma sanyin jikin ta a kusa da Khady.

Khady Dake kallonta tare da nazartar yanayin tane ne tun lokacin da ta tunkaro inda Suke ta fahimci kamar ba lafiya ba,sai dai bata kawo komai ba tabarshi a kan Rashin son zuwa ganin likitan ne na d'azu, A hankali ta furtawa Halee "lafiya dai koh" Kai Halee ta d'aga kawai tare da furta "lafiya Lau " Atak'aice,tana k'ara tunano yanayin da likitan ya shiga alokacin da sukayi yayi ido biyu da ita afarko,wanda ita har yanzu bata dauke sa akomai ba sai dai mamakin faruwar abun takeyi har yanzu har Wanda taji kwad'ayin son jin dalilin sa na razana da ganinta,gashi likitan ma ko sunan shi bata samu damar dubawa ba.

Baba Adee ne da ke tsaye ya na ta jiran fitowarta,bayan ganin ta fito kamar tasamu natsuwa ya katse mata tunanin ta ta hanyar Furta shalele Kinga likitan ko eh ta Furta Masa tana mik'asa prescription ship din ta na medications " Yar k'aramar takarda ce da ake Rubutun magani acikin ta ta Mik'a Masa tana Furtawa cikin sanyinta" yace nan da sati uku adawo,karbar takardar Baba Adee yayi Yana dubawa, Yana cikin dubawar ne kuwa sai ga Dr yusuf ya iso inda Suke Bayani yakarayiwa Baba Adee kamar yadda sukayi da Dr Ammar da Kuma Abunda ya Gani acikin file d'inta da Kuma shaida Masa akwai inda za,a karbi maganin ta har an tura bayananta wannan takardar bata da wani amfani yabata itane saboda Kuna Baki awannnan Asibitin,domin komai ana yin sa system ne acikin computer,duka masu files sabbin patient ne masu referrel da transfer da suka fara ,zuwa yau,farin ciki ne ya kama Baba Adee Dan dama baida wasu kudin saboda tsakan wata ake ciki,godiya Baba Adee ya yiwa Dr yusuf cikin Rashin nuna sarakkutar da ke Neman shiga tsakanin su,cikin Yar kunya Dr.yusuf ya Furta Babu komai Baba✍✍.

Bayan sun karbi maganunnukan nata A Babban pharmacy din da ke cikin Asibitin sannnan suka kama hanyar Bungud'u sai gida.

Ab'angaren Dr.yusuf tun bayan fitowarsa office din tunani ne fal aransa sai yanzu yasamu damar Kara yin nazarin wasu abubuwan bayan sunyi sallama da su Haleee din yakoma office dinsa ,tambayoyi ne fal aransa Wanda baida Mai Basa amsar su ayanzu,duk da yasan dama da gangan ya d'ora hannunsa akan Halee baiyi zaton abun zai Yi hurting din sa ba Kai tsaye domin yaga kallon da yake bin Halee dashi a lokacin da suke tsaye itada shi Wanda shikansa Bai lura cewa kamar ya zuba idanunsa akanta ba,Wanda shikuma kallon ya tsarga Masa Abu zuciya Wanda Baya fatan ya auku Anan gaba domin yasan daga lokacin komai yakare Masa,Wanda shine

dalilin da yasa ya yi saurin Saka hannu agoshin Halee kenan Dan ya karyar dashi daga Abunda yake hasashe Wanda zuciyar sa ke hasko Masa.

toh akan wanne dalili zaiji zafi kenan,ya Furta ma kansa cikin shakku da tsoron Amsar da zuciyar sa zata Basa domin bashi da Mai Basa amsa face ita ayanzu.

Gaban sa ne ya fad'i Bayan tunano da kallon da kallon da yaga sunyi wa juna itada Dr.Ammar, wani tunani ne daban zuciyarsa ta hasko Masa Wanda ya Sanya k'irjin sa fad'uwa,Wanda yasanya sa saurin janye sa ta hanyar barin office din nasa Dan k'ara zuwa Duba patients d'in sa na sashen Yara Dan Achan aka kaisa yanzu (pediatric ward) Dan yasan achanne zai samu natsuwa sosai achan ta hanyar kula da yaran da Kuma watsar Masa da duk wani damuwa nasa ta Dan sakewar da yaran sukeyi dashi.

WAYE DR.YUSUF

Cikakken sunan sa Yusuf sulaiman janyau,haifaffen garin Gusau ne,Mahaifin sa rik'akken Dan siyasa ne,yayi karatun sa na likitanci a India,Yana da ilmin Arabia gwargwardo,shikad'ai ne ga Mahaifan sa,Shima dai kyakkaywa ne, kyakkyawan farin bafullace sai dai Bai Kai Dr.Ammar kyau ba a tsawo ne zasu zo kamar dai dai,sannan shi mutun ne mai hak'uri da basar da wasu abubuwan saboda Shima baida hayaniya arayuwarsa wannan kenan.

FULANI..

Abubuwan duniya sun taru sun mata yawa na damuwar da mama khairiyya ke ciki game da zamantakewar ta. Da mijin ta Wanda ayanzu mama khairiyya Tayi Kiran wayarta cikin kuka take sanarda ita kashin da mijin ta yake bata bayan komawarta gidan.
Tayi Amfani da shawarar su hajiyar safkare da su Unni ta rufe idanun ta akan komai na mijin nata kamar yadda su hajiya suka bata shawara,sai dai saboda Yau da kullum sai ta watsar da shawarar tasu,kuka take sosai tana sanarda Fulani halin da take ciki,ayanzu ko Abunda zataci wuya yake mata Sau d'aya yake bata abincin,wani lokacin ma bata samu,duk da kasancewar sa hamshak'in Mai kud' na gaske,gashi bata yin wata sana'ar ta rufama kanta asiri,Fulani cikin Dan yanayin damuwa ta Furtawa mama khairiyya kiyi hakuri Auta nayi dana sanin tilasta Miki Auren wannan Alhajin,Amma ki cigaba da Hakuri in Sha Allah komai zai zo karshe,ta D'ayan B'angaren mama khairiyya hawaye ta share tana Furta Fulani nagaji wallahi,lallashinta ta k'arayi da bata Baki cikin d'acin Rai sukayi sallama da juna.

KUD'I BA SHINE FARIN CIKI BA,KARKI YI WASA DA RAYUWARKI.✍✍

Nadama ce ta dabaibaye Fulani wadda takeji tana saukar mata marar iyaka A yanzu tashin hankalin ta ma shine ranar da mama khairiyya zata gane son zuciyarsu ne sanadin shigarta damuwar da duk take ciki ayanzu guntun hawayen ta tashare tana Addu,ar Allah yadawo da Abdul Rashid cikin A halin sa kodan samun wani b'angare na farin ciki ga yarta,da Kuma Neman yafiyar ubangiji.

Like and share please
more comment more pages ✍✍

Inaganin comment naku Kuma inajin dadi
□□□
Maman Abba

Ayeesha Abdullahi,
Mrs Abdul
Sai uwayen complain😂
Maman Khalid
Nusaiba
Yau dai ansamu long page no complain😂
Dukkanin ku Ina godiya dama wayenda ban anbata ba,Allah yabar k'auna.zumunci
Mai daurewa

Wayenda Basa comment ashanye dadin page ayi shiru Kuma Ina godiya,

Faiza Almustapha
FIRSTLADY
Yar lelen Taskira

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG
heart touching story

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

First lady

_Yar lelen Taskira _ ---
TASKIRA WRITER'S FORUM
T. W. F

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA
_____

بسم الله الرحمن الرحيم...

(صل الله عليه وسلم) فيدك، ابي وامي يارسول الله

Free

EPISODE1
PAGE54

TYPING□□□

follow me please on

@Arewabooks
@Faizatou

Wattpad
@Fai'zaMurai

Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠

Zaune take akan makeken gadon ta tasaka waya agaban ta tana ta kallo,Kiran Dr Aj take Jira da yace mata in yadawo masallaci sallar Isha zai kirata, Kira ne ya shigo awayan ta ta,sai da wayan tayi ringing biyu ana uku ta d'auka cikin sallama da farincikin ta ta Furta yaya Aj Barka da dare,a d'ayan b'angaren Aj cikin Dan murmushi da shauk'in soyayya masoyiyarsa tasa Nisa da tayi Masa shiga farat d'aya tamasa mugun kamu,ya Amsa yawwa matar Aj"Yar k'aramar dariya tayi cikin Jin dad'i da ficewar furucin bata re data shirya Masa ba ta Furta Allah ya nuna mun ranar da zan zama Mrs Aj ranar da za,a kaini d'akin ka yya Aj takai karshen maganar cikin gwalalo idanunta fahimtar subutil kalaminn da tayi,Aj kuwa dariya yayi ciki ciki mai nuna Jin dadin furucinta sannan ya Furta "AMIN Allah ni na matsu ma Ad'aura muna Ad'aure jinake kamar akawo mun ke yanzu ma,yakai k'arshen maganar cikin yin murmushi Mai sauti,A b'angare Nisa ma cikin Yar saurar kunyar da ke cinta ta Furta "Nima haka yaya Aj " Dariyar furucin ta ne ta kubce Masa ta farin ciki,wanda ita kanta bata San sub'util kalamin da tasake yi ba,kunsan mutuniyar ku..sai dai taji Yana kwasar mata dariya inda tak'ara fahimtar Abunda ta Furta,kunya ce tasa ta Yanke Kiran tana dariyar kanta itama k'asa k'asa cikin shauk'in k'auna.

Kiran ta yasakeyi bayan yagama kwasar dariyar da Kuma Jiran ta samu natsuwa kunyar ta rage mata,Kira uku yayi bata d'aga ba,sai da ya rubuto mata text kamar "Please Mrs Aj pick my call"murmushi ta saki bayan karanta sak'on,Kira ne yasake shigowa awayanta sunan da tayi Masa saving dashi ne ya Bayyana hayaty,tare da wasu emojis masu nuna alamar so Mai tsanani, murmushi ta K'ara saki tana d'aga Kiran, shiru tayi har sai da Yafara magana cikin sakin murmushi da Kara saukar da murya ya Furta "meyasa kik'a kashe mun waya?"shiru tayi har saida ya Furta sweet kina jina fa! Yar k'aramar Dariya Mai had'e da murmushin ta Mai kyau tayi Jin sunan sweet din da ya kirata dashi,turo d'an karamin bakin ta tayi kamar l tana Gaban sa sai Kuma A hankali ta kawar da maganar ta hanyar jawo wata firar daban,duk da ya fahimci wayonta sai Bai nuna ba yabar zancen nan kamar yadda ta buk'ata domin Ayanzu Abunda take so shine nasa,sunzama kamar dare da yini d'aya Baya rayuwa batare da d'aya ba,har sai lokacin da ubangiji ya raba,firar su ta soyayya suka cigaba da yi gwanin burgewa,cikin bama juna kulawa.

A B'angaren Dr.Ammar kuwa tun ranar da ya had'u da Halee kwanciyar hankalinsa da natsuwar sa ta k'ara gushewa dama tun farko Yana b'oye damuwarsa ne,Amma awannan Karon yakasa, yarasa dalilin da yasa har yanzu yarinyar take Masa gizo fiyeda yadda take zo Masa Amafarki,Abu d'aya ne ke k'ara tayar Masa hankali shine tarayyar ta Dr.yusuf Yana tsoron faruwar wani abun Wanda shi kansa Bai San matsalar da hakan zai janyo Masa ba,kwance yake akan makeken gadon sa na

Alfarma Mai cin mutun uku,yayi d'ai d'ai akan gadon dagashi sai short fari k'ar,fuskar sa tana kallon pop din d'akin Mai tsarin kyau,hannayensa rungume akan k'eyarsa k'afafunsa kad'an ya rage su sauko kan bed table, ganinta yakeyi tana Masa murmushin da ta sa ba,Yi Masa a mafarkansa da Wanda ya ci Karo dashi a kan kyakkyawar fuskarta a ganin ta na farko ,ya kafe silin da ido kamar tabbas ita din ce agurin,ko Ina tsif ga sanyin A.c ta ko Ina sai yanayin sanyin damuna na ruwan da suka sauka da Rana, sai uban k'amshin da d'akin keyi Wanda ya had'e da dadd'an kamshin turaren sa.A cikin d'an haske hasken Dake a bedroom din nasa Wanda yake dim light ne, kyakkyawar fuskar sa Kake hangowa da ke ta shining kamar na ruwan gold yak'arayin wani kyau na musamman. faffad'an k'irjin sa da ke cike da Albarkatu wayenda suka Yi lub kamar sunji relaxer ya d'an shafa tare da Sauke numfashi da wata iriyar ajiyar zuciya Mai nauyi kamar yaron da ya kwana biyu Bai ga uwarsa ba,Jin kamar zuciyarsa na suka,A gogon d'akin ya kalla karfe 1:30 Am na dare ya nuna Masa,A hankali ya Lumshe manyan idanunsa yayi masu cike da bacci da damuwa Wanda har sun d'an Yi red daga yanayin farin su Mai kyau.
Sai Kuma A hankali ya janyo remote na Ac Dake gefen sa Ayashe ya rage gudun Ac din,tare da kashe bed site lamp wadda dama itace kad'ai ke Bada haske alokacin
Gyara kwanciyarsa yayi tare da janyo tattausan blanket din sa white and pink colour ya rufe jikin sa dashi daga bakin Abdomen nasa zuwa kan kyawawan legs nasa,gefen dama ya k'wanta kamar yadda Annabi Muhammad saw ya koyar asiffofin kwanciya bacci bagan gama Addu,oin na sa,D'ai daga cikin pillows din Dake Jere a kan makeken gadon nasa ya
Rungume kamar za,a k'wace Masa tare da rufe idanunsa,inda tun Yana motsi A hankali da juye juye na Rashin Jin dadin komai har barci b'arawo yayi awon gaba dashi.
Asuba ta gari likita✍

BUG

A B'angare su Halee Halee kuwa sun Isa gida lafiya,tana cigaba da Shan maganunnukan ta akan k'aida Wanda kullum sai Khady tayi rigima da ita domin bata kaunar magani ko kad'an,A b'angare d'aya tana tsintar kanta cikin yawaita yin murmushi Wanda ita kanta tarasa dalili Wanda har Khady Sai da magantu Data ga abun na Halee na Neman wuce wuri domin tasan bata cika murmushi haka kawai ba,duk da shine Asalin Abunda ke kwance akan fuskarta Wanda yake K'ara fito da Asalin kyawunta,lokacin da Khady ta tambaye ta,bata Furta Mata komai ba lokacin Dan bata da amsar bawa Khady domin ita kanta bata San meye yake sanyata murmushi ba,duk da wani lokacin in tayi murmushin sai k'irjinta ya buga tunano wani abu Dake zaune Azuciyarta Wanda sai Kuma murmushin ya gushe mata,haka dai takeyin abubuwan nata kamar Mai shafuwar iska Wanda har ita kanta ta fara zargin hakan akanta tsoro da shakku suka shigeta,sai dai bata sanar wa da Khady ba.
A B'angaren soyayyar ta da Dr.yusuf kuwa komai na tafiya dai dai,bawan Allah yana k'ara tattalinta ta yanda yake ji aransa bazata iya fad'awa soyayyar wanin sa ba.

INDIA

LUBNA damb'are akan lallausar carpet din da ke shimfid'e afalon take sai kuka takeyi kamar an ce mata Appah ya mutu ko Aunty Laila,takarda ce a hannunta wadda Dr.Ammar ya rubuta Musu itada su ziyad wadda ta iso hannunta ta gurin gate man nasu,da su Dr Ammar suka bawa,Anyi lallashinta har angaji,su kansu su ziyad karfin hali ne kawai da dauriya gudun kar su tayarwa da iyayen Su da hankali ga Kuma Lubna agefe Daya zata iya ya Kara rudewa domin kanta Bai cika daukar hayani ya ba itama, domin sun Saba da Dr Ammar sosai Wanda ayanzu Suke jinsa kamar

jininsu,Aunty Laila ce Dake zaune akusa da Appah achan gefe cikin falon sun buga tagumi da damuwa akan fuskokinsu ta Furta, acikin Yar damuwar Dake mak'ale Azuciyarta da fuskarta "Abban Norah yakamata kanemi mutumen nan ni nagaji da k'asar nan,ni Nasan duk Rashin A haline akusa ke damun Lubna,tun yaushe muke lallashin ta Amma abu yaci tura kamar muna k'ara mata gudun kukan nan ni ban San wace irin shak'uwa ce ta shiga tsakaninsu da wannan yaro ba,Ina tsoron rasa Lubna akaro na biyu atare da ni ya kamata muyi wani abun kafin yaran nan hakurin su yakare,cikin Yar damuwa Dake sauraren matar tasa Dake magana acikin rauninta da yak'ara fallasa kansa kamar zata fashe da kuka,ya furta Nima kaina Lailah nagaji inason ganin ahalin mu Ina son gusar musu da damuwar su nasan cewa suna acikin damuwa Mai yawa,sai dai har yanzu wannan mutumen Bai ce komai ba,ma,ana Bai Kira ba tun shekarun Baya da mukayi magana dashi shiru,inaji dama bamu yarda dashi muka zo nan ba, sai dai nakanji sanyi araina in na tuna yanayin kamalar da nagani akan fuskar sa dakuma wadda na hango acikin idanun d'an uwansa Mai face mask,shiyasa nake d'an Jin zamu iya jiransa bamu San abun da yake shiri Akai ba,ko sun Kai k'arshen matsalar Azzalumman mutanen ko basu Kai ba Allahu wa alam,Amma Kuma yashida mun A achan Baya cewa wayenda Suke so suga karshen mu zasu iya samun labarin inda muke su bibiye mu tunda k'ungiya ce wadda ta shahara Aduniya,suna da connection A dukkanin wasu k'asashen shiyasa yake ta ka tsan tsan gurin yin communication damu domin yasan Suma za,a bibiyesu,,sai Abu d'aya da yatsaya mun arai yadda wannan mutumen Mai mask yake bawa wannan Umurni kamar shine Babban sa Wanda narasa gane ko waye shi da dalilinsa na rufe muna fuskar sa,Kuma Ina tunani dukkanin Abunda ke wakana wannan mutumen ne Mai mask ke tafiyar dashi,Ajiyar zuciya yasauke Jin komai ya dawo Masa sabo na barowarsu cikin A halinsu,da aka so arabasu dasu.

MU WAIWAYA LABARIN BAYA,abun da ya faru

Zaune yake akan sallaya da wata kyakkyawar k'aramar yarinya wadda ak'alla zatayi shekara Daya da watanni Tara haka ko biyu agefensa.

Inda Duk Yakaranta aya sai ta karanta acikin gwarancinta domin bata da wani Baki yarinyar tana da d'an b'acewar harshe bakomai take iya furtawa ba sai dai daganin yarinyar irin masu wayon nan ce Tasha k'aramin hijab red Wanda ya K'ara haskaka kyakkyawar fuskarta Dake d'auke da manyan idanu Masu haske,ga Kuma d'an madaidaicin sajenta da yafito acikin gefe da gefen hijab din nata wanda dagani yarinyar irin masu gashin nan ce,d'an k'aramin Bakinta take juyawa Mai dauke jajayen lips tana bin tilawar da Mahaifin nata yakeyi,K'arar wayar sace Dake achan kan gado ce ta fara ringing sai da tayi ringing kusan Sau uku Wanda har sai da Aunty Laila Dake chan awani d'akin ta lek'o tana Furta Abban Norah wayar ka nata ringing Ashe kana kusa na ma zata kunbar d'akin,sai da yakai aya Sannan ya Furta zan d'aga Kiran so nakeyi natsaya a inda yadace ga Yar ki ma natayani ita ala dole sai Tayi karatun gashi bakin har yanzu harshen nata yak'i zama kamar lokacin da Autan maza Yana k'arami Shima haka yake shi ta biyo,Ya dubi yarinyar da ta tsurawa Aunty Laila ido tana kallonta sai Kuma tayi d'an murmushin ta Wanda ya bayyanar da fararen hakoranta tare da dimples dinta dasuke aboye cikin Yan kumatun ta,hannu Aunty Laila ta d'aga mata tana Furta NORAH aiki nakeyi ki cigaba da karatun ki gurin Uncle domin ta fahimci Abunda take nufi tana son ta zo gurin ta ne,Kai yarinyar ta d'aga wadda aka Kira Norah,murmushi Aunty Laila tayi sannan ta juya zuwa aikin da takeyi na gyaran kayan Nora da ta wargaza ad'azu gashi nanny din ta ba ta zo ba yau bata da lafiya.

Murmushi Appah yayi Shima sannan yacigaba da karatun nasa inda ahakan itama tacigaba da binsa tana d'an wasar ta da jelar rigar ta da taji kud'i wadda daga ganin ta kasan naira na aiki awajen.

Bayan kamar minti goma haka,ya Kai k'arshen surar da yake karantawa suratul kahfi, Domin Ranaar ta kasance juma,a ranar da ake son kowanne musulmi ya karance ta tsaf domin falalar ta dakuma Neman tsari daga dujjal,inda hakkan ya zame Masa d'abi,a.
sannan ya rufe Quran in Yana mik'ewa da yarinyar ajikinsa ya Maida Quran in amazauninsa. wani Kiran ne yasake shigowa awayan tasa inda har ya katse Kuma,Daukar wayar tasa ne ya Basa damaar ganin ten missed call ajere inda yake ta tunanin duka yaushe suka shigo wayantasa cikin mamaki Kuma daganin Kiran rututu daga bakuwar lamba ta k'asar mu cikin mamaki A hankali ya danna Kira Alayin ringing d'aya aka d'aga Kiran alamar kamar Jiran sa akeyi.
'Cikin tashin hankali wanda ke ad'ayan b'angaren ba tare da ya Amsa Sallamar da uncle yake Masa ba ya Furta ba,magana mutumin ya yafara Wanda Uncle Bai gane sa ba ko ince Bai San Saba,ya Furta Allah yataimaki sarki Umar cikin karramawa da girmamawa,Bai bari Uncle yabasa Amsa ba ya cigaba da magana yana mai Furta "ku Had'a duk abun da kuke buk'ata kabar k'asar nan Kai da iyalanka munyi muku booking na ticket da visa da komai,Domin Akwai matsa sosai sarki Umar rayuwar ku na cikin had'ari,...Anan ya sanar dashi duk abunda ke faruwa na Shirya farmakin da za,a Kai musu batare da yasanar dashi su wanene masu son suga Bayan nasa ba,da Kuma shi d'in wane ne,tashin hankali wanda ba,a sakawa rana ba,bak'aramin razana uncle da aka Kira sarki Umar Wanda alokacin shine kan karagar mulki yayi ba,tunanin sa d'aya waya tare wa wani abu, su waye wayen nan mutane da ke Neman rayuwarsa ido rufe,tashi hankalin da ya tsinci kansa aciki Mai yawa ne,tashin hankalin sa ya bayyana K'ara K'ara zuface ke ke to Masa ta ko ina Babu inda yafi d'aga Masa hankalin Jin gaba ki D'ayan iyalan su har Wanda Bai ji Bai Gani ba,abun zai iya shafuwa.
Aunty Laila da bata dad'e da shigowa d'akin ba duk taji komai Abunda mutumen ya ke furta Masa saboda akwai loudspeaker sosai awayan Kuma Bai rage ba,Rufe bakin ta tayi cikin tashin hankali wanda take idanunta suka rikide suka sauya kala tare da ruwan hawaye
Sai Kuma A hankali ta Furta mun shiga uku Abban Norah su waye Mai Shirin ganin ganin bayan mu Mai muka Musu ne ?takai karashen maganar wani mahaukacin kuka na kubce mata,Itama Norah Dake hannun Mahaifin nata ganin Mahaifiyar ta na kuka yasa tafara kukan itama Lallashinta uncle yakeyi Yana cigaba da sauraren maganar da mutumen ke Masa inda yake Furta Masa Anjima zai shigo masarautar ta k'ofar Baya guraren silisin dare d'aya bisa uku ma,ana zuwa karfe 2:00 pm na dare zasu zo su dauke su m,sannan ya sanar Masa da duk sak'on ba daga gare shi bane daga wani mutun ne d'an uwan sa musulmi Wanda shi yasanya aka Kira sa.sannan suka Yanke Kiran.

Bayan sunyi sallama ne ya umurci matar sa Laila da tayi Had'a musu kayaan su na buk'ata bayan lallashin da yayi da kyar,takardun sa ya had'a guri d'aya da duk wani abuna buk'atar sa awata Yar k'aramar jaka,k'atuwar jaka Aunty Laila ta Had'a musu na sururar da zasu buk'ata dukansu tana kuka tana share hawayennta na bak'incikin rabuwa da A halinta rana tsaka da tsoro da shakku da suka farmata na wayen nan mutane.

Dukkaninsu jugum Suke rungume da juna da Yar su d'aya tilo ajikin Aunty Laila har tayi bacci bayan Mahaifin nata ya lallashe ta,suna Jiran lokacin da wannan bawan Allah ya sanar dasu wanda duka mamaki sukeyi Taya akayi har suka San da k'ofar baya din har suka iya Bude ta,a Ina suka San da wayen nan mutanen,tambayoyi ne fal azuciyar Uncle Bai da Mai Basa Amsar su.

Cikar lokacin ke da wuya dukkanin su suka Kara tsintar kansu cikin damuwa ta rabuwa da ahalin su batare da sanin a Ina zasu koma da rayuwar su ba,da Kuma abun da zai faru agaba,mik'ewa sukayi dukannin su suna yima gidan kallon bankwana Wanda Suke ji kamar sun rabu kenan da ahalin su,bazasu k'ara iya had'uwa da su ba may be sai A Aljannar Firdausi..
Allah kasanya mu Aljannar musha dad'i mu huta. □□

Dukkaninsu sai da suka yi k'walla har sarki Umar da ke namiji, Norah a hannun Aunty Laila rungume akafadar ta,jakun ku nansu rik'e a hannun uncle haka suka bar masarautar cikin d'acin Rai da bak'in ciki Wanda har suka bar cikin fadar Babu Wanda bar masarautar Babu Wanda yagansu ko Ina tsif tsif kasancewar dare yariga ya tsala.
Mutun biyu suka tarar awajen bayan isowar su k'ofar inda suka tarar da 'Yar k'aramar k'ofar awangale,mutun biyun kuwa suka tarar awajen d'aya da facemask d'aya ba facemask,Marar face mask din shine Wanda sukayi magana da shi D'ayan Kuma basu San kowaye ba Sarki Umar ya gane hakan ne ta Muryar sa,D'ayan kuwa Bai magana sai dai yayi Alamu kamar wani kurma,sarki Umar yaso yagane sa sai dai kasancewar su acikin duhu ne Babu wadataccen haske yasa ya share bai matsawa kansa da son gane waye ba tare da Kawar da tunanin da ke son shiga akansa.

Mota mutumen yasaka musu kayansu tare da rufe k'ofar bayan sun sunfito sun rufe k'ofar, sannan suka shiga motar tare da mutumen Mai face mask agaba suna barin unguwar..
Tafiya Mai Nisa sukayi sannan suka kawo awani D'an madaidai cin gida Mai kyau aka parker motar,shiga gidan sukayi inda suka zab'i d'aki Daya,A ranar dukkaninsu basu Yi barci ba,sun duk'ufa suna kaiwa Allah kukansu,Itakuwa Norah baccin ta take sha hankali kwance.
sai gangar Asuba bacci b'arawo ya kwashe dukkanin su har Mai gadin gidan da yakasance Baya barci kasancewar sa Mai yawan ibada ne,Wanda yabar k'ofar gate din awangale alokacin da yaji kamar motsi ya lek'a wajen..
Norah ce ta cikin yanayin tsoron duhun da ya kasance bata so ta farka cikin kuka ta ke Furta um ma!um ma! Tana rarrafawa acikin duhun tana mik'ewa cikin tafiyar ta ta Yara masu wayau wadda itama sai Ahankali kasancewar bata cika taka k'afafun ba,saboda kullum a hannu ake yawan d'aukar ta.
Sai Kuma A hankali ta fara zagayen dakin tare da Furta sautin Aunty tana kuka na ban tausayi da Yar k'aramar muryar ta da sanyin iskan mota yashiga ta shak'e,inda cikin kukan nata da Bai fita sosai ta baro d'akin nasu har ta fito wajen gidan tana dundune acikin duhun gashi alokacin wata yashiga duhu ba bu hasken farin wata bare hasken fitila,har ta iso bakin k'aramar k'ofar gate din tana rusar kukan inda har Muryar tata ta Kara disashewa gwanin ban tausayi ta Had'a majinaa a fuska ga tsoro ga Rashin iyayen nata akusa da ita musamman mahaifiyartà da take ta faman Kiran sunanta, Ahankali ko cikin tafiyar tata ta fice daga gidan gaba d'aya har tabar unguwar alokacin komai Rashin imanin ka Inka ganta sai ka tausaya mata,Babu Abunda take furtawa acikin kukan nata sai Ambaton Aunty da uncle takeyi Wanda Baya ma fita,Wanda ba kowa Zai gane abin da take furtawa ba sai Wanda yakware akan sanin yadda yara suke karye harshen su, baiwar Allah fuskar ta tayi jawur abunka da farin mutun..✍✍✍

Wayyo Allah 😭😭
Norah Allah yakawo Miki mafita□□
Ko ya zata kaya....
Mu had'u next page gobe in Sha Allah □

Like pls and comment
Faiza Almustapha

FIRSTLADY
Yar lelen Taskira

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG
heart touching story

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

First lady

_Yar lelen Taskira _ ---
TASKIRA WRITER'S FORUM
T. W. F

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA
_____

* بسم الله الرحمن الرحيم*...

*(صل الله عليه وسلم) فيدك، ابي وامي يارسول الله *

Free

EPISODE1
PAGE55

TYPING

Idan Baki karanta ba ki fara karantawa kar abarki Baya atafiyar nan,domin LITTAFIN AMAFARKI NASANTA daban yake,labari ne da ya had'a komai Dake faruwa awannan duniyar tamu musamman abun da ke faruwa a wannan k'asar tamu,labari ne da ya d'auki dogon lokaci Ina tsara shi,littafin ya wahalar Dani sosai yadda Baku tsammani,zan iya ce muku yayi shekara biyu wannan littafin atare da ni sai dai akwai dalilin da yasa nakasa wallafasa atake,Ina Baki shawara ki karanta domin na goge Alkalami na nayi rubutu da basira ta Babu kissa Babu munafunci bare shakkar wani,domin Babu Wanda nake tsoro face Allah na.
Shiyasa nabar muku shi a free domin Alumma su Amfana dashi sosai,saboda darasin da ke acikin book d'in.

Allah Ina rok'on ka kabani Ikon kammala wannann book lafiya□□□□□□

----------''''''''''----------''''''''''----------

follow me please on
@Arewabooks
@Faizatou

@Wattpad
@Fai'zaMurai

@Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠
□□□□□□□□□□□□□□□□□

_____

'Da innalillahi wa Inna ilaihi raji'un Aunty Laila ta mik'e daga kan carpet din da suke kwance itada sarki Umar,wayen da bacci ya kwashe,bayan gama mugun mafarkin ta da Norah,wasu zakuna ne biyu sun biyo ta zasu cinyeta tana ta kuka tana neman agaji gashi bata ma iya gudun.zufar Dake saukar mata take sharewa tana cigaba da Neman Agajin ubangiji,A hankali ta ida mik'ewa daga kan sallayar bayan Jin kiraye kirayen sallah sama sama,hasken fitilar wayarta ta kunna sai dai wayam tagani bayan haska kan gadon inda ta kwantar da Norah cikin tashin hankali ta tada sarki Umar tana Ambaton sunan NORAH cikin tashin hankali da yanayin kukan da ya b'alle mata tunano mafarkin da ta gama yanzu,A Ahankali cikin shesshekar kuka take sanar dashi Rashin ganin Norah akan gadon.

Cikin tashin hankali dukkaninsu suja fara binciken d'akin har toilet da sauran Spare rooms din sun duba,sai dai Babu ko Mai kama da itane,sun tsinci kansu cikin tashin Marar misaltuwa bayan da suka tambayi Mai gadin gidan in yagan ta,ko yaji kukanta, ko yaga fitar ta gidan ko yaga alamar wani ya shigo gidan,sai dai dai Ina Babu Amsa cikin tashin hankalin da yatsinci kansa Shima yashaida musu bacci yaci k'arfinsa ya bar k'ofar gate Abud'e jikin su yayi mugun sanyi fahimtar cewa ta bar gidan kenan ba dauke ta akayi ba,Aunty Laila Dake tsaye kawai suka ga ta zube cikin tashin hankali aka Nemo ruwa aka yayyafa mata,Koda ta bud'e idanunta da sunan NORAH ta fara magana tana cigaba da kukan ta,A hankali uncle Dake rungume da Aunty Laila yake nazartar yadda tabar gidan inda take yagano cewa tabar gidan ne tana halin Neman su bayan ta farka atsakar Daren taci karo da fitilar wayar sa da ya kunna ta mutu inda ta dunduna acikin duhu,har ta fice sanadiyyar wayarsa da tadauke Babu isasshen chaji wadda ya kunna mata hasken ta.

Komawa cikin gidan sukayi domin Babu damar fita waje Duba tilon Yar su wadda ita kad'ai suka mallaka aduniya,Dakyar sarki Umar ya lallashi Aunty Laila wadda ke ta kuka kamar zata shide tayi har ta gode Allah,Sallar asuba suka gabatar sunyi jugum sai ga wannan mutumen da sarki Umar yayi magana dashi yazo shi kad'ai kawo musu abun breakfast, cikin tashin hankali sarki Umar yake Masa bayanin duk abunda ke faruwa. cikin tashin hankali wannan mutumen Wanda basu San sunanshi ba ya Kira D'ayan mutumen Mai facemask inda yake shaida Masa Abunda ake çiki,cikin tashin hankalin sa da yabayyana k'arara A chan b'angaren Shima mutumen ya ke nanata innalillahi wa Inna ilaihi raji'un cikin jimamin wannan Alamari da Kuma tashin hankali take ya Basa umurnin yasaka anemo ta indai tana kusa batayi Nisa ba za,a ganta in Sha Allah,kafin su tashi tafiya domin karfe Tara jirginsu zai d'aga.sallama

sukayi inda mutumen nan ya Musu bayanin komai tare da bawa Sarki Umar ticket nasu da komai Wanda sai dashi zasu iya barin kasar..

Tashin Hankalin da Aunty Laila tak'ara tsintar kanta itada sarki Umar Wanda yake ta kokarin boye yanayin da yake ciki Bayan Neman Norah da akayi ba,a ganta ba,Gashi Babu halin Neman ta radio da television,har k'arfe Tara tayi ba,a ganta ba idanun Aunty Laila sunyi sutu sutu na Rashin ganin tilon Yar ta,Shima Appah dauriya kad'ai yakeyi gudun K'ara k'arya zuciyar Matarsa.

Filin jirgin aka Kai su a mota direct inji wannann mutumen da har yanzu basu San sunansa ba,Hankali Aunty Laila Bai k'ara tashi ba sai da taga dagaske tafiyar zasu Yi Subar yarsu a inda basu San halin da take ciki ba,kuka take tana Furtawa cikin mahaukacin kukan Dake cinta" ita Kam bata zuwa ko ina tabar Yar ta ana agigice take wayen nan maganganun Wanda dakyar suka shawo kanta inda sai da mutumen ya Yi mata Alkawarin zai Nemi yarta akowanne irin yanayi zai dawo mata da ita yayi mata Alkawari Wanda duk da haka dakyar ta yarda ta shiga jirgin.

Haka suka bar Nigeria cikin jimamin Rashin Yar su da rabuwa da ahalinsu.
Sun sauka Ak'asar India lafiya domin dama chan ne mutumen ya tura su.
Tun bayan da suka zauna agidan da mutumen ya Musu hayar sa Aunty Laila kullum cikin kuka take har ciwo sai da ta k'wanta,bayan kwana goma da tafiyarsu mutumen nan ya kira yasanar musu da Anga Norah,tun kwaanakki biyar da suka wuce sai dai yayi ta Neman layin da suka Basa na kasar india basu same Saba sai yau,sannan daga k'arshe yabasu hakuri Yana sanar musu da Yar su sun ajeta akan hanya wani mutume ya dauke ta saboda zaman ta ahannunsu wata Babbar matsala ce yau da gobe zaza iya samun matsala,kuma yasanar musu da ogansu yayi Alkawarin zai Saka ido akanta,yasanar musu data shiga hannu na k'warai da yardar Ubangiji Babu Abunda zai sameta,tundaga lokacin kaso saba'in na bak'in cikin Dake cin zukatan su ya ragu har suka fara cigaba da Al amurransu acikin jam,a,har suka Saba da wasu daga cikin mak'otan su inda har yaran indiyawan Mak'otan nasu suka lak'awa Laila,Aunty Laila Wanda har yabita Yayanta su ziyad suka taso suna kiranta dashi har zuwa kan Lubna, Bayan d'an lokaci shima Appah ya nemi aiki da takardunsa ta hanyar wani mak'ocin sa Mai aiki agurin office na (C.B.I) central burea investigation India Mumbai har ya zamo shine shugaban office din Baki d'aya,wannan kenan.

MUDAWO CIKIN LABARI
A hankali ya share guntun hawayen sa da gefen tafen hannunsa gudun kar wani daga cikin su ziyad da suka shigo yanzu sundawo islammiyar da suka je da kyar suka bar Lubna na darzar kuka suka wadda Kuma ayanzu suka dawo su Gani yadda suka barta.
Ahankali Aunty Laila taji tausayin mijin nata na sake shigarta,Lubna da ke gefe zaune gwanin tausayi taci kuka har ta gaji da takarda ahannunta har tafara gyangyadi.
Ziyad ne ya matso A hankali ya matso kusa da k'anwarta sa yacire takardar Dake hannunta Yana Furta haryanzu bata daina kukan ba Aunty Laila,cikin Yar damuwa Aunty Laila ta Furta dukkanin mu nida Appah nku munyi rarrashin ta Amma taki yin shiru dama yanzu nake son na Maida ita d'aki Amma na fison barcin nata ya Riku sosai,d'an shiru tayi sai Kuma a hankali ta Furta cikin damuwa ni narasa wacce irin shak'uwa ce kukayi da wannan yaro haka,Ahankali ziyad ya Furtawa Mahaifiyar tasu Aunty Laila Had'in Allah ne,Kai kawai Aunty L ta iya girgizawa na tausayin Ya Yan nata ganin ziyadah itama dake gefe tayi tagumi,ziyad ne ya d'auki lubnah ya d'ora Bisa kafad'arsa bai sauke ta ko Ina ba sai akan makeken gadon su itadah ziyadah, shimfid'eta yayi Yana k'ara mata gudun Ac,sannan ya fito A hankali bayan ya shafa mata Addu,oi,falo ya dawo inda Mahaifannasa Suke da alwashi aransa na yau sai ya tambayi iyayen nasa dalilin da yasaka wasu lokuttan yake yawan ganin su cikin damuwa Dan yanzu duka yaga yadda suke cikin damuwa Kuma yasan badai matsalar

suce suda Lubnah ba,akwai wani abun da daban duk da yasan cewa suna da didi,wadda ayanzu ko iyayen su basu San inda take ba to Amma meya rabasu,me ne silar damuwar,ko itace damuwarsu,koma mene ne zaiji yanzu...

Bayan ya iso falon ne ya iske kowannen su zugun da damuwar da ke ransu itama ziyadah da tamaida kanta akan makeken Tv n dake falo bakomai take fahimta ba Wanda kallo d'aya zakayi mata ka gane hakan.

A hankali ziyad ya durk'usa akan gwiwowinsa agabansu Appah yana Furta,Aunty Laila!Ziyad yayi maganar cikin yin k'asa da muryar sa Mai nuna Abunda yakeji azuciyar sa agame da tausayin iyayen nasa,ya cigaba da magana kumin Alkawarin zakumin wata Alfarma d'aya,cikin k'akalo murmushi Aunty Laila ta furta wace Alfarma ce wannan Hassan domin haka take kiransa awasu lokuttan,cikin d'an murmushi shima ya Furta nidai Appah kuce kunmin Alfarmar Alkawarin duk abunda na tambaye ku zaku sanar Dani,cikin faduwar Gaban da tasame su suka Kalli junansu Jin furucin ziyad sai Kuma A hankali Appah ya Furta Munyi ziyad..cikin d'an rawar murya ya Furta Alfarmar danake Nema itace inason kusanar damu dalilin rabuwar ku da din mu da Kuma ahalin mu,shiru falon yadauka na Dan lokaci jikinsu Appah yayi sanyi Jin tambayoyin na ziyad,Ajiyar zuciya Appah yasauke yana Furta yanzu kuwa zaka ji komai ziyad domin dama b'oye b'oye baida Amfani bamu San Abunda rayuwa zatayi ba,nan gaba gara kusan komai Wanda ko da ta Allah ta kasance akan mu zaku iya Neman Dangin ku afadin duniyar nan tunda kunsan inda suke.ziyadah da ke sauraren su ceta dawo kusa da iyayen nata Jin tattaunawar su da Dan Uwanta....

Labari Appah ya basu na familyn su har b'acewar D'an uwansa,harzuwa dawowar su India da rabuwar su da Norah har jiran Kiran wannan mutumen da Suke Yi ayanzu Wanda yataimaka musu..
Babu Abunda ke tashi afalon kamar gidan mutuwa sai koke koken su ziyad da Aunty Laila wadda ke Jin komai yadawo mata sabo rabuwar ta da yarta tana Jin kamar yanzu abun yafaru tana tunano lokacin da ta kwantar da yarta akan gado sai dai ta wayi gari Babu ta hawayen ta tashare tana cigaba da yin kukan zuci Mai k'unar Rai.
Ziyadah ce cikin kukah take Furta Allah ya tonawa ko suwaye ke da Saka hannu acikin silar raba mu da ahalin mu da Didin mu asiri,Ziyad ne Shima cikin hawaye ya Furta Allah Kuma ya Isar muna da isarsa kasaka muna rabamu da masarautar mu da sukayi Yana tunanin wai Mahaifin su ne Gudan sarki ne Babba da kuma muk'amin (SIC) minister, security and investigation crimes na Nigeria,nan ma Kuma shine shugaba (C B I) central burea investigation na India,Sannan ace wai su Yan Nigeria ne kamar yadda sukayi ta sak'e sak'en shida Yar uwarsa kasancewar iyayen nasu basu sanar musu ba,sai dai sunyi hasashen hakanne ta wasu d'abiun na Mahaifan su da Suke kamanceceniya da na mutanen Nigeria,da wasu aladu da Suke kwatanta koya musu na Nigeria.. kenan hasahen su ya zama gaskiya su din Yan Nigeria ne l,iKon Allah ya Furta aransa cikin alajabin wannan Alamari..wani farinciki ne ya K'ara kama sa na tuna watarana zasu je Nigeria in Sha Allah,Dama Nigeria tana cikin manyan k'asashen da yake son zuwa ba tun yanzu ba.
A hankali yaji muryar ziyadah tana Addu,ar Allah yabayyana musu Didin su suganta tagansu.Amin dukkanin su suka Furta,kiraye kirayen sallar la,asar ne yasanya Appah da Ziyad mikewa suna yin alwalla suna wucewa masallacin unguwar tasu cikin jimamin abun da ke cikin zukatansu,Suma su Aunty Laila bedrooms din su suka wuce Dan gabatar da sallah akan lokacinta.

NIGERIA

K'aton d'akin taro ne da ya k'unshi manya manyan sojoji da Yan sanda masu fad'a aji suna tattaunawar akan videon da yayi trending akafafen sada zumunta na Yan

sandan da akayi ta Nema ruwa ajallo wayen da suka b'ata lokaci d'aya an Neme su anrasa sai dai me Rana tsaka aka Samu videon su Ashe kidnapping nasu sannan anyi musu kisan wulakanci na gilla Wanda Babu tausayi acikin kisan ko kad'an Wanda duk Wanda yakalli videon sai ya zubda k'walla na tausayin su,musamman yadda namun daji ke fisgar namansu...

Dady soja ne na hango cikin uniform na Sojoji Yana zaune ad'ai daga kujerun da aka tanadar don manya agaban kujerar sa an sanya akan wani tambari Mai dauke da sunansa, Major jabir Muhammad soja,domin yasamu k'arin girma,akwanan Baya.
Agaban rigar sa ma anyi abreviation na sunan sa MJM..da Kuma star uku aka fad'arsa.

A hankali Taron ke cigaba da gudana kowa Yana tofa albarkacin bakinsa,Muryar Dady soja ce cikin Rashin son wasa da yanayin sa na zaman sa babban soja yakw Furtawa cikin d'aga murya da b'acin Rai,"A wannan karon bazamu tab'a raga musu ba dukkanin mu ayanzu munsan wayenda da suke daurewa bandit din nan gindi duk wani ta'addanci suna mara musu Baya ne,Dan haka yanzu tunda mun Riga munsan komai bazamu tab'a bari ta addancin su yayi tasiri agare mu ba,dole mu tashi tsaye mu cece jihar mu Dama k'asar mu Baki d'aya,sun mamaye mu ne da har suka shiga gidan tsohon gwamna suka d'auko yarsa azaton mu bazasu iya shiga gidan Mai kud'i haka ba awannan lokacin ganin yanzu ko wa ya waye yana saka mugun tsaro agidansa,musamman kuma ace gwamna guda...
Ayanzu dukkanin duniya laifin mu take Gani Dana gwamnati basu San yadda muke iyakar kokarin mu ba muga ansamu saukin wannann Alamari,asamu zaman lafiya Wanda mukan mu mungi su buk'atar hakan,Wanda idan da zasu Duba laifin gwamnatin k'asa yafi yawa aciki wanda ita take da Iko da Alhaki da kowa ce jiha Ak'asar nan musamman ta bangaren tsaro wanda ita ya kamata ta Kara musu makamai da jami'ai domin zata iya k'ara musu din saboda manyan dakarun ta datake dasu agefe Basa lissafuwa,wani idan aka ce Maka sojan Nigeria ne bazaka yarda ba,Wanda da ace ta sanya hannun aciki da yanzu in Allah ya yar da Ankai Karshen wannan matsalar.. wasu mutanen Basa ganin kokarin mu ko kad'an duka rayuwakkan mu suna acikin rauni ne yau ko gobe Amma ahakan wasu ke muna kallon matsorata wasu har Furta Suke Yi yanzu idan munga bandit guduwa mukeyi mata muke komawa gabansu,maganar na k'ona mini Rai,duk da nasan hakan Yana faruwa ta sanadin Rashin manyan makamai da bama dasu, yanzu ka had'u da su kana da yar karamar bindigar ka da harsashe Daya su kuwa sun Kai d'ari biyu kowannen su da Ak 47 da uwar sarkar albarussai ajikin Mai zakayi wa kan ka mafita idan ba gudu ba,domin idan ba haka zaki salwantar da rayuwar ka abanza,abun haushi ace sojan Nigeria wani ko bindiga Bai da ita Amma kaga b'arawo da bindiga wadda ko afilms na America ba kasafai kake ganinta.. Rashin makamai shine Abunda ke saka jami'an gudu,da ce suna da kayan aiki wallahi Nasan da sun tsayu anyi ruwan wuta in Rai in mutuwa.....Kuma duka wannan laifin gwamnatin k'asa ne da ta jiha. kamar yadda na fada muku A chan Baya ko wa yasan laifin gwamnatin jihar mu ne inda suka dage da yin sulhu da su,Wanda da farko abun yaso yaje dai dai, sai dai kowa San b'arawo Bai da tabbas Bai da Amana Kuma baida Yar da ko atsakanin sa da Dan uwansa ne. ayanzu Koda gwamnati zatayi wannan sulhun mu bazamu yarda ba domin ta hakan ne suka shiga jikin mu suka kara samun damar cutar damu suka karanci wasu alamurran mu Wanda ayanzu abin bak'in ciki suturar mu itace tasu saboda lalalacewar k'asar mu..

Kuma dama a meeting din da mukayi da da governor ya Kara sanar muna Babu sulhu atsakanin sa da su Wanda Dama hakan yafi domin wayen nan Azzalumman mutanen bazasu tab'a barin satar yayan talakawa ba har da ma na masu kud'i,suyi musu fyad'e su ci musu mutunci su hanasu cigan rayuwa bayan dawowar su gida Gaban iyayen su,a Hana su shiga jama'a, domin naga mata da yawa da suka Auru dakyar, wasu kuwa suka kasa Autuwa gaba d'aya ta sanadin kidnapping Wanda Babu Wanda

ke iya tun karar su saboda bakin fentin da suka shafa musu,Wanda Koda Bai kasance da mace ba Alumma sun Riga sun shaidar saboda kasancewar hakan dabi'ar barayin.tabbas dole mu fito mu yake su takarfin mu..,Mai girma gwamna yakara sanar damu isowar wasu sabbin makaman yak'in,sannan an Kara fito da wasu hanyoyi na dabarun yaki fatan mu kawai awannan Karon muceto dukkanin bayin Allah Dake hannunsu batare da an karbi dukiyoyinsu ba ,Domin Ayanzu duniya ta d'auka cewa cewa 'yar wajen tsohon gwamna tashiga hannu yan dabar zamfara Wanda ya tab'a yin sulhu dasu ashekarun Baya Wanda kowa albarkacin bakinsa ya ke fad'a akan wannan Alamari,yanzu haka ana nan ana shirin Kai masu kudin fansa Wanda ak'alla kudin zai Kai billion d'aya,domin sune Abunda suka Nema na fansar ta,in sha Allah zamu Yi iyakar kokarin mu kamar yadda na fad'a yanzu mu ceto ta tare da yayan talakawan da iyayen su basu da kudin fansar ya yayansu ma.kuma in Sha Allah zamu k'watarwa wayen nan Police naku da aka kashe hakkin su zamu nunawa duniya ba,a kashe su abanza ba rayuwar su bata je abanza ba zasu ga irin wulakantaccen kisan da zamuyi wa wayen nan Azzalumman mutanen...A haka taro ya cigaba da gudana cikin tsari kowa Yana cigaba da Bada tasa shawarar tare da Kai matsayar Shirin da zasu mamaye su dashi.

***Yau tun safe yajejin fad'uwar gaba sama sama yarasa abunda ke damunsa,komai yak'ara dagule Masa ga tunanin da yazame Masa abokin fira akoda yaushe,itace yake Gani tana Masa gizo,ayanzu mafarkin nasa da ita yazamo kullum sai yayi sa da zarar bacci b'arawo ya kwashe sa zai kasance da ita acikin baccin nasa..
Yau Kuma ya tashi da faduwar gaba ga kansa da ke mugun sara Masa na rashi samun isasshen baccin da tun lokacin da yayi ido biyu da ita sai ya zame masa sai dai b'arawo ya sace sa,yau da wuri ya shirya saboda Ranar da sukeyin surgery ce Wednesday,ya shiryawar sa tsaf cikin had'add'un English wears yayi stocking abun sa ya tsuke acikin white t shirt Mai dauke da Rubutun MEN HEART da jeans blue black Wanda yazauna Masa d'ass tare da glass nasa k'irar company Rado Mai kyau Wanda ba kullum yake Saka Saba,dalilin Saka shi yau ma Baya son iyayen sa su gane wani abu na damunsa na yanayin da yake ciki Wanda zasu iya karantar sa aciilkin idanunsa, domin ya fahimci damuwar sa da rauninsa sun fara Bayyana kansu afili,fuskar nan tasa shek'i takeyi yayi wani fiyau da shi sai Yar ramar da yayi ta Kara masa kyau wadda ta Bayyana kanta karara,Amma hakan Bai Hana kyawawar fuskar sa Kara Bayyanar da siririn kyawunta ba, kyakkyawar fuskar sa sai Kara shek'i takeyi kamar Anmasa wankan zinare pinks lips dinsa da suka Sha lipbalm sun k'ara yin wani jaa gwanin burgewa,dogon hancinsa kuwa yak'ara bayyanar da tsininsa na Yar ramar da yayi bayan gama Shirin sa ne ya saka takalminsa rufaffu masu kyau farare tass masu kyau Wanda daganin su kaga naira ta zauna ajikin su,turarrukan sa oud yak'ara fesawa masu k'amshin dadi Yana barin d'akin nasa,batare da ya tsaya gyaran gashin kansa ba da ya d'an barbazu kamar yadda yasaba..Wanda duk da haka sai hakan yakara yiwa kyansa Armashi Wanda daganin sa kaga gwarzon namiji.

Tun daga nesa k'amshin sa ya Bayyanar da zuwan nasa cikin falon har zuwa inda su Unni Dake falon kan dinning suna break fast,wayar sa yake pressing atsanake Yana replying na Whatsapp messages da Instagram da suka tarar Masa sanadiyyar gushewar natsuwar sa.

A hankali bayan isowar sa kan dinning din ya mayar da wayar tasa cikin aljihu..

Cikin sauti Mai kyau A hankali ya Furta Nurul hayat BONJOUR da yaren french,Ina kwana da yaren mu na Hausa,cikin D'an kafesa da ido ta Furta lafiya Lau cikin yaren ta na larabci,fahimtar Abunda yake nufi sai dai bata iya mayar Masa Wanda ko wannan word din gare sa ta koya...tana k'ara furta meyake damun Kane Nur,cikin Rashin damuwa ya furta ba komai kawai

Unni stress ne,kallon sa kad'ai tayi batare da ta yarda da Shiba dan Yan Kwanakkiin nan tana lura dashi ko yar walwalar sa ta rage ga Rashin maganar sa da misklillancin sa da yak'aru,tasan cewa Ammar Bai cika mata k'arya ba,Amma awanann karon yayi mata,Dan tasan ba gaskiya ya fad'a mata ba,akwai Abunda ke damunsa,Amma ba komai zata cigaba da Sa ido akan yaron nata taga iya gudun ruwan sa domin ba kasafai yake iya had'iye damuwar sa ba tare da yasanar mata ba ko Aj, Amma a wannan karon yayi inda hakan ya tabbatar mata Babban Abu ne ke damun Ammar din.inda tayanke shawarar idan har taga abun yayi yawa zata tambayi Al Amin taji komai tayanke shawarar da zuciyar ta.

Mahaifiya kenan
Allah yasakawa iyayen mu da gidan Aljannar Firdausi□□

Muryar sace ta ta dawo da ita daga maganar zuciin da takeyi inda yake gaida Mahaifin nasa ta hanyar Furta yaya Dady Ina kwana cikin yaren india Ahankali sarki Ali Yayi murmushi tare da Furta yau Kuma mutanen India Akai na suka motsa,to ai da yake Nima na Dan iya wasu kalmomin daga cikin yaren,Nasan gaisuwar safe ce nasamu haka,Yana Furta kucch kucch ho lagayaniye lafiya,murmushin gefen Baki Dr .Ammar yayi wanda ya Dade baiyi ba,su mahir ma dasu Nisa da unni dariyar sukayi na Jin yadda yaren Indian in da Sarki Ali ya had'a da hausar mu wai lafiya,Kuma wai gaisuwar safe ce,Shima kansa sarki Ali dariyar yakeyi...
A hankali yajawo D,aya daga cikin kujerarun ta kusa da Unni da sarki Ali ya zauna Yana ya mutsar kyakkyawar fuskarsa najin kansa na Kara Sara Masa tare da cigaba da faduwar gabansa,duk abunda yake Yi dukkanin su iyayen nasa suna lure dashi,Kai kawai Unni ta girgiza Dan tasan badai lafiya ba ,ayanzu tak'ara tabbatar da maganar da yafurta mata ba gaskiya bace.

Had'add'en shayi da yasha kayan k'amshi Unni ta Had'a Masa yau anyi sa,a zai tsaya yin breast fast din dan kullum cikin sauri yake,mafi yawan lokutta sai dai Akai Masa breakfast din chan Asibiti Wanda Kuma b'aci yake ba yadda ya kamata,ko yace akoshe yake Kuma duka ya tsiro da wayen nan halayen ne acikin Yan Kwanakkiin nan Dan damuwar da yake ciki baza ta barsa zaunawa yasakawa cikin sa wani abun kirki ba,filet tajawo Mai kyau ta zuba masa soyayyen biredi da masar kwai da Irish da yaji had'in kwai wato sultan chips,agabansa ta tura Masa tare Sanya Masa pork aciki,tana furta Bismillah,kallonta kad'ai yakeyi ganin uban shayin da Ta zuba Masa a cup Wanda sai da tacika Masa shi,ga Kuma filet da ta cika Masa Wanda baijin zai iya Cinye duka abincin,ita kuwa Unni tayi hakanne Dan tasan yadda cikin sa yake,Bai wasa dashi,Kuma tana sane dashi Yan kwana biyun nan ya rage cin abincin da yawa.
Tabbas yanajin yunwar ayanzu haka cikin sa Yana Jin Yana d'an kugi kad'an na yunwa Amma Yana jin kamar bazai iya Saka komai acikin nasa ba.

A hankali ya janye idanunsa akan Mahaifiyar tasa Ganin irin kallon da take Ma idanunsa ayanzu da yacire glass akansu Wanda ke nuna kamar tana karantar wani Abu akansu ne, Yana Karb'a gaisuwar da su Nisa ke Masa,tare da fara yin breakfast hankali kwance,cikin natsuwar sa yake yin sipping din shayin da yaji yamasa dadi Wanda Bai ankara ba har yasanye sa,kadan ya tsakuri this thing😂 Dake cikin filet din sannan ya Sha ruwa tare da yago k'atuwar tissue Dake kan dinning din ya goge gefe da gefen bakinsa da labb'ansa da ke shek'i,sannan ya mik'e Yana yiwa iyayen nasa sallama,tare da Karb'awa Yan uwansa da ke Furta Adawo lafiya" Yana Furta Allah yasa" suna Amsawa da Amin,Da Addu,ar iyayen nasa yafita ta fatan nasara da kariya agaresa da Yan uwansa Yana ficewa daga masarautar Baki d'aya acikin farin cikin Addu,ar iyayen nasa.
A cikin hadadd'iyar motar sa k'irar lemo XIN bak'a wulik wadda shugaban k'asa yayi musu kyautar ta aranar bikin Bude Asibiti,wadda shi yake tuk'a kansa da kansa Dan

Dama Bai cika son wani yayi driving nasa ba,yafi son simple life,shiyasa kwata kwata yake gudun sarautar ta gidansu,saboda yasan ta kurar da ke cikinta..

.BUG.
.....✍✍✍
Typing Long page is'nt easy wallahi😫😲

COMMENT KAD'AI NAKE BUK'ATA DA LIKE✍✍✍✍

Faiza Almustapha
FIRSTLADY
Yar lelen Taskira

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG
heart touching story

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*

A MAFARKI NASANTA
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
Fa'eeh BG

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai

First lady

_Yar lelen Taskira _ ---
TASKIRA WRITER'S FORUM
T. W. F

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA
_____

بسم الله الرحمن الرحيم...

*(صل الله عليه وسلم) فيدك، ابي وامي يارسول الله *

Free

EPISODE1
PAGE56

TYPING

follow me please on

@Arewabooks
@Faizatou

Wattpad
@Fai'zaMurai

Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠

***

_____Halee ce kwance yau tun safe bata da lafiya sai Kuma ciwon ya K'aru akan Abunda Baba Asabe ta Yi mata akan ta zubar da garin Koko ba da gangan ba,ta zazzage ta tare da mari, Mari har biyu,tare da kalamai marassa dad'i, A yau ta na Jin bazata iya hakuri ba tanason sanin itadin Wacece,Ayau ta d'au Alwashin duk da yadda take Jin Rashin lafiyar na damunta ta matsanancin ciwon kan da take fama dashi sai ta Rok'i Baba Adee Da yasanar da ita d'in Yar tsintuwa dince Yar gaba da fatiha kamar yadda Baba Asabe ke yawan Furta mata...
Ahankali hawaye masu zafi suka silalo mata masu zafi da rad'adin Rashin makama,gwanin ban tausayi gefen hijab d'inta tasanya tashafe,Khady Dake kallon kyakkyawar fuskar ta da yan yatsun Baba Asabe suka kwanta rad'am akan kyakkyawar fuskar ta kamar an Dora su abu ga farar fata,Kai ta girgiza kawai na tausayin Yar uwarta ta,Dake cikin rad'adin Rashin gata na Mahaifiya, Addu,a tayi Allah ya bayyanar da iyayen
Halee idan har suna Raye da ahalinta,tunda dukkaninsu yanzu sun San ba yar Baba Adee bace.

Sallamar Baba Adee ce ke katse ma Khady maganar zucin da takeyi,Dan dama yaune yasanar zai dawo Dan yak'ara Duba jikin Halee da yatashi Kwanakkiin baya ,fitowa Khady tayi ta tarbesa cikin farin ciki,ruwa takawo Masa da Abinci bayan karb'ar jakarsa takaimasa da'ki,A hankali ya Furta Khadija Ina shalele,cikin Yar damuwa Khady ta Furta tana d'aki batada lafiya tun safe A hankali cikin dattako da kulawa ya Furta shine ba,a kirani aka sanar Dani ba,ina ita Lauren take ne,Khady cikin Jin haushin Mahaifiyar ta ta tafurta cikin gayya ta tafi gidan indo,Dan sai da ta kwabe ta akan kar tace Masa gidan indo taje,shiyasa tace mata tace wai tace gidan Baba mudi taje,Mahaifin Baba Adee"wurin ganin iyah,Dan tasan ya Hana ta zuwa gidan Indo domin yasan harda chan ake k'ara b'ata Masa mata ake hure mata kunne tadawo tana wulakanci guda guda ga Halee,shanye b'acin ransa yayi Yana Furta kiramun ita inganta in tana iya fitowa..da touhKhady ta Amsa Masa tare da juyawa tana dosar d'akin su Dan Kiran Halee,Zaune ta iskota ta tsurawa gefe guda ido tana ta faman tsiyayar da hawaye gwanin tausayi hannunta dafe da kanta Dake mugun sara mata,Khady bata ce mata k'ala ba sai hawayen da ta share mata tana riko hannunta d'aya,ko ba,a fad'a mata ba tasan gurin da Khady zata kaita Dan taji Muryar sa,A hankali suke takawa har suka iso inda yake har yafara cin abincinsa,kallon Halee yakeyi cikin tausayi da soda kaunarta da yakeji har cikin ransa fiye da Yar cikin sa Khady.
" Sannu ya Furta mata cikin tausaya wa, bayan Karb'a mata barka da zuwan da take Masa,
"Meya samu fuskar ki ne naga kamar kwanciyar yatsu ajiki ga Kuma kwanciyar Jini acikin idanunki gefe da gefe, yakara tambayar ta bayan ta d'aga Masa kanta alamar yawwa.

A hankali cikin in in Ina ta furta Dady saurayen da akayi jiya ne naje dukan su sai na doke kaina,har nabuge fuskana,jiya bamu samu wuta ba,tana Kai k'arshen maganar ta duk'ar da kanta k'asa alamar Rashin gaskiya a maganar ta,kallon ta kad'ai yayi Badan ya yarda da zancen ta ba,Tambayar ta yak'ara yi in Tasha magani kanta tad'aga Masa alamar ehh,Abun ci ya K'ara tambayar intaci,Kai kawai ta d'aga Masa tana k'ara dafe kanta Wanda take ta Dan mazewa agabansa.,cikin tausayi Baba Adee ya furta rik'ata Khadija kuje ta kwanta sai ta samu Hutu,taji furucinsa Amma ta kasa mik'ewa saboda tambayoyin Dake cin harshen da zuciyar ta,da damuwarta ayau,Khady Dake tsaye gefen ta ne ta Furta tashi muje Koh,ka fad'a ta mak'e Alamar bata zuwa,Dan kallonta Baba Adee yayi sai Kuma ya Furta" meyasa bazaki je ki kwanta ba kinason k'ara wa kan ki ciwo ne ayanzu bacci kawai kike buk'ata shiine zai Saka ki Kara samun relieve nan take.
'Wasu hawaye ne masu zafi suka silalo mata tasanya gefen hijab dinta ta goge.

Kara kallon ta Baba Adee yayi cikin nazartar ta ya Furta "meye matsalar Halimatu sadiya " d'ago kanta tayi Jin ya ambaci Cikakken sunan ta Wanda duk lokacin da ya Kira ta cikakken sunan nata da tanajin wani iri kamar akwai wani Wanda yake kiranta da irin wannan sunan haka sak two names din,Kuma ta kan ji wani iri ajikinta. Ahankali Kuma ta Furtawa Baba Adee cikin damuwa da marairaice Masa Dady Alfarma nake Nema, Alfarma! kai ya Jin jin jina mata Tare da kafe ta idanusa,Dan shiru tayi kamar bazatayi magana ba sai Kuma A hankali ta Furta Dan Allah Dady kasanar Dani ni din wacece,su waye Iyaye na,suna Raye ko Basa Raye,inadasu ko bana dasu,na rok'e ka badan na gaji da irin kulawar da kuke bani ba,hasalima Dady wasu lokuttan nakanyi kuka na Rashin fitowa daga tsatson ka naso ace ni jininka ce kamar Khady Dan shiru tayi tana share hawayennta tare da d'an runtse ido da dafe kanta sannan Ahankali ta bud'e idanunta ta suka rine sukayi jawur na azabar da take ci na ciwon Kai da da damuwar da ke cinta ta Furta Inason ji ne daga gareka Dady ni yar halak ce ko akasin ha....kuka ne ya kubce mata Mai karfi batare da ta karasa maganar ta ba,kuka ne takeyi Mai cin Rai musamman in ta tuno wannann Kalmar ta Yar gaba da fatiha da Baba Asabe ke yawan Furta mata ayanzu Kuma tsoro ne yashige ta gudun Jin abun tashin hankalin da Baba Adee zai Furta mata,dukkaninsu sai da suka tausaya mata,irin kukan da take maicin Rai da rad'adin azuciyar maiyinsa ko Mai sauraron sa.

A hankali Khady ke taping bayanta tana lallashinta,Baba Adee da ke ta nazartar kalamanta ne Jin irin furucin da tayi,tunani barkatai ne suka shigo Masa Akai 'waya gurb'ata mata tunani waya Sanya mata kokwanto akan rayuwarta, kenan tuntuni Abunda ke ranta kenan baiwar Allah Kuma ta iya hakuri har aka Kai wannan lokaci bata nemi sanin Wacece itaba zuciyarsa ce ta Karaya na tausayinta da Jin bakin ciki marar misaltuwa akan maganar nan ta ita ba yar halak bace tabbas da ace yasan Wanda ya har mutsa mata tunani da ya masa wulakanci yasan koda ya tambaye ta ba zata fad'a Masa ba Amma tabbas duk ranar da ya kama ko waye sai yagane kurensa.

Hmmm ni Kam nace

Ahankali yaji ayau tabbas dole yasanar da ita komai daga cikin Abunda yasani,nadaga rayuwarta kafin bayyanar Ahalinta agareta tunda ta Rok'esa da Kuma wannan mummunan kalamin da aka sanyamata azuciya. Tausayin ta ne ya K'ara kamasa ganin yadda hawayen ta sai Kara kwaranya Suke Yi,Wanda yasan cewa na bakin ciki ne,kansa ne yaji yafara juyamasa kamar zai rabe gida biyu kamar zai bar duniyar Addu,oi yadinga Yi azuciyar sa inda take Ahankali ya fara samun natsuwa kan yadaina juya Masa, A hankali Kuma ya Furta mata Bayan samun natsuwar tasa, ki

share hawayen ki H sadiya ayanzu Kuma ayau zan sanardake yadda akayi kika zo hannu na kika zamo Amana agare ni.

LABARI

A wata safiyar talata ce nadawo daga Gusau gurin siyayyar kayan Khadija alokacin tana gab da cika shekara guda da watanni shida kayanta duk sun matse ta kasancewar ta yarinya Mai jiki sosai A lokacin,na kawo guraren hanyar da zata Kaika Nahuce,kasancewar maraice tayi hanya Babu kyau kowa Yana sauri ya Isa gida gudun had'uwa da masu garkuwa da mutane,.kukan yarinya ne k'arama nake ji Yana shiga kunnuwa na har na iso inda nake Jin kukan yarinyar sosai Wanda sai k'ara shiga kunne na yakeyi har na yanke shawarar in ta fiyata sai Kuma wata zuciya ta gargade ni da kadawo ka Duba yarinyar da ke cikin halin taimako ta yuyu uwarta ce ta Yar da ita akan hanya kamar yadda Yan mata masu cikin da ba,aso ke Yi,Kuma kar kamanta kana da ya mace gida irin haka in ka taimake ta Allah zai taimake ka haka na bi shawarar zuciyata ta kwarai,na dawo baya da mashin Dina dai dai saitin inda nakejin kukan yarinyar,sauka kan babur Dina nayi na shiga cikin dajin inda na Rika bibiyar kukan yarinyar har na kawo saiti wata Yar k'aramar yarinya wadda bazata wuce shekara biyu ba,gata zaune ta juya Baya sai kuka take ta tsalawa, A hankali na K'ara ta kawa na Isa Gaban yarinyar na durk'usa, kyakkyawar yarinyace kamar diyar larabawa fara tass kamar ka k'wanta jini ya fito nayi ido biyu da ita taci kuka har tagaji ta gode Allah idanunta sunyi jajir gwanin tausayi, Ahankali ta d'ago kanta Dake k'asa ta kalle ni da rinnanun idanun ta da suka rikide sukayi jaa sai Kuma A hankali ta sauke ajiyar ta zuciyah tare da numfashi kamar wadda tadade ba taga Mahaifiyar ta ba ko mahaifinta Rana tsaka ta gansu.. ta Furta mini cikin gwarancinta Ann cle tana tsaida kukan nata,Wanda yatsaya Chak kamar dama ni take Jira,Un cl! Un cl din take ta nanatawa tana mik'omin hannunta Alamar in d'auke ta cikin farin cikin da nagani kwance akan fuskar ta, kallon yarinyar kawai nakeyi kamar insaka mata kuka na tausayin ta,ace yarinya k'arama zaune acikin wannan Daji wadda na fi tunanin yarda ita akayi cikin Daji irin wannan Kuma a irin wannan zamani da muke ciki.
Tun lokacin da na Had'a idanu da yarinyar naji Allah yasanya mini Sonta da tausayinta azuciyata Wanda har naji zan iya had'ata da Khadija in Raine su har ma in fifita ta akan Yar cikina, Inaji kamar ace itama din jini nace, ta fito daga tsatso na sai dai Kash,Allah ne ya had'ani da ita alokacin da banyi tsammani ba ko Aune ba, Hannayenta da tad'ago mun na sunkuya na mik'ar da ita tsaye,doguwar rigar da ke jikinta fara tass,da hijab pink Dan k'arami da Yan madaidaitan takalmanta Suma masu kyau suma farare tass da ganin shigar ta kasan cewa ta fito daga gidan masu arziki ne ko Babban gida,Hannunta da ke cikin nawa ne na lura da Dan k'aramin hannunta na dauke da zoben gold A yatsar ta mai bi ma Babba zoben na dauke da wata kwalliya ajiki Mai kyau da tsada inda atsakiyar sa Anyi rubutu Mai kyau da tsari an rubuta wasu haruffa guda biyu had'e da juna Wanda ko ni sai da nayi dakyar nagane Dan sai da nazauna na K'ara Duba zoben inda aka rubuta HA Wanda shi yak'ara Tabbatar mun da cewa yarinyar ta fito daga Babban gida ne Kuma Masu kud'i domin wannan zoben nata kudin sa akiyasi a wanchan lokacin zai Kai miliyan goma,d'aukar ta nayi nad'aura akan ka fad'ata ganin duhu ya fara Wanda duka alokacin tadaina kukan sai ajiyar zuciya da take ta saukewa,....
A hankali naji ta Furta mun cikin Yar k'aramar muryar ta da gwarancinta cikin yaren turanci,un cl Pape r inda shi yak'ara Tabbatar mini da yarinyar Mai wayo ce da basira Jin yadda ta fito da Kalmar turanci abakin ta,Chak na tsaya Dan na fahimci abunda ta Furta saboda saboda inada saurin gane maganar Yara,Kuma tabbas d'azu naga faduwar takarda ahannunta lokacin da na mik'ar da ita tsaye, dawowa nayi da Baya nadauki farar takardar Dake nad'e ak'asa,hannu nasanya na warwareta,tare da karanta abun da takardar ta k'unsa,Bayan Sallamar da aka gabatar akayi rubutu kamar haka...

(Bawan Allah karike wannan yarinyar da ka tsinta,kadauka cewa Allah ne ya baka Amanar ta,wannan yarinya da ka ke Gani akwai had'ari Mai yawa arayuwarta da ta iyayenta shiyasa muka zab'i mu ajiye ta Anan Allah ya kawo na kwarai ya tsinceta tabbas muna da yakini akan Ko wanene ya tsinceta,muna da yakinin zata shiga hannu Mai kyau da yardar Ubangiji,kad'auketa matsayin Amanar Allah please!! Sunan ta shine Halimatu sadiya ana mata lak'ani da (Norah) Sunan Mahaifin ta Umar) ga Abunda zaka iya samu daga cikin rayuwarta kenan wassalm.

Bayan gama karata sak'on da takardar ta k'unsa sai Na tsin ci kaina cikin tsoro da tausayin wannan yarinyar na ganin ta k'aramar yarinya ta tsinci kanta acikin rayuwar Rashin galihu Rana tsaka tun alokacin naji cewa zan iya kula da ita da d'an karfin da Allah ya hore mini,na rik'e Amanar da Wayen nan Bayin Allah suka bani suka bani amatsayin Amanar Allah Acikin takardar.takaradar nasanya Acikin Aljihu na sannan muka fice daga dajin daga nan nadaura ta Akan babur Dina,Alokacin ne Kuma na cire zoben Dake hannunta Dan gudun wata Alama da zata bayyanar da ita akan masu bibiyar rayuwarta alokacin,Ayanzu haka ko lauratu bata San da zaman zoben ba da takardar,Mun iso gida lafiya na damk'ata wa lauratu Amatsayin Amana tacigaba da kula Dake da Khadija,nayi iya kokarina Dan in kare ki Alhamdulillah har yanzu babu wata matsalar da ta tab'a kutso Kai agare ki game da maganar da sak'on takardar ya Kunsa na hatsarin Dake acikin rayuwar ki,ni fatana kawai Allah yasa iyayen ki sun fita daga sharrin Azzaluman Dake Neman salwantar da rayuwarsu.
Ayanzu haka takardar tana nan da zoben ki, A hankali ya mik'e yad'auko tsohuwar ajiyar yafito da takardar da ke ciki wani d'an akwati k'arami inda yake ajiyar Abu mai mahimmanci wadda har ta chanza kala,takarda ce lankahe da zobe acikin ta d'an madaidaici irin na Yara sai walk'iya yakeyi gashi nan sak kamar yadda Baba Adee ya siffanta sa,mik'a mata takardar yayi inda tafara karantawa har Takawo inda ake cewa rayuwarta na cikin hatsari itada iyayen ta,kan ta ne yayi wata irin sarawa ya fara juyamata tunanin take aranta kenan iyayen ta basa Raye duk yadda take so ta gana dasu Ashe an Riga an kashe mata su..

Ahankali Baba Adee Dake kallonta ya Furta cikin tausayinta"ke ba bayar gaba da fatiha bace ke Yar halak ce,Dan banason Kara Jin irin wannan maganar,Kinga yanzu ke Yar Sunna ce,Dan haka ki cire ko kwanto aranki domin daga yanayin wannan rubutu ya Kara tabbbatar muna Dake Yar halaliya ce Kuma shi ya tabbatar muna ke wacece.

Hawaye take ta zubarwa tana juya zoben Mai kyau A hannunta,tana share su wasu na zubowa,Khady Dake gefe itama kallon Yar uwarta ta take Yi cikin tausayin ta,A hankali suka ga idanunta na lumshewa suna budewa daddafe kai tayi tana cigaba Furta innalillahi wa Inna ilaihi raji'un,sai ga hawaye Shar sun sauka akumatun sai Kuma kamar k'yaftawar idanu ta fad'i k'asa sumammniya kamar bata da Rai
Uwar k'ara Khady tasan ya Ganin Halee bata numfashi hankali tashe Baba Adee ya yayyafa mata ruwa Amma Abanza ko kad'an bata motsi, Hankali tashe Baba Adee ya fiddo yar k'amar wayarsa keypad Yana dannawa makwafcin sa driver waya cikin damuwa ya sanar dashi halin da ake çiki,mu had'u k'ofar gida ya Furta Masa ad'ayan b'angaren Suna Yanke Kiran da gudu Khady ta shiryo tare da d'akkowa Halee dogon hijab tasanya mata tana cigaba da rusar kuka ganin kamar Babu Halee d'in komai yayi collapse ajikinta,Haka suka d'auketa kamar gawa gashi Dama ga yadda jikin na ta yake Sanya ta cikin motar sukayi Khady tashiga Baya tare da ita kusa da Halee,Baba Adee agaba sai driver..har zuwa wannan lokacin kuwa Baba Asabe batadawo ba,sai dai Baba Adee ya rufe gidan suka kama hanyar Gusau "Norah specialist Hospital Gusau" tun amota Baba Adee yake ta Jin nadamar sanar da ita labarinta Wanda yake ta tunanin zai kawo mata sauyi arayuwarta,Ganin yadda ta

Rok'esa da Allah,sai dai Bai da zab'in da ya wuce yabata labarin Domin samun kwanciyar Hankalinta Kuma yasan tilas ne dole wata Rana zata sani, tausayin ta ne ya k'ara kamasa ace karamar yarinya tana had'uwa da jarabawowi iri iri.

Alhamdulillah komai Yana ta warware muna,A hankali zamu bud'e komai,in Sha Allah ✍✍✍✍✍✍✍

Me kuke tunani A had'uwa ta biyu tasu...
Mudai had'u anjima zaku ga komai✍✍
Nasan Zaku ji dadin page din □□

Kuyi hakuri da jina da kukayi kwana biyu shiru....

Like pls and comment
Faiza Almustapha
FIRSTLADY□
Yar lelen Taskira □ □

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG
heart touching story

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*

□□□□□□□□□□□□□□
□A MAFARKI NASANTA□
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

□First lady□

_Yar lelen Taskira _ ---
TASKIRA WRITER'S FORUM
□T. W. F□

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA□

بسم الله الرحمن الرحيم...

*(صل الله عليه وسلم) *فيدك، ابي وامي يارسول الله □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

Free

EPISODE1
PAGE57

TYPING

follow me please on

@Arewabooks
@Faizatou

Wattpad
@Fai'zaMurai

Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠

Da isarsu Cikin Asibitin aka gungura Halee a table bed ba,azarce da ita ko ina ba sai emergency,Nurses ne suka duk'ufa akanta sunyi iyakar kokarin su duk yadda zasuyi sudawo da numfashi ta dai dai abun ya gagara,har mouth to mouth resuscitation (kiss of life) wata sister tabata,inda zaka bawa mara lafiya numfashi ta hanyar baki da Baki,Amma ko kad'an numfashi ta yak'i dawowa...
Da gudu d'ai daga cikin Nurses din Dake cikin emergency din ta watsa da aguje zuwa office din Doctor Ammar ko sallama batayi ba ta fad'a office din nasa samunshi tayi zaune akan kujerar sa sai faman jujjuyawa takeyi dashi idanunsa Alumshe,cikin tashin hankali ta Furta Doctor we have an emergency patient right now munyi iyakar kokarin mu but still she's unconscious,Doctor we need your attention there no need to wait...

A hankali idanunsa da ke alumshe ya watsawa Nurse feedo kallo guda yayi mata ganinta cikin tashin hankali wanda shi zai nuna dagaske pt din na Neman taimakon sa, dauke Kan yayi,Nurse wadda yaji shigowarta hankali tashe yasan Abunda dama zata Furta Masa kenan emergency case ne dasu Jin ko Neman izini batayi ba,Wanda ba yanzu ne farko ba,inda duk yaga nurse ta shigo office nasa hakan yasan emergency case ne,inda sunfi son su Isar da sak'on ta baki duk da telephones Dake akwai a inda Suke wadda take da connection akowanne wuri inda za,a iya samun Doctors...

Ya Furta mata go and meet Doctor Alamin,Am not feel ok,yakai k'arshen maganar tare da Kara Lumshe manyan idanunsa Jin wani kalar tsinkewa da zuciyarsa takeyi ayanzu...
Cikin sauri Nurse feedo Dake cike da Jin haushin sa aranta saboda izzar sa data Masa yawa gashi ko d'an k'yale _k'yalen nan da takeyi inzata zo Asibiti dansa Bai tab'a ko yimata kallo biyu ba arana magana ma wannan Bai cika tanka mata ba ko da gurin aiki ne suka had'u...

Tura office din Dr Aj tayi tashiga da sauri Wanda ta iske sa Yana soyewar sa da masoyiyarsa...da sauri tasanar Masa da halin da ake çiki Shima cikin azama ya yanke Kiran wayar tasa Yana Furta sweet I will call you back ! Dasauri suka fice daga office d'in nasa zuwa emergency,daga farko Bai gane Wacece patient din ba,sai daga

Baya da yamatsa kusa da ita. kyakkyawar fuskar ta yaci karo da ita tayi wani irin kyau na ciwo fuskar ta tak'ara yin wani jaa Mai kyau sai walk'iya takeyi kamar anyi mata wankan Madara...

Ahankali Dr Aj ya Furta Halimatu sadiya Umar cikin ransa,cikin tausayin ta yake tambayar kansa meyasameta haka da ya tado da ciwon nata.,cikin sauri da son ceton ranta yafara gwada dabarun aikin su na likitota. dukkanin kayan aikin da nurses sukayi Amfani da su yayi har su Ampu bag ,da wannan na ,urar Mai kama da ion na manta sunan sa,ni ko ion machine resuscitation ne,ya jona mata yasanya mata Amma shiru kiss of life ne kad'ai baiyi mata ba Hankalin sa ne ya tashi ganin ta ki motsawa ko kad'an duk da wannan na'urar da ya jona mata wadda duk Wanda akayiwa akanci nasara indai Bai Yi Nisa ba yakai gargara numfashin sa zai dawo take ko da ba Yi Daya bane,cikin Yar damuwa ya fice daga A&E din cikin tausayin yarinyar bai zarce ko Ina ba sai A office na Dr Ammar,Lumshe idanunsa suke kamar yadda nurse feedo ta barsa,k'ara Lumshe idanun nasa yayi bayan Dan kallon inda Aj yake tsaye... Yana k'ara Jin kamar yabi zuciyarsa Yana jin kamar yaje ya bawa pt din taimakon gaggawa tare da k'ara Jin damuwar Dake cikin ransa tana k'ara Bayyana,ga Kuma tsinkewar zuciya da ayanzu yake jinsa kamar ya K'aru...

A hankali cikin Yar damuwa Dr.Aj y Furta dude kaje ka Duba patient Dinka har yanzu she's un ncouncioun ,A hankali manyan ya Idanunsa suka ware akan fuskar d'an uwan nasa Yana Furta "pt d'ita" bisa labb'ansa Jin furucin na Aj kamar zai k'ara yin magana Sai Kuma ya fasa ganin yanayin damuwa kwance akan fuskar Dr.Aj,A hankali ya mik'e Yana ficewa daga office din nasa cikin yanayin sanyin jikin sa da rauninsa da yake Jin yak'aru.Dr Aj Dake nazartar sa Yan Kwanakkiin nan kallon sa kad'ai yayi Yana girgiza kansa cikin tausayin d'an uwan nasa,Dan yashiga tarko Mai wuyar fita sanin da yayi an Riga anyi Masa tigaye akan Abunda yake wahalar dashi Wanda ayanzu yagano dukkanin damuwar d'an uwan nasa,Bin bayansa yayi cikin tausayin sa har suka shige Emergency ward d'in....

Su Baba Adee da Khady zazzaune Dake zaune areception sun rafka tagumi musamman Khady kowannen su na cikin zullumi da fargar faruwar wani abu ga Halee,ganin da sukayi anja lokaci Babu wani bayani daga likita ko nurse,sai dai ganin da sukayi anata shiga da fice a emergency room ward din Wanda yake tabbatar musu da Halee na da sauran Rai kila har yanzu ba,ayi nasara ba ko ana ta kokari kanta ne.

A B'angaren Dr Ammar kuwa tun lokacin da ya shiga unit din yafara Sassanya mata wasu irin na urori cikin kwarewa wayenda zasu taimaka ma dai dai dai tuwar numfashinta da dawo da bugun zuciyarta sai dai har minti uku tacika Babu alaamar motsi atattare da ita,Wanda duk abunda yakeyi ayanzu Yana yin sa ne cikin kuzarin sa da sauri da sauri Wanda yaji kamar an Saka Masa k'warin gwuiwar yin aikin,duk da ta wani b'angaren Yana Jin tsinkewar zuciya da faduwar gaba..

Duk wani Abu da yadace yayi mata yayi Amma shiru resuscitation d'aya yarage yayi mata shine (kiss of life) tun da duk an yimata sauran sai dai ba,ayi nasara ba,inda yakejin alamar nasara awannan na karshen saboda ana dacewa sosai,Wanda yake tunanin ba,ayi mata shi ba..

Bai da wani zab'i face na yimata mouth to mouth resuscitation d'in (kiss of life)..
Dr.Aj Dake kallonsa ne Yana Jiran yaga reaction nasa,ya Furta azuciyar sa "Yana nufin har yanzu baigane fuskar ta ba ko pretending ne yayi ?....
Maganar zucin sa ce ta katse ganin uwar zaburar da Dr.Aj yayi bayan cin karo da kyakkyawar fuskarta wadda ta bayanna na agaresa alokacin da yake k'okarin bata numfashi ta Baki,ganin ta ya masa bazata,kallon ta yakeyi Bako k'yaftawa,Yana Jin wani sanyi na ratsa zuciyar sa bugun zuciyar sa na dai daita bayan cin karo da

Abincin ruhinsa Wanda yasanya sa sauke k'atuwar ajiyar zuciya batare da ya shiryawa fitowar ta ba,kallon ta yake Yi cikin bege da soyayyar ta Mai tsananin azuciyarsa wadda ayanzu ta kasa b'oyuwa,tausayin ta ne yak'ara kamasa,Farin ciki yake ji na ganin ta ko akasin haka a zuciyarsa,tambayar kansa yayi me yayi shock d'in ta haka Wanda har yajawo mata doguwar Suma haka Kuma shock irin Wanda ba,a so cikin zullumi da tausayin ta yayi sauri Yana Dan k'ara matsawa akusa da ita domin ceto ranta Wanda yake k'okarin sakawa kansa karfin hali da yin Amfani da zuciyarsa ta maza duk yadda yakejin razana acikin zuciyarsa haka ya lullubeta da sanyawa kansa k'warin gwiwa wajen ceto ranta.

A hankali ya K'ara matsawa akusa da kyakkyawar fuskarta gudun kar Nurses da doctors din Dake gurin suyi Masa wata fassarar duk da dukan su Basa Gaban sa, Ahankali ya sunkuyar da kyakkyawar fuskarsa iZuwa tata kallonta yakeyi deep down inda yasauke breath Mai zafi ji yakeyi kamar ya had'iyeta saboda k'auna da tausayin ta yanaji kamar ciwon jikinta yadawo garesa cikin wani yanayi da rauninsa da ke Shirin bayyanar da kansa...

Kyawawan labb'an ta yake kallo wayenda suka bushe suka k'ara yin wani pink,Wanda yakejin wani abu na shiga jikinsa kamar ana Jan sa ko Ina na jikin sa na Amsawa,A hankali yasauke b'oyayyiyar Ajiyar zuciya tare da Lumshe manyan idanunsa masu cike da bacci da damuwa, sannann A hankali yak'ara sunkuyawa tare da Kai hannunsa akan d'an k'aramin Bakinta ya wara sa kad'an sannan ya yakai d'an k'aramin bakinsa akan tattausan lab'bbanta d'aura bakin nasa akan nata inda hakan yasanya sa Lumshe manyan idanunsa Jin taushin da lips d'in ta suke dashi Wanda ya ratsa kwanyarsa da gangar jikinsa kallon kyakkyawar fuskarta yakeyi fes wadda ayanzu ya K'ara kusanta da ita kallonta yakeyi kamar Mai Neman wani Abu atattare da ita cikin shauk'i, hancin su yana gugar na juna,A hankali ya fara hura mata numfashi abakinta inda wani ni'imtaccen k'amshi ya ziyarci bakin sa Wanda ya fito daga bakin ta bayan bud'a d'an k'aramin bakin nata, in a romantic way haka yayi ta sauke mata numfashin domin ceto ranta,sai da yayi minti biyu yana bata numfashinsa sai dai shiru bata motsa ba,ganin haka yasanyasa k'okarin janye d'an k'aramin bakinsa akan nata da niyar ya K'ara Had'awa da wasu da barun kafin yacigaba da bata numfashin,sai dai me abazata yaji ya tsinci tongue din sa acikin bakin ta wani d'and'ano ne Mai gard'i da d'umi Mai Sanya natsuwa yaji ya garwaye bakinsa bayan shigar harshen nasa abakin ta wani dad'i ne ya mamaye sa ya ratsa kwanyar sa da gangar jikinsa inda ya garwaye ilahirin jikinsa Wanda yasanya sa Lumshe manyan idanunsa akaro na biyu da waro su waro Jin bazatar abun,A hankali cikin son yin control din kansa da faruwar wani abun kunyar ya fara k'okarin zare harshen sa,Wanda ahakan ma yake d'an bata numfashin nasa da dubara kamar ance idanunta biyu ko tsoron wani yagansa...
Cikin yardar Ubangiji kuwa ta Nisa da karfi tasauke numfashi kamar an fisgo mata shi A lokacin da yake K'ara kokarin cire harshen sa tare da bata d'an guntun numfashi Wanda Shima dakyar yake fisgosa nasa domin komai ya kwance Masa gabb'an sa sunyi lak'waas yatsinci kansa cikin Rashin kuzari....

Ita kuwa Halee da numfasa Jin wani Abu Mai taushi acikin bakinta da d'an dano yasanyata chafke Tattausan harshen Dr AMMAR tana ta faman tsutsa kamar ta samu lolipop dama ita mayyar zak'i ce azaton ta sweet ne ko wani abun Wani kalar tsutsa takeyi Masa kamar yaron da yadade Bai Sha nonon uwarsa ba,wani kalar french kiss ne Mai tsayawa azuciya take Basa Wanda ke iya Sanya lafiyayyen namiji kasa control din kansa, Ahankali Kuma kamar wadda akace ki saki harshen tasake sa tare da kama soft lips dinsa suma tana basu wani irin tsutsa na musamman Mai tsayawa azuciya....

Shiko Dr .Ammar da yaji abun bazata yayi mutuwar zaune ya Suma ba adadi A hankali sak'on ke Isa a gangar jikinsa Wanda har yafara sanyaya jijiyoyin jikinsa

fitowa rad'o rad'o musamman na fuskar sa, A B'angare D'aya ma ba,a cewa komai Domin motar Dake Parkey agarage har ta fara Neman Agajin fita da ita,har ta fara kunna kanta□cikin wani yanayi yasauke wahalalliyar ajiyar zuciya ta sanadin abun yake ji ajikinsa Wanda yadade baiji ba irin sa ba,wannan abun Bai tab'a faruwa dashi ba wannan shine kiss nashi na farko ko ince kiss na farko da aka Masa Wanda yafitar dashi hayyacinsa batare da ya an karaba,domin yakasa dakatar da abun saboda yadda yakejin komai na ratsa zuciyar sa da gangar jikinsa.,idanunsa yakara Lumshewa wayenda suka d'an rune na chanjin mood d'insa...

Muryar Dr.Aj ce dake gefe tsaye Yana kallon iKon Allah yayi Tari Mai nuna alamar ankarar da Dr Ammar din,duk da daman shi kad'ai ne a gurin Sauran Drs da nurses sunfita Duba wasu pt da aka kawo sunyi mugun car accident,domin yi musu dressing na wounds da wayenda ke buk'atar tiyatar gaggawa (emergency surgery).

A hankali yafara dawowa cikin hankalinsa ganin aika aikar da yake Shirin ya aikata Wanda ya d'ora laifin akansa Wanda har ya fara mayar mata da kiss d'in ta hanyar Shan lips d'in ta nak'asa da zuk'ar saliva din ta masu gargadi da k'amshi.. domin yakasa control d'in kansa.
Jaye labb'ansa yayi acikin bakinta Bayan ya jaye nata da dubara tare da cire harshen sa A hankali....

Itakuwa Halee Ahankali take bud'e idanun nata Jin kamar ancire mata lollipop din ta Mai taushi da gard'i da zak'i acikin yanayin da take Jin sa kamar MAFARKI anata tunanin sai dai bayan ware manyan idanunta da suka d'an fara washewa taci karo da kyakkyawar fuskar Dr.Ammar akusa da tata labb'ansu suna Shirin had'ewa da na juna ido ta waro ganin yanayin da Suke ciki Wanda shi Kam yakasa K'ara yin wani motsin sai ido da yake bin ta dashi,ga Kuma hijab nata agefe Wanda aka cire d'an k'aramin da Babban Wanda yazama na daga ita sai Yar doguwar Riga ta roba Marar nauyi me hannayen vest,Rabin manyan tsayyayun breast dinta duk awaje sun buntsulo daga kwancen da take,Yar k'aramar k'ara tasaki bayan ta gama k'are ma kanta kallo dakuma kyakkyawar fuskar ta Dr.Ammar Wanda kallo d'aya tagane sa...

Kokarin mik'ewa zaune takeyi duk da Rashin k'warin jiki da bata dashi jaaa Baya tayi tare ingiza Dr.Ammar Baya da iya kar karfin ta ,Wanda sai yanzu ma ya lura da yadda breast din nata da suka fito awaje har suna d'an zuzar k'irjin sa na kusancin su. d'an kawar da idanunsa yayi Jin wani shock da yasake shigarsa bayan Wanda yaji alokacin da ta d'aura kyawawan hannayensa akan kirjinsa dan ta tura sa Baya....Wanda ko gizau baiyi ba kamar ta tura dutsen da yafi karfin ta.

A hankali ya fara dawowa dai dai Jin sautin kukan da take rerawa cikin natsuwa k'asa k'asa sai faman Kakkare manyan breast din nata takeyi,da Kuma haushin kasa Ture sa da ta kasa Yi.

Dr.Aj Dake kallonsu ne cikin burgewa da tausayin d'an uwansa, Yake ta faman sakin dariya k'asa k'asa ne ya furta Ka bar Yar mutane ta sake ka nannad'e ta haka daga taimako yayi maganar da yaren India wanda Dr Ammar ne kad'ai zai gane Abunda ya Furta....yakai k'arshen maganar cikin yin Yar k'aramar dariya..

Ganin Dr.Ammar Bai tankama sa ba ne dama baiyi zaton zai tanka Masa ba yasake Furta ka rubuta Musu maganin da zata Sha yanzu kafin mudawo masallaci,ganin Dr.Ammar din Wanda yanzu yad'ago ya juya ma Halee Baya,daga kusancin da ke tsakaninsu sai dai yasamu kansa da kasa yin motsi saima Lumshe manyan idanunsa da yayi masu cike wani kalar yanayi da yake Jin kamar zai zautar dashi.... Ta b'angare d'aya kukan ta yake ji Yana susar zuciyarsa saboda ya tsani Jin kukan mace bare

Kuma Ace nata ne ,duk da yanajin maganar ta Dr.aj ayanzu baijin Yana da bakin Amsa Masa...

A hankali bayan ware manyan idanun nasa Dake Lumshe Bai bari sun had'a ido da Dr Aj d'in ba ya jawo takardar Dake cikin bedside locker na gadon ta yayi prescribing na drugs nata Wanda zata Nema yanzu ya aje mata agefen gadon Batare da ya Furta mata k'ala ba Dan har yanzu Bai koma dai dai ba Dan yanayin da yake ciki idan yayi magana zai iya tonuwa duk da yanajin bazai iya ma Furta komai ba ayanzun..
A hankali ya juya da niyar barin d'akin Yana bin bayan Aj da ya kama hanya..
Wani tunani ya fad'o Masa a Rai,inda da sauri ya juyo ya koma ciki, tunowar da yayi bata da hijab hula ce kad'ai akanta dabata rufe lalllausan gashin ta ba wadda har ta kusa zamewa kasancewar gashin ta Mai shegen tsantsi..

Wani kishi ne yaji ya taso Masa bayan gama tunanin Wanda yake Jin haushin kansa da baizo ba tin farko da ko Dr.Alamin Bai kalle Masa ita haka ba tuno yadda yaga Rabin breast nata asake Kenan duk haka Nurses din maza Da Doctors suka gane Masa ita,cikin b'acin Rai da Jin haushin kansa da kishi da yarufe idanunsa ya taka a hankali cikin izzarsa batare da ya furta komai ba k'aramin hijab din ta dake Dake gefen gadon akan lockern Wanda nurses suka manta su bawa relatives nata saboda yanayin da aka kawo ta na halin mutuwa ko Rai,ya jawo tare da d'ora mata akan jikinta,Halee Dake kuka k'asa k'asa kukan takaicin kallemata jiki da akayi dakuma yanayin da tagansu aciki itada wannan likitan taji an d'ora mata Abu mara nauyi ajiki duk da taji k'amshin turarensa Wanda gaba d'aya jikinta ya kwashesa saboda turaren Mai k'amshin tsiya ne da rik'e jiki,D'an cunno bakin ta tayi gaba cikin son share sa,sai Kuma ta samu kanta da son d'ago kanta Dan ta kallesa. A hankali kuwa ta d'ago Dara daran idanunta masu cike da hawaye ta zuba Masa su eyeslashes nata sun cuccure guri d'aya gwanin burgewa idanunta kuwa sunkara wani kyau na musamman sanadin kwanciyar hawayen da ke ciki,A hankali ya ji tsikar jikinsa na tashi na sanadin kallon da ta ke Masa,kawar da kansa yayi gefe tare da janye nasa idanun Yana Jin kansa Yana d'an Sara Masa tare da wani Sabon yanayin da ke sake shigarsa A hankali ya furtamata in a cool voice da wani irin sauti na musamman yayi Amfani da golden voice tashi " wear it " tare da nuna mata hijab din nata da ya d'ora mata, shuru tayi Masa kamar bataji sa ba duk da hankalinta na kansa tun sauke nata idanun da tayi k'asa, sai da taji yak'ara maimaitawa sannan cikin gunguni ta furta bayan angama kallewa mutun jiki Kuma sai atakura Masa da Sanya hijab bayan an kalle sa takai karshen maganar tana d'aukar hijabin nata k'arami tasanya tare da K'ara cunno d'an k'aramin Bakinta Wanda yajik'e da danshin saliva na Dr.Ammar inda suka k'ara yin wani kyau Mai Jan hankali..

Dr.Ammar Dake jinta sarai Bai tanka mata ba saima Lumshe idanunsa da yayi tare da ware su Yana sakin murmushi azuciyarsa.

Saka hijab din sai yak'ara haskaka kyakkyawar fuskarta kamar ta larabawan ethopia ko na Makkah masu kyau,d'an kallonta yayi akaikaice tundaga sama har k'asa, ganin kamar ana ganin tudun breast dinta da basu da bra cikin hijab din roba din yasanyasa jawo Babbban hijabin nata ash colour Mai kyau,Mik'amata yayi cikin tsuke fuskar sa yana k'ara furta mata Atak'aice " wear this one again "cikin wani irin sauti da Wanda yafi na d'azu Mai nuna alamar tausayi ga Mai maganar da rok'o..
A hankali ta d'ago Jin wani yanayi na shigarta na daban ta masa kallon shek'ek'e tana d'an murgud'a k'aramin Bakinta,duk da Yana kalle da Abunda takeyi Bai nuna akan fuskar sa ba sai murmushin da yake Yi azuciyarsa, sai ma Maida hankalin sa da yayi gurin kallon had'add'en wristwatch nasa Mai kyau da naira ke magana ajikinsa ganin lokacin sallah nagabda wucesa ya Furta A hankali cikin golden voice nasa cikin wani salo da yafi na d'azu "please Halimatu sadiya kisanya d'in nan badanni ba" yakai

k'arshen maganar cikin sauke numfashi tare da fatan ta bi umurninsa Dan bazaiso ya kasance yayi forcing d'in kansa ta hanyar Saka mata hijab din ba domin zai iya Yana so yabi ta ne Ahankali.

K'irjin ta ne ya buga da karfi Jin irin yadda ya Kira Cikakken sunanta cikin sauti Mai dad'i kamar shi ya rad'a mata sunan,sai taji wani iri ajikinta sai taji kamar shine Mai kiranta haka domin bata wani ji irin Abunda takeji aduk lokacin da wani ya Kira Cikakken sunan nata ba,hasalima wani yanayi ta tsinci zuciyar ta aciki wanda bazata iya fassara shi ba...

D'an kallonsa tayi akaikaice tare da tambayar kanta ya akayi yasan Cikakken sunanta badai ya rikesa tun ranar ba,pls d'in da yasake maimaitawa ne ya Sanya ta dole d'aukar hijab d'in ta rafka ajikin karamin,sauk'in ta ma ba lokacin zafi akeba ga Kuma Ac da ke aiki a dakin,Jin kamar yana yin maganar kamar zai Saka kuka ne ko yana cikin damuwa..

Dan kallon ta yayi ganin ko yanzu Bai wani rufe komai ba ajikin ta akan Dan iya ganin tudun su sai dai ba sosai ba,ga Kuma yadda hijab d'in yak'ara fiddo da Asalin kyawunta kunsan kallar ash ko bakin mutun kyau yake Yiwa bare ga farin mutun farin ma Mai kyau..

A hankali yayi ficewarsa d'akin batare da ya Furta mata komai ba duk da yadda yaga ta K'ara cunno baki gaba ga gunguni da takeyi k'asa k'asa Wanda ba dabi'arta bace Amma bata San dalilin da yasa take yiwa wannan likita haka ba batare da Jin bata kyauta ba ko Babba yake agareta..
Yana Jin idanunta na yawo ajikin sa har ya bar d'akin..
Wanda Halee haka kawai da samu kanta da bin bayan sa da idanun ta..

□□□□□□□□Wazai mini typing ✍

Yau Nasan zangaji da comment
..kuma nikam Baki na da goro ba magana□□□□□□

WASAN YANZU AKA FARA✍✍

shin jama,a Ina labarin Dr.malini tamu ta India Nasan wasu har sun manta da ita ko,sannan Ina labarin su Lawisa Mai bleaching?Suma Ina tunanin wasu sun manta su Kam,duka zamu koma layin su in Sha Allah Dan Jin yadda zata kaya.....✍✍✍

Kudai cigaba da bibiyar Alk'alamina,in Sha Allahu zaku nishadantu ku wa'azantu zuciyar ku ta tab'u kuyi Allahwadai da halin wasu,kunemi tsari daga irin halayen wasu...✍

A MAFARKI NASANTA DABAN YAKE□

Like pls and comment

Faiza Almustapha
FIRSTLADY□
Yar lelen Taskira □ □

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG
heart touching story

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*

https://whatsapp.com/channel/0029VaZmQcv4yltXZ8zJiD3y

Idan kina buk'atar dagafarko kuyi joining channel Dita□□□

https://chat.whatsapp.com/H60CWiGISVFKEFT6NedEUw

Sabon update acikin group□□□□

□A MAFARKI NASANTA□
I know her in my dreams
By
Pha'eezah Almustapha
Daga Alkalamin✍✍
□Fa'eeh BG□

Dedicated to my lovely sis lailat Almustapha Murai□

□First lady□

_Yar lelen Taskira _ ---
TASKIRA WRITER'S FORUM
□T. W. F□

Rubutu Baiwace Ga Wanda Allah Ya Baiwa Da Hikimar Mu Muke Alfahari

TASKIRA ASIRIN MARUBUTA□
_____

بسم الله الرحمن الرحيم...□□

((صل الله عليه وسلم) يارسول الله ابي وامي فيدك، □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

Free□

EPISODE1
PAGE58

TYPING□□□

follow me please on
@Arewabooks
@Faizatou

Wattpad
@Fai'zaMurai

Facebook&instagram
@Pha'eezah Almustapha

♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠♠

Bayan fitar sa ne tasauke ajiyar zuciya tare da Lumshe manyan golden eyes nata tare yiwa kanta tambayoyi masu yawa wayenda ko ita tasan cewa bata da Mai bata Amsar su,tambayar zuciyar ta tayi shin me zai Sanya ta dole Saka hijab har biyu,dalilin sa take son ganowa duk iya yin ta takasa wani tunani ne ya shigo zuciyar ta kamar an cillo sa sai dai take ta watsar da tunanin duk da yanayin yazauna mata azuciya musamman yadda yake mata wani irin kallo alokacin da ya ke bata umurnin Sanya hijab d'in...

Kawar da tunanin tayi ta hanyar tunano da Dr.yusuf d'in ta yadda yake nuna mata k'auna Mai tsafta,wadda take ji baza ta iya rabuwa dashi ba komai rintsi.nace hmmm Ysuf namu bawan Allah.....

K'ara tunano yadda ya Kira sunanta yayi,sai da jikinta yayi tsam tuno yadda yafitar da sautin cikin wani salo na daban..

D'an shiru tayi tare yin wani tunanin zucin da magana da zuciyarta akan yadda akayi sunanta yazauna haka abakinsa ' tun ranar kenan yarik'e sunan ta haka duk da tarin patient da ya yi attendig aranar wani sanyi ne ya mamaye ta na Rashin Dalili Wanda har d'an murmushi tasaki batare da ta San da fitowar sa ba,
Kamar ance ta juya kan bed site locker Dake anan kusa da gadon ta hango file d'inta d'auke da sunan ta an rubuta Halimatu sadiya Umar ajikinsa,wani haushi ne taji ya kamata naganin Ashe ma anan yadau sunan yanzu cunno d'an k'aramin bakin ta tayi kamar Yana kusa da ita tare da b'ata beautiful face dinta wanda yak'ara mata kyau...
Sallamar Khady ce da tashigo bayan nurses sun sanar mata da dawowar ta councious,shi ya katse mata d'an tunanin d'an yanayin da take ciki da tunanin ta,A hankali taji taji damuwar da take ciki ta dawo mata sabuwa fal ganin Khady da tashigo yanzun hawaye ta tashare masu zafi tanajin zafin Rashin iyayen nata akusa da ita da bata San ko suwaye ba,Wanda sai ayanzu komai yadawo mata sabo.kukanta tacigaba da rairawa Mai tsuma zuciya A hankali ciwon kan ta ke dawowa mata sabo fall bisa ga d'azu da ta tashi kamar anyaye mata shi,Dan ko doguwar magana bata Jin zata iyayi yadda kan nata ke Sara mata kamar zai rabe gida biyu,Khady Dake kallon ta cikin tausayi ta fara lallashinta,har ta fara yin shiru tadaina kukan,nagodewa Allah da ya yasanya ta furta Alhamdulillah da kika rayu kikasance tare damu,na tsorata Matuk'a Halee ta Furta ma Halee cikin farin ciki Kuma ta rungume ta tare da share guntun hawayen ta da ya zubo tana tuno yadda suka kawo Halee d'in Rai hannun Allah.

Sallamar Dr.yusuf ce da Khady ta Kira ta sanar dashi ta katse Khady daga maganar da take niyyar K'ara furtawa Halee,A Hankali Halee ta d'ago kyakkyawar fuskar ta ta Kai Duba iZuwa ga masoyin nata cikin k'auna,a in da yake atsaye ta kafe sa da manyan idanunta da suka jik'e da ruwan hawaye,sai hawaye shaaaa kamar an bud'e famfo,kansa ya girgiza mata Alamar rarrashi cikin kaunar ta da begenta da soyayyar ta,har ya Tako Gaban gadon nata akusa da ita yajawo kujera yazauna cikin sanyin murya da yanayin da muwa ya Furta luv kiyi shiru kidaina wannan kukan kinji, shiyake K'ara Sanya Miki ciwon Kai,kiyi hak'uri komai zai wuce,Kuma in Sha Allah zai Bayyanar Miki da ahalinki,akullum Ina yimaki Addu,a Kuma inada yak'inin Karb'ab'iya ce in sha Allah,domin yasan damuwar ta ayanzun Bai wuce ta gana da iyayen ta ba.

Handkerchief d'in sa pink colour Mai k'amshin turarensa Mai dad'i ya Mik'amata Yana Furta "pls luv wipe your tears suna k'ona mini Rai....

A B'angaren Dr.Ammar kuwa tun lokacin da yabar d'akin nata ya zarce sai masallaci ko da ya Isa an kusa gama sallar la,asar d'in da lokacin ta yayi,Raka'at biyu kad'ai yasamu,Bayan gama sallar ne suka jero shida Dr.Aj Dake zaune gefe Yana zaman jiransa, Ajere Suke tafiyar gwanin burgewa mata masu jini ajika gwaraza Kuma kyawawan likitota masu rik'e da Norah specialist hospital,haka suke tafiyar su cikin natsuwa musamman Dr Ammar da ke Jin Rashin kuzari ajikinsa Wanda Dama haka yake tafiyar ma yadda kasan wata mace,Har suka gota Baba Adee dukkanin su Babu Wanda ya lura dashi,Anasa B'angaren yagansu sai dai Bai wani tantance su ba ko amatsayin likitota sai dai daganin yanayin shigarsu yasan Suma likitota ne na wannan Asibitin..

Tafiya sukeyi Ahankali har suka shige cikin Asibitin ...

Dr.aj ne ke Jan sa cikin wasa da mugunta yake Furta waini yau surukin ka na koma ne naga kana ta wani d'addauke mini mini Kai kamar kana Jin kunya ta,ya akayi ne...yakai k'arshen maganar Yana sakin dariya k'asa,Yana k'ara Furta nifa bari in fad'a Maka ad'azun nan ido na rufe Suke makanta ta same ni Banga komai ba in ma zaka ware ne ka ware yak'ara sakin wata dariyar k'eta...

K'aramin tsaki Dr.Da ke sauraren sa yayi Biris dashi yaja cikin Kara tsuke kyakkyawar fuskarsa....

Dr.Aj kuwa Cikin wata dariyar da ta taso Masa bayan Kara tunano abin da idonsa yagane Masa d'azun ne ya Furtawa adai dai lokacin da suka office din na Dr.Ammar," wai dama dude haka Kake da jaraba bansani ba,kasamu Yar mutane mutane duk ka tsotse mata Baki,duk da wani kallo da Dr.Ammar yayi Masa a yanzu Bai hanasa K'arasa maganar Saba..
Babu ko kunya, kenan da yanzu ban Maka Signal ba daka zarce yakai k'arshen magaanar tasa Yana sakin murmushi Mai had'e da dariyar k'eta ganin irin kallon da Dr Ammar ya jefo Masa...

Dr.Ammar da har yazauna ne cikin Jin haushin Dr Aj ya Furta "fitar mun a office idan har surutu yasa kabiyo ni office D'ina,Murmushi Dr.Aj yayi Yana Furta karka damu yanzu zan bar nan, Amma meyasmu masu muryarka,wani banzan kallo Dr Ammar yakara cillo Masa,shikuwa dariyar k'eta yasaki Yana Furta ok ni bari inje in k'ara Duba patient d'in mu da jiki yakai k'arshen maganar Yana sakin murmushin k'eta tare da ficewa daga office din,domin yasan dole zai biyo sa in ya fahimci inda zaije in ya fahimci wace patient yake nufi.

A hankali Ammar Dake zaune Yana recalling yanayin su da kasance ad'azu shida Halee,idanunsa ne suka k'ara hasko Masa kyawawan breast nata da Suke atsaye cur gwanin burgewa wayen da yayi ido biyu dasu ad'azu,kansa ne ya Sara Masa inda Ahankali ya Lumshe manyan idanunsa Dake Ad'an rikid'e cikin wani yanayi tare dafe kansa,Yana k'ara tuno moment din nasu Wanda yakusa zautar dashi..

A hankali Kuma maganar Da Aj yamasa bayan sun fito masallaci tadawo Masa inda ya furtamasa dude kar dai ace kishin yarinyar nan kakeyi,ganin Bai tanka Masa ba, yacigaba da magana "idan ba haka ba meyasa ka tilasta mata sanya hijab, kenan kana gudun wani yaga Abunda ka Gani ne atare da ita,ni naga zaka b'ata mini lokaci ne shiyasa na fitowa ta nabarka har ka gama taka kalar soyayyar,Amma kasani cewa

akwai yak'i agaban ka,inda Aj yayi Masa wannan maganar ne afarko kafin sauran zolayar ta biyo Baya ganin kamar Yana Jin kunyar kallonsa ma bare magana dashi...

Gaban sa ne yaji ya fad'i tare da Tausayin kansa bayan tunano da Dr yusuf Wanda yake Shirin yimasa shamaki da Halee "A hankali ya Furta Afili,"Kenan wannan abun da nake ji akan ta da tarayyarta Dr janyau shine kishin,kenan Yana son Halee yake Yi da gaske kamar yadda yake k'okarin yak'ar zuciyar sa tun farkon yin ido biyu da ita...

A hankali yad'aukar wa kansa Alwashi sai ya Nemo soyayyar ta Tako wane irin Halee..

Niko nace wahala,mukam dai mun Riga munyi gaba□□

Sai yakasa Dr.yusuf bisa tire,wani kishine yaji yak'ara taso Masa amak'oshi Wanda take idanunsa suka k'ara rinewa inda zuciyarsa ta ayyana Masa yanzu haka Yusuf na tare da ita Kuma tacire hijab d'in Dan yaga bata Jin magana Halee d'in,sai kuma maganar Dr.Aj ta fad'o Masa arai na pt din mu da yafurta,kenan Shima gurinta ya tafi,..Lumshe manyan idanunsa yayi ganin wani rainin hankali na Aj me zai kaishi gurin ta Dan iyayi sanin sa Dai yabata maganunnukan da take buk'ata bare yace magani zai je ya rubuta mata,shiko Aj tausayin yarinyar yakeji shiyasa yake iyakar kokarin sa na Ganin yabata kulawa koba matsayin sa na Doctor ba.

A hankali ya fito daga office din nasa kamar Wanda ake jaaa baiyi tsinke ko Ina ba sai ad'akin da take cikin emergency d'in Ahankali ya tura k'ofar wadda bata Ida rufewa ba bayan Baba Adee yafice zuwa bungud'u saboda maraice da ta gabato hanya Babu kyau,yabarwa Khady ta kula da Halee tayi jinyar ta kasancewar anyi Admission nata Anan,inda Dr yusuf yace yabar komai a hannunsa...

K'aramar sallama yayi wadda idan baka saurara da kyau ba bazakaji komai ba,Dr .Alamin da Dr .Yusuf ne suka Amsa Sallamar,Banda khady Dake gabatar da sallar la,asar wadda lokacinta yake Neman ficewa...

Itakuwa Halee tashiga toilet domin ta watsa ruwa ta kuma d'auro alwallah Wanda bata da k'arfin jiki sai da taimakon Khady tasamu ta mik'e ta shigela toilet d'in.

Ahankali sauke manyan idanunsa a inda yabar ta kan gadon ga sai dai wayam yagani Babu ta agurin sai k'aton hijab nata da ke aje akan gadon da ta cire Wanda yasanyata sanyawa,da tacire kafin ta shiga toilet,Wata Yar matashiyar kawai yagani zaune akan sallaya wadda take d'an yanayi da Halee d'in Wanda yake tunanin k'anwarta ce ko itace yayarta tana ta Addu,o,, i bayan gama sallar..
Ido suka Had'a da Dr.yusuf da yarasa dalilin da yasa yakejin matsanancin kishin Halee aduk lokacin da Dr.Ammar ya wanzu akusa da Haleensa

A b'angaren Dr Ammar kuwa wani ma mak'ok'on bak'in ciki ne yake taso Masa na mugun kishin Dake cin zuciyarsa musamman Ganin Dr.yusuf Akusa da gadon na Halee da kuma hijab nata da yagani akan gadon Wanda yake da yak'inin akusa dashi tacire sa,idanunsa ne yaji suna Neman rufe Masa kan yadda kansa ya Sara Amma yayi jarumta yashanye dukkanin Abunda yake ji na taso Masa....A hankali yadauke manyan idanunsa da ya dorawa dr.yusuf Wanda Suke Yiwa junansu kallon kallo.

Dr.Aj Dake zaune Shima achan gefe kan wata kujerar Yana pressing phone d'in sa,Yana chat da Nisa ne,tun lokacin da Dr Ammar d'in yashigo ya kallesa yacigaba da chat din sa bayan Karb'a Masa Sallamar sa tare da yin murmushin azuciyar sa Yana Furta Nasan arina..

Girgiza kansa yayi bayyan ganin irin kallon da Dr.Ammar din keyiwa Dr.yusuf na kishi,Tausayin d'an uwan nasa ne ya K'ara ka Masa na ganin irin tarkon da ya afkawa Mai wuyar fitowa fad'awa soyayyar Wanda ya da Wanda yake so,so maso wani kenan, domin ko yau d'in ma ya K'ara tabbbatar da irin soyayyar Dake tsakanin Halee da Dr yusuf..

A Hankali Bayan tayi wanka ta mayar da doguwar rigar da ta cire duk da tanajin k'yank'yamin kayan na Rashin zab'i,wayenda take Jin kamar sun rik'e k'amshin Asibitin Wanda ita kuma bata Jin dad'in sa.....tunda basu zo mata da kayan ba tafiyar bata shiri ba ce.
Alwallah tad'auro tare da rike k'aramin hijabin ta a hannu da hular ta,A hankali take takawa har ta Isa k'ofar fita toilet d'in...
Murd'a handle d'in k'ofar tayi A hankali kuwa k'ofar ta bud'e inda tasanyo kyakkyawar k'afarta har ta Ida fitowa da jikinta gaba d'aya kasancewar bata da wani karfin jiki,k'ofar tajawo Ahankali,tana gyara dogon lallausan gashin ta Dake zube agadon bayanta sai faman rufe mata fuska yakeyi tana kokawa dashi Dan tasamu tayi Masa d'aurin guda, A hankali cikin Yar damuwa ta Tako inda Khady ke zaune kan sallaya d'in cikin yanayin sanyin ta da shagwab'a ta Furta wa Khady pls kamamun wannan abun tare da yin k'asa tana bawa Khady kan nata,Khady d'an murmushi tayi tana Furta shi gashin shine wannan abun takai karshen maganar tana sakin murmushi...

"Nidai ki d'aure mini ni wallahi duk ya takuramun takai karshen maganar cikin shagwab'a da son yin kuka Dan iyakar gaskiyarta gashin na takurata...cikin dariya Khady ta Furta ai kece in na Miki dubara na d'aure Miki sai ki warware sa wai zafi ke kinfison kullum kalaba kalabar da bata ma Dadewa akanki take ba warwarewa har gara ma kitso Yana sati ga kitson ma baso kike yi...takai karshen maganar tana kama uban gashin na Halee Mai tsawo da yawa ga taushi kamar kan jarirai..

Tana gamawa ta Furtawa Halee Nad'aure Miki Norah Kuma kika sake warware sa nikam zuba Miki ido zanyi takai karshen maganar tana murmushi Mai had'e da dariya..tafara kiranta da Norah ne ayanzu tun da taji cewa shine Asalin lak'anin ta,Halee Dake duk'e da kanta ta d'ago dasauri Jin sunan da Khady ta kirata dashi wai Norah,sai yanzu ma ta k'ara tunano da labarin da Baba Adee yabasu inda ya shaida musu lak'aninta Norah ne, Ahankali Kuma tak'ara tunano da furucin da likitan nan ya tab'a Yi a gareta cikin sauti mara hayaniya wanda tana tabbacin ita kad'ai tajisa alokacin Dan yadda yayi furucin daban ne,to me hakan yake nufi yasanta ne ko me ne ne da har ya iya Ambaton ta da sunan da ko ita kanta ba ta San tana dashi ba sai yanzu, kasancewar tun tashin su Khady ta rad'a mata Halee.A hankali ta mik'e tana yiwa Khady godiya cikin turo bakinta na furucin Khady na d'azu akan bazata koma d'aure mata gashin ba..

Cikin kawar da tunanin da ke son shigo mata akwakwalwa Wanda ita kanta bata San ma,aunin da zata kaishi ba,sai dai tabbas abun yatsaya mata arai a Ina yasan wannan sunan ne.likitan yanayin wasu abubuwan Dake bata mamaki Suke Kuma d'aure mata Kai yau had'uwarsu ta biyu kenan Amma abubuwa da Dama akansa suna mata zagaye azuciya tarasa a inda yakamata ta d'aura Al amarin sa zuciyarta ma, zuciyar ta kan buga a duk sanda ta tuno da shi Wanda tarasa dalilin faruwar hakan duk da haushin sa da take ji with no reason d'an Lumshe idanun ta Tayi sannan Ahankali ta mik'e tsaye bayan Khady ta Sanya mata hularta da ta bata..

Tare da barin wannan tunanin Azuciyarta kasancewar Al amarin na Neman shigar da ita wani yanayin da bata San kansa ba.

Hijab d'inta take k'ok'arin Sanyawa Bayan ta mik'e tsaye,kamar ance takalli sashen da yake tsaye a inda Aj ya ke zaune kusa da kujerar da yad'aga, Wanda ya fice Dan Yin waya da masoyiyarsa,sak'ak'e tayi tana kallon sa da hijab A hannunta ...

Tsaye yake ya rungume hannayensa ak'irji manyan idanunsa Dake binta da kallo wayenda sun ka k'ara rinewa sunyi jaa kamar Wanda yasha barkono tunda ta fito daga toilet d'in.

Kallon junansu sukeyi itada shi ita tana Masa kallon mamaki duk da ba wani abun mamaki bane kasancewar sa likita Mai Kuma kula da lafiyarta,kallo ne Mai cike da shauk'in k'auna da mugun kishi Dr.Amma ke binta dashi ido cikin....

A hankali yajanye nasa idanun ta hanyar D'an Lumshe idanunsa tare da ware su Yana kawar da kansa gefe,tare da sauke boyayyiyar ajiyar zuciya wadda tun d'azu yake son sauketa sai dai Bai samu damar fitar da ita yadda yake Jin zuciyar kamar zatayi bindiga tin bayan fitowar tata.

Runtse manyan idanunsa yak'ara Yi da da suka k'ara hasko Masa kyakkyawar surarta acikin doguwar rigar Dake jikinta ta roba duk da bata fito da surar jikin ta ba,kasancewar ta ba matsatstsiya bace,jikinta kamar anzanata shape din ta ya Bayyana K'ara K'ara inda shi yake ganin rigar ta matse ta Wanda alokacin dukkanin gab'b'ansa sai da suka Amsa Wanda sanadin hakanne ya Sanya sa kasa iya d'auke idanunsa akanta...ta truck shi kansa da ya kasa dauke nasa idanun akanta,kenan yakalle Masa ita,shine Abunda ya rikid'ar da idanusa Wanda wannan abun duka zuciyarsa ce ke sarrafa gangar jikinsa har ta iya fallasar da abun da ke cikin zuciyarsa a cikin manyan idanunsa masu kyau da Kaifi...

A hankali kuma yake ta nana ta sunan NORAH da yaji Khady ta Furta mata.kenan itace ta mafarkinsa kamar yadda zuciyar sa ta shaida Masa,kansa ya girgiza A hankali no ya Furta aransa ba ita bace Dan a lokacin da ya Furta sunan,batayi response ba Wanda zai nuna masa ita ce mamallakiyar sunan sai dai ko Mai kama da ita ce ba ita d'ince ba Wanda har yanzu hakan na tayar Masa da hankali Baya son yaji labariin ko yaga wani abun da zai nuna masa ba ita din ce ba,duk da yana da tabbacin taji furucin sunan...

A hankali ya kawar da tunanin sa Yana d'an gyara tsayuwarsa tare da Sanya hannayen sa Aljihunsa Wanda hakan sai yak'ara bayyanar da mazan takarsa da tsagwaron kyawo da Allah ya zuba Masa,kamar irin had'add'un black Americans din nan.

A hankali Halee da ta kawar da na idanun cikin wani yanayi da ta tsinci kanta ta d'an kallon da sukayi wa juna Wanda Babu abun da tahango acikin idanunsa Yana yawo face wani Al amari da bazata iya fassara shi ba ayanzu kasancewar kanta da yake akulle,ganin ya janye nasa idanun masu d'aure jijiyoyin jiki wayenda taga sun sauya mata ba ganin farko ba,Wanda yanzu ta hango damuwa da tashin hankali acikinsu tunanin ta kad'ai me yake damunsa ayanzu chanjin idanunsa nasa ya bawa zuciyar ta wani rauni wanda take Jin zafin abun har cikin ranta,domin tasan kome ne ne damuwa ce Babba... Duk da abun da zuciyar ta ke lissafo mata..

hijab d'in tasanya tana sauke wata b'oyayyiyar Ajiyar zuciya, A Ahankali Kuma tajuya Dan d'aukar Babban hijabinta,sai dai cin karo da Wanda bata tsammane Saba yasa tad'an dakatawa.

Dr.yusuf ne zaune akujerar Da yake Kai tun d'azu ya kafe ta da idanunsa wanyenda suka fara chanza launin farin su zuwa jaa na kishin kallon da yaga Dr.Ammar da Halee suna yiwa junansu,sauke idanunta tayi k'asa tana Furtawa acikin zuciyarta kenan yadawo daga fitar da sukayi shida Baba Adee, A hankali cikin d'an Jin tausayin sa haka kawai da yasaukar mata,Dan ta tabbatar da yaga irin kallon da likitan nan nata kemata, A hankali tacigaba da d'an takawa har ta Isa inda yake,A hankali cikin sanyin da yazame mata jiki ya had'u da yanayin Rashi lafiyarta da Kuma wani sirri da zuciyar ta take k'okarin b'oyewa agareta cikin shakku da tsoro...

Ta Furta "Yaya Yusuf mik'o min hijab D'ina "takai karshen maganar tare da k'awata fuskarta da murmushi,Wanda tayi hakanne Dan kawar Masa da wani sashe na damuwar da tafara bayyana a fuskarsa,sauke idanunsa yayi Yana sauke ajiyar azuciya bawan Allah, Sai Kuma yasanya hannu yad'auki hijab d'in Dake kusa dashi Yana Mik'amata,cikin sanyayayen murmushin data San Yana matuk'ar k'auna ta Furta Masa nagode mijina ta Furta cikin Yar k'aramar muryar ta wadda tak'ara yin k'asa da ita wadda shi kad'ai zaiji,A hankali yaji zuciyarsa tana wankewa daga kishin da yake ji Wanda ya fara taso Masa sanadin murmushin data Masa da kuma furucin mijina da ta Kira..
Yana Sakin murmushin da Bai shiryawa Yi ba, Halee ba ta k'ara kula dashi ba ganin yadawo cikin natsuwarsa yasanyata juyawa tana Hawa kan sallayar batare da sake kallon sashen da Dr Ammar yake ba,Wanda Take Jin manyan idanunsa masu Kaifi na yawo ajikin ta Kuma suna tasiri azuciyar ta shiyasa ma takasa kalon inda yake ayanzun domin bazata jura ba,Kuma bazata so Dr.Yusuf yak'ara shiga wata damuwar ba.

Dr.Ammar Dake tsaye kamar wani soja hannayensa cikin Aljihu,ya d'an kallo sashen da Khady take wadda ke tambayar kanta wannan had'add'en gayen wanene kuma me yake Jira gashi dai yazo yayi tsaye yakasa Furta komai sai wani abu da ta hango tattare da shi akan Yar uwarta, hankali ta karanto sunan sa Dake rubuce akan tag din Dake mak'ale da d'an k'aramin aljihun rigar sa Mai kyau kamar na gold Wanda ba koyaushe yake make'ala Saba, inda taga an rubuta Dr.AA lokacin da yake Furta mata cikin Muryar sa Dake nuna..
B'acin ran da yake ciki da mugun kishin da ke nukurkursar zuciyarsa,ga Kuma wani sanyi da jikinsa yayi lokaci d'aya..

"Yar uwar kice patient d'in?Kai tad'aga Masa tare da Furta eh, tare da kallonsa ganin Yana fitar da maganar cikin wani salo kamar Baya son yin maganar cikin yanga da ciccijewa...

Cigaba da magana yayi tasame sa a office din sa yanzu kan case d'in Halee game da Abunda yagani a na'ura d'azu alokacin da bata cikin hayyaacin ta,ficewa yayi daga d'akin Bai k'ara ko kallon inda Take ba ko Dr.yusuf d'in,,cikin wani mugun b'acin Rai yafice da sassarfarsa har cikin ransa Yana ji kamar zuciyarsa zatayi bindiga kan furucin da Halee ta Furtawa Dr.yusuf din ta mijina Kuma cikin wani sauti Mai ratsa jiki,da sautin murmushin ta da yaji Masa,Wanda yake ganin kamar da gayya tayi Masa,kishine dan k'are da zuciyar sa,da tausayin kansa akan soyayyar so maso wani da ya fad'a,har ya Isa office din sa Bai San ya akayi yakai ba saboda yadda zuciyar sa ke cigaba da azalzala akan yanayin da yagansu,yana ji kamar ya kuwwata,duk ya tuno da Kalmar mijina;bugun zuciyarsa na linkuwa da fargar da tashige sa lokaci d'aya Wanda ya hadda sa Masa sanyin jiki....

Zaunawa yayi akan kujerar tasa yana ta faman sauke numfashi Mai had'e da ajiyar zuciya alokaci guda cikin wani yanayi tare da Lumshe idanunsa da suke arikid'e har yanzu.....

Sallamar Khady ce ta sanyasa ahankali Amsa mata cikin Sauti mara k'ara Wanda ke nuna yanayin da yake ciki na damuwa da kishin da ke cin sa..

Zama Khady tayi ad'ai daga cikin biyu Dake fuskantar Dr.Ammar din wayenda ke Gaban k'aton table din sa.
Ahankali ya k'aka'lo d'an murmushi ya d'aura akan fuskarsa cikin son b'oye Abunda ke zuciyarsa...

Sai dai ya Riga ya makaro domin Khady akwai saurin fahimtar irin wayen nan abubuwan wayenda da ma ta gansu zahiri ba bad'ini ba..sai dai ayanzu wani Abun mamaki take Gani agare sa da Haleen ta domin kuwa kama ta hango a tsakaninsu kamar Kuma ta fito Fili wadda sai kasan d'ayansu sosai zaka iya hangota Wanda sai da gabanta ya fad'i,k'are Masa kallo take k'arayi Dan tabbatar da kamar shi da Halee d'in akaro na biyu..
Ahankali ta tsinkayi muryar sa Yana Furta "Khadija bana son kallo" cikin d'an murmushi Khady da mamakin Jin sunan ta rad'am abakinsa ta Furta Afwan Dr.
Tare da gano inda yarik'e sunan ta,Wanda yaji Halee ta Furta ne achan emergency room d'in har yarik'e...

Aranta kuwa kunya ce ta kamata ganin ya gane kallon tsaf da take Masa.

A hankali taji ya K'ara furta "Yakama ta ku k'ara kiyaye duk wani Abu Wanda zai b'ata ma Norah Rai,domin dabadan Allah ya kiyaye Kun kawo ta akan lokaci ba da mun rasata,Amma cikin iKon Allah da taimakon magungunan da muka bata munyi nasara,da ba haka ba bamu san yadda za,a Yi ba,ayanzu zan k'ara rubuta mata wasu maganunnukan wayenda zasu taimakawa k'wak'walwarta wajen iya controllong duk wani damuwar da zata bijiro mata,sannan ki k'ara sanarwa da Baba ai tare kuke dashi Koh,Kai tad'aga Masa cikin d'an sark'ak'iyar da zuciyar ta ke ciki, cigaba da magana yayi kisanar masa sati Mai zuwa zaku dawo domin ayi mata aikin,a yau za'ayi mata Booking,ranar laraba zaku dawo Alhamis za,a shiga da ita aiki kasancewar ba'anan garin kuke ba,da sai ince ranar alhamis ku dawo da wuri...

Numfashi yasauke a hankali na doguwar maganar da yayi cikin wani yanayi tare da bawa zuciyarsa k'warin gwuiwa..

Prescribe sheet ya mik'a wa Khady,godiya tayi Masa tare da karb'ar takardar maganunnukan sannan ta fice daga office d'in da tunani kala kala Azuciyarta...

Tofa jama,a yakuka ji wannan page...□mudai Dr.yusuf's team Bai muna dadi ba wannan shiga sharu ba shanu har Ina□ gaskiya da sake 😭😭🥹□bazamu lamun ta ba..□□□□

Su Maryam masu Jira adawo masallaci mundawo□□□

Ke Kuma khady me kika hasaso nuna ne,me ne ya kulle Miki Kai...
Ni ma tabbas inason ji,mu had'u a next page,may be kusamu anjima sai dai ban muku Alkawari ba,saboda Shekaranjiya nayi muku bansamu cikawa ba kunsan d'an Adam ajizi..✍✍□□

Maaman Abba
Ayeesha Abdullahi
Babylour
Deenarht
Maryam
Beauty.hafsat Umar
Nusaiba
Hamamerh

Comment din ku na zazafa ni ta yadda Baku tsammani kamar ma shine sugan labarin mu,Ina alfahari da ku sosai Allah ya bar k'auna

Kema maman Usman Ina godiya Ina ganin stickers naki na godiya da irin k'aunar da kike nuna mini,Ina alfahari Dake

Ayi comment da yawa yawan page yak'aru

Like,share pls
Faiza Almustapha
FIRSTLADY
Yar lelen Taskira

Daga Alk'alamin ✍✍✍
FA'EE BG
heart touching story
love competition

Neman K'arin bayani sai ku tuntub'e ni ta wannan lambar.*08069059746*